MATAR MUTUM BOOK 1

LABARI/RUBUTAWA

MARYAM FAROUK (UMMU-MAHIR)

Arewabooks@Maryamfarouk01

Wattpad@MaryamahMrsAm

Telegram @08142548705

Ko a tuntubeni a WhatsApp kan 07061838488

Littafin Matar Mutum na kudi ne, ki biya 500 ki karanta cikin salama

0709290797

Access bank

Maryam farouk Umar

NAGODE

Page 1

"Wallahi Allah shine shaidata bani da masaniya akan yanda akayi kudin nan suka bata. Kowa a nan ya gani ga lissafi nan na duk abinda ya  shigo kuma ya fita saga duka companies dinmu tun farkon shekara zuwa yanzu. Idan har duka lissafin da accountants dinmu suka kawo daidai ne tayaya za'ayi ace yanzu an sake lissafi an rasa wasu kudade? Nidai ban ci ba sedai a sake lissafi tun daga qasa ta yuwu a nan aka samu kuskuren lissafi" AMINU BECHI ya fada cikin tsananin tashin hankali. Sati biyu kenan da al'amura suka rikice a BECHI GROUP OF COMPANY lokacin lissafin shekara yayi bayan daya gama hada komai a matsayinsa na AG lissafi yasha banban da abinda aka bashi a rubuce da kuma tsurar kudi da suke a qasa inda aka samu rarar naira na gugan naira har Miliyan dubu biyu da dari biyar (2.5Billion) wadda bayan bashi damar yayi bincike da MD da kuma Chairman sukayi yauce ranar da aka taru duk wani daya isa a company domin jin ta yanda akayi aka haihu a ragaya.

Alhaji ZAKARIYYAH BECHI dake ta jujjuyawa a kujerarsa yana wani miskilin murmushi da babu wanda ya tantance kona menene ya kalle shi yace

"To Aminu kaida kanka kace dukka lissafin da aka gabatar maka daidai suke kuma baka karba ka saka hannu har seka bincika komai ka tabbatar da haka yake. Sannan a iya saninmu ku biyu kuke da access da central account dinmu dakai da Chairman duk wani wanda ze shigar ko fitar da kudi bayan ku biyun seya samu

approval a gurinku to tayaya kake zaton zamu yarda idan kudi ya bata kuma kace mana bakada masaniya akai kenan Chairman ne da kanshi ya kwashi kudaden ko kuma me kake nufi?"

Aminu ya kalli Chairman din da tun zamansu bece komai ba ya tallabe haba da hannaye biyu yana bin duk wani da yayi magana a cikin su da kallo, Dattijo ne da a qalla zeyi shekaru 70 zuwa sama, dukda a zaune yake amma kana kallonsa zaka san Zabgegen mutum ne Jindadin rayuwa yasa har yanzun yake da sauran kwarinsa. Aminu ya hadiye yawu muqut saboda yanayin fuskar Chairman daya gani, bashi da yawan fara'a daman amma kuma yanayinsa na yau ya banbanta da kullum kana gani kasan zuciyarsa a kusa take koda yake ai dole, batun kudi akeyi fa, kudin daya qare rayuwarsa yana nemansu ya tara ace lokaci daya wasu su ringayi masa zari daidai dole hankalinsa ya tashi.

Seda ya daidaita nutsuwarsa kafin ya kalli MD dake jiran jin ta bakinsa yace

"Nidai na gama magana, ban ci kudin nan ba ban kuma san wanda ya dauke su ba. Amma dai kamar yanda nace kowanne gida (sector) su sake turo mana da lissafinsu na shekara a qaramun lokaci zan sake bin komai daki daki zan zauna da duka Bank Managers dinmu in Allah ya yarda za'a gano duk ma inda kudin suka shiga" ya qarasa muryarsa na rawa kuma cike da roqo da yaqinin Alhajin ya yarda dashi ya bashi wannan damar. Idan ya rasa besab ina ze dosa ba, abu biyu ne dole daya ya faru, dukda kasancewar Dan Chairman na cikinsa a sabgar Company basa kawo wannan relation din, ya sani kodai yayi Aman kudaden nan tas Miliyan dubu biyu da dari biyar wanda ko an siyar dashi da matarsa da yayansa  da abinda ya mallaka baza'a hada wannan kudi ba abu na biyu kuma in wancan be samu ba yasan garqameshi za'a yi a prison still kuma A siyar da duk abinda ya mallaka Company ya rage Asara maganar aikin sa daman tun ranar da kudin sukayi batan dabo ya rubuta resignation letter ya ajiye dan ko be bari ba korar sa za'ayi.

"Maganar wani lokaci ko a sake bincike duk bata taso ba dan a tsayin faruwar abun zuwa yanzu da da wani abu da zakiyi tuni kayishi, just admit it Aminu kai kaci kudaden nan ka dawo dasu baki alaikum base magana tayi tsayi ba" NAZIRU BECHI ya fada yana wani zazzare masa ido

"Nima dai abinda na gani kenan, idan kuma yayi taurin kai Maigirma Chairman ina ganin a barshi da Legal department suyi aikinsu nasan su zasu sna ta yanda zasu tirsasashi yayi aman kudin ko kuma su miqashi inda ya dace"  Alhaji Zakariyya ya qarasa miyar gishiri, cikin Aminu ya kada, ya ringa raba ido tsakanin Alhaji BABANGIDA BECHI da kuma YAKUBU BECHI da yake matsayin mataimakinsa AAG

wanda tun fara taqaddamar kamar ma baya gurin wayarsa yake dannawa kunnensa saqale da Bluetooth tabbacin ba jinsu yakeyi ba hakan yasa ya tsayar da idonsa kan Alhaji Babangida cike da roqon ya saka baki amma seyaga ya saukar da kansa qasa bece komai ba.

Dakin ya sake daukan shiru na wani lokaci kafin cikin murya me cike da Izza irin ta wanda suka ci suka tada kai Chairman, Alhaji AUDU BECHI ya fara magana yana cewa

"Duk naji bayanan ku kuma na duba takaddun da aka rigada aka gabatar mun tuntuni. Account general, ina so daga yanzu zuwa qarfe biyu ka gabatar da takaddar barin aikinka da kanka saboda idan muka koreka zamu bata maka career be zama lallai ka sake samun aiki a wani gurin ba, kudi kuma duk wanda ya dauka yaje dan kansa" yana gama fadar haka ya tsuke bakinsa yana kallonsu daidai.

Aminu ya sauke ajiyar zuciya me nauyi tamkar wanda ya hadiyi kunama, jiki da bakinsa suna rawa ya zame daga kan kujerarsa ya durqushe yana cewa

"Nagode Alhaji, Allah ya qara girma nagode nagode".

Naziru da Zakariyya wanda farkon maganar Alhaji yayi musu dadi, sun dana kuma ta kama suka kalli juna tareda yin signa akan idon Alhaji Babangida dake lura da duk wani motsinsu ya girgiza kai kawai. Bazeyi kaffara ba idan ya rantse cewar shirinsu ne saboda sun nuna baqin ciki qarara da kujerar ta Aminu amma baze saka baki a cikin maganar na domin rayuwar gidansu rayuwa ce irin ta kowa tasa ta fishsheshi shida Yan dakinsu.  Tunda Aminu ya samu wannan matsayi qarara mutane da yawa a gidan suka nuna qyashi da hassada bayan rasuwar Mr Adekunle Balogun wanda shine AG na BECHI GROUP din tun kafuwarsa Alhajin bisa shawarar Legal Department da sukaga cancantar Aminun aka dorashi, shekaru biyu kenan tun kuma hawansa abubuwan da ba'a saba dasu ba suke faruwa amma wannan al'amari shine mafi girma wanda baze yuwu a dauke kai ba.

Cikin zafin ran dake nuna hassada qarara Alhaji Zakariyya yace

"Ranka ya dade (haka suke kiransa muddin sabgar data shafi aiki ce) naji kace yayi resigning kawai banji maganar dawo da kudi ba ko wani hukunci da za'a dauka akansa?"

"Da alama kunnenka ya soma samun matsala ko? To ka tambayi na kusa da kai su maimaita maka abinda nace, maganar wanda ze maye gurbinsa for now Yakub

should take over kafin mu sake zama muga abinda ya dace da ayi ina ganin mun gama abinda ya taramu you can all dismiss" Alhajin ya fada ba tareda ya kalleshi ba. Alhaji Zakariyya ya hadiye yawun takaici ta wani bangare kuma yaji dadin cewar YAKUB BECHI ne zeyi taking over dukda sunso ace anyi confirming nasa ne take as the newa AG amma hakan ma nasarace sunyi nasu Hajiya zata qarasa aikin a gida. Shiya fara miqewa ya kalli Aminu dake harhada takaddun gabansa cikin izgili yace

"Dama anyi gadon farar qafa dole a tsammaci abinda yafi wannan, Allah dai ya sauwaqa ya kuma tsayar iya kanku kar a bata mana sauran iri da halin bera" yana gama fadar hakan ya juya ya fice daga gurin dukkan su kuma sunji abinda ya fada, Da daddaya suka ringa ficewa daga conference room din ya rage Alhaji Audu, Alhaji Abdullahi wanda yake heading bangaren Siminti kuma dane a gurin Alhajin Audun ma'ana dan Yayansa ne da suka hada uba se Mustapha Manzo, shugaban Legal department na rukunin kamfanunuwan Bechi. Alhaji Abdullahi ya kalli Alhaji Audu dayayi shiru da alama yayi nisa a tunani, cikin ladabin da yake masa tun usulan yace

"Gaskiya Baba a iya fahimtata da kuma binciken da nayi bana zargin cewar Aminu yana da saka hannu a cikin batan kudaden nan"

"Nima dai abinda zan fada kenan, nayi amfani da duk wasu measures da muke using gurin gano me laifi banga wasu alamu na rashin gaskiya a tattare dashi ba. Amma abinda yake bani mamaki shine tabbas kudi sun bata amma babu wata alama da za'a iya tracing a ga inda kudin suka tafi tunda ba transfer akayi ba and we don't deal with huge cash here ballantana ace cash aka debe su. Ni dai what I'm thinking is that kudin nan dama babu su, lissafin bogi aka bashi kawai kuma ina ganin matsalar badaga ko ina aka samota ba se daga Oil Sector. Tunda Naziru ya fara heading gurin nan ake samun runton lissafi Mr Obasaki yana yawan kawo mun qorafin idanna sanar maka Alhaji baka daukan wani mataki na sosai and i don't know your reasons for that. Ire iren wadannan abubuwan ya saka mutane da yawa basa mixing Family with business saboda abinda bare zeyi maka ka dauki mataki idan Jininka ne dole ka daga amsa qafa, amma maganar gaskiya idan ana so a ga daidai se an gyara saboda kowa yasan can ne bangaren dayafi kowanne kawo profit idan aka cigaba da irin wannan tafiyar ina tsoron kar wata rana a wayi gari babu uwar kudi ma balle riba" Mustapha Manzo ya fada, yanda yake maganar duk wanda ya saurareshi dakyau ze fahimci jirwaye yakeyiwa Alhajin me kamar wanka. Kai tsaye baya so ya dora alhakin batan kudin akan Naziru tunda bashi da hujja amma yana so Alhajin ya bincika da kansa ya tabbatar.

Alhaji dake sauraronsu a zahiri yana gyada kai amma a badini kanzil bazece yaji daga abinda suke ta babatu akai ba maganar farar qafa da Zakariyya yayi ce take masa yawo a zuciya wasu shudaddun Al'amura da suka faru a baya suka shiga

dawo masa kamar auransa da Mahaifiyar Aminun, abubuwan da suka gidana a tsakani har zuwa rabuwarsu.

"Nidai Baba idan ze yuwu a janye maganar korar Aminu daga company nan, za'a iya suspending nasa na wani lokaci amma Yaron yana da matuqar qoqari kuma ya dace da gurbin da aka sakashi akai" Alhaji Abdullahi ya sakeyin magana se sannan Alhaji Audu ya dubeshi, kallon dansa na cikinsa yakeyiwa Abdullahin saboda shi ya fara riqewa kafin ya samu nasa yayan, haka kuma yana yi masa biyayyar da qalilan daga cikin wadanda ya haifa a cikinsa ne sukeyi masa irinta. Cike da Izzar data zame masa jiki yace

"My decision is final, idan shi Barrister Manzo be sani ba, kai kasan Hadiza ka kuma san dalilin rabuwata da ita dan haka bazan yi ganganci a matsayin kuskure ba" daga haka ya miqe tsaye yana gyara zaman babbar rigarsa datasha wani aiki irin na sarakai.

A baya suka biyo shi duk rayukansu babu dadi har suka shiga Elevator Barrister Manzo yana so ya sake magana amma Alhaji Abdullahi ya hanashi. Tun kafin qofar Elevator ta gama budewa gaba daya suke jin hayaniya, Reception din cike da ma'aikata da sukayi cirko cirko se muryar Naziru dake tashi kamar ana yaqi. Cikin karadi da kwaroroto irin na Mahaifiyarsa yake cewa

"Wlh Babu inda zaka je se ka bude jakar nan mun cajeta, hauka ma akeyi kenan. A kamaka dumu dumu da laifin sata a koreka daga aiki sannan ka lullubo jaka zaka fita bamu duba munga meye a ciki ba salon ka kwashi sirrikan mu ka fitar ka saidawa Yan hamayya ko to baka isa ba" ya fada yana kiciniyar fincikar Bag pack din Aminu daya saka duk wani abu nasa me muhimmaci da yake a tsohon office dinsa tunda an sallameshi daga gurin.

Alh Abdullahi da Barr Manzo suka nufesu da sauri jin abinda yake faruwa, Alhaji Audu kuwa ko a jikinsa ya nufi qofar da zata fitar dashi daga building din. Daf da ze fita kunnuwansa suka jiyo masa wasu mata biyu ma'aikata dake saga gefe suna kallo daya tana cewa

"Nidai Safna da arziqi irin na wadannan mutanen gara talauchi da kwanciyar hankali, su fa basu san abin kunya ba, wlh Chairman dai bewa kansa tanadi na kwarai ba Allah ya baka arziqin zuria amma ka tarwatsasu babu soyayya bare shaquwa a tsakaninsu kowa so yake yaga kasawar dan uwansa yanzu idan baka sani ba wlh ba zaka taba yarda MD Oil and Gas da AG ubansu daya ba dan ko barene beci yayi masa irin wannan tozarcin ba ballantana jininsa."

Dayar tace

"Uhm kedai bari Halisa kinsan su CMD yayan Mowa ne shiyasa suke sharafinsu, bandama AG da MD Agric wa kika gani a yayan nasa yana aiki a nan se yayan yan uwa dana abokanai ragowar kina kallo duk wanda yazo baya zama yake neman hanyar da zata bulle dashi to ko nice wlh ba zan zauna ba Arziqin ubana amma a fifita wasu su zasu amfana ai dai idan Chairman ya sheqa be gyara kan gidansa ba to kuwa kwanciyarsa qalilan ce a kabari dan kullum se an tashe shi yaga tsiyar daya bari a duniya da ransa ma ji yanda suke akan dukiyar inaga an raba gado wani be samu yanda yake tsammani ba" suka tafa hannu suna cewa

"Allah dai ya kyauta.

Alhaji Audu ya daga qafa dakyar ya qarasa ficewa daga gurin bayan ya gama sauraron hirar tasu. Tunanin maganganunsu yakeyi a ransa, ba yau aka fara fada ba ko ya faraji wasu su fada masa akan idonsa wasu a boye suti gulma kamar dai wadannan kuma tun abin baya damunsa yana daukar sa ba a komai ba har ta kawo matsayin da shida kansa ya hangi illar da yayiwa kansa da rayuwar Ahalinsa gaba daya. A lokacin daya dora tubalin ginin sam be hango rashin ingancinsa ba, be hasaso ranar da ze iya ruftawa dashi ba seda lokaci ya qure masa akazo matakin da ko yana so ya gyara mawuyaci ne hakan ta yuwu.

A yanzu da yake cikin Shekara ta Saba'in da uku a duniya yaci ace yana kwance a gida yana hutawa da kuma shirye shiryen tarar da ubangijinsa ta hanyar yawaita tuba da ayyukan Alkhairi amma a maimakon haka tashin hankulan da be san suna wanzuwa ba a baya yanzu suke riskarshi. Bashida kwanciyar hankali a gidansa, tsakanin Matansa koda ace ba dukka kullum ta Allah idan ba safiya ba rana idan ba rana ba Dare se Binta ta tayar da tashin hankalin da ze kwana ya wuni cikin quncin zuciya. Ubangiji yayi masa ni'ima ta Yaya Maza zarata wadanda ya dora buruka da yawa a kansu sedai be gino rayuwar ta sigar da baze cimma mafarkin sa ba ya shuka barna yanzun kuma yana girbinta ne, yayan daya kwallafa rai akan zasu taimake shi a lokacin da qarfinsa ya tashi qarewa sedai sam hakan ta gagara a maimakon nutsuwa a kullum tukuicin tashin hankali yake samu daga garesu wanda shine silar komai ya sani ba laifinsu bane laifukansa na bayane suke farautarsa a yanzun.

Yayi zurfi cikin tunani har besan sun isa gida ba seda Driver sa ya bude masa murfin qofar bangaren da yake. Ya fita ya tsaya yana qarewa Tamfatsetsiyar harabar gidansa kallo ga motoci nan birjik kamar a gurin saida su. Gida ne daya amsa sunan gida wanda ko baka shiga ciki ba zaka iya wassafa tsaruwarsa, Get din gidan me

kama da qofar Gari kansa abin kallo ne ga wasu shuke shuke da akayi a harabar na dogaye da gajerun bishiyoyi da suka qara qawata gurin se manya manyan Street Light jere da Zanqaleliyar Katangar gidan kamar ta mutanen Niger kana gani base an fada maka ba kasan idan dare yayi haske har yawa yakeyiwa Harabar. Gini ne Duplex a tsakiya yana kallo ka idan ka shigo nan ne kuma turakar Alhajin dakuna uku ne a sama da falo a qasan kuma kantamemen falo ne da aka zubawa kujeru saiti uku da bandakin baqi a gefe se kuma wani qarami Daga can gefen wanda fadar tsaruwarsa bata baki ne a nan Alhajin yake saukar baqinsa na Mutunchi Babban Falon kuma na Meeting ne tsaf yake dauke jama'ar gidan duk yawansu.

A cikin harabar akwai qofofi biyu dama da Hagu, ta hagun ce zata kaika cikin gida inda bangaren Matansa yake ta Dama kuma ta kasu biyu, daya ta inda dakunan samarin gidan yake ne dayar kuma dakunan masu aiki maza.  daidai qofar da zata shiga dakai sashin samarin gidan ya hango Faisal yana tahowa da wasu kwaftara kwaftaran takalma a hannu irin na taqadiran Black Americans din nan yana waigen bayansa, baya tsammanin ma ya lura da tsayuwarsa ya giftashi yana cewa

"Dan kutumar uba da ka biyo ni mana da wallahi sena farke ka a gidan nan" ya fice abunsa ya bar Alhaji da zuciyarsa take tsalle da lugude, dawa Faisal yake fada da har yake furta wadannan munanan kalamai wai ze farke shi kamar wani Dan Daba?

Salim daya fito daga qofar shima kamar an harboshi yana kwalawa Issa daya daga cikin Buzayen da suke gadin gidan kira ya taho da gudu ya durqusa cikin maganarsa ta buzaye yace

"Gani Alhajji me kuke da buqata?"

"Ina Faisal?" Ya fada a fusace, Issa ya daga hannaye sama yana cewa

"Ya fita Alhajji yanzun ya fice ta qofa"

"Zonan Salim" Alhaji Audu ya fada ganin shima be lura da tsayuwarsa a gurin ba. Ya wani ja iska kafin ya matsa inda Alhajin yake, kadan ya rusuna yace

"Barka da Rana Alhaji"

"Meya hadaku?" Ya tambayeshi ba tareda ya amsa gaisuwar tasa ba wadda idanda ace a shekarun bayane ma tabbas seya kife shi da mari kan wannan gaisuwar rainin daya masa.

Cikin qunquni Salim din yace

"Takalma na ya diba kuma na rantse da Allah sena masa dukan mutuwa idan muka hadu" babu tsoro ko shakka a muryarsa ya fada. Alhaji ya qara tsumewa dukda cewar zuciyarsa tsinkewa take ta ciki akan al'amuran dake wakana dashi yace

"Me yasa kuke haka? Saboda dan uwanka ya dauki takalminka shine zaka fito kana daga murya kuna zubar da mutunchinku a gaban masu aiki kamar wanda ya daukan maka wani abu me muhimmanci? Bana son haka kar kuma na sake ji, shi ya wuce yana zage zage kai kana cewa zaka masa dukan mutuwa me kukeyi hakan"

Salim ya daga kai ya kalli Alhajin da wani irin duba kamar wani sa'an sa yace

"Shi daya wuce ka tsayar dashi kaji ba'asin zage zagen da yakeyi?"

"Ban tsayar dashi ba saboda.."

"Base ka fada komai ba saboda shi dan so ne basa laifi, nida ya daukarwa abu nayi magana nine mara gaskiya to se a biyani kudin takalmina idan ba haka ba kuma na rantse da Allah sena kwantar da yaro" Salim ya datse Alhajin babu dar bare shakka tsabar mamaki kallonaa kawai Alhajin ya ringayi ya kasa cewa komai. Shi Audu ne yayi lalacewar da Kalan Hanji a cikin yayansa ze ringa mayar masa da magana?

"You are very stupid Salim Alhajin kake gayawa wannan maganar saboda baka da hankali?" Ahmad da shigowarsa kenan ya tarar dasu ya fada, Salim ya kada qeyarsa ya juya yana cewa

"Ai gaskiya na fada Yah Ahmad da ace ni na daukarwa Faisal din abu da yanzu an hada Family meeting ance mun barawo shi kuwa tunda dan gaban goshi ne kaga ni ya bawa laifin ina masa hayaniya a gida a biyani abu na kawai a zauna lafiya" daga haka ya barsu tsaye kamar sokaye saboda mamaki.

"Kayi haquri Alhaji gaba dayansu se na bata musu zan zauna dasu" Ahmad ya fada cikin girmamawa, Alhaji ya jinjina kai irin na wanda Idea ta qarewa kafin ya juya ya shige Falonsa maganganun daya sha yau suka masa rufdugu a kwakwalwa tabbas makomar gidansa tana cikin garari, idan kuma beyiwa tukfar hanci ba za'a samu gagarumar matsala.

Sama ya haye dakinsa ya zauna bakin gado bayan daya rage babbar rigar jikinsa ya qara gudun Ac, tunanin baya ya shigayi, so yake ya gano bakin zare ta inda ya kuskure ko Allah zesa ya samo hanyar gyarawa. Kamar Film ya shiga hasko rayuwarsa tun daga tushe.

ABDULWAHAB TIJJANI Shine Asalin sunansa, AUDU da mutane da  suka sanshi dashi yasa ake daukar cewa ABDULLAHI shine sunansa kamar yanda duk inda kaji Audu a gurin bahaushe tunanin na karkata da cewar Abdullahi ne sedai shi Alhaji Audu ya samu sunan ne ta dalilin wata kakarsu tun suna yara ya tashi da bala'in son kudi, da sallah idan ya samu yan silallarsa na barka da sallah ya ringa yawo dasu kenan a aljihu yana karkadawa suna qara idan ka tambayeshi menene se yace

"Kudina ne tara su zanyi se sunyi yawa sosai" shikenan take kiransa da Audu kudi tun befi shekara biyar a duniya ba kuma sunan ya bishi aka manta da Abdulwahab sedai Audun kawai har girmansa kuma wannan dalili ya saka koda Yaransa suka Shiga makaranta Malamai sukayi musu register da ABDULLAHI TIJJANI BECHI a cewarsu Audu ba suna bane.

Alhaji Audu haifaffen wani qauyene da ake kira Bechi cikin qaramar hukumar Kumbotson Jahar Kano. A yanda labari ya iske su kakansu daya haifi Mahaifinsu Tijjani wato Malam Lawan shine me garin Bechi na farko ance seda suka shekara Talatin da matarsa Asabe kafin Allah ya basu haihuwar Tijjani hakan yasa suka dauki son duniya suka dora masa sedai Allah beyi zasuyi doguwar rayuwa tare ba domin kuwa shekarun Tijjani bakwai a Duniya Mahaifinsa Malam Lawan Me gari ya rasu wata hudu tsakani ya rage kwanaki goma Goggo Asabe ta fita daga takabarsa itama ta amsa kiran Mahaliccinta shikenan Tijjani ya tashi maraya gaba da baya riqonsa ya koma tsakanin dangin Mahaifinsa yau yana wannan gida gobe yana na can wanda gaba dayansu sunayi ne saboda tarin dukiyar qasar da Mahaifinsa ya mutu ya bar masa ba kuma sun bari ya girma ya samu komai ba se wata gona kwalli daya wadda itama wani qanin mahaifiyarsa ne yayi tsayin daka gurin ganin bata salwantaba se fili wanda gidan da iyayensa suka zauna ya kamachi a bashi amma Sabon me garin da aka nada wanda yake qanin Mahaifinsa ya gaje ya shiga ya zauna a ciki dukda cewar gadon Tijjani ne, badan ma suna tsoron tijarar Kawun nasa ba shine dalilin daya saka ya bashi wani fili daban yace ya gina.

Da wannan gona daya tsira da ita yaci gaba da kula da rayuwarsa ita yake nomawa abinda ya samu ya siyar yayi buqatunsa har yayi aure ya auri Fadi yar Kawunsa yayan mahaifiyarsa haka suka zauna tsayin shekaru cikin rufin Asirin Allah har tayi yaya biyar Maza uku mata uku Lawan da suke kira Baba se Hashimu, Maryam, Amina, Aminu da kuma Zulai. Bayan Baba da Hashimu sun tasa su suka cigaba da taimaka masa da gonar da ita kadai ce hanyar samunsu, abinda suka noma a ciki zaau cire abinci, ragowar a siyar a ringa buqatun yau da kullum wannan dalili ya saka rani damina koda yaushe cikin shuka yake musamman da Allah ya taimakeshi gonar tasa tana kusa da wata fadama dan haka bashida matsalar ruwa sabodan

noman rani sannan tana da girma babu laifi shiyasa yake noma nau'ikan abici kala kala.

Suna zaune lafiya da Fadi lokaci daya ya bijiro da zancen son qarin aure bayan daya hadu da Hafsatu Farar bafillatana baquwa da sukazo qauyensu kawo Amarya Tijjani na ganinta yace tayi masa, be samu matsala da Fadi ba, inda ma yar tangardar take be wuce damuwar yanda al'amura zasu kaya musu ba idan ya qaro auran dalili da cewar lallaba rayuwa sukeyi ba shida wata hanyar samun kudi idan ba noman nan da yakeyi ba dukda rayuwa nada sauqi a wancan lokacin amma nauyi ze qarar masa idan yayi auran, rarar da suke samu ta amfani gona har a siyar bw zama lallai aci gaba da samu ba tunda wacce ze auro din itama haihuqa zatayi wata rana wannan Fadi taso ta fahimtar dashi amma ya nuna komai na Allah ne shi yake ciyarwa kuma yanda ya nufeshi da qarin auran ze hore masa abinda ze cigaba da kulawa dasu haka kuwa akayi ya auro Hafsatu zaman au gwanin dadi da Fadi tana bata girma sosai a matsayinta na wadda ta girmeta kuma tana sama da ita a gidan aure wannan ladabi nata yake qarawa Malam Tijjani sonta.

Shekara daya ta haifi Da Namiji aka saka masa Yakubu, shekarar biyu ta haifi Audu se Bilkisu, Aisha da kuma Muktar me sunan Babanta suna ce masa Baballiya.

Rayuwa ta qarayiwa Malam Tijjani da iyalan sa tsanani saboda sun qara yawa kuma madogarar tasu dai guda daya ce wannan gona, qari da haka hatta da Maryo da Amina yayan Goggo Fadi da aka aurar mazajensu duk suma ba masu qarfi bane se ya zama har dasu ake noma gonar Malam Tijjanin abinda aka fitar a raba kowa yaje yayi ta jalautawa da iyalansa wannan matsatsin rayuwa ya saka Audu tashi da burin son yayi kudi saboda Baffansa ya huta da wahala. A lokacin farko shigowar Boko Yaro dayane a garin yake karatun Bokon Shamsu wanda yake dan Me gari shima ya kaishi cikin Kano ne yana zaune gidan wani Hakimi se shekara shekara yake zuwa gidan. Sa'an Yakubu ne amma duka Abokanai suke dasu Audu tunda tazarar shekarun ba yawa kuma tare suke karatun Allo kafin aka kaishi birni  idan Shamsu yazo kuma zeyita bawa su Audu labarin Birni da Turawan da suke koya musu karatu har yace suyiwa Baffansu magana suma akai su dan Malamansu sun gaya musu idan suka dage sukayi karatu zasu samu aiki a ringa biyansu Albashi wadanda suka iya turanci kuma har Ingila zasu tafi dasu.

Zancen kudi da Audu yaji yasa hankalinsa ya tashi ya kuma quduri niyyar zuwa Birni Yakubu kuwa da tun qaraminsa ya tashi da Burin Zama Alqali, ko wasa akeyi zece shine Alqali ayita zuwa gabansa ana kawo shari'a shima Shamsu yace masa a birni da akwai Kotu ba irin yanda ake shari'a anan ba sedai aje gaban me gari. Audu yacewa Yakubu suyiwa Baffansu maganar zuwa Boko amma se yace Aa dan shi

yana da sanyi ba kamar Audun ba yana gudun yiwa Baffan magana yayi masa fada dan lokacin da aka kai Shamsu be manta ba harda Baffansu a masu cewa an kaishi ze koyo yahudanci Audu beyi qasa a guiwa ba ya samu Mahaifiyarsu da suke cewa Dada da zancen tayiwa Baffa magana ya samu me gari idan Shamsu ze koma birni su bishi take kuwa ta nuna rashin amincrwa itama dai kamar Yakubu ta tuna masa da Mahaifinsa na Adawa da Karatun Boko da ya shigo daga nan aka bar maganar badan har zuciya Audu ya haqura ba sedai yayi shiru ne kawai zuwa wani lokaci saboda tunda yaji zancen kudi fa hankalinsa yayi kan Birni kuma kota halin qaqa dai se yaje shi.

Seda aka shekara kafin dama ta sake zuwar wa Audu a wannan Karon a gurin Malamin da yake musu karatun yaji cewar ze kai Yara Birni can tsangayar Malaminsa Gwani Musa a unguwar Kabara. Audu najin wannan batu yana komawa gida ya sanarwa da Dada a wannan karon itama bata ce Aa ba tasan kuma shima mahaifinsu baze hana ba inda zaa iya samun matsala be wuci yanzu da suka tasa ba suna taya sauran yan uwansu aikin Gona amma tasan hakan baze zama wani abu ba. Haka kuwa akayi ta damu Malam Tijjani da batun yayi na'am har yace ze samu Malam Tsalha malamin tsangayar tasu yaji kanun maganar, bayan duk shirye shiryen da suka kamata Audu da Yakubu suka bi tawagar Yaran Gari zuwa birni Almajiranci, dukda Malam Tijjani yaso iya Audu ya tafi Yakubu ya tsaya amma Audu ya kafe kaida fata se sun tafi tare saboda shirinsu na karatun Boko wanda Yakubu ya fishi buri akan abu shi neman kudi kawai yake so yaje yayi a Birni ba wani Karatun Allo kona boko ba.

Seda suka shafe wata uku a tsangayar Gwani Musa suna kuma karantar birnin na Kano, basu san inda zasu nemi Shamsu ba balle ya kaisu makarantarsu, Audu a shige shigensa yayi Abokanai anan cikin Magashi suka shaqu da wani Yaro Sa'an sa Hayatu yaron gidan da Audu yake yiwa aikace aikace ne. Hayatu da sauran yan uwansa suna makarantar boko dan haka Audu ya nuna masa shida dan uwansa Yakubu suna sha'awar karatu kuma abinda ya fito dasu daga qauye kenan. Hayatu ya sanarwa da Mahaifinsa wanda a lokacin suna cikin mutanen da suka karbi Boko sosai yaji dadi kwarai da wannan abu dan haka ba tareda bata lokaci ba yaje da kansa ya samu Gwani Musa ya sanar masa da buqatar su Audu tayin karatun Boko. Da yake Malami ne me fahimta kuma shi kansa cikin yayansa akwai wadanda suke Bokon saboda yanda Sarakuna da masu kudi da suke samun damar fita Waje suke fada musu Alfanun Bokon be hanasu Audu ba, ya kafa musu sharadi dai na dole zasu cigaba da daukar Karatu, da safe suje bokonsu su dawo Yamma da dare su zauna a makaranta suyi karatun Qur'ani haka kuwa akayi su Audu suka fara zuwa makaranta shekara daya da haka yace shi ya gaji saboda Shamsu ce masa yayi idan anyi karatu za'a samu aiki a samu kudi shi kuwa kullum karatu ake dora musu

bema ji ranar da za'a gama ba dan shekaru ake lissafowa Yakubu ne yayi ta tausarsa akan yayi haquri da sannu zasu kai matakin da suke buri.

Haka suka ci gaba, Yakubu na matuqar maida hankali ga Karatu yayinda Audu turanci kawai ya saka zuciyarsa ze koya saboda idan ta tabbata sun gama makaranta za'a kaisu turai kar yaje ya rasa bakin magana. A hankali ya faratiwa Makarar asha ruwan tsuntsaye, Sadi, da aka kawosu Almajiranta tare amma shi dan Bagwai ne shiya fara nuna masa hanyar Kasuwa. Da safe idan sun tafi Boko shida Yakubu ze zame ya tafi bakin Asibiti anan zeyi duk wani aiki daya samu, dako ne, aike, duk wani abu da zeyi a biyashi haka ya ringayi kan jiki kan qarfi dake ya saka abin a ransa kuma yana da zuciyar yi se gashi baya jin wahalar kowanne irin aiki indai ze kawo masa kudi.

Da Yakubu ya gane baya zama a makaranta yace ze gayawa Malam seya dakata da zuwa Kasuwa, cikin yan kudaden daya samu ya auno Aya da gyada ya kaiwa Matar Malam da suke kira Nene dayake suna shiri yace tayi masa gyada me gishiri da Aya me siga ya daura abarsa a Boko ya siyar a Allo ya siyar se gashi an gane shi a unguwa Audu me gyada da Aya kuma sosai yake ciniki abinsa. Seda suka shekara biyu kafin sukaje gida, a lokacin sun fara zama samari dan Yakubu nada shekaru sha biyar Audu nada Sha uku. Cikin yan kudaden jarinsa yayiwa Dada da qannensa harda Baffansu tsaraba.

Kowa yaji dadin yanda ya gansu, Dada ce ta ringa masa fada akan ina ya samu kudi yayi wannan siyayya be boye mata ya sanar mata da duk abubuwan da yakeyi harda zancen Boko da sukeyi shida Yakubu ya kuma qara da fada mata gaskiyar dama saboda ya samu damar neman kudi Yakubu kuma yayi karatu yasa sukace zasu Makarantar Allon. A wannan karon kafin su koma seda ta sanar da mahaifinsu gaskiyar komai gudun kar wata rana ya gane yace sun hada baki sun munafurceta, da fari ya ringa fada dan sosai yake Adawa da karatun Boko har yana cewa ba zasu koma Birnin ba se kuma daga baya basu san yanda akayi ya canza ra'ayi ba da kansa yayi musu shirin komawa ya kuma yi musu nasiha tareda gargadin su tsaya a turbar Allah karsu yarda masu jajayen kunnuwa su dorasu akan wata hanya sabanin wadda Addinin Islama ya dora mu akai. Ya sake jawa Audu kunne sosai akan banbance tsakanin Halal da Haram tunda yana zuciyar nema baze daku she shi ba, abinda ya janyo masa sakkowa harya haqura zasu koma dinma bayan sunyi magana da Hashimu dansa na biyu shiya nuna masa Alfanun abinda su Audun sukeyi tunda baya kaucewa shari'a bane.

Yace masa "Baba idan ka dubi yanda rayuwa take tafiya a kullum abubuwa qara yi mana wahala sukeyi dan abinda muke nomawa ba wadatar mu yake yi ba balle har mu samu na siyarwa muyi sauran buqatu kuma ko a cikin karkarar nan idan ka duba masu fita fatauci Abokanan mu zakaga suna samun Abun rufin asiri har su taimaka mana muma, da ace tun muna qanana kamar su muma mun tashi da wannan tunanin qila da rayuwar ta mana sauqi amma yanzu tunda Allah yasa su sun himmatu zasuyi a barsu muyita rakasu da Addu'a Aminu ma da ze bisu suje can birnin yayi Bokon koya kama sana'a kamar Audu duk da hakan yayi".

To haka su Audu suka koma ba tareda Aminu ba dan yace ba zashi ba da yake Auta ne Goggo Fadi bata takura masa ba kuma shi kadai ya rage gabanta tunda duk an aurar da Maryo da Amina Mazan ma Hashimu da Lawan sunyi Aure. Rayuwa taci gaba da garawa Audu da Yakubu a birni, iya wuya Audu neman kudi yakeyi yana kuma riqe da hudubar Mahaifansa akan ya tsaya ga halal karya kuskura yaci abinda Allah be halasta masa ba kuma da yake a lokacin duniya na zaune lafiya cuta da bata gari basuyi yawa ba shiyasa abun yazo masa a sauqaqe. Tun yana Dako a kasuwa ko aikace aikace har ya fara kayi nayi, ze karbi kaya ya fita dasu ya siyar ya cire ribarsa har ta kai ya hada yar tireda yana kasa kayan koi gefe gida kuma ya ajiye Baro duk wani dan itace na marmari da ake yayi a lokaci ze saro ya ringa siyarwa yan kasuwar har mamakinsa suke ganinsa yaro qarami dukda yana da baragen girma amma zafin neman sa ba duk babbaba shiyasa yayi shura a bakin Asibiti babu wanda besan AUDU BECHI ba haka suke masa inkiya da garinsu.

Duk qarshen shekara suke zuwa gida kuma duk sanda zasu tafi haka ze hada tsaraba himili duk wanda ya shafe shi seya riqe masa wani abu ya kai masa dan badaga nan ba Audu akwai kyauta kuma a wannan yanayi Girma da Wahala suka fara kwantar da mahaifinsu dukda shekarunsa basu kai ace ya kwanta tun yanzu ba amma yanda rayuwar ta faro tun quruciya jiki yana wahalar data zarce abinda ze dauka shiya janyo masa ciwo yayi masa kwaf yau lafiya gobe babu haka yasa idan zasu je gida Audu ze siyi magungunan ya tafi masa dasu da irin mayukan zafi saboda qorafin ciwon jiki da yake yawanyi.

A wannan gantafalfala suka kammala Primary tareda Saukar alqur'ani ta biye wadda Audu dai ba zuwanta yake ba a sati befi ya leqa sau daya ba ita kanta Allon Karatun dare kadai yake zama Gwani yayi fadan yayi nasihar amma Audu ya toshe kunne, dadinta daya yana biya karatu daidai ya wanke Allonsa akan lokaci wannan yasa Gwani yake daga masa qafa Bokon ma idan ana jaraba zeje yayi kuma zeci ga turancin daya saka kansa ya iya radau dan ko Yakubu me qulafucin Bokon Albarka shiyasa Malaman suke ji dashi, Audu akwai rashin ji amma akwai kwakwalawar daukar Karatu.

Yakubu ya tafi makarantar kwana dan cigaba da karatun sa, burinsa ne ya zama Alqali Audu kuwa yace yayi sallama da Boko ya kama neman kudi kuma. Shi yayiwa Yakubu duk wani shiri na tafiya makarantar, haka kuma yana kai masa ziyara idan anyi hutu Yakubun Bechi yake tafiya yayi hutunsa acan Audu kuma ana Kano ana ta fafutukar rayuwa.  Inda ya kafa yar tiredar tasa aikin fadada titi yabi ta gun dole ya tashi daga qarshe ya koma zuba kayan kolin nasa a  Baro yayi ta zaga kasuwa yana waqa ta kiran customers yanda yake waqar abin dariya yake saka wasu siya badan ma sunyi niyya ba. Yakubu yana shekara ta uku a makaranta lokacin kuma aka aurar da Bilki wadda take bin Audu, ba qaramar Bajinta Audu yayi a auran nan ba dan dama ya dade yana tanadi saboda mutuniyarsa ce ko irin fadan sako da sakon nan basa yi da akwai fahinta sosai a tsakaninsu a kuma Bikin Bilkin ya dabbaqa soyayyarsa ga Bara'atu wadda tayiwa Bilki babbar qawa. Tun suna yan yara Audu yake sonta an dauka yarinta ce ashe shi har ransa ya riqe abun yanzun daya furta yana son ta da yawa wasa suka dauki abun saboda idan ka dubi a yanda akewa yara aure Bara'atu ta isa kaiwa daki dukda shekarunta sha biyu ne a sannan amma ga Bilki da take sa'arta an mata aure itama Audu kuwa yana shekara sha bakwai koda Maza suna saurin Aure a qauyen amma be isa ba tukunna, ga Yakubu me sha tara da Aminu me Ashirin da biyu nan basuyi aure ba bare Azo kansa haka dai ya ringa hurewa Bara'atu kunne da soyayyarsa seda ya tabbata ta mato ta yanda ko ya koma birni ba zata saurari wani ba zata jira shi kafin ya koma Birni ya bar Audu da suke hutun makaranta zasu shiga Aji hudu a sannan.

Satin Audu daya da tafiya jikin Malam Tijjani ya motsa kuma ciwon yafi na ko yaushe zafi dole Yakubu ya bazamo Kano neman Audu saboda Malam din da yake ta nanata a kira masa Audu gashi babu waya a sannan, kwananansa daya suka juya hankali tashe yanda ya tarar da jikin Mahaifin nasa ya tayar masa da hankali ya shawarci manyan yayyensu akan su tafi da Malam Kano a akaishi Asibiti amma suka qi a cewarsu anayin na gargajiya wai a yanda ya ganshi ma jikin da sauqi, cikin daren Ranar Malam Tijjani ya amsa kiran Ubangiji har yaja numfashinsa na qarshe kuwa be dena maimaita musu su tsaya akan gaskiya ba kuma duk rintai duk wahala karsu yada zumunchi suci gaba da hada kansu kamar yanda suka tashi.

Sunyi kuka sosai da jimamin rasuwar mahaifin nasu, daga Audu har Yakubu suka kasa komawa inda suka fito saboda mahaifiyarsu da mutuwar Malam din ta tabata sosai har itama ta kwanta jinya, ita din bata da kowa a yanzu se Malam dasu yayanta dan Iyayenta duk sun rasu Yayyenta biyu suma shekara uku kenan Babban Ya rasu me bi masa kuma be cika shekara da rasuwa ba shima yanzu ga Malam shima ya tafi. Seda sukayi dagaske suka qarfafa mata guiwa kafin ta dangana taci gaba da zaman takaba. Audu ya damu Yakubu akan batun komawa makaranta dan

tuni hutu ya qare an Koma amma duk sanda yayi masa maganar se yayi shiru yaqi ce masa komai. Audu be fahimci dalilin Yakubu naqin komawa makaranta ba seda akayi sadakar Arba'in din Mahaifinsu, a ranar kuma dattawan qauyen suka zaunar dasu akan maganar rabon gado.

Page 3

Malam dai sun sani Gona guda daya ya bar musu se gidan da suke ciki, aka raba musu komai yanda shari'a ta tanadar, ba'a samu wani surutu ko hayaniya ba saboda yawansu daya kowanne bangaren sunada Maza uku mata biyu se iyayensu mata. Zancen gida duk sun yarda akan kar a raba iyayensu suci gaba da zama ciki tunda kowa yasan bangaren da yake mallakinsa haka Gona sun yarda akan za'a ci gaba da nomata yanda aka Saba ana raba amfanin kuma lokacin daman yayi daidai dana girbi dan haka kwana kadan akayi girbi aka kawo amfanin Gona gida kuma daman abinda ake dan jalautawar yayi qasa banda ma Audu da ya zo da yan kudade shi yake ta hidima da gidan tun bayan Rasuwar Malam.

Su Audu sunyi zaton za'ayi rabo ne matsayin cewar kowa yana da gado cikin abinda aka girbe din amma se sukaga sabanin haka. Sanda akayi rabon baya gida yana gurin Bara'atu yaje tadi. Yakubu da akayi a gabansa kuma kanzil bece musu ba suka kacaccala kayan suka ware musu nasu wanda dama ba dukka aka fito dasu ba kadan aka yafito daga Rumbu aka zuzzuba musu Masara, Gero, dawa buhu bibbiyu Alhalin a shekarar an samu amfanin gona ko wanne launin Abinci yafi Buhu Hamsin amma abinda suka basu kenab se shinkafa da sukeyi wadda yawanci daman ita Siyarwa akeyi to bata isa girbi ba. SedaAudun ya dawo ya tarar da kayan a bakin qofar dakin Dada inda suka ajiye musu, duk da cewar Rumbun gidan a kasonsu ya fado amma su Hashimun sun kulle tulin abinci sun tafi da muqulli. Sanda Malam yana raye duk nan ake ajiye komai duk wadda zatayi girki ta shiga ta diba su kansu su Hashimun sedai su dibi wanda ze ja musu lokaci idan ya qare a kuma diba.

Audu ya gama kallon kayan kafin ya shiga dakin Dada suna zaune suna cin tuwon Dawa da Aisha ta tuqa musu suna hira jefi jefi ya ajiye musu qullin soyayyar karfasa daya taho musu dashi Dada ta saka masa Albarka tareda tura masa nasa kwanon tuwon da aka ajiye masa. Kai ya girgiza alamar ya qoshi dan yaci a gidansu Bara'atu, Innarta Da takeyi dashi shiyasa dui sanda yaje gidan seta tisa dole ya shiga in da darene se yaci tuwo tun yana kunya har ya sake dan ko beci ba zata hado shi dashi ya taho gida. Seda ya bari sun gama cin tuwon kafin yayi magana yace

"Dada naga Hatsi a qofar daki na waye?"

"Yawwa daman kai nake jira ka kamawa Yayanka ku shigar dasu dakin Malam (shima Rabon su ne) wannan uban sakalcin wai baze iya ba" ta nuna Baballiya dake rakube gefen gado wai bacci yake so yayi ita kuma ta hanashi tace se tuwon daya ci ya ratsa masa.

"Abinda ban gane ba Dada waya kawo Hatsin?" Ya sake tambayarta. Ta miqe tana cewa

"Rabon mune na amfanin gona da aka fitar dasu yayyenku suka raba, to kaga Rumbun nasu ne yanzu shiyasa nace ku saka a dakin Malam tunda nan babu guri"

"Wancan abun ne rabon mu rai shida a cikin sama da buhu dari da aka fitar, kenan buhu daddaya muka tsira dashi cikin gadon uban mu ba wai kyaimuta aka bamu ba?" Audu ya fada cikin zafin rai yana miqewa se a sannan Yakubu yayi magana yace

"Abinda suka ga ya kamata su bamu kenan kuma kar kace zakayi magana muje mu shigar dakin kamar yanda Dada tace"

"Wallahi Baze yuwu ba, banda ma tsabar rainin wayo roqarsu mukayi da zasu tsammana wannan abun ko kuwa? Dole a fito da komai a sake rabo me yasa ma da zasu fara baka kirani ba" yana gama fadar haka fuuu yayi waje Dada da Yakubu na kiransa amma beko saurare su ba yayi dakin Goggo Fadi.

Dada da Yakubi sunfi Audu sanin yanayin zaman gidan a yanzu saboda kusan shekara bakwai kenan daya fara zaman birni idan yazo yan kwanaki yakeyi ya koma kuma duk sanda zezo da abin hannunsa dan haka kowa haba haba yake dashi. Yakubu kuwa tunda ya fara makarantar kwana nan yake hutunsa dan haka yasan duk wata kitimurmura dake faruwa tsakanin Goggo Fadi da yayanta da yawan qorafin da sukeyi akan Abinci wanda a cewarsu su suke wahala su Noma Hafsatu da Yayanta sedai kawai suci harda Bilki da ake aikawa dukda shi Mijinta babu laiifi yana da rufin asiri dan haka be shiga cikinsu ana noman tare ba amma in akayi girbi se Malam yasa an loda itama an kai mata acewarsa tana da haqqi cikin gonar.

Iyakar qoqari Malam yayi gurin ganin cewar kan Ahalinsa be rabu ba kuma har ya mutu yana musu wannan nasihar wadda kuma sunyi qoqarin boye taciki sun hada kai a gaban idonsa to amma yanzun basa jib zasu cigaba da bautawa Hafsatu da yayanta shiyasa suka fara da haka a ganinsu ma sun musu Adalci da suka basu wannan din ladan Aikin da Malam yayi kafin ya kwanta dama.

Audu kuwa da sallama ya shiga dakin Dada yana qoqarin danne bacin ransa, suna zaune ita da Baba da Hashimu suna hira. Ya tsugunna daga gefe ya gaidasu suka amsa fuska a sake kafin sukayi shiru gaba daya. Seda ya saisaita muryarsa ta yanda zasuyi magana cikin risilama kafin yace

"Yaya Daman naga hatsi a qofar mune dana tambayi Dada se tace mun wanda aka rana aka fitar mana ne"

"Na'am, haka akayi" Hashimu ya fada yana karkacewa dukda cewar shi Audu da Baba yayi magana, shiru suka kumayi ganin da yayi basu da niyyar tanka masa dan Goggo Fadi ma wata hira take neman jefo musu tana tambayarsa yaushe ze koma Birni dan haka yace

"Yaya tambaya fa nakeyi shi wancan abun ana nufin shine rabonmu mu biyar da Mahaifiyarmu kenan?"

"Ga amsa ka bawa kanka Audu me kuma kake da buqata?" Baban ya magantu sannan yaci gaba da cewa

"Ko yayi yawa ne? Tunda kai ba mazauni bane Yakubu ma Makaranta ze koma Innartaku daga ita se Aisha da Baballiya Aisha ma jiya na hadu da Hayatu yake roqar arziqin a basu ita tadan taya Bilki zama inaga an samu qaruwa ne ko yace bata da kafiya dama yanzu nake so idan zan fita na leqa nayiwa Goggon maganar to gaka ma seka shaida mata idan ka koma kaga wannan abinci ai ya isheta ita da Baballiya".

Ran Audu ya qara baci amma ya daure murya a daure yace

"Amma dai Yaya koda ace cikin Dada ne ita kadai kamata yayi a raba komai kai daya yanda shari'a ta tsara tunda dai muna da gado a ciki wannan ruwan mune bisa Adalci mu qara muku tunda kun fimu buqatar abincin"

"Babu shakka rashin kunya zaka manq Audu mu kake kallo kana cewa mun fiku buqatar abinci wato ga mayunwata ko?" Goggo Fadi ta fada tana tafa hannu. Ko a jikinsa yace

"Ni ba abinda nake nufi ba kenan Goggo, nufina su Yaya suna da Iyalai mu kuwa bamu da nauyin komai kamar kuma yanda ya fada mu ba mazauna bane dan haka abincin zeyi mana yawa ku kuma ya muku kadan"

"To yanzu me kake so ayi?" Baba ya tambayeshi, Audu ya gyara zama yace

"Rabo za'a sake na gaskiya a fitarwa da kowa haqqinsa idan ma ta kama a kirawo su Liman da me gari su raba"

"To ba za'ayi hakan ba ubanmu, kai karfa kaga wai ka fara riqe yan kudade ka dauka kafi mu ko zamu bika to baka isa ba wlh da zaka zo kana yiwa mutane magana da sigar umarni. Bari ma kaji wannan rabon da kaga an baku dan dai Goggo ta saka baki ne amma da mu bamuyi niyyar baku kamar hakan ba saboda babu guminku ciki mu muka sha wahala muka noma abinci dan haka daga yanzu in har kuna son kuci abinda aka noma cikin gonar nan to sedai ku shiga ayi daku" Hashimu ya fada, Audu ya kalle shi kafin ya miqe yana cewa

"Amma dai muna da gado a cikin gonar ko?"

"Su kuma ai ba bayin ubanka bane da zasu sha wahala su noma kuna zaune su baku kuci" Goggo Fadi da se yanzun ta saka musu baki ta fada wannan ya tabbatar masa da cewar shawararsu daya dan haka ya fice yana cewa

"Ai kuwa in har haka kuka zaba sedai a raba gonar idan yaso se na gani in abinda kuka samu ze isheku ku noma abincin shekarar". Goggo Fadi ta hau tafa hannu tana salallami wai yazo har daki ya qare musu tanadi.

Audu kuwa yana fita dakin da suke kwana ya shige zuciyarsa na tafarfasa dan yasan idan ya koma dakin Dada ma fada zatayi masa ta bashi rashin gaskiya amma ya qudure a ransa kome za'ayi sedai ayi tunda ta haka suka zaba to su zuba su gani su waye zasu sha wahala. Kenan ita Goggo Fadi luf luf tayi musu sanda Malam na raye suke zaune lafiya da Dada shine yanzu daga mutuwarsa ko kwana sittin be cika ba fitina zata fara bullowa daga barayinta. Idan taqamarsu su suke noma gona ai su kuma suna da kaso a cikin qasar ya zama tamkar sun basu aro ne suna biyansu shikenan tunda dai basu hango wannan maslahar ba to za'ayita yanda suke so dan idan rigima ce kowa ya sani kaf karkarar bashida mahadi. Tun yana dan mitsitsi fada ne dashi kamar dage babu randa baz fita wasa ba tareda an kawowa Dada ko Baffa qarar ya daki wani ba shiyasa ma ya dena wasa da sa'anninsa ya shiga cikin su Yakubu amma ko su din idan kaga yanda yake a cikinsu seka dauka ya girme su kura ce tayi lafiya kuma tunda aka tabota kowa ze dandani kudarsa.

Yana kwance yana saqa da warwarar ta inda ze bullowa al'amarin, yanzu idan ya koma Birni Yakubu ya koma makaranta kenan zaman gidan in ba'ayi wasa ba gagarar Dada zeyi to kuwa baze taba barin haka ta faru ba. Yakubu ya shiga dakin rai a hade yace ya tashi su kwashe kayancan amma ko gezau Audu beyi ba, daya isheshi da magana yace

"Ka qyaleni baza'a kwashe ba se gobe tayi an sake Rabo sannan su kwashe nasu daga Rumbu tunda ai ba rabonsu bane ba"

"Audu kasan me kake so ka taso kuwa?" Yakubu ya fada yana zama a gefen qafafunsa Audu ya wuntsila ya tashi zaune yace

"Na sani, naje na same su sunce tunda bamu noma ba dan haka iyakar abinda zasu bamu kenan kuna daga yanzun ma muddin muna son Abinci sedai mu shiga ayi Noma damu"

"To ai gaskiya suka fada, shiyasa nace maka bazan koma makaranta ba na haqura da karatun zan zauna na kula da Dada dasu Aisha kai kuma ka shirya ka koma Birni kaci gaba da Buga bugar ka" Yakubu ya fada cikin sanyinsa, Audu ya galla masa harara tsabar takaici daya rasa me zece masa kawai yayi tsaki ya koma ya kwanta. Haka Yakubu ya gaji da masa maganar ya tashi su kwashe kayan qarshe se Aminu daya shigo gidan ne ya taimaka masa suka kwashe, shima seda ya tambayi Yakubun kayan menene wannan yayi shiru bece masa komai ba.

Daya shiga gurin Goggo Fadi lokacin su Hashimu sun tafi gidajensu  ya sake tambayarta nan ta wassafa masa qarya da gaskiya akan Audu, Aminu yayi shiru kafin ya kalli Mahaifiyar tasa yace

"Amma zancen gaskiya wannan ba Adalci bane Goggo, wannan hatsin da ake magana fa Malam ne ya noma shi a gonar sa mu duk mun tayashi aiki ne a matsayinmu na yayansa, kinga kenan duk wani Magajinsa yana da rabo daidai da kowa a ciki koda kuwa Jinjirine yau aka haife shi. Sannan maganar kuce idan basuyi Noma ba baza'a basu abinci ba bata taso ba saboda yau idan sukace a raba gonar nan kun sani Kason da zamu samu baze isa mu ringa noma abinda ze riqe mu ba, kuma ko cewa sukayi mu ringa haya muna biyansu bamu da abinda zamu basu. Nidai a ganina ayi maslaha koda kuna ganin ba za'a ringa raba daidai ba tunda mun fisu yawan Ahali a ringa fitar musu da abinda ze ishe su har su saida suyi sauran buqatu hakan duk taimakon kaine".

Goggo Fadi tayi kasaqe tana kallonsa kafin tace

"Babu shakka Aminu wato Hafsatu da Yayanta sun fimu a gurinka kenan ko?"

"Ba abinda nake nufi kenan ba Goggo, ni wlh kece ma kike bani mamaki gaba daya kin biyewa Yaya Hashimu yana doraku akan wata hanya ta daban dan Yaya Baba ma babu ruwansa sedai idan yanzu shima ya dauki hudubar tasa, har Malam yaja numfashin qarshe yana mana nasiha da mu hada kanmu kar mu bari baraka ta shiga tsakaninmu me yasa kuka zauna tsayin shekaru lafiya dasu se yanzu daya mutu sanda yafi buqatar mu hada kai mu cigaba da yi masa addu'a sanann ne kuma fitina da rabuwar kai zata bullo?

Kowa ya sani Dada bata da matsala kuma kome zakuyi ba zata daga kai ta kalle ku ba amma ai mutum ya kamata yasan daidai ba se an tunatar dashi ba ina amfani cikin danne haqqin wani wannan abun fa magana ake ta dukiyar marayu da wanda ya cinye kudi da kadarori daku da kuke shirin cin kwayoyin hatsi a gurin Allah baku da banbanci Goggo, nidai shawarata tun wuri ku farga karku bari shaidan yayi tasiri a zukatanku. Yanzu an fara rigima akan Gona gobe kuma se ace za'a raba gida shikenan zumunchin da Malam yake ta mana takarar mu riqeshi kinyi sanadin murqusheshi"

"Nice ma zan raba muku zumunchin?" Goggo Fadi da jikinta yayi sanyi da maganganun Aminun ta fada, ya miqe yana cewa

"Eh mana saboda duk fitinar da su Yaya Hashimu zasu zo da ita idan kika tsawatar musu dole su bari amma idan kika basu goyon baya kinga gaba zasu qarayi" daga nan ya fice ya wuce can dakinsu inda suke kwana dasu Audu.

Tun Asuba da suka fita masallaci Audu be dawo ba kaitsaye qofar gidan Liman ya tafi ya jirashi yana zuwa kuwa ya zayyane masa abinda ya faru dan ya rantse baze bar maganar ba, shirye shiryen komawa Birni yakeyi tayaya hankalinsa ze kwanta a can Alhalin an fara irin haka ga Yakubu yana maganar ze haqura da mafarkinsa saboda ya zauna ya kula da mahaifiyarsu shi kuma baze yarda ba shiyasa zeyi iyakar qoqarinsa yaga komai ya daidaita sannan su rankaya su koma Kano dan yayi rantsuwa muddin yana numfashi seya cikawa Yakubu burinsa na zama Alqali.

Liman ya gama jin bayaninsa yace yaje ze samu me gari daga nan za'a kira duka yan uwan nasa su zauna haka akayi kafin yamma duk an kai musu sammaci bayan sallar isha'i suka hallara gaban me gari Hashimu se muzurai yakeyi Baba dai

fuskarsa kadaran kada han. Liman yace Audu ya maimaita abinda ya faru tsaf ya sake rattabo musu Yakubu se faman harararsa yakeyi aka tambayi su Hashimu sukace haka ne daga nan Liman ya fara musu shari'a ya karanto musu abinda Shari'a ta tanada akan rabon gado, koda ace wani da Guda daya shine kan ragamar juya dukiyar Ahali gaba daya, muddin dai wannan dukiya mallakin mahaifinsu ce duk randa ya mutu hatta da Jinjiri idan ya bari yana da gado a ciki, babu zancen kai kasha wahala ka tara dukiya tunda dai ba taka bace to ta kowace gaba daya. Liman yace gobe za'aje a fito da Hatsi gaba daya a rabawa kowa nasa idan yaso se su sake hadewa su ajiye duk inda suka ga dama.

Hashimu zeyi magana Baba ya hanashi, haka aka tashi rayuka babu dadi washe gari kuwa Liman da wakilan me gari sukaje aka sake rabon Hatsi dukda cewar a cikin daren Hashimu yasa an kwashe fiye da rabi an kai gidansa ya boye a hakan seda aka fiddo da huhunhuna hamsin da biyar, aka hada dana gurinsu Audu shida ya zama sittin da daya nan aka raba musu kowanne bangare suka tashi da Talatin, guda dayan kuma aka bawa masu rabo ladan aikinsu wanda ba shari'a ce tace a bayar ba tsabar son zuciya ya saka su karba.

Cikin zafin rai Hashimu yace

"Toh tunda anyi haka se a fadi yanda za'a cigaba da kasafin Abincin dan wlh babu yanda za'ayi musha wahala muyi noma suna zaune mu ringa raba komai daidai dasu. Audu yayi tsugul yace a raba Gona kowa ya dauki kasonsa. Yakubu ya zabga masa harara yana cewa

"Idan an raba kai zauna ka nomata?"

"Se mu bada haya, idan kuma su zasu karba ma bismilla ayi qiyasin abinda zasu ringa biyan mu duk shekara" Audu ya sake fada. Dada dai ta rasa abin cewa dan duk bata san tsiyar da aka qullo ba seda aka zo rabon abincin kiran da aka musu jiya da suka dawo babu wanda ya fada mata inda sukaje. Haka dai aka tashi a matsayar zasu bar musu barin gonarsu suci gaba da nomawa, ladansu duk shekara abinda aka samu za'a raba uku, su dauki biyu su basu kaso daya matsayin ladan hayar gona kowa yayi na'am da hakan dukda zuciyar Hashimu da Sama'ila Mijin Amina dan karere sunyi wani qullinsu na daban.

Audu be koma Kano ba seda suka tabbatar sun saita komai, sun siyarda wani kaso na abincin suka barwa Dada kudin a hannunta saboda laluran yau da kullum kafin ya tasa Yakubu a gaba kamar shine qanin suka koma lokacin tuni zangon karatu yayi nisa har ana shirin jarabawa dakyar aka karbeshi yaci gaba.

Audu yaci gaba da buga bugarsa a birni yana hada kan kudade, sana'a babu wacce baya gwadawa, idan kasuwar ta gusa seya saki ya koma leburanci, shine aikin gini shine zuwa gidan Burodi har sannan kuma yana zaune a makarantar Gwani Musa dan bashida wani guri da zeje ya ringa kwana idan ba nan din ba. Yana lissafe da su Yakubu sunyi hutun makaranta har an dawo wata rana ya shirya zuwar masa Visiting kamar yanda ya saba sedai bayan yaje makarantar aka shaida masa Yakubu be dawo hutu ba. Kwana biyu tsakani ya tasamma Bechi dan yaje yaga meya hanashi komawa makarantar, bayan isarsa ya tarar da Dada bata da lafiya,a yanda aka gaya masa wai Barayine suka diro tsakar dare suka kwashe musu abinci sannan suka farmaki dakinta suna neman Murjaninta da wata sarqar Zinare data gada gurin Mahaifiyarta da basu samu bane shine suka mata duka ita da Aisha har Aishar ta samu karaya a hannu.

Audu rasa abin cewa ma yayi, tunda aka haife shi a qauyen be tabajin ance barayi sun haura wani gida ba, ba wannan bama ace da suka shigo iyakar Rumbunsune ya tsone musu ido basu taba nasu Goggo Fadi ba sannan zancen Murjani tana dashi wanda ya taka na Dadansu a Daraja dan har shagube takeyi tace se Auran Aminu Autanta ya tashi zata bayar aje birni a siyar dashi tayi hidima duk basu bi sun dauka ba se na Dadarsu. Yayi niyyar tayarda balahira Dada tace Akul, ko bata sani ba idan yayi magana bata yafe ba wannan yasaka jikinsa yayi laqwas, tsanar da be taba zaton zeyiwa jininsa ba ta dirar masa domin yasan shirin sune.

Haka yayi sati daya ya juya dan Yakubu ya rantse masa baze sake komawa makaranta ba gaba besan abinda ze faru da su Dadar ba. Har kuka Audu yayi akan shi ze zauna Yakubu ya tafi ya qarasa karatunsa amma yaqi, yace to sedai su zauna duka nan Yakubu ya ringa lallabashi akan ya tafi shiya haqura da Boko haka Allah ya qaddara bakin abinda ze samu kenan ze zauna ya fara sana'ar dinki daya koya a zamansa a Kano yaci gaba da kula da mahaifiyarsu. Da banbaki ya yarda ya juya Kano da burin nema domin ya samu ya fiddo da mahaifiyarsa da yan uwansa daga Bechi suzo suyi rayuwa me kyau.

Page 4

Haka rayuwa taci gaba da garawa, iya wuya Audu ya dukufa gurin neman Halalinsa kuma ubangiji ya sanya masa Albarka a abun duk abinda ya taba nan da nan se ya karbeshi sedai kuma wani ikon Allah daya fara ganga ganga se sana'ar ta turgude sedai ya saketa ya kama wata wannan yasa aka koma yi masa laqabi da Audu sana'a Goma dan da yawa suna ganin kawai zafin nema ne ya saka komai seya

taba. Wata shida shida yake kai ziyara gida idan kuma ya tashi tafiya haka ze hada tsaraba tuli ya kaiwa yan uwansa harda yan Dakin Goggo Fadi da tun abinda ya faru akan Gona aka koma zaman doya da manja idan ka cire Aminu shikadai ne suke mu'amalla dashi yayi Aure har matar ta haihu sun samu Abdullahi yaron idan ka ganshi se kace Audu ne ya haifeshi su Yaya Hashimu kuwa ana fama da baqin rai amma hakan be hana idan Audu yaje da kayayyaki ya basu babu kunya su karbe, a kwai zuwan da yayi Malam babban dan Yaya Baba yace ze bishi Birni Goggo Fadi tayi kicin kicin ta hana a cewarta baze tafi dashi ya koyo masa fitsara da rashin mutunchi irin nasa ba dukda Yaya Baban yaso hakan amma babu yanda ya iya Audu ya koma cike da baqin cikin Yakubu da duk zuwan da zeyi seya masa magiyar ya koma yaci gaba da karatunsa amma yaqi.

Shekaru uku suka shude a sannan Audu nada shekaru Ashirin a duniya ya zama cikakken saurayi ta kowanne fanni, neman Kudi kuwa se abinda ya qarun masa, tuni an aurar da Aisha Yakubu ma yakai kudin aure a can rigar su Dada ya samo budurwa Balaraba kyakykyawar bafilatana har an tsayar da rana watan Azumin tsofaffi wata uku kenan masu zuwa shirin Auran yasa Audu ya qara qaimi gurin neman kudi, a cikin gidansu suka yanki fili Yakubun ya gina daki ciki da rumfa saboda gurin yana da yalwar tsakar gida kowa dai yasan yanda akw gini a zamanin da, mutum daya na iya faro gida yaya su tasa duk suyita yankar fili suna tada dakuna a ciki suma.

Hada qarfi sukayi shida Audu sukayi ginin dan shima yana taba Dinki kuma da yake yazo da zamananci za'ace ba kamar yanda aka saba a karkarar ba se ya zamana yayi suna har daga maqwaftan qauyukansu ana kawo masa dinkin. Tsaf suka gina daki dukda ginin qasane amma anyi Sumunti da daben qasa wanda daga Kano Audu ya taho da simintin haka dakin Dada ma an daga mata shi anyi dabe da fulasta, dakinsu da suke ciki a da wanda yake Rabon yaran Goggo Fadi ta zugasu sun karbe wai Hashimu ne yake ajiyar Hatsi dan yanzu ya siyi gona tasa daban yana nomawa kuma a tasun ma haka zeyi bake bake idan an girbe yafi kowa kwasa wannan dalili yasa Audu ya gyara Asalin dakin Malam wanda suka mayar na ajiyar shigi shima yayi dabe da fulasta ya zama gurin saukar sa idan yazo, da ana aikin ma so yayi da ayi katanga a raba gidan tunda har Bandaki sukayi dan Asalin na gidan a barayin Goggo Fadi yake sunyi wani tun rashin lafiyar da Dada tayi bayan rasuwar Malam akayi mata bandaki daga kusan dakunan ta yanzun ma kuma anyi a gefen dakunan Yakubu wanda Audu yace za'a dan kewaye masa bangaren saboda sirri.

Ya koma Kano da niyar se bikin Yakubu ya rage sati biyu ze dawo kafin nan ya sake roro abinda za'ayi hidimar biki. Da akwai Malam Mudan dan Bechi ne amma yana

yawan shiga Kano dan baya rufa wata biyu beje ba ta hannunsa Audu yakeyin aike ko su aika masa daga nan.

Wata sabuwa ce ta bullo daga bangaren Bara'atu yarinyar da Audu yake mutuwar so yake kuma burin aure, tun dama dai Babanta ya matsanta matuqa akan ta fidda miji, duk sa'anninta an musu aure har sun fara haihuwa kullum ta Allah se yayi wannan mitar amma Inna tayita danneshi saboda ita tana son Bara'atun da Audu to wannan karon yace ya gaji duk danginsu babu yarinyar data taba shekara goma sha Shida a gida se a kanta kuma bawai bata da masoya ba dan haka seji kawai Inna Hajara tayi ya karbi kudin auran Bara'atun da saka rana wata uku kusan lokaci daya ze kama dana Yakubu kenan.

Bara'atu tasha kuka hankalinta ya tashi batayi qasa a guiwa ba tayi tattaki ta samu Yakubu dukda yar kunya da suke a matsayinsa na yayan saurayinta haka ta ringa masa kuka akan yaje ya gayawa Audu karya bari a aura mata wani ba shiba, yana komawa gida kuwa ya sanarwa da Dada tace yayi shiri ya taho Birni dan daman tasan za'ayi haka, duk sanda Audun yaje seta masa zancen ya kamata yasan me suke ciki da Bara'atu se yace mata ba yanzu ba yana so abubuwa su qara daidaitar masa akwai shirye shiryen da yakeyi.

Dole Yakubu yayi tattaki ya tafi Kano wanda rabon shi da zuwa tun hutun makaranta wanda daga shi be sake dawowa ba shekaru hudu kenan.  Yakubu Kano be zarce ko ina ba se Tsohuwar makarantar Allonsu wato makarantar Gwani Musa dan yasan Audu bashi da wani masauki se can, sedai yayi rashin sa'a Malam ya sanar masa tuni Audu ya bar nan, ya kan dai kawo musu ziyara lokaci lokaci dan ba'afi sati bama yazo kuma Almajirai suna ganinsa a Kasuwar bakin Asibiti idan sunje yawo yace musu yanzu a Goron dutse yake zaune bedai san takamaiman wani guri a can din ba. Yana zaune a bakin Masallaci yana jira ko Allah ze kawo daya daga cikin yaran da sukace sun san inda yake zama a Kasuwa su rakashi sega Hayatu, yaron gidan da Audu ya yiwa aiki wanda Babansu ya kaisu makarantar Boko a lokacin.

Cikin mamakin ganin juna suka gaisa yace suje gida a can yaci Abinci yanata kallon Hayatun daya zama kalar yan gayu da gani ya fara jiquwa a Boko.

"Tunda ka tafi makarantar kwana shikenab bamu sake haduwa ba shekaru kusan takwas kenan amma banji dadi da Audu yace mun ka bar Boko ba, kaga ni yanzu haka ina shekarar qarshe a Jami'ar ABU zaria ina karantar Engineering da ace ka cigaba kaima yanzun ko baka gama ba kana kan hanya" Hayatun ya fada. Yakubu yayi murmushi kawai amma bece komai ba, duk wanda ze so masa da yayi Boko a

bayan kansa ne dan mafarkinsa ne ya zama Alqali tun besan me hakan yake nufi ba. Ganin bazeyi magana ba yasa Hayatu cewa ya tashi suje ya kaishi inda Audun yake dan shi suna haduwa sosai har inda ya kama hayar shago yake zaune a can Goron dutsen ya sani.

A kasuwa suka samu Audu yamma tayi anata hada hadar kasuwa dan a sannan ma ake cin kasuwar sosai, kayan yaji yake siyarwa a sannan da sauran kayan qamshi zuwan Yakubu tasa dole ya tattara komai suka tafi masauki. Seda sukayi sallar Magriba da isha, ya rasa ma me ze ajiyewa Yakubun, ya kwaso Wasu yadika dinkakku kala biyu kowanne saiti uku a ajiye masa sannan ya sake dakko Shadda dinkin babbar riga shima guda biyu ya ajiye yana cewa

"Na Baballiya ne ba'a gama ba, daman Juma'ar nan nake cewa idan Malam Mudan ya shigo zan hada masa yayo mun gaba dasu kar kaya suyi mun yawa idan na tashi tahowa"

"Yanzu dai duk ka ajiye wadannan ka saurari maganar da nazo maka da ita" Yakubu ya fada yaba tattare kayan gefe, Audu ya zauna yana kallonsa se a sannan ma ya lura da cewar Yakubun bashida walwala dukda dai shi daman bame hayaniya bane sosai. A taqaice Yakubu ya bashi Labarin daya gigitashi jin cewar an sakawa Bara'atu rana da wani dan uwanta ya shiga share zuba dukda qofar Shagon a bude take ga iska na busowa amma Audu zufa yakeyi kansa ya shiga sarawa jin ze rasa Bara'atunsa macen daya gama kwallafa duk wani buri na duniya akanta. Shikadai yasan irin tanadin da yakeyi akan auransu shine yanzu Babanta zece ya bawa wani ita.

"Shiyasa kullum Dada take maka magana akan kasan me kake ciki saboda gudun haka, ban dama Inna Hajara tana tataka ai kasan tuni Bara'atu ta dade a daki Bilki da suke sa'anni kana gani da ciki yana tsaya mata ai tayi yaya biyu ko uku yanzu tunda dai ga Aisha nan da ciki Auran bana se ita kake so tayita zama har se sanda ka gama shirinka duk sa'annin ta sunyi Aure har an fara zundenta a gari " Yakubu ya fada. Audu dai bece masa komai ba haka suka kwanta amma fa be iya bacci ba, cikin daren ya hada yar jakarshi, Asubar fari suka dauki hanya dan yace baze tsaya ganganci ba dole yaje a san me ake ciki amma da ransa baze bari wani ya auri Bara'atu ba.

Bayan dogon tirka tirka da yayyensu daga qarshe suka yarda zasuje tambaya masa Auran Bara'atun, sunje da fari Babanta yaso yayi gardama akan shi ya rigada ya amshi maganar wani ya basu haquri suka taho gida Hashimu har yana Allashi qara

ai gara haka, seya koma can Birnin da ya liqe yagani idan ze samu macen da zata aure shi babu wanda yasan saga inda yake kujifa. Kwana biyu tsakani Audu na kwance yana jinya tunda yaji cewar baza'a bashi Bara'atu ba sega dan aike daga gidansu akan Babanta yace ya turo yau a daura musu Aure ashe wai Rijiya ta durfafa dagaske zata fada idan ba'a fasa auranta da wancan ba, harta tsoma qafa daya babanta yaga dai dagaske bata hayyacinta shine yace ya janye amma fa sedai Audu ya turo yau a daura Aure dan muddin aka kai ranar daya saka da wancan tofa sedai ta mutu shine Innarya ta tashi Yayanta ta aikoshi, Audu najin batun ya miqe beyi wata wata ba ya kama hanyar Gona inda su Yakubu suke can suna gyaran kunya kamar wani yaro ya zube yana basu labarin abinda akace.

Daga qarshe dai Yaya Baba da wasu Abokanan wasansu biyu ne suka sake zuwa dan Hashimu yace ba inda zeje, an samu Baban Bara'atu ya haqurq da zancen daura aure ranar aka tsaida magana akan rana daya dana Yakubu. Da wannan farin ciki Audu ya koma Kano, dukda ba haka yaso ba. So yayi ace se yayi gida a Kano sannan zeyi aure dan biki yake so yayi irin wanda akeyi A Kano yayiwa Bara'atu lefw na yargata wanda ze zama abin tarihi a garinsu harda kewaye, amma yanzun ma bata baci ba, zeci gaba da qoqari kuma ko ba yanzu ba seya biya bashin duk abinda ya qudurci yi mata. A haka kwanakin Biki sukazo, a zatonsa za'a daura aurene kawai tunda kowa yasan bashida Mahalli yayi qoqari ya siyowa Bara'atu kayayyakin fitar Biki daga Kano aka dinko harda takalma da mayafai kala hudu yayi mata na yan birni. Ana saura kwana hudu daurin Aure ya tafi Bechi bayan yayi sallama da Abokanasa na kasuwa dana unguwa dukya shaida musu zeyi aure, amma biki ba yanzu ba suka hada masa gudummawa kuwa sosai har seda yayi mamaki, koda yake shidin ba daga baya ba gaskiya bashida rowa ko kadan, haka Biki, suna, ta'aziyya sedai idan beji ba suma duk sun masa Alqawarin idan biki ya tashi zasuje tunda yanzu abin yazo a qurarren lokaci basu shiryi tafiyar ba.

Ranar Juma'a aka daura Auran, na Yakubu aka fara daurowa da safe a can Rigarsu Balaraba suka dungumo da Amarya da yan uwanta, se bayan sallar Juma'a aka daura na Audu da Bara'atu. Murna kam ba'a cewa komai a gurin Dada da tasha kwalliya cikin kayan da Audu ya dinka mata, haka qannensa Bilki da Aisha sun sha Anko Baballiya kuwa shaddarsa iri daya data angwaye wanda dama Audu ya dinka musu da niyyar suyi fitar bikin Yakubu se gashi abu yazo a daidai. Qarfe tara suna can Majalisa da Abokanai ana ta shaqiyanci sega Baballiya da gudu yake fada musu wai an Kawo Amaryar Yaya Audu. Kowa yayi mamaki dan ko jiya da yaje gurinta seda suka sakeyin maganar tace masa Innarta tace se daga baya zata tare tunda abin yazo babu shiri Babanta kuwa Magriba nayi ya tada ballin se an kaita, an ce masa babu daki yace ta rakuba a na Babarsa da ya san be shirya auran ba yayi haka yan uwa suka rakota ita kam ko a jikinta dan ko cikin Rumbub gidan aka ce ta zauna shiga zatayi tunda dai burinta ya cika ta Auri Audu.

A dakin sa aka sauketa da qawayenta da zasu kwana, daren ranar Audu tunanin yanda zeyi kawai yake, da yasan za'ayi haka da ya ququta ko babu dabe itama an tayar mata da daki ko ciki dayane, haka dai gari ya waye, da hantsi yan uwan Balaraba suka gama mata jere tsaf irin na yar gata harda Kumbo nan suka fara shirin tafiya bayan sun qara damqa Amarta a hannun yan uwan Yakubu. Daga bangaren Bara'atu dai babu wanda yazo se qawayenta da suka kwana.

A can gidansu ana ta taqaddama tsakanin Babansu da Innarta akan yace ko tabarma baze kai mata ba tunda bata bi abinda yake so ba, ita kuma ta rantse se yayi, da yasan haka ne seya bata lokaci ita da take son auran zatayiwa yarta komai amma yanzu banda kwanuka babu abinda ta tanada dan haka dole ya fito da kayan gado danbaze barwa yarta abin gori ba bayan ba rasa abinda zeyi mata yayi ba gashi tun rana bata daga ba labarin jeran da akeyiwa Balaraba ya fara bazuwa a gari dan itama Babanta Attajirine a rugarsu kuma itace Auta a mata dan haka sun mata bajinta.

Hayaniyarsu har dakin Ilu Abokin Audu da suka kwana a gurinsa maqota suke dasu Bara'atun kuma dakinsa jingibe yake da dakin Soron su Bara'atu inda Innar tata da Baba suka shiga wai suna sirri saboda yan biki dake ciki se gashi Audu yaji komai, sulalewa yayi ya tafi cikin garin Kumbotso saboda yafi masa kusa akan yace ze tafi Kano, yasan gurin lokaci lokaci yana zuwa dan har Aboki yake dashi kai tsaye gurinsa ya tafi bayan sun gaisa be bata lokaci ba ya zayyane masa abinda yake tafe dashi na batun kayan daki saboda garinsu Babu Kafinta meyin kayan katako, gadon qarfe kuma a gurinsa shi da yake zaune a birni yake ganin kayan gado da akeyi na Alfarma ya fitar masa yayi.

Nura ya kaishi gurin wani Kafinta da ake ji dashi a Kumbotso dan a Kano ya koyo aiki wasu kayan ma daga can yake dakkowa ya kawo. Ya numa masa wani Gado Lamba 1 da Kobud dinsa me biyu ta yan gayu dan harda mudubi a jikin murafenta ga kuma mudubi shima me durowa uku a jiki kayan sunyi kyau gasu Ruwan Hoda irin kalar da Bara'atu take so sedai kudin da aka saka musu a yanayin da yake ciki sun masa yawa ga Katifa da ze siya da pillo, aka tirza aka tisa dakyar dai kaya suka siyu, shima seda Nura yayi masa ciko daga baya zasu warware tunda suna haduwa A Kano, aka loda masa su a A kori kura da dundumemiyar katifa da pillow biyu harda Abin shimfida dana rufa ya kama hanyar gida.

Sanda ya dawo yamma tayi rana na gabda faduwa, a waje ya bar masu mota ya shiga ciki nan ya tarar da Dada da yan uwanta da basu wuce ba suna ta kiciniyar kwashe yan kayayyakinta ana shigar dasu dakinsa nasa kuma suna waje da alama dakinta za'a mayar dasu daman ba wani shirgi ne dashi ba Gadon qarfe ne da wata Katifa da yake ta saka ranar canzata tunda ba kullum yake kwana a kai ba se yayi ta mantawa se akwatinsa guda daya. Kunya ta kamashi yanda aka faka kayan a gefe, kenan Dada dakinta zata basu kuma wannan Gadon za'a sakawa Bara'atu

"Yawwa ga Audu" Matar Yayan Dada da basu yada zumunchi ba ta fada dan tun safe ake nemansa an rasa shi ga babu waya bare aji inda ya tafi. Dada ta yafa gyale ta yafice shi suka yi soro, Goggo Fadi, Maryo da sauran Maqwafta yan tsogumi da suka baza tabarma, sun gama kallon dakin Balaraba suka fito aka kafa gulmar ana jira aga me za'a sakawa Bara'atu ita kuma,

"Koda yake ina dakin ma?" Fadar Goggo Fadi, Maryo ta karkace baki tace

"Dukdai qaryar Birnin ta qare, ayita zuwa ana burga a bikin jama'a ga nashi ya tashi ko dakin da za'a ajiye Amarya babu idan da gaske da kudin ai daga tsaida rana yaci a dora ginin Bulon sumunti ma bana qasa ba" suka tafa da matar Hashimu dake kusa da ita.

Dada kuwa suna zuwa zaure tace

"Ina ka tafi Audu bayan kasan halin da ake ciki babu inda dan uwanka bw zaga a garin nan ba amma ba'a ganka ba Jama'a har ana cewa ka gudu". Dariya ta kwace masa yace

"Na gudu kuma Dada naje ina kamar wani mara gaskiya?"

"Oho dai duk ba wannan ba, Hasiya tazo ta gaya mun Baban Bara'atu yace bazeyi mata kayan daki ba, da ace mun san da tariyar nan da tuntuni mun fara shiri amma yanzun ma se ayi amfani da abinda Allah ya hore, na bar muku dakina tunda kaga yafi girma ni se na koma na Malam, Babana kuma ya shiga cikinsu Idrisa (Yaran Yaya Baba da suke zama a gidan) kafin muga abinda Allah zeyi, idan an kwana biyu filin can na gefe seka shigo mata dashi ayi bandaki da gurin girki irin na Yayanka kaga shikenan a sannu Allah ze hore duk kuyi muhalli irin wanda kuke buri, wancan gadon naka ma gaskiya Audu ba'a bawa Amarya ba ga Katifa duk Babana yaci qaniyarta idan da sarari ko katifa ce ka siyo da ledar daki a shimfida mata".

"mma Dada da baki fita daga dakinki ba wancan dinma ya isa ta lallaba kafin muga abinda Allah zeyi" Audu ya fada, Dada ta juya tana cewa

"Kaje dai muga ko katifar da Ledar zasu samu" ya tsayar da ita yana cewa

"Shaf na manta da Ledar wlh sedai ko Bilki taje yanzu inda za'a samu, leqa kiga ga kaya nan dai na samu dukda dai nasan basu kai yanda akeyi ba".

Dada ta leqa, baki ta saki ganin kaya tuni kuma yara da matan Unguwa da sukazo shiga gidan suka baibaye motar ana kallo dan ba'a taba ganin irinsu a garin ba.

"Audu, Kano kaje har ka dawo wannan kaya haka?" Dada ta fada cikin mamaki, Audu yayi murmushi yace

"A turo Bilkin ta samo Ledar tunda ita akw fara shimfidawa ko anjima zan miki bayani.

Dada ta koma ciki bakinta a washe yaqi rufuwa ta tura masa Bilki. Gidanta ta tafi ta dakko ledar data siya take shirin canza ta dakinta bata rigada ta shimfida ba dama ta bari se an gama hidimar Biki nana da nan aka hadawa Amarya daki ga gado na Alfarma kamar wani gidan zoo haka mata keta leqawa masu gyaran daki na korarsu dan sun hanasu yin aikinsu yanda ya kamata tuni kuma labari yakai wa Innar Bara'atu, ta fashe da kuka tana cewa

"Allah na gode maka daka nunawa masu gulma da munafurci qarshensu" tun safen suke qullawa da warewa da yan uwanta akan yanda za'ayi, ta hada dan abinda ya samu, Gadon katako taso tayiwa Bara'atu dan ance Amaryar Yakubu ma shi aka mata amma abinda suka hada baze isa ba kuma wanda za'a tasa ya tafi Kumbotso a yammar shine aiki har sun saddaqar a dauki na qarfen anje shima me siyarwar wai baya nan abin duniya duk ya mata yawa sega wannan labarin farin cikin dukda tasan wata sabuwar gulmar za'a samu ace Miji ne yayi mata ko babu komai sabon salo ne dan babu yarda Miji yaso haka a garin har yayi mata kayan daki.



Kafin dare dakin Amarya Bara'atu ya dauki haske bakin yan gulma yayi muqus qiri qiri Goggo Fadi ta kasa boye baqin ciki da wannan abu ta ringa yada magana wai Dada tadai tsananta binciken inda Audu yake samunkudi haka ya za'ayi ace daga fita ya dawo da irin kayan nan waya sani ma ko wasu ya bige ya dakko? Ita dai Dada tun tana mamakin lamarinta harta dena, a zamansu idan aka ce mata wata

rana Goggo Fadin zata zama yanda take a yanzu qaryatawa zatayi se gashi da ido ta take gani bawai fada mata akayi ba.

Innar Bara'atu ta aiko da kwanuka da tayi tanadi aka jere masu reras tun daga qasa har sama. Tana can bagaren Balaraba tun safe Dada tace suje can da qawayenta suyi wanka suka karya nan suka hade da qawayen Balaraba ana ta raha har dare kafin suka fara shirin tarar Angwaye. A bangaren Balaraban tayi wanka tsaf ta shirya cikin daya daga kayan daya dinko mata daga Kano, Balaraba ta bata Humra ta shafa dan ita dai babu shiri aka hankadota, suna zaune Aisha tazo tace au koma can an gama gyara mata daki suka bar Balaraba da nata qawayen can kuwa se santin daki sukeyi qaunar Audu ta sake linkuwa a zuciyarta ko banza ya fitar da ita kunya ya mata abinda tasan ko Baffabta bazeyi mata kamarsa ba.

Se qarfe Goma Aka rako angwaye, Yakubu aka fara rakawa tunda shine babba kuna duk Abokanan nasu daya, bayan barkwanci da abinda aka saba akayi siyan baki sukayi musu yar nasiha da tunasarwa akan aure da qalubalen dake ciki dan gaba daya Abokanan da sukayo rakiya su bakwai mutum daya ne mara aure wasu da yayayensu dan haka sun san yanda lamarin yake nan akayi addu'a suka sallami yammata wadanda zasu tafi gidan Fadima Amaryar da su Balaraban suka kawo garin harta hadu da Yakubu. Daga nan aka raka Audu, basu jima ba nan ma akayi addu'a kowa ya watse suka raka Abokanan qofar gida kamin suka koma ciki, Yakubu ya shige bangarensu bayan yayiwa Audu sallama ya sakace qofa, Audu ya tsaya kawai yana tunani, duk yanda yaci burin ranar auransa gashi bata zo masa a yanda yake mafarki ba.

Lissafi yake yanzu Yakubu Asirinsu a rufe suna da komai a bangarensu babu wanda ze san me suke ciki amma shifa? Rufin asirin ma bandakin da yake kusa da ace har yanzu da tsohon suke Amfani da tareren yayi yawa. Haka ya shiga daki jiki babu karsashi sosai ya saka a ransa bazeyi komai ba har se randa ya samu yanda yake so dangane da muhalli. Bara'atu ko harta fara gyangyadi akan sabuwar Katifa daman jiya ba wani baccin kirki sukayi ba kuma sun tashi da wurwuri motsinsa ya farkar da ita ta shiga jan mayafi tana boye fuska. Ya bude musu Kazar da suka shigo da ita dakyar ta iya ci saboda Yunwar da takeji taci kadan tasha ruwa tace ta qoshi.

Qofa yaji ana kwankwasawa, seda ya tambayi waye yaji muryar Inna Hasiya, ya bude ta miqo masa wani qaton Flask din ruwan zafi wanda ya siyawa Dada a Kano guda biyu saboda lokacin sanyi dukkansu cike da ruwa tana cewa

"Da akwai na sirki nan cikin bambu", ta sake miqo masa wani kantamemen baho irin na wankan Jego tana cewa "Allah ya tashe mu lafiya".

Kamar wani munafuki haka ya tattara bahon da fulasan gefe ya ajiye ya kalli Bara'atu data takure a gefen gado kamar jinjirar kyanwa yace

"Kiyi shiri ki kwanta dare yayi"

Da "toh" ta amsa masa ta miqe amma duk ta diririce ta rasa abinyi fahimtar kamar kunya takeji yasa ya fita ya tsaya daga qofar dakin, yana fita ta bude jakar da aka sako mata yan kayanta. Doguwar rigar yadi me laushi ta ciro da qaramin Hijabi. A gurguje ta shirya, ta ninke wanda ta cire kafin ta haye gado ta duqunqune kamar me bacci daidai nan Audu ya shiga dakin. Shirin baccin shima yayi, ya hau kan gadon yanajin wani banbara kwai wai yau shine gado daya da mace.

Dukda yanda yayiwa kansa Alqawarin baze tabata ba har se sunyi kebantaccen guri kamar nasu Yakubu amma ya kasa, cikin tattali da tsantsar So ya mayar da ita tasa, a cikin daren ya taimaka mata ta gyara jikinta kamar yar baby haka ta shige bahon ta gasa jikinta tsaf kamar yanda yayarta ta gaya mata kafin tayi wankan Ibadah dukda kunyar idon Audu haka ta shirya shi kuma ya juye ruwan bokiti ya fita dashi ya dawo ya goge gurin tas kafin ya sirka wani ruwan ya dauko fitila ya wuce bayi. Seda yayi wanka shima ya shirya kafin ya kwanta gefen Bara'atu da tuni bacci ya kwasheta, wani irin farin ciki da annushuwa yake ji, daman haka auran yake? Kai dole ashe Abokanan sa su ringa cewa Aure da dadi.

Ya tuna Yakubu ma yana can yana kashe Arna qilan yanzu shi kadai kamar sabon kamu ya fashe da dariya a haka bacci ya dauke shi shima cike da nishadin samu Bara'atun tasa a yanda beyi tsammani ba.

Kiran sallar farko ya farka dan ya rigada ya zame musu jiki tun suna qanana da an kira sallah Malam ze tayar dasu suyi nafila kafin lokacin Asuba su fita masallaci shiyasa jikinsu ya saba duk gajiya duk bacci basa tsallake wannan lokacin se sun farka. Motsin saukarsa daga gado ya farkar da Bara'atu wadda itama bata da nauyin bacci. Ta kasa kallonsa yayi murmushi yace

"Ki kwanta, kiran farko ne". Seta tashi zaune sosai a kunyace tace

"Ai bazan iya komawa baccin ba".

Audu ya dakko baho ya zuba ruwan zafi ya sirka, ya sake hada wani a buta kafin ya kalleta yace

"Toh gashi nan ko zakiyi amfani" yana fadar haka ya dauki wata butar daya cika da ruwa ya fita daga dakin dan bata sarari. Seda ya kalli bangaren Yakubu da suka garqame qofa Asirinsu a rufe babu wanda yasan halin da suke ciki kafin ya wuce Bandaki ya kama ruwa yana cikin daura Alwala aka haskoshi, ya kare fuskarsa tareda kallon inda hasken yake tahowa saga bangaren Goggo Fadi ne, da alama kuma inda yake take nufowa seya dauke kai yaci gaba da Alwalarsa harta iso kansa tana cewa

"Har gabana ya fadi wlh na dauka gamo nayi" banza ya mata ya miqe ta sake cewa

"Aa, angwayene har aka iya miqewa da farar Asuba? Kaga bayan gudan namune ya fara alamun fadawa shiyasa naji tsoron karna shiga da duhu na rufta kafin a kawo mun agaji ma qila na nutse ina Amaryar, ta tashi ko se an kawo Agaji?"

Tsabar takaici harya tsaya ze bata amsar maganarta ta farko amma qarshen yasa ya wuce ba tareda ya ce mata komai ba, wai a kawo agaji ita dai tana tsufa amma se a hankali. Dakin ya koma lokacin Bara'atu ta fita daga ruwan data ji dadinsa sosai ta daura alwala tana tsaye tana tunanin yanda zatayi da ruwan ya shiga dakin. Kamar dazun ya sake juyewa a Bokiti ya dauraye ya fita dashi ya zubar can bakin rariya ya kife bahon qofar Dada tunda ya gama amfaninsa ya koma dakin, seda yayi Nafila kafin aka kira sallah dan haka ya dauki carbinsa ya fita daidai nan Yakubu ya fito daga bangarensa suka rankaya suka tafi masallacin duk su biyun babu me cewa komai suka zama kamar wasu surukai kowanne fuskar sa cike da annuri irin na sababbi Angwaye.

Bayan an Idar da sallah Abokanan su suka tare su da tsokana, nan suka zauna har gari yayi haske kafin suka doshi gida seda sukaje soro kuma suka tsaya saboda jiyo muryoyin mata alamar kowa ya tashi har an fara hidimar gida. Audu ya kalli Yakubu kamar tababbu suka fashe da dariya lokaci daya harda duqewa kowanne shiyasan dalilin dariyarsa. Yakubu ya kalli Audu yace

"Bazan iya shiga gidan nan ba kunya nakeji"

"Ai gara kai daka sha kunu ka wuce ka sakayo qofa shikenan ka gama abinda zakayi a ciki ka fice ni kuwa komai zanyi akan idon mutane" cewar Audu.

Shigowar Aminu ta sakasu shiga gidan dole yana ta tsokanarsu shima, a dakin Dada suka yada zango suka gaisheta kamar yanda suka saba, bakinta kamar ze yage

saboda farin ciki, yau din wata ranace ta musamman a gurinta burinta ya cika na ganin Yakubu da Audu a matsayin magidanta sauran mata Autanta Baballiya da tasan ba lallai tayi tsahon ran da zataga wannan lokacin ba. Seda gari ya gama wayewa tangarau kafin kowanne ya koma dakinsa. Bara'atu na kishingide ya shiga ta miqe ya kalleta da murmushi yana cewa

"Aa yi kwanciyarki Jaruma"

Ta rufe fuska da Hijabin jikinta jin abinda yace wai jaruma, to jarumtar me tayi?"

Muryar Inna Hasiya dake magana ta sakashi fita ya dawo ya kwashi fulasan jiya ya kai mata ya tambayi Bara'atu Qaramin fulas din Shayi ko Jug ta nuna masa inda suke ya dauka ya fita ya kaiwa Innan daga can ya wuce dakin Shafi'u inda yayi ajiyar kaya.

Inna Hasiya tayi sallama Bara'atu ta amsa kafin ta shiga da fara'a Bara'atu ta miqe ta karbi kayan dake hannunta kafin ta duqa har qasa ta gaidata ta amsa tana tambayarta kwanan baqunta ita dai se murmushi take Innan tace mata

"Ga ruwan wanka can a kewaye kije kiyo se ki karya sannu ko" ta fada cikin tausasawa. Kan Bara'atu na qasa tace

"Toh Inna, amma Kwandon wankana yana bangaren Yaya Balaraba a can na barshi jiya"

Cikin jin dadin Yayar da ta kira Balaraba dashi Inna Hasiya ta fita da zummar karbo mata, a hasashe dai Hafastu tayi dacen surukai masu tarbiyya da kuma kunya. Seda ta dauki abin karin su Yakubu wanda Bilki ta ware kafin ta kai musu ta kuma karbowa Bara'atun kayan wankanta. A bandakin ta tarar da Ruwa har bokiti biyu, tayi wanka me kyau ta gasa jikinta dan ruwan da zafinsu kafin ta fito tana sunne kai dan Inna Hasiya da Bilki na tsakar gidan, dab da zata shiga daki Goggo Fadi ta taho tana cewa

"Aa Amarsu wanka akayi?"

Bara'atu ta durqushe tana gaisheta ta amsa fuska washe da fara'a, Inna Hasiya da fuskarta ta hade bayan fitowar Goggo Fadin tace

"Tashi maza kije ki shirya karki bushe".

A dakin bayan ta shafa mai ta ciro wata yaluwar Atamfa me ratsin fari dinkin Tazarce riga ta wuce guiwa an tsagata daga gefe gefe se zani ta saka. Ta bude qaramin kwandon da aka zuba mata kayan kwalliyarta. A qyalle ta zazzaga powder ta shafa ta dakko jagira tana niyyar zanawa se kuma ta dakata. Kwalliyar Balaraba ta jiya ta tuna, daga ita har qaqayenta da sukazo daga ruga babu wadda zakaga dambareriyar kwalliya a fuskarta hoda kawai suka saka se kwalli da man lebe kuma sunyi kyau kodan kasancewar su fararene oho?

Dukda cewar a ruga suke amma sun fita ita da nata qawayen wayewa ta ta'allaqa hakan da cewar garinsu Wailari yafi nasu kusada Birni har wasu daga cikinsu sukan kai tallar Nono cikin Kano qila a can suke gano kwalliya irin ta matan Birni wanda daman Audu yana kwatanta mata sam baya son wannan Jagira dasu jambakin da suke cike fuska dashi amma ita a ganinta idan ba tayi haka ba ba kwalliya tayi ba.

Zuciyarta ta shawarta mata ta gwada simple kwalliya irin ta Balaraban dan haka ta ajiye jagirar, brush ta dauka ta taje girarta da take a cike me kyakykyawan yanayi kamar an zanata fitina take sakata dambara baqin jagira akai ta qarawa fuskarta da bata haske baqi. Bayan ta taje girar ta saka kwalli a dara daran idonta, bazata iya haqura da jambaki ba dan haka ta shafa kadan ta kawo man lebe me kyalli da Audu ya sako mata a kayan fitar biki ta dora akai ita da kanta ta ringa sakin murmushi ganin yanda tayi kyau, fuskarta har qyalli take cike da Annuri irin na Amare. Ta mayar da kayan kwalliyar ta feshe jikinta da turare kafin ta ware dankwari bayan ta gyara zaman ribbon din data tufke jelar Shukun da aka mata. Daurin Maryam Babangida tayi wannan kam gwance ita a gurin kashe dauri, ta ringa juyi a gaban Kwabarta me mudubi daga sama har qasa tana dariyar yarinta dan tayiwa kanta kyau Addu'a take Audu ya shigo ya ganta taji me zece.

Motsin qofa yasa ta nutsu ta shiga neman farin gyalen data fitar tareda kayan. Audu ya shigo da sallama hannunsa riqe da Baqar leda babba kana gani kasan gwangwanaye ne a ciki ya kalli Bara'atu fuskarsa ta sake washewa zuciyarsa tacika da alfaharin kasancewar ta mallakinsa ita kuwa se sunne kai take na kunya. Ya kalli kayan karin da aka ajiye musu alamar bata ci ba yace

"Kar abincin ya huce kizo kici" a kunyace ta zauna qasa, ya fitar da gwangwanin Madara Peak dana milo se sukarime iyali kwali biyu ya ajiye mata ya juya da ragowar yana cewa

"Bari na kaiwa su Yakubu".

Kicibus sukayi da Bilki, ta miqo masa Babban farantin silba da aka dora kwanukan samira guda biyu se ledoji farare da aka qullo Madara, Milo da sugar tace

"Gashi farfesun Inna tace nata ne ita kadai ta ci ta shanye romon" ta fada cike da shaqiyanci tana kallon Bara'atun, ta dago kuwa ta maka mata harara, idon Audu ne yasa bata bata amsa ba tunda su din qawayene daman sun saba da caccakar juna. Audu ya karbi Farantin ya ajiye ya kwashe kayan shayin cikin ledar wanda yasan cikin manyan gwana gwanan da yake siyowa Dada duk sanda ze zo aka debo yace

"Maida su na taho mana da namu mantasu nayi dakin Shafi'i"

"Toh Yaya" Bilkin ta karba ta cigaba da tsayuwa dan so take ya fita ta tsokani qawar tata, karantarta yasa yace mata

"Muje toh" ba yanda ta iya ta fita amma dai ze fita ya barsu a gidan yau kam Bara'atu ta banu a gurinta dan dalilin daya sakata kwana a gidan kenan ma.

Tare suka karya da Bara'atun dukda yanda take ta noqewa bayan sun gama ya miqe yana cewa

"Zanje dakin Shafi'i nayi wanka, idan kina buqatar wani abu ki aiko yara su gaya mun"

"A dawo lafiya" ta fada tana miqewa itama bayan ta hada kwanukan da sukaci abinci dasu suka fito a tare bayan ta saka takalmi. Gurin da taga an tara wanke wanke ta ajiye na hannunta Audu kuma ya fita daidai nan Balaraba itama ta fito da nasu kwanukan tasha kwalliya kamar dai Bara'atun, suka sakarwa juna murmushi ta ajiye kayan hannunta kafin suka shiga gaisawa. Dakin Dada suka nufa tare suka tarar suma sun gama karyawa kenan Bilki na tattare guri Baballiya na kwance kamar gawar sababi yana tabara ko kunya bayaji waishi Auta.

Inna Hasiya ta dana masa duka tana cewa

"Dallah tashi ka basu guri su zauna", Dada da bakinta yaqi rufuwa se sannu take musu suka zauna kowacce na sunne kai suka shiga gaishe su. A mutunce suka amsa, tamkar ba surukai ba haka Dadan ta ringa jansu da hira suna amsa mata daddaya cike da kunya Inna Hasiya ta fice tsakar gida se Bilki dake tsokanarsu Dada tana tare musu.

"Kuje ki rakasu su gaida Goggonku" Dadan ta fadawa Bilki, ta miqe suka bi bayanta suna fita ta dafa Bara'atu tana cewa

"Qawata ya kikaji Auran?"

Inna Hasiya ta rafka salati tana cewa

"Kin banu Bilki wannan fitsara har ina sirrin Yayan naki kike kiji kome? To bari Audun yazo daidai yake dake".

Bilki ta ringa dariya su Bara'atu dai se murmushi da haka suka qarasa dakin Goggo Fadi sun tarar da ita da Aminu wanda tun Asuba daya shigo gidan yana can kome suke tattaunawa se Allah. Cike da girmamawa suka gaidata ta amsa itama basu jima ba suka basu guri, bayan sun fito Bara'atu ta kalli Balaraba tace

"Muje kiga dakina nima" suka rankaya Bilki ta wuce gurin Inna Hasiya data kirata. A dakin Balaraba ta ringa santin kayan Bara'atu, hira suka shiga tabawa Bilki ta dawo nan ta tasasu gaba da tsokana suka ringa hira gwanin dadi kafin qawayen Bara'atu suka fara zuwa yan kwadayin ragowar kazar Amarya.

Kazar ta basu Balaraba ma taje ta dakko musu sauran tata dan ita qawayenta tasan yanzu sun kai gida tunda Asubanci me motar da ze mayar dasu yace zasuyi ze wuce Kano dakko kaya. Wuni guda tsakanin bangaren Balaraba da dakin Bara'atu sukayi shi, Inna Hasiya kuwa bata gaji da hidimta musu ba wanke wanke da shara babu yanda basuyi ta basu ba taqi tace su huta. Haka aka ci sati Angwaye da Amare na tsinkar furen qauna hankali kwance. Dukkaninsu sunyi bulbul abinsu kana kallonsu kasan basu da damuwa banda ma matsalar rashin sirri da take hana Audu yanda yaga dama wannan yasa ya quduri a ransa dole idan ya koma Kano kafin ya dawo ya gyara musu bangare a katange kamar na Yakubu dan gaskiya wannan zaman na kwarar sa.

Seda akayi sati hudu da biki kafin hankalinsa ya fara komawa Kano dalilin yan kudaden hannunsa sunyi qasa ga hidimar yauda kullum a wannan rutsin kuma ya sake fahimtar cewar a yanzu ne ma yake da dalilin tashi tsaye ya nemi kudi ka'in da na'in kodan Iyalan da suka fara ajiyewa. Ya fara shirin tafiya, da daddaren ranar ana saura kwana uku ya koma Kano ya samu Dada da zancen ya kamata Yakubu ya koma yaci gaba da karatunsa.

"Dada yanzun nauyi ya hau kanmu, bazan so mu qare rayuwarmu cikin wahala tamkar ta mahaifinmu da sauran yan uwanmu ba kina kallo dai yanda suke fama basu da wata tartibiyar madogara se Noman da sukeyi.

Karatun Yakubu nada muhimmanci na farko Burinsa ne na biyu kuma idan ya kammala ze samu madafar da ze riqe kansa tunda shi ya gaza maida hankali akan Kasuwanci kamar ni kuma gaskiya bazan zuba ido ina kallo da quruciyarsa aikin wahala ya kashe shi ba dan haka kiyi masa magana ya bar duk wani abu daya dauka yazo mu koma Kano ya zana jarabawa yaci gaba da karatunsa".

Dada tayi shiru tana nazarin maganganun Audu tabbas gaskiya ya fada yanzun nauyi ze qarar musu kuma baze yuwu ace shi kadai zeci gaba da daukar ragamar gidan gaba daya ba. Ta numfasa tace

"Zanyi masa magana babu damuwa da yardar Allah".

Hakan kuwa akayi Dada tayiwa Yakubu magana take ya nuna rashin Amincewa da maganar a cewarsa idan duk suka tafi Birni waye ze ringa Kula da Dadan da yaran mutane da suka Auro? Dada tayi dariya tace

"Kai dai kace bazaka iya tafiya kabar matar kaba" Yakubu ya sunkuyar dakai kamar ya nutse dan kunya ya kasa cewa komai se Dada ce taci gaba da cewa

"Kodan saboda su karatun naka nada muhimmanci Yakubu a yanda Audu yayi mun bayani. Idan ka duba kwanannan nauyi ze qarar mana, badi iyanzu idan muna da rai kun dauki Yayanku akwai buqatu marasa yankewa da zasu qaru kaga dan uwanka yana matuqar qoqarinsa akan mu, idan ka gama Karatun zaka samu madogara tunda ga Fa'izu (yaron me gari da shima ya kaishi Kano yayi karatu) kaga yanzu maganar da akeyi yayi hanyar da Gwamnati zata gina mana Firamare a nan qauyan dole za'a nemi malamai, kaga ko wannan aikin ka samu tunda ance biya akeyi ai an samu madogara seka hada da yar sana'ar da kakeyi Asiri ze rufu kodan saboda dan uwanka ka daure ka cika burinka wanda har ya fika damuwa da hakan".

Haka dai Dada da Audu sukayi nasarar tausarsa ya yarda ze koma Kano ya ci gaba da karatunsa, tafiyar Yakubu data taso ya saka Audu qara kwankin tafiyarsa dan su shirya a tsanake. Ana saura kwanaki biyu su tafi da daddare Hashimu da yayi balaguro tun daurin auran su Audu da kwana hudu ya dawo gari. A daren ranar suna zaune a dakin Dada Malam, dan gurin Mairo ne yayi kiransu inji Baba Hashimu. Audu da Yakubu ne sukaje, yana zaune tareda Goggo Fadi suna hira gabansu Kaza ce gasashshiya suna ci Audu da Yakubun suka samu guri suka zauna suka gaishe su. Hashimu ya cire tsinken da yake sakace dashi ya kalli Audu yace

"Naji labarin kuna shirin Tafiya Birni shine nace kafin ku wuce ya kamata mu zauna muyi magana, so nake yi ku siyar mun da barin gonarku ya zama mallakina tunda dai ba nomawa kukeyi ba, abincin ma idan an baku saidawa kuke kun koma cin kalar na Birni se shinkafa da Taliya ko?" Ya qarashe cikin sigar tambaya.



Yakubu ya nisa yace

"Ban fahimce ka ba Yaya, kaji labarin muna somu siyar da gonar ne ko yaya?"

"Ko daya, ina dai so ne nasiya kuma a shirye nake ko nawa kukayi mata kudi zan biya" Hashimun ya sake fada, Yakubi ze sake magana Audu ya tareshi yace

"Shikenan zamu siyar, Allahya kaimu safiya se a kira su Malam Audi suyi mata daraja daga nan se muga yanda za'ayi" yana gama fadar haka ya miqe dole Yakubu ya bishi ze fara masifa Audu yayi masa alamar da yayi shiru, daga cikin dakin suka jiyo dariyar Goggo Fadi Hashimu kuma yana cewa

"Sunyi kyan kai dan ko basu siyar munta arziqi ba to zasuyi Asararta a banza"

Wannan magana ta daurewa Yakubu kai ya kasa fassara abinda yake nufi a haka suka koma dakin Dada take Audu ya gaya masa dalilin kiran, Dada tayi shiru kafin tace

"To me kuka ce masa?"

"Nace masa zamu siyar da safe zan nemo au Malam Audi ayi mata kudi"

"Amma meyasa Hashimu duk gonakin da suke garin nan se tamu zece ze siya kuma..."

"Dada, dan Allah kar a tada maganar nan, gona yake so ko za'a siyar masa daga nan a raba kudin kowa ya kama abinda zeyida kasonsa" Audu ya katse Dadan se sannan Yakubu yayi magana yace

"Wannan ma ai maganar banza ce, ta yaya zamu siyar da abinda ita kadai muka mallaka ciki muke ci muke sha? Kai me yasa baka lissafi ne kawai abinda kwakwalwarka ta gaya maka kakeyi?"

"Kadaiji da kunnenka abinda ya fada shawara ta rage taka ko ka bari a karbi kudin ko kuma ta salwanta a banza kaga munyi asara da hujja" Audun ya fada yana miqewa yayi musu sallama ya fice daga dakin yana tafe yana tuna Gonar Baffaye wani tsohon Abokin Malam ne da gonarsa take gabas da tasu, bara waccen shekaru uku kenan Hashimun ya nemi ya siyar masa dan harkoki suna ta bude masa babu kuma wanda zece ga inda yake samun kudi Baffayen yaqi, daminar Bana yayi shuka lafiya har ta fara yabanya haka kawai aka wayi gari komai ya bushe shekarar haka ta qare ko Kara be cire a gonar zancen da akeyi yanzu gonar ta zama tamkar kufai, aciki ne ma ake zaton Gwamnati zatayi ginin firamaren da za'a bude wadda me gari ya bashi shawarar ya bayar dan abinda za'a biyashi ya nemi wata ko qarama ce ya siya.

A labarin daya ringa kewaya gari ance anga Hashimu yana zagaya gonar da dare bayan sunyi zancen cinikin Baffaye yaqi wanda ba'a kwana biyu ba wannan ibtila'i ya fadawa Baffaye, bawai ya yarda da abinda aka fada ba amma kalaman Hashimun na dazu sun saka qara masa hujja nacewar ze iya yi musu mugunta a kan Gonar. Ransa fal da baqin cikin hanyar da yan uwan nasu suka dauka bayan gushewar Malam da bashida burin daya wuce ganin sun hada kansu amma abu ya gagara, haka ya kwana da takaicin abin a zuciyarsa washe gari kuwa qarfe goma na safe gaba dayansu suka hallara yan dakin Goggo Fadi dana dakinsu. An kirawo Dillai a gaban kowa sukayi wa gonar kudi da daraja abinda ya qara qonawa Hashimu rai dan kafin zuwansu seda ya samu daya daga ciki har cin hanci ya bashi akan su kassara farashin gonar, haka ya tishe kudin cas ya basu abinda ya qara bawa kowa mamaki su kam sun rasa a ina Hashimu yake samun kudi haka.

Audu da yan uwansa suka qule a dakin Dada, Yakubu nata fada akan abinda ya faru, Bilki da Aisha ma dai sunbi sahun Audu nayin amanna da siyar da gonar dan har Bilki na cewa daman taji a bakin Mijinta Hashimun na fadar koda tsiya se ya mallakin barin gonarsu ya zama nasa to gara da kayi ta arziqi shikenan.

Audu ya kalli Dada yace

"Yanzu ya za'ayi da kudin nan?"

"Ni a ganina a nemi wata gonar a siya idan yaso ko haya ce a bayar ko kuma a nemi ma'aikata su ringa nomawa ana biyan su lada" Dada ta bada shawararta, Audu yayi shiru kafin ya kalli Yakubu yace

"Kai kuma ya kake gani?"

"Daka zarce hukuncin a siyar da baka shirya abinda za'ayi da kudin ba?" Yakubu ya fada a cikin fada Dada ta daga masa hannu tana cewa

"Bana son haka, karka kuskura ka saka wannan abin a ranka balle har sabano ya shiga tsakaninka da dan uwanka. Kaifa ka gaya mun abinda kukaji ya fada jiya, kasan hatsabibancin Hashimu, ladan hayar da suke bamu kana kallo lalataccen da kwari suka taba ake tattarowa a bamu duk dan a zauna lafiya yasa ban taba magana ba yanzun daya nuna yana so gara a bashi dan qarshe zamu iya rasata baki daya".

Yakubu be iya cewa komai ba tunda Dada ta goyi bayan Audu, qarshe bisa shawarar Audu da Bilki suka yanke cewar za'a tada gini Jikin katanga a fitar da qofar

shago ta waje da kuma ta cikin gidan inda zasu zuba duk wasu abubuwan buqata da suke wahala a Qauyen, mutum daya ne yake shiga Kano yayo sarin kaya shima se yafi wata beje ba dan haka abubuwan buqatu da yawa sedai a haqura ayi amfani da wanda ya samu sannan Bilki tace tana so Audun ya ringa aiko mata da zannuwa da sauran kayan kwalliyar Mata daga Kano tana siyarwa dan shima Mace daya ke wannan sana'ar Asabe Dillaliya, sunyi na'am da shawarar, aka kasafta kudin kowa aka fidda masa rabonsa kafin suka sake hadesu Audu ya adanasu cikin kayan tafiyarsa.

Cikin abinda ya masa saura a hannu ya tafi Kumbotso dan yiwo musu siyayyar abubuwan amfani, dayace Yakubu yazo su tafi qi yayi dan har sannan a qule yake dashi, yasa an siyar da Gona kuma ba'a siyi wata ba an tattare kudi wai za'a juya su. Se ya liqis ya dawo Bechi niqi niqi da siyayyar da yayiwo, a qofar gidan ya tarar da magina sun jiqa gefe ga bulo da alama gini ake a cikin gidan. Ne damu dasu ba yayi musu sallama ya shige sedai abinda ya gani ya sakashi dakatawa tareda tsayar da yaran da suka tayashi daukar kaya.

Hashimu na tsaye da Malam Sha'aibu magino suna magana, ga katanga nan da aka fara dorawa daga bakin qofar soron har jikin katangar baya ta gidan da Alama an tasarma raba gidan ne. Bawai Rabawar ne ya bashi mamaki ba Aa yanda aka tada katangar idan aka gine ze zaman su basu da hanyar shiga bangarensu kenan ko kuwa Katanga zasu ringa tsallakawa oho.

Aminu ya fito daga dakin Goggo Fadi kana ganinsa kasan a fusace yake beko Iura da Audu ba ya kalli Hashimu yana cewa

"Tun wuri ka dakatar da wannan ginin wai me yasa duk abinda ze janyo tashin hankali a gidan nan shi kakeyi? Yanzu ta ina kake so su ringa shiga barayinsu?"

Cikin ko in kula Hashimun yace masa

"Ko su fasa wata qofar ko su siyi fukafukai duk matsalarsu ce gida ne dole a raba kuma a sannu yanda na raba su da gonar shima gidan seya gagre su zama sun barshi".

Zuciyar Audu ta harzuqa amma ya daure bece komai ba ya wuce da qafa ya tunkude bulon da basu gama kamawa ba aiki Yar katangar da ta fara tsayi ta ruguje ya shige abinsa yaran da sukayo masa dako suka bishi, a fusace Hashimu yabi

bayansa har qofar dakin Dada seda Audun ya dire kayan hannunsa kafin ya kalli Hashimu dake numfarfashi ze fara bala'i yace

"Idan ka manta bari na tuna maka soron a cikin rabon gadon mu yake, saboda idan muka ja katanga baku da ta inda zaku fasawa Mahaifiyarku qofar fita shiyasa muka barshi amma da tuni na dade da sakawa an toshe qofa mun canza mata fasali" yana gama fadar haka ya shige ciki ya bar Hashimu da yayi shiru yana tunani, tabbas gaskiya Audun ya fada Soron rabonsu ne tsabar shaidan da yake masa kururuwa yasa ya manta ganin yafi kusa da bangarensu idan kuma suka toshe din da gaske basu da kusurwar da zasu bullawa Goggo qofa dan ta bamgarensu sun fisu yawan dakuna haka zakila Kudun su da yamma jingine suke da gidaje babu damar su fasa qofa sabanin su Audu da suke ta gabashin gidan inda fili yafi yawa kuma babu gini jikin katangar ta bangaren.

Cike da borin kunya ya tafi yana cewa

"To se kuzo kuyiwa soron kudi a biyaku dan babu fashi gidan nan se an raba shi".

A cikin daki kuwa Dada ta girgiza kai mamakin lamarin Goggo Fadi da yaranta ya kasa sakinta a kullum sabon abu suke tsiro dashi to wai me yasa tun Malam na raye basu bayyana halinsu a fili ba se yanzu daya kau? A daren Audu da Yakubu suka tara matansu nan dakin Dada suka qara jan kunnensu tare dukda basu da matsala, lafiya lau suke zaune Dada kuwa a yaya ta daukesu ba surukai ba idan kaga yanda suke gwanin sha'awa. Kamar yanda suka fara girki daya sukeyi kuma a hakan zasu cigaba, Sadiya yar wajen Bilki zata ringa taya Balaraba kwana, da farko Innar Bara'atu tace zata turo mata qanwarta se daga baya kuma tace Babansu ya hana. Daga qarshe Abdullahi mutumin Audu dan gurin Aminu aka bata dukda Goggo Fadi da Hashimu basu so ba, da yake shima Aminun tsayayye ne yayi musu fes yace dan sa ne kuma ya bawa Audu halak malak ko bayan ransa yayi Tijara kafin magana ta Mutu Abdullahi ya dawo dakin Bara'atu lokacin shekarunsa hudu a duniya.

Audu da Yakubu sun dawo Kano cike da kewar Matayensu kowanne yana jin jiki haka suka duqufa abinda ya maido su, sunyi register rubuta jarabawar kammala Sakandire da suka ci sa'a daidai lokacin an fara kwana kadan suka rubuta cikin yardar Allah sakamako ya fito dukkaninsu sun samu sakamako me kyau. Yakubu ne ya tirsasa masa kan cewar seya rubuta dukda yace shi ba karatu ze ci gaba ba amma idan ya ajiye takaddar wata rana zatayi masa Rana. Kudin da suka zo dashi Audu ya zuba suka fadada kasuwancinsu, yayi sarin kaya masu yawa ya aika dasu Bechi an bude shago wanda dama sun bar alhakin aikin a hannun Mijin Bilki Baballiya ne yake zama kuma ba qaramin ciniki akeyi ba dan kusan komai na buqata an kai harda ma sababbin abubuwa a gurin mutanen qauyen ba'a rufa sati

biyu is anyi sabon sari an aika idan suka aiko da cinikin da akayi ta hannun Qanin Hayatu Mijin Bilki da yake jan motar kaya yanzun.

Tareda Yakubu suke fita kasuwa, tuni kuma an tayar da ginin filin da Audu ya siya a nan Goron dutse inda yake zama, filin nada girma babu laifi dan haka aka rabashi biyu shida Yakubu kamar yanda daman ya tsara. Gini aka tada daki ciki da falo kowanne se safaya guda daya da kuma kitchen da bandaki ginin bulo, idan ka shigo soron gidan daya ne sannan zaka tarar da qofofi guda biyu na shiga kowanne bangare. Yakubu ya dage akan Audu ya maida hankali gurin gyara nasa bangaren dan shi fa bega abinda ze rabo shi da Bechi ba, koda ya fara Karatu ze ringa tafiya duk hutu irin yanda ya ringayi lokacin yana makarantar kwana dan baze yuwu su tattaro su dawo Kano su bar Dada ita kadai a can ba ko bayan haka sam shi bashida sha'aqar zaman Kano ma baki daya haka dai aka ci gaba da rarrafa rayuwa watansu uku a Kano kafin sukaje ganin Matansu niqi niqi da abin Arziqi dan a watannin ba qaramin Alkhairi aka samu da kudin da aka juya ba ga can Shago da Sana'ar Bilki ma se sambarka.

Sun tarar da matansu da Dadarsu lafiya sumul ga qarin abin farin ciki Balaraba nada shigar ciki, wannan abu yayi wa kowa dadi, satin Audu biyu ya koma ya bar Yakubu dayace seya qara hutawa shi kuwa daya baro dukiya be bar me juya masa ba dole ya koma, kwanansa biyu da komawar shima saqo ya riskeshi wanda yakeyiwa Yakubu cuku cukun samun gurbin karatu ya aiko masa da cewar an samu dan haka Yakubu ya shirya ya tafi Domin har Samista ta fara nisa acan makarantar dole Audu ya juya Bechi. Dan qaramin yaqi sukayi da Yakubu sanda Audu ya gama wassafa masa abinda yake faruwa. Ya rasa me zeyi, ashe wai Audu can Jami'ar Ikko ya nemawa Yakubu gurbin karatun Shari'a ta hannun Tsohon Abokinsu na Magashi wato Hayatu duk a tunanin Yakubu anan kwalejin Shari'a da aka bude a Kano ze nemar masa Gurbin ashe shine dalilin daya sa be gaya masa komai ba akan zancen makarantar.

Yakubu yace ba zeje ba, ya za'ayi ma ya tsallake ya tafi har Kudu da sunan karatu? Idan jami'ar ce baga ta nan a Zari'a ba tunda ta kano basu fara karatun shari'a ba a sannan ko ba wannan bama shi karatun Jami'a ya masa girma a lokacin baze iya ba, seda Dada tayi masa wuji wuji sanna ya haqura.

"Me yasa Yakubu duk qoqarin da dan uwanka yake akanka baka gani ko da yaushe cikin gwasaleshi kakeyi? So kakeyi kuma ku zama kamar su ace babi jituwa bazaku hada kai da baki shawararku ta zama daya ba? Idan kuna haka suma qannenku abinda zasu dauka kenan ni kuwa fatana ko bayan raina ace duk abinda zaku zartar a tsakaninku se kun shawarci juna kuma babu babba ko yaro in har daya ya bada

shaqara me kyau da zata amfane ku ku karba ku zartar amma gashi kai da kake babba kai ne duk abinda aka kawo se kayi Adawa da hakan bana so bana jin dadi ka dena hakan" Dada ta fada masa.

Yakubu yayi shiru, har ga Allah baya jin dadin yanda Dadan take goyon bayan duk wani hukunci da Audu yake zartarwa dukda dai ba abu mara kyau yakeyi ba amma yin hakan ze saka ya dauka cewar komai yayi daidai ne ba kuma ze ringa duba muraden waninsa ba in har abinda zuciyarsa ta raya masa kawai shine daidai. A komai na rayuwa shawara nada kyau amma ya za'ayi ya ringa zartar musu da hukunci kamar wasu Yayansa ai ko Baballiya beci ace Audu ya turashi wani gari can karatu ba tareda son ransa ba balle shi da girmansa harda iyali ya ajiye ayi masa wannan abun yanzu haka ze tattara ya tafi ya bar yar mutane har tsayin wane lokaci ze dauka kafin yazo? Nan da Kano ma suna daukar watanni inaga Ikko da tafiyar kwanaki ce kafin kaje, anan cikin qauyensu da akwai Abokanansu biyu da suka tafi neman Arziqi shekara uku kenan zuwansu daya gida kuma sun basu labarin yanda Kudu take tayaya ma ze iya zama a can fisabilillahi amma ya ya iya? Yanda ran Dada ya baci yasan ko yayi mata bayani ba lallai ta fuskanta a fuskar salama ba.

Haka ya fara shirin tafiyar jiki a salube danma Balaraba ta dage da qarfafa masa guiwa tana gaya masa duk saboda ita da abinda zata haifa zeyi wata rana kuma komai ze zama labari a sannu idan yaje garin ma ya gane kan komai zasu iya tafiya tare dan ita akwai Yayanta da yake kai Shanu can Kudun saboda yawan zuwan da yakeyi ya kai matarsa daya can take zaune wannan yasa hankalinsa ya dan kwanta amma idan ya tuna ze tafi ya barta da ciki qila har se abinda zata haifa ya fara zama ko rarrafe ze zo ya ganshi duk se yaji abin ya qara fita a kansa. Haka ya shirya, duk wani abu da ze iya nema na dangin abincin da ba lallai ya samu can ba Dada da Balaraba sun hada masa. Harda dambun nama Dada tayi masa, gasu Yaji, quli quli harda Alkaki Audu ya ringa dariya wai kamar me tafiya qasar waje. Randa zasu tafi Kano Balaraba ta kasa daurewa ta ringa kuka duk ta qara sanyaya masa jiki dakyar ya iya tafiya Goggo Fadi da yan fadarta suka ringa yadawa Dada magana wai ta watsa yara sun tafi Bariki ga Yaran mutane sun auro sun ajiye wannan ai ba daidai bane iya dai bata kulasu ba suka gama jajanta tafiyar su Audun kafin kowa ya dauki dangana sukaci gaba da rayuwa yanda suka saba.

Audu kuwa seda ya raka Yakubu har Ikko, tafiya ce kamar ta yada shege musamman su da basu taba zuwa ba a hakan ma wai dan mota me kyau suka hau basu bi motar Arha wadda ake loda mutane ba. Satinsa daya ya juyo bayan Yakubu ya samu gurin zama ya gama duk wasu abubuwa har ya fara shiga aji. A dan tsukin Seda Audu ya leqa kasuwa ya gano sabgogin arziqi aiko ya qyarawa Yakubu da

zarar ya gama gane kan gari ya shiga kasuwar Hayatu ze taimaka masa ya dubo musu abubuwan da ake buqata a Arewa da suke sauqi acan.

Ya dawo Kano cike da kewar Dan uwansa ya kuma cigaba da kasuwancinsa ka'in da na'in, sabanin da da yake share watanni yanzu wata biyu yakeyi yaje Bechi wani lokacin ma wata daya da kadan zeje ya kwana uku ko hudu ya juyo haka ze musu siyayya kuma ya hada harda yan uwansa dukda barakar da suka samu be fasa yi musu ba suma kuma babu kunya basu qi karba ba. Balaraba nata rainon cikinta daya fito sosai yana wata na bakwai sannan. Ba yanda Audu beyi akan suje Kumbotso Asibiti ba tunda su nan babu amma Dada taqi a cewarta Ahalinsu kaf babu wadda ta taba zuwa wani Asibiti kuma lafiya lau suke rainon ciki su haihu duk wani taimako kuma daya kamata tana bawa Balaraban shima zaman Birni yasa har yake wani zancen Asibiti banda haka a garin kaf wayaga tana zuwa wani Asibiti banda Matar Shafi'i Hedimastan primary su Baballiya da aka bude.

Har fushi yayi amma Dada taqi saurararsa, ya samu Balaraban akan ta shirya a sace ze kaita dan shi fa ya daukarwa Yakubu Alqawarin kula masa da iyalinsa ba kuma yason kowanne tsautsayi ya gifta wani abu ya same su ma se Balaraba tayi dariya tace

"Bana jin komai Yaya Audu lafiyata qalau kamar yanda Dada ta fada in sha Allahu zan haihu lafiya base munje Asibiti ba daga can Rugar mu ma Innata tana yomun aiken saiwoyi babu wata damuwa da yardar Allah".

Badan yaso ba ya barta, watan Haihuwar Balaraba na tsayawa ya dawo Bechi yanda kasan shi za'ayiwa Haihuwar, kwanan sa biyu da dawowa Balaraba ta fara Naquda cikin dare har garin Allah ya waye bata haihu ba duk irin taimakon da Dada da Goggo Fadi tareda Unguwar zoman da suka kirawo suka baya amma abu ya gagara, haka ta sake wuni sur cikin ciwo kuma abin takaici sun hana akaita Asibiti acewarsu dama haihuwar fari akan dade, hankalin Audu ya tashi ganin har duhun Magriba ya fara kawo kai amma Balarana shiru zuwa sannan kuwa ko baa fada ba ka kalleta kasan qarfinta ya fara qarewa. Beyi shawara da kowa ba ya fita neman motar da zata kaisu Kumbotso, duk masu motocin daukar kaya na garin abin takaici kamar hadin baki duk gurin wanda yaje ae yace masa bashi da Mai yau ko aiki be fota ba.

Har gurin Alhaji Magaji yaje wanda a lokacin shi kadai yake da motar hawa a garin amma be samu alfarmar ya taimaka masa su kai Balaraban Asibiti ba ga duhu yayi dan tuni anyi magriba Isha ake shirin yi. Zuciyarsa ta quntata ya rasa abinda zeyi, be taba jin burin mallakar abin hawa na irin na wannan dare. Hankalinsa be qara

tashi ba seda Bara'atu ta fito tana kuka hankali a mugun tashe take sanar masa Jikin Balaraban ya qara rikicewa har ta fara zubda jini gasu Dada can duk sun rude suna salati. Suna tsaye nan cikin rashin mafita kamar daga sama sega Kasim, Abokinsa ne amma irin wanda alaqar bata da qarfi sosai. Audu ya sauke ajiyar zuciya yana yiwa ubangiji godiya daya kawo masa Kasim din. Alfarmar Baburinsa ya nema ya bashi haka aka cocciba Balaraba da sam bata cikin hayyacinta Dada ta hau bayanta suka sakata a tsakiya suka tafi Kumbotso aiko wannan abu ya qara hura wutar gori Goggo Fadi ta ringa masifa tana fadar maganganu cewar Dada batayi kara ba. Ita kuwa Dadan tsabar rudu da tashin hankali yasa sam bata san sanda ta haye mashin dinba dan gani takeyi idan wani abu ya samu Balaraba itace sila tunda babu yanda Audu beyi suje Asibiti ba tun gari nada haske.

Page 7

Cikin hukuncin Allah isarsu Asibitin babu jimawa Balaraba ta sauka sedai yar tazo babu rai wanda ko ba'a fada musu ba sun san wahalar data sha a ciki ce tayi Ajalinta ita kanta Balaraban babu yanda take hankulansu basu dan kwanta ba seda Likita ya tabbatar musu da Balaraba zata samu lafiya da yardar Allah. A nan cikin Asibitin suka kwana, da sassafe Audu ya tafi Bechi tareda gawar yarinyar can aka shiryata akayi jana'iza kafin Bilki ta hada duk abinda Balaraba zata iya buqata suka juya Kumbotso tareda Bara'atu da Mariya matar Aminu se Maimuna Amaryar Hashimu da itama tana hulda dasu Balaraban dukda mijinta baya so. Goggo Fadi data kwafe tun jiya cewa tayi ba zataje ba dan haka sula tafi. Seda Balaraba ta kwana uku Asibiti kafin aka sallamota dan ba qaramin jiki taji ba. Ta rame fiyau se haske data qara kamar mara jini duk wanda ya ganta seya tausaya mata ga rashin jaririyarta ga Yakubu baya kusa yana can nisan duniya bema san abinda ya wakana ba. Haka sukayi ta tausarta harta saki zuciyarta, kwananta Ashirin da haihuwa Dada tayi mata izinin tafiya can Rugarsu dukda yan uwanta sunzo sun dubata har sun bar mata yayarta daya ita ke kula da ita amma Dadan tace taje ta huta kota qara rage kewa a sannan tuni Audu ya koma Kano ya kuma aikawa da Yakubu wasiqa ya sanar masa da abinda ya faru.

Haka aka cigaba da lallaba rayuwa, Su Yakubu sun samu hutun shekarar farko a karatunsu ya taho gida cike da kewar matarsa da kuma Alhinin yarsa daya rasa. Tsaraba niqi niqi yayo daga ikko, kowa seda yasan da dawowarsa domin dangi kaf kowanne gida seda abin Alkhairinsa ya leqa. Yaya Baba da kansa yake cewa

"Tabbas yaran nan sun san Alkhairi, ka dubi duk abinda mukeyi musu amma basu riqe mu ba ba kuma su canza daga kyautatawar da sukeyi mana ba"

Hashimu da yayi maganar a gabansa yayi tsaki zuciyarsa tayi baqi, haka siddan shedan yake hura tsanar su Audu a zuciyarsa yana qissima masa cewar duk abinda suke samu shida yan uwansa ya kamata ace sun same shi amam basu Audun ba.

Shidin mutum ne me shige shigen zuwa gurin Malamai, a yawonsa aka binciko masa cewar Yayan Dadan suna da taurarin arziqi, yabi malamai sun fi nawa amma kamar hadin baki duk inda yaje se a ce masa su dun zasu daukaka irin daukakar da beyi zato ba, da yake yayi ammana da zancen Malaman nasa shikenan qyashi da hassada ya darsu a ransa ya kuma dage ta duk wata hanya dayake tunanin daukakar zata zo musu yake qoqarin tosheta sedai rashin sani irin nasa fadar Malaman tsibbunsa ba gaskiya bace, idan kuma anyi katari sun canki daidai to wayo ko dabararsa basu isa su canza abinda ubangiji ya qaddara faruwar iya wuya se abinda ubangiji ya qaddara ya faru.

Cikin tsarabar da Yakubu yayiwo wa matarsa data qaninsa harda qananan kaya irin wanda Arna suke sakawa, a cewarsa daya kalli haram a jikinsu gara ya kawowa Balaraba ta saka masa yasan zasuyi mata kyau matuqa ya kuma hado da Bara'atu itama tayiwa dan uwansa kwalliya harda Bilki da Aisha dasu Amina ya warewa kayane riga da skirt wasu da wando irin me roba idan an saka suna kama jiki a lokacin su kansu Arnan basu fara shigar badala ta rabi tsirara suna yawo a gari ba amma dukda haka su a gurinsu irin wadannan dinma sababbin abu ne. Aiko da yar bafulatanat tasa ta saka ba qaramin kyau tayi ba, seda Audu yazo Bechi Bara'atu ta tsantsara masa kwalliya da nata kayan, yanda tayi kyau ta burge shi ya sakayi cewa Yakubun mezzo hana su fara kawo ire iren qananan kayan na Mata dana yara harda ma na Maza dan suma yazo musu da Jeans da shirts tunda yace duk akwai su kuma suna da sauqi a can.

Haka kuwa akayi Bayan Yakubu ya koma ya qullo dila guda ya aikowa Audu. Tun kafin kayan su iso daman yayi tallarsu dan haka yana bude dila bata rufe sati ba se burbudi masu siyan daidai da sari sun kwashe, yanda mata suka dinga zuwa suna siya da siyawa yaransu ya bashi mamaki, kuma a lokacin bakin Asibiti kaf shi kadai ya bude irin kayan wannan dalili yasa saya tashi turawa Yakubu kudi ya ninka wanda suka siyo da farko kamar wasa se gashi sana'ar ta karbeshi ya zama wata dilar ma idan ya kwance bata kwana dan ya dena siyar da guda daidai ma yan sari ne suke kwasa a qasa da wata shida se gashi ya kama hayar Rumfa a cikin kasuwar sabon gari inda akafi siyar da ire iren wadannan kayayyakin ya kumayi suna idan ka shiga kasuwar tun daga qofa daka tambayi shagon BECHI za'a kaika. Cikin wannan yanayi ludufi da budi yayi ta zuwar masa, be kuma tsaya kan iya kayan nan ba yaci gaba da gwada duk wata sana'a daya san zata kawo kudi, kantin da suka bude a gida kuwa kullum sake habaka yakeyi dukda kwanaki sun samu Asara an farke shagon an kwashi kaya daga baya aka kama yaran da sukayi kuma sukace Hashimu ne ya sakasu, Dada ce ta hana su daga maganar, an dai je har gaban Me gari akan ayi musu iyaka da Hashimun wanda a wanann karon Goggo Fadi kanta ta nuna

masa bacin rai akan abinda yayi Audu kuma ya sake sarar kaya harma da wanda da babu a shagon ya zuba.

Tun haihuwar Bara'atu ya qudurce a ransa cewar ze kafa sana'ar siyar da fetur a Bechi, koda masu Ababen hawa da suke da buqatar Fetur din daidaikune amma abinda ya faru na rasa wanda ze taimaka masa ya kai Balaraba Asibiti yasa ya yanke shawarar ze fara Bunbutun koda kuwa ba za'a siya kullum ba wata rana tana iya daurowa a samu me siyar. Aiko ya samu wani Abokinsa Falalau da suke cewa Fala dan bakin Kasuwa ne a nan cikin Kano tare suke a bakin Asibiti kafin ya kuma bunburu da kuma siyar da kayan gyaran mota, a gurinsa ya sari Mai harda su man juye da sauran yan abubuwan buqata, anan qofar gidansu ya kafa Katako inda ya dora jarakunan Man, Baballiya na kula da shago yana kuma kula da Man shida Abdullahi kuma cikin ikon Allah da masu motocin daukar kaya suka gane da yawa basa damuwa da su shawo Mai a Kano kafin su dawo gida tunda sun san da akwai.

A cikin Kanon ma ya bude guri nan cikin Goron dutsen ya ajiye wani yaro yana kula masa da Man shi kuma ya tafi Kasuwa, an samu shekara daya a haka zuwa sannan Ya fara damuwa da rashin samun cikin Bara'atu domin Balaraba harta kuma samun wani cikin yanzun bayan zuwan Yakubu hutun qarshen shekara ta biyu a karatunsa na shari'a. Damuwarda Bara'atun take nunawa yasa ya danne tasa sannan kullum Dada na nuna musu cewar Haihuwa lokaci ne idan Allah ya kawo zasu samu tunda ga yar uwarsa Bilki nan me shekara biyar a daki har yau bata samu ba itama toh suyi haquri suyi addu'a ubangiji ya basu a lokacin dayafi musu Alkhairi.

Da Abokinsa ko muce Amininsa Lado ya tattauna maganar, shiya ke ce masa daman yawanci Matan matafiya basu cika samun ciki da wuri ba, Audu yace ya akayi Ita Balaraba ta samu ciki toh bayan yafi Yakubu yawan zuwa gida? Lado yayi dariya yace

"Ta yuwu lokutan da kake zuwa basu dace da irin lokutan da mace take daukar ciki ba, shi kuwa kaga idan yazo ya kanyi wata guda ko sama da haka a gida kai kuwa zuwanka a tsitstsinke ne wani sa'ilin ma baka wuce kwana biyu uku ka juyo, nima wani Abokina da yake karatun lafiya naji ya fada an musu a karatunsu cewar da akwai wani lokaci bayan gama Al'ada da kwayayen halittar mata suke nuna su shirya daukar ciki to idan anyi dace an samu tarayya a irin lokutan nan shine zakaga an samu rabo bawai yawan kwanciya da mace ne yake kawo ciki ba".

Wannan magana da sukayi da Lado ta sakashi bayan yaje Bechi ya roqi Dada akan yana so su tafi Kano tareda Bara'atu ze kaita Asibiti dan yana so a gaya musu

wanne lokaci ne mahaifarta take shirya daukar ciki, Dada bata qi ba suka tafi satinta daya ya maidata bayan tasha yawo a Kano ya kaita gurare dan wannan shine karonta na farko da taje, ya nuna mata gininsu da qiris ya rage a kammala ta ringa murna kuwa tana komawa ta qyarawa Balaraba dukda Audun ya gargadeta akan karta gayawa kowa tukunna amma murnar zasu koma Kano yasa ta kasa daurewa cikin ikon Allah kuwa komawarsa babu jimawa ta fara amaye amaye ko ba'a fada ba ansan ciki ne Dada ta ringa cewa gashi nan da suna garaje harda zuwa Asibiti ashe da cikinta ma lokacin bayyanarsa ne beyi ba. Da Audu ya sake zuwa kuwa haka ya kwashe su da Balaraba sukaje Kumbotso inda take Awo akayiwa Bara'atun itama register zata fara zuwa idan cikinta yayi wata hudu a sannan watansa biyu da kwanaki. Ko tari Dada batayi ba dan ba zata so a maimaita abinda ya faru a cikin Balaraba na fari ba shiyasa ko Audu bezo gari ba ranar Awonsu tazo da kanta take tasa su gaba ta rakasu ko kuma Bilki ba kuwa qaramin surutu take sha gurin Goggo Fadi ba wai rashin kunya ce.

Wani lokaci Audu yazo gida kamar yanda ya saba, a lokacin cikin Balaraba nada watanni takwas na Bara'atu kuma yana wata biyar. Da yammaci ta tasashi gaba da wai makani take so taci, ya rasa inda ze samoshi anyi shukar makanin amma ba'a fara kawoshi gida ba. Cikin Bara'atun irin me dan banzan tsirfa ne idan kuma ta rasa abinda take so haka zata wuni ranar tana kuka da baqin Rai haka Audu ya fita akan Sabon Mashin din daya siya saboda zirga zirgar kaisu Asibiti ya ajiyewa Baballiya, gurin Shamsu Abokinsa ya tafi yana tambayarsa inda za'a samu Makani, ya ringa tsokanarsa suka hau mashin din suka tafi gonar Usman da Shamsun yace yayi shukar makani kuma ko babu yawa za'a iya cirar wanda ya nuna. Gonar tasa tana can kusan babban titi wanda tanan zaka gangaro ka dauki hanyar shiga Bechin sun samu Usman din ya debo masa da yawa kuwa cikin wanda ya fara cirewa.

Sun fito daga Gonar suna magana hankalin Audu nakan wata mota can daya hango tsallken Titi tun shigarsu gonar ya ga motar a tsaye yanzu kuma har mutanen ciki sun fito sun bude gabanta da alama ko lalacewa tayi. Seda ya daure ledar Makanin a kan mashin kafin ya cewa su Shamsu yana zuwa ya tsallaka can gurin motar, tun kafin ya qarasa yake jiyo muryar mutumin da yake zaton shine me motar yanayiwa Driver sa fada cikin harshen turanci shi kuma se faman haquri yake bashi. Audu ya qarasa yayi musu sallama dukda bashida tabbacin Musulmaine, mutumin ya juyo ya kalle shi, tabon sallah daya gani a goshin sa ya tabbatar masa da cewar Musulmi ne. Mutumin ya amsa sallamar Audu yana qare masa kallo kamar yanda shima Audun yake kallonsa, Dattijo ne dan a qalla ze iyayin shekaru Hamsin da biyar zuwa sama fari tasa me matsakaicin jiki ya tsuke cikin Coat baqa kana kallonsa kasan ya juqu a Bako sannan motarsa zata sanar maka cewar babban mutum ne da gani.

Cikin Turanci Audu ya gaishe shi yana tambayarsa meya faru dan beyi zaton yanajin hausa ba tunda turancin yaji yana yiwa Direba ga mamakinsa se yaji ya mayar masa da Hausa yace

"Wallahi Motar muce ta tsaya, na dauka ma wani gyara ne kuma wai Ashe mai ne ya qare mana qarqaf kuma saboda shashanci wannan Direban be duba man ba kafin mu kamo hanya gashi yanzu a nan bansan yanda zamuyi ba babu kuma service din kira a nan gurin ballantana nayi waya cikin Kano a kawo mana wata motar" ya qarasa yana daga qata waya da sau daya Audu ya taba ganin irinta hannun wani Bature da yake siyan kaya a gurinsa.

Direban ya sakeyin qasa da kai yana cewa

"Kayi haquri Sir, nidai nafi zaton malejin motar ne ya samu matsala dan seda na duba komai kafin mu taso kuma naga man da muke dashi ze iya kaimu gida har yayi ragowa lokaci daya ya sauka kuma motar ta mutu"

Mutumin ya galla masa harara ba tareda yace komai ba tunda motar ta tsaya yake nanata masa maganar wai malejin ne be nuna masa daidai ba yaci gaba da daga wayarsa yana neman service yana kuma dan waige waige a fakaice dan a tsorace yake, koda yake duniya na kwance a sannan amma wannan Titi da yake shiru tun tsayuwarsu ko Keke be gifta ba balle mota se Audu daya fado musu katsaham kamar Aljani kar suje ba shi kadai bane a mamaye su ayi musu wani mugun abun.

Audu yayi murmushi yana cewa

"Ayya lamarin qarfen nasara babu tabbas, ku jira bari na shiga cikin gari sena kawo muku Man yanzu indai shine matsalar" yana fadar haka ya juya cikin sassarfa ya tsallake titi ya koma inda su Shamsu suke jiransa. Su ukun suka hau Mashin din suka koma cikin gari. Hankalin mutumin da Driver sa ya tashi, karfa gayya zeje yayo azo ayi musu wani abun? Suka kalli juna kowanne kana iya karantar firgici a fuskarsa, ga mota taqi tashi idan sukace su kwasa da gudu kan suje ko ina su Audun zasu iya cimmasu gaba daya nadamar zuwa Taron daya kawo shi Kano ta kamashi, yana zaman zamansa qungiyarsu ta masu lasisin haqar man futur ta shirya musu taro a Kano kamar baze zo ba ashe Ajaline ya kirashi. Jiki a sabule ya shige motar ya zauna ya hada kai da kujera danya gama saddaqarwa yau kam tasa ta qare, qarar mashin dayaji tasa shi dagowa a firgice sedai ganin Audu tareda Shamsu daya rungumo Qatuwar jarka ga bututu da tiyo a hannunsa yasa shi sakin ajiyar zuciya babu shiri zufar dake keto masa ta fara qafewa har iska na fifitashi.

Fitowa yayi daga motar lokacin har Audu ya bude jarkar yana jiran Direba ya bude gida man a zuba musu shi kuma yana kallon ubangidansa cikin jiran umarni, kai ya gyada masa alamar bada dama ya bude musu, seda ya cika musu tanki taf da mai kafin ya rufe jarkarda dan ragoqar daya rage ciki yana kallon Direban yace

"To ka kunna mu gani"

Direba ya kunna mota se gashi kuwa ta tashi, fuskar Alhajin ta sake washewa yana kallon Audu yace

"Amma a ina ka samo Fetur haka?"

"Ina siyarwa ne anan cikin garinmu" ya bashi amsa. Alhaji ya zura hannu a Aljihu ya zaro kudaden da besan yawansu ba ya miqawa Audu yana cewa

"Nagode kwarai samari"

"Aa ka bar kudinka Alhaji kyaiuta na baku"

"Amma kace siyarwa kakeyi" Alhajin ya fada yana sake miqa masa kudin. Audu yayi murmushi yace

"Eh siyarwa nakeyi amma ku kyautana baku, da zan karbi kudinka tun farko zance maka ina siyarwa ka fadi na nawa za'a zuba maka"

Alhaji ya gyada kai cike da gamsuwa har sannan fuskarsa dauke da murmushi yace

"Hakane, nagode kwarai, yanda ka kaimakeni kaima Allah ya kawo maka wanda zero taimake ka a lokacin da bakayi tsammani ba" suka amsa da Amin. Ya sake saka hannu a Aljihu ya ciro wani dan kati me kyau ya miqawa Audu yace

"Ga katina, idan ka samu dama ka nemeni kaji, Nagode kwarai dagaske Allah ya saka"

Audu ya karbi katin da aka rubuta 'ZAKARIYYA PAKI AND SONS' ya jefa a Aljihu daga nan Alhaji ya shiga mota yana daga musu hannu har suka bar gurin.

Audu da Shamsu suka hau mashin Shamsun nata mita akan me Audu be karbi kudinba yace shi taimakonsu yayi saboda Allah kuma iya addu'ar da yayi masa ma ta ishe shi.

Yanayin garin lokacin sanyi ne dan haka Dada nata fama da mura me zafi wadda daman tanayinta duk sanyi har da daukewar numfashi wani lokacin take samu tun su Audu na qanana haka suka tashi sukaga tana shan wahalar nan duk sanyi shiyasa ya siya mata manyan fulasan ajiye ruwa sannan sanyi na shigowa zasu cire labule me saukin da yake a jikin qofa a saka mata jibgege haka dakin baya rabo da rushi amma dukda haka data fita tsakar gida ta shaqi hazo da sanyi haka zatayita haki tana jan numfashi. Maganin gargajiya take sha tuntuni wannan karon kuma tun zuwan Audu yake fama da ita akan suje Asibiti dan zamansa a Kano yasan cutar Asthma, akwai qanin Hayatu Magashi da yake da ita kuma duk yanayin ciwon nasa haka Dadar take fama sedai taqi yarda suje Asibi balle a dorata akan magani tace tafi gane na gargajiyar da take sha tun tana yarinyarta.

To wannan karon ciwon nata yadan ta'azzara dan dalilin daya hanashi komawa Kano kenan kusan satinsa biyu a Bechi se jikin yayi sauqi se kuma ya dawo. A daren ranar ma kwana sukayi zaune saboda yanda ta kasa bacci tana jan numfashi dakyar tun bayan data dafawa su Bara'atu makani hayaqin Karan datayi girkin dashi ya cika mata qirji shikenan numfashi ya fara sama sama washe gari kuwa da sassafe Audu ya kwasheta duk yanda take tirjewa seda sukaje Asibiti. An mata Allura an kuma rubuta mata magunguna ya siya bayan dokoki da sharuddan da likita ya kafa mata akan ta kiyaye duk wani abu daze hadata da qura ko hayaqi suka dawo gida. Wunin ranar zur a dakinta yayi shi haka qannensu da matansu duk suna nan suna hidima da Dadan da gaba daya tayi wani laushi dukda tace taji dadin Allura da maganin data sha abinda take ji a qirjinta ya yaye amma jikinta babu qarfi dama kuma likitan ya gaya musu magungunan akwai me kashe jiki yasa bacci dan haka Audu yace ta kwanta ta huta.



Goggo Fadi ta ringa sakin maganganu a tsakar gida wai Lamarin Dada dai ta rasa ma abinda zatace akai wannan rashin kunya har ina ta ringa hawa mashin Yara na goyata sannan danbata da lafiya kamar wata jinjira ta langwabe duk se wani zuruftu yara suke akanta, lokacin da take maganar Dada ta fito Aisha ta rakata kewaye ta fito tana daura Alwala. Seda ta idar ta kalli Goggo Fadin da murmushi tace

"Yaya kenan, indai nice kin kusa ki dena ganina ballantana nayi abinda ze sakaki surutu".

Goggo Fadi ta ce

"Eh ba shakka Hafsatu wato daman naji ance zakuyi qaura Birni yo ni ai haka nake so ku tattara ku tafi ku barmin gidana yanda kuka zo kuka sameni, bari ma wannan

yaron yazo kuyiwa gurin naku kudi kawai ya fiddaku shikenan wanda ya hada ya raba"

Har Dadata zura qafarta a daki ta sake waiwayawa tana murmushin da seda gaban Goggo Fadi ya yanke ya fadi haka kawai tace

"Toh ai Malam ba sauri yayi ba Fadi, zan bishi kema kuma komai dadewa zaki biyo bayanmu" daga nan ta shige dakinta tabar Goggo Fadin na sababi ita kadai.

Da dare Audu ya kawo mata Kaza gasashshiya da Madara sabuwar tatsa dan gama tafasata kenan ya karbo ko hucewa batayi ba. Dada na cin naman Baballiya na gefenta yana so yaci Audu ya hanashi Abdullahi daman tuni ya gudu gurin Bara'atu tunda yaga Audun ya shigo da ledoji kuma har Goggo Fadi seda ya miqawa. Dada taci ta qoshi ta turawa Baballiya tana cewa

"Ci ubana kaji haka kawai yabi ya takuramun kai"

"Wlh Dada ke kike dada sangarta yaron nan ya girma amma baze dena sakarci ba a haka kake cewa zakaje aikin Sojan" Audu ya fada, Dada ta kishingide tana sakace tace

"Ze dena ne, aikin Soja kuma nasan indai kana raye seka cika masa burinsa kamar yanda ka dakko hanyar cika na dan uwanka. Ina Alfahari dakai Abdulwahabu ina kuma roqon Allah yaci gaba da hada kanku ya baka ikon ji gaba da jajaircewa akan zumunchinku, ina fatan har yaya da jikoki kuci gaba da hada kanku karku yarda qata baraka ta shiga tsakanin ku, Banida haufi domin kunyo dacen mata na kwarai saboda rayuwar Namiji komai nagartarsa idan yayi kuskuren dace da macen aure anan yake samun tawaya dan haka ina horar ku cewar ko gaba koda ace kunyi sha'awar qara aure kuyi qoqari gurin zabo matar da zata tayaku kuci gaba da hada kan gidanku ba wadda zata tarwatsa muku farin cikin da kuka ginu akai ba. Sannan yan uwanku kuci gaba da haquri dasu kuna jan su a jiki da sannu wata rana zaku koma tamkar baya sanda Malam yana raye".

Haka ta ringa masu nasiha me shige da wasiyya, Baballiya na gama cin kazarsa ya sheme a gurin ita da Audu sukaci gaba da yar hira har ta fara gyangyadi kafin ta hau gadonta yaja mata abin rufa bayan ya shafa mata man zafi a tafin qafarta ta saka safa. Seda ya zubo toka me zafi a babban kaskon da ake ajiyewa a dakin yayi masa mazauni me kyau saboda gudun tsautsayi kafin ya tashi Baballiya ya gyara kwanciyarsa yaja musu qofar ya fita jikinsa a sanyaye saboda maganganun da Dada ta fada masa, yanda take nanata masa hadin kan Iyalinsa kamar wadda take hango

wani abu a gaba haka ya shiga dakinsu Bara'atu har tayi bacci ya raba gefenta ya kwanta sedai be jima da kwanciya ba bugun qofar gida ya farkar dashi.

Da mamakin wayake musu bugu cikin dare ya dauki fitila ya fita, seda ya tambayi waye, muryar Yakubu dayaji ta sakashi bude qofar da sauri ya rabe ya shigo ganin yanda yake rawar Dari dan rigar jikinsa bata da nauyi haka nan kansa babu hula ga dare ya tsala dan haka gari yayi sanyi qarara. Yakubun na goye da Jakarsa medan girma kana kallonsa ko baa fada maka ba zaka san yasha wuyar tafiyar da yayiwo ya wuce ciki Audu yabi bayansa zuciyarsa na bugawa abinda ya fara zuwar masa Yakubun ya samu matsala da karatunsa ne. Yana so ya tambayeshi daga ina haka cikin dare ba kuma ya so hayaniyarsu ta tayar da Dada ko Goggo Fadi ta samu abin sharri dan haka yabi Yakubun daya doshi dakin Dada kai tsaya ya tura qofar ya shiga Audu yabi bayansa.

Tana kwance tana bacci hankalinta kwance ya kai hannu ze tayar da ita Audu ya riqeshi yana cewa

"Haba dai ya zaka tayar da ita tana bacci"

"Na kasa nutsuwa saboda ita na baro Ikko babu shiri me ya samu Dada kullum cikin tunaninta nak abin kuma har ya zarce misali?" Yakubun ya fada yana duban Audu, Audu yayi waje yana cewa

"Babu abinda ya sameta kaje ka kwanta kaga dare yayi da safe se muyi magana" suka wuce, seda yayita kwankwasa qofar barinsu kafin Balaraba ta taso a dan rikice da alama tana baccin itama bugun ya riske ta, ganin Yakubu ne kuma se fuskarta ta washe da murna suka shiga suka maido qofa se sannan Audu ya shiga dakinsu zuciyarsa fal da wasi wasin abinda ya taso Yakubun haka koda yake ya sani shidin me qulafucin uwa ne ta yuwu rashin lafiyar Dadan ce ta taba shi har ya kasa zama ya taho ya ganta haka ya ringa juyi a gado sedai sam bacci ya qauracewa idonsa dan haka ya tashi ya dauro Alwala ya shiga Nafila Bara'atu dai tayi daidai abinta a gado dan cikin nata irin me baccin nan ne da se a iya sace mutum sedai ya farka ya ganshi a wata Nahiyar.

Asubar Fari kururuwar Baballiya ce ta saka Audu sallame sallar da yakeyi babu shiri ya fita daga daki da gudu, a bakin qofa sukayi kicibus da Yakubu da shima ya fito a rikice dan da gani ma daga wanka ya fito ya saka dogon wando ga rigarsa nan a hannu ko sanyin da ake busawa ma bayaji suka shiga turereniyar shiga dakin Dada inda Baballiyar yake qarawa Ihunsa qaimi matan kuma da duk suka fito suma harda Goggo Fadi sun tsaya daga waje kowanne abinda zuciyarsa ta bashi wuta ce tunda lokacin sanyi ana yawan samun wannan matsalar saboda Rushi da ake kaiwa daki

dan aji dumi idan yazo da tsautsayi abinda ze iya kama wuta ya shiga ciki se kaga gobara ta tashi amma kuma basu hango jan wuta a cikin dakin ba ko kuma hayaqi to ko wani mugun kwaron ne ya cije shi?

Yakubu ne akan gaba, burki yaci yana kallon Dada dake kwance idanuwanta a bude tana kallon rufin dakin hannunta daya na dafe da qirjinta dayan kuma ya saki ya sakko qasa, dukda cewar gawa daya ya taba gani ido muraran wato ta Malam amma baya buqatar a gaya masa cewar Dadan ta rasu. Lokaci daya wani kuka me cike da rauni ya kufce masa, ya durqushe gaban gadon Audu ya tsallake shi ya qarasa shigewa dakin dan be fahimci dalilin tsayuwar Yakubun ba ga Baballiya dabe fasa ihu yana kiran ya shiga uku ba.

Hannun Dadan dake qasa ya daga ya maida kan gadon, sanyi qalau yaji shi, ya shiga jijjigata yana kallon fuskarta tareda kiran sunanta ganin ta zubawa guri daya ido Yakubu dake kuka kamar qaramin yaro, ashe Alhinin rasa mahaifiya ne ya hanashi sakat har seda ya kamo hanya ya dawo sedai an saba haduwar, bashida rabon zasu sake zantawa da ita rai yayi halinsa. Kama hannun Audu dake jijjiga Dadan yayi cikin kuka yace masa

"Bari jijjigata ta rigamu gidan gaskiya"

Ze iya cewa be fahimci abinda Yakubu yake nufi ba dan kwakwalwarsa gaza fassara hausar tayi dan haka ya shiga qoqarin dagata yana cewa Yakubun ya tayashi su fita da ita ya kaita Asibiti Yakubu ya miqe yana janye shi cikin daga sauti yace masa

"Ka dena wahalar da ita Audu na gaya maka ta rasu" kalaman da suka fi duk wasu kalamai daya tabaji a rayuwarsa Muni, Dada ta rasu? Dadar da suka gama hira dazu daman duk wasiyya take masa?

Kalaman Yakubu suka janyo hankalin su Goggo Fadi dake qofar daki take suka fasa kuka kafin kace me maqota sun jiyo aka fara shigowa rayuwa kenan tabbas dan Adam abin tausayi ne yanzun kaine qiftawar ido ana iya cewa babu kai. Duk wanda yaji rasuwar Dadan se yace jiya fa da La'asar sakaliya ya ganta a Mashin Audu ya dauke ta har sun gaisa, a masallaci ana idar da sallah aka bada sanarwar Jana'izar, kafin ko gari ya gama wayewa tangararau har an shiryata tsakanin Yayanta baka iya fidda wanda mutuwar tafi duka. Bilki suma tayi sanda saqon ya risketa Aisha tafita dauriya kuka ta ringayi Audu kansa duk taurin rai irin nasa ya koka hada kai sukayi da Yakubu suka ringa kuka gwanin tausayi.

Bayan an kaita an dawo aka zauna zaman karbar gaisuwa, Goggo Fadi tayi wata zugewa lokaci daya, mutuwar Dadan ta daketa matuwa ta kuma yi nasarar maidata cikin hayyacinta.

"Malam beyi sauri ba, nima zan bishi kuma kema kina tafe komai daren dadewa" kalaman Hafsatun na jiya suka ringa mata yawo a kwakwalwa ashe mutuwa Hafsatu zatayi? Da tasan haka da bata takaleta ba, data nemi yafiyarta akan abubuwan da ita da yayanta suka ringayi mata. Hashimu kansa yaji mutuwar amma da yake Dan Adam ne ana kwana daya ya ci gaba da sabgoginsa be ko sake zama gurin karbar gaisuwar ba ya bar su Audu dasu Aminu da idan ka ganshi zaka dauka mahaifiyarsa ce ta rasu. Su Audu kuwa ba'a magana duk sun sukurkuce bayasu ba baya matansu ba amma ya zasuyi haka aka share zama bayan anyi bakwai Abokanan Audu na Kano sunyi masa kara mota guda suka yi sukaje masa gaisuwa bayan da suka samu labarin rasuwar a bakin masu daukar kaya yan garinsu.

Wannan karon tsakanin Audu da Yakubu rasa wanda ze lallashi wani ya koma bakin nemansa akayi. Seda Dada tayi sati biyar da rasuwa, Yaya Baba ya kirasu cike da Alhini bayan ya sakeyi musu gaisuwar rashin da sukayi kafin yace musu

"Naga dukkanku baku da alamar komawa bakin neman ku musamman kai Yakubu da kuke tsaka da Karatu ka taho ya kamata kuyi haquri ku dauki dangana zamanku bashi ze maido da Goggo ba A yanzu Addu'a kadai take da buqata daga gareku sannan kuci gaba da jajircewa akan abinda take da burin ganin kun cimmasa".

Maganar Yaya Baba tasa suka fara shiri jiki a sabule babu wani karsashi sun kasa sabawa da Rashin Dada, tunanin yanda rayuwarsu zata cigaba ba tareda ita ba sukeyi yanzu dawa zasu ringa barin matansu? Tunanin Audu kenan. Da dare ya samu Yakubu a bangarensu yana zaune shiru Balaraba na gefensa itama shiru duk ta fice hayyacinta tamkar Bara'atun sa ga tsohon ciki haihuwa ko wanne lokaci na iya zuwa shigowar Audun yasa ta cicciba ta basu guri.

"Wata shawara nake da ita Yakubu" Audu ya fada bayan daya gyara zamansa. Yakubu ya kalle shi Audu yaci gaba da cewa

"Daman akan Iyalanmu ne, kaga yanzu Babu Dada gaskiya hankalina baze taba kwanciya ace mu barsu a nan ba kaga dai halin da gidan nan yake ciki lokacin da ranta ma yaya balle yanzu da babu idonta"

Yakubu ya jijjiga kai yace

"Hakane, ni kaina ina wannan tunanin ga yanayin da suke ciki gaba daya kowacce na da buqatar kulawa ta musamman, amma kai menene shawawararka me kake gani za'ayi?"

"Dama dai tun zuwansu Ma'aruf na gaya mishi ya dauki kudi cikin cinikin da akayi a qarasa ayyukan da suka rage na gidan nan mu koma can kawai gaba daya da zama kaga hankalina zefi kwanciya na kuma tsaya a guri guda amma kai me kake gani?" Audu ya fada. Yakubu ya muskuta yana cewa

"To wannan shawara ce amma kana nufin kenan zamu bar Bechi da zama gaba daya?"

"To me muke dashi a nan da ze sa muci gaba da zama? Karka manta mun rasa uwa da uba dangi kadai suka rage mana kuma zamu ringa kawo musu ziyara lokaci lokaci musamman kaga Bara'atu iyayenta suna nan baze dauki lokaci me tsayi ba zamu ringa leqowa muna ganin dangin mu" Audu ya sake fada.

"To gida kuma fa haka zamu barshi ya lalace?" Yakubun ya sake fadaz cike da qosawa Audu yace

"Nidai na rigada na yanke shawara bazan iya cigaba da zama a gidan nan ba idan na kalli dakin Dada gani nake kamar zata fito daga ciki zuciyata bazata iya ci gaba da dauka ba" yayi maganar a raunane sukayi shiru baki daya kafin can Yakubun ya sake cewa

"Ina ganin zan kama daki a Ikko da zamu iya zama da Balaraba zuwa na qarasa karatuna kafin muga abinda Allah zeyi"

"Wannan shawara ce me kyau, amma kuma a halin da take ciki baze yuwu ka dauketa ba dole sedai a jira har seta haihu kuma kaga lokaci yana qara tafiya kamata yayi ka fara yin gaba kaje ka shirya duk abinda ya kamata idan ta sauka ta yada wanka se kazo ka dauke ta ku tafi ko ba haka ba?" Shawarar Audu.

Yakubu yayi na'am da maganar tasa dan haka suka shiga shiri, sun sanar da matayensu abinda ake ciki haka yan uwansu da suke uba daya, Goggo Fadi ta fasa musu kuka sanda suka gaya mata shirin nasu tana cewa wai me yasa zasu ce zasu

bar gidan kenan ita basu dauketa uwa ba ba zata iya kula musu da matansu ba? Daga Yakubun har Audu babu wanda ya kula maganganunta dan gani sukeyi ihu ne kawai bayan hari basu yarda wai har zuciya Goggo Fadin tayi tuba na gaske ba. A satin suka shirya tafi, sun tsara da gida ya kammala Audu ze kwashi Bara'atu da Balaraba duk su koma Kano da zarar Balaraban ta haihu kuma zata koma Wailari tayi wanka inda daga can zata bi Audu, da akwai Yayanta da yake zama a Ikkon shima Shanu yake kaiwa daga baya kuma yayi zamansa can matansa biyu ya kai daya can sunzo ganin gida zasu jima dan haka suka bari akana idan Yaya Iron ya tashi komawa zata bisu su tafi tare.

Ana i gobe zasu tafi da maraice Balaraba ta haihu ta samu ya mace wannan karon Ubangiji ya bata da sauqi dan da tasowar ciwon gaske da haihuwar beyi awa daya ba, Audu ya fita qaraso musu siyayyar dan abinda zasu buqata kafin su koma Kano se dawowa yayi ya tarar da yar Baby me kama da Dadarsu sak haka ya kwasheta seda sukaje Asibiti aka tabbatar ita da yarta duk lafiyarsu qalau, farin ciki ba'a magana, Yakubu yayi mata hudu ba da Hafsatu zasu ringa kiranta Dada dan duk wanda ya gabta se ace Dada ta tafi Dada ta dawo. Haihuwar tasa suka qara kwana biyu, yan Uwan Balaraba suka dauketa zuwa gida wanka Audu ya wuce Kano tareda Yakubu daze koma Ikko. Wata daya bayan haka Audu da Bara'atu tareda Baballiya sukayi qaura Kano, qarshen zamansu a Bechi kenan.

Ranar da zasu tafi mota guda ya dakko aka kwashi yan rakiya dan an kwashe kayansu daman tuni. Yan uwan Bara'atun uku Yayarta daya se Matar wanta da qanwar Babarta sauran sukace a hankali zasuje suga inda suka koma se murna suke tasu ta koma Birni suma sun samu gurin zuwa haka Inna Hajara har wani qafafa take tana yadawa wanda suka ringa Adawa da Auran Bara'atun da Audu magana ciki harda Babanta. Yan gidansu Audu ma kafataninsu su Bilki dasu Amina harda Matar Yaya Baba data Aminu da Amaryar Hashimu wadda se bayan sun tafi ya samu labari ya ringa tijara yana rashin mutunchi Goggo Fadi da tabi hanyar Allah tuni tun bayan rasuwar Dada batace masa qala ba, ita kanta taso zuwa amma ciwon qafa daya sakata gaba kwana biyu ya hana amma Audu ya mata Alqawarin da kansa ze dawo ya dauketa taje ta kwanar musu biyu kuma tafiyarsu ba tana nufin sunmanta dasu bane, basu da wasu dangi a duniya bayan su, su goman nan da Mahaifinsu ya haifa sune dangin Kansu.

Yan Bechi suka ringa santin gida, kwanan su daya suka juyo Audu ya hado su da sha tara ta Arziqi qememe Abdullahi yaqi bin Babarsa Audu yace a barshi daman ai Abdullahi Dansa ne, uwar bata so ba dan daman ita ba wai son zaman da yake a gurin Bara'atun take ba kawai dai dan Aminun tsayayyae ne yasa ta kasa magana yanzun da Audu yace a barshi tace

"Amma Babansa be sani ba zeyi fada idan aka koma babu shi"

"Idan kin koma ki gaya masa ni Audu na riqe Abdullahi idan yana da jaa yazo ya dauke shi da kansa" ya fada mata zata sake magana Amina ta harareta tana cewa

"Sedai kece zaki cr bakya son zamansa a nan dan dai Yaya Aminu ya dade da fadawa kowa ya barwa Audu Dan nan kuma wannan baqin ciki kikewa Danki ze zauna a Birni yayi Karatu me kyau ya tashi a waye"

"Meye haka Yaya Amina?" Audu ya katseta, ta sake cewa

"Gara na fada mata ai idan kuma ta ce se a bata danta gashi nan ta tarkata su tagi dana Koma zan hadowa Muzammilu kayansa a kawo maka shi ga Yaran nan tuli a dangi har wanda zaka riqr ze gagara ne?"

"Audu yayi murmushi kawai jin abinda tace ya tashi ya fita bayan ya Ajewa Aminar saqon maganin ciwon qafa yace ta kaiwa Dada, haka suka koma Bechi aka bar su Bara'atu a sabon guri.

Sannu sannu rayuwa taci gaba da tafiya, Balaraba ta yada wanka har taje Bechi daga nan tayo Kano ta kwanarwa su Balaraba Biyu kafin suka kama hanya da Audu daze rakata dan Yayanta Iro ya tafi da Shanu matarsa kuma tana da ciki ta kusa haihuwa wannan yasa Iyayensu sukace ta zauna ta haihu tukunna ta koma. Seda Audu yayi sati ya dawo rayuwa taci gaba. Sosai kasuwancinsa yake garawa. Kudin gonar su da suka siyar ya qara jari da shekara ta zagayo sun ninka kansu wannan yasa ya shawarci Bilki data kawo musu ziyara akan me ya kamata suyi, sun yanke cewar su nemi qananan Gonaki a ringa siya ta yanda a hankali kowa ze mallaki tasa aci gaba da juya kudaden kamar yanda yakeyi yana kuma fitar da riba yana bawa kowa saboda buqatu, gidansu ma Bilkin cewa tayi suyiwa su Hashimu tayi ko zasu siya dan ya mayar da gurin Rumbu kayan gonarsa yake ajiyewa a ciki Audu yace mata Aa su barshi saboda idan sunje su samu gurin sauka ze dai saka a gyara gurin a hankali.

Page 9

Ranar wata Talata Bara'atu ta sauka a Asibitin Murtala inda Audu ya yankar mata katin Awo tun bayan dawowarsu Kano ta samu Da Namiji murna gurin Audu dasu Baballiya ba'a magana, wata maqociyarsu Baba Larai da suke mutunchi da Bara'atun tun tarewarsu ce tayi mata biqin kwana biyu kafin Audu ya tattarasu suka tafi Bechi, se ganinsu sukayi da jinjiri aka ringa murna a gidansu ta zauna seda akayi suna yaro yaci sunan Malam wato Tijjani suke kiransa da Babangida, Raguna

biyu manya Audu ya yanka haka ya mata kayan barka irin na Birni duk inda ka shiga a Bechi labarinsu akeyi, lafiya lau tayi wankanta kwananta Hamsin da Haihuwa suka dawo Kano rayuwa taci gaba da garawa cikin ludufi da Amincin ubangiji.

Kasuwancin Audu kam yana habaka dukda dai har sannan yana kan canje canjen sana'a dalili da duk wadda ya fara tabawa da an kwana biyu se abin ya fara sakin hannunsa tilas yake sake cafkar wata sana'ar ya dora wannan dalili yasa yana da ido acin kusan duk wata sana'a da ake juya kudi a samu riba, ba babbab ba qarama duk yana tabawa ita kanta Bara'atu be barta a zaune ba ya sakata tana taba sana'oi na mata na cikin gida kuma tana samu babu laifi ga Kitso da daman ta iya shima tanayi shiyasa idan suka tashi zuwa Bechi Sallah, Biki ko suna bayan abinda Audu ze bata haka itama zatayi ta Alkhairi wa yan uwanta da nasa, gida su kuwa baya rabo da dangi duk wanda ya samu dama ze zo Kano ya kwanar musu biyu ya koma.

Yakubu na Ikko abinsa tunda Balaraba ta bishi seda suka shekara biyu kafin suka zo lokacin ya rage masa shekara daya ya kammala karatunsa kenan. Daga shi Har Balaraba idan kalle su seka qara, Yakubun ya waye ya zama wani baqin Bature hatta shigarsa ta canza zuwa coat baqa da farar yar ciki irin dai shigar su ta masu karatunshari'a ita kanta Balaraba Turanci har ya kama bakinta saboda suna tsakiyar wanda zo in kashe ka basu sani ba da Hausa. Ga Dada data jima da yayewa tayi kubibi abinta fatarta me haske irinta uwarta har sheqi take saboda zama cikin lullumi ga cin naman ruwa da suke se tsohon cikin da take dashi haihuwa ko wanne lokacin dalilin dawowar tasu ma kenan.

A Kano suka sauka suka ringa yiwa Juna tsiya ita da Bara'atu da itama take dauke da ciki na Biyu watannin Babangida goma sha daya ta samu ciki sati daya kenan Inna Hajara ta dauke mata shi tunda ta kusa sauka amma ba bisa son ran Audu ba. Seda suka kwana biyu suka huta kafin suka tafi Bechi gaba daya niqi niqi da tsaraba daga can Balaraba taje garinsu su kuma suka juyo Kano seda ta gama kwanakinta ta dawo.

Zamansu gwanin dadi, idan safiya tayi Mazajensu suka fita Kasuwa inda Yakubu yake bin Audu Baballiya da Abdullahi su tafi makaranta duk wadda ta riga gama aikin bangarenta zata shiga gurin yar uwarta, nan ma girki daya suke kowa ta dibarwa iyalanta.

Wannan karon ma Balaraba ce ta fara haihuwa ta sake samun Mace kwana biyar tsakani Bara'atu ma ta haihu ita kuma Namiji wannan Dalili yasa Audu da Yakubu da

duk sukace babu wadda zataje gida aka hade taron suna, ranar kwana bakwan Balaraba akayi mata yanka yarinya taci suna Maimunatu amma taro seda da dan Bara'atu Yusuf dayaci sunan babanta ya kwana bakwai akayi Yan Bechi sunzo da dangin Balaraba an sha buduri sosoi taro ya watse se yan zaman wanka da kowacce aka kawo mata daga gida Yakubu ya koma Ikko saboda makaranta haka suka cigaba da wanka Balaraba na yada wanka taje garinsu da Bechi tayi musu sallama Audu ya kaita tasha da Yayanta suka bi Yakubu Bara'atu kuma taci gaba da rainon Babannan da Babangida wanda Audu ya kafa kwarzaba seda aka dawo masa da Dansa ga kuma Baballiya da Abdullahi abinsu gwanin Dadi suke zaune.

Bayan Baballiya sun rubuta jarabawar kammala sakandire wadda tsallaken Aji akayi masa saboda girmansa akayi sa'a kuma yana gane karatun daman yana Aji Takwas suka baro Bechi dan haka suna zuwa Kano Audu yasa aka kaishi Aji biyu na babbar Sakandire, ya dage akan shidai aikin soja yakeyi, tun Audu baya daukar abinda muhimmanci har nacin Baballiyar yasa shi tambayar yanda ake shiga makarantar sojojin. Wani Maqocinsa a Kasuwa ya tambaya dan yanajin yana fadar da akwai qaninsa daya tafi aikin soja, shiya gaya masa qanin nasa yana makaranta a Kaduna shima wani Dan uwan mahaifiyarsu ne dayake zaune a can ya samo masa kuma ance daya gama ze fito a babban soja ne ba kurtu irin wanda mutanen mu a wancan lokacin suke zuwa suyita wahalar banza ana kashe su a yaqe yaqe ba.

Wannan dalili ya saka Audu shirin tafiya Kaduna kai Baballiya makaranta. Yace masa ya shirya kayansa kala hudu zuwa biyar a jaka ya kuma hada takaddunsa, Bara'atu ta ringa musu dariya tana cewa

"Dukda dai bamyi karatu ba amma nasan ba haka taka ake kai mutum makaranta ba dole se anbi matakai ka nemi gurbi idan ka samu kafin ka tafi ko?"

"To ai nima ba cewa nayi zan kaishi kaitsaye ba, zuwa zamuyi can muji yanda tsarin komai yake saboda ban gsu da bayanan Labahani ba besan takan komai ba kawai shirme yake gayamun gara muje kinga idan abin babu wahala kinga ba se anyi jeka ka dawo bazan baro shi can kawai" Audu ya bata amsa. A daren tana hada masa nasa kayan Babannan dake wasa ya zubo da wata jaka da Audu ya cukuikuye takaddar kammala sakandirensa ya jefa a ciki da takaddun gonakin da suka siya a Bechi, ta tattare ta mayar tana masa fadan ya fiya qiriniya, Babangida ne ya daga wani qaramin kati ta bata ankare dashi ta mayar ba ya fita dashi. Audu na qofar dakin inda ta baza musu tabarma saboda zafi suna Hira dasu Baballiya da murna tasa ya kasa bacci.

Abdullahi Babangidan ya kaiwa katin hannunsa, ya haska da yar fitila yana karanta abinda aka rubuta a jiki kafinya miqawa Audu yana cewa

"Baba ga abinka Baba ne ya dauko"

Audu ya karbi katin ya haska shi tunaniya tafiyi na menene, duk sonya tuna kuma ya kasa, Kaduna daya gani a Address din dake jiki ya sakashi bawa Abdullahin yace ya miqawa Ummansu ta saka masa cikin jakar da ze tafi dashi, komana wanene yana da yaqinin zeyi masa amfani tunda zashi Kaduna.

* MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na *GHT wato  good health treatments

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out  ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane  , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri *

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

*Seda suka hau mota har sun wuce Zariya kafin katin ya fado masa take kuma ya tuna inda ya samo shi, wannan Alhajin daya taba taimaka ya basu Mai shekaru kusan uku kenan nasa ne. Farin ciki ya kamashi, a ransa ya ringa Addu'a Allah yasa yana raye kuma yana Kadunan idan sunje ze neme shi su sada zumunchi. Ikon Allah kenan, qila rabon su sake haduwa yasa Babangida binciko katin dan ko da kudi bazece ga a inda ya ajiyeshi ba, zaton sa ma ya fadi tun a ranar. Haka suka sauka Kaduna, Baballiya nata dan banzan raki wai tafiyar Nisa ya gaji Audu ya balbaleshi da masifa yana cewa a haka zeje aikin sojan qato dashi amma se ragonci kamar Mace.

Ganin yana nema yayi masa kuka ya sakashi neman gurin me abinci a cikin tasha ya siya masa, suna zaune yana tunanin ta ina zasu fara, gashi la'asar harta kawo kai dan motar da suka hawo se a hankali kamar sun hau Jaki. Wani akwatun waya ya hango wanda ake biya ayi kira ya miqe yana laluba Aljihunsa inda ya saka katin Alhaji Zakariyya ya tafi gurin. Ya bada lambar aka kira masa, kiran farko ba'a daga ba seda akayi na biyu muryar mace cikin harshen turanci ta ratsa kunnensa.

Gyara nasa harshen yayi suka gaisa kafin ya shiga tambayar mamallakin lambar wanda a katin yaga an rubuta Zakariyya, "wa za'a ce masa?" Ta tambayeshi yace mata

"Kice masa Audu Bechi ne" Audu ya fada duda yasan babu tabbacin Alhajin ya gane tunda ba gaya masa sunansa yayi a wancan lokacin ba idanma ya tuna ya taba haduwa da shi kenan.

Matar tayi shiru kamar me tunani kafin tace ya riqe waya tana zuwa. A can bangaren sakatariyar Alhaji Zakariyya ce ta dauki wayar wadda take a cikin ainihin office dinsa, ta sani lamba ce da yake magana da mutane masu muhimmanci dan haka duk wanda ya kira tabbas yana da muhimmanci gurin Ogan nata. Kwankwa

qofa tayi, Alhaji Zakariyya ya bata damar shiga. A taqaice ta sanar masa da kiran daya shigo din, sunan Bechi data fada kawai ya sakashi zabura kamar wanda akace anga Dan uwansa daya bata. Fuskarsa a washe har haqoransa sun bayyana cikin son tabbatarwa yake tambayarta

"Kikace BECHI"

"Yes sir, haka yace sunansa Audu Bechi" ta bashi amsa.

Alhaji Zakariyya ya daga kan wayar dake ajiye kan teburinsa wadda take a hade da ta teburin sakatariyar, Audu nacan saqale da waya a kunne cikin jiran tsammani yaji sallamar Alhajin kamar daga sama har wata Ajiyar zuciya ya sauke ya shiga gaishe shi.

"Har na fitar da rai da zaka kirani, kullum da tunaninka nake kwana nake tashi, na kasa manta Alkhairin dakayi mun" Alhajin ya fada cikin tsananin murna. Audu yayi murmushi yace

"Haba dai Alhaji dan wannan abin ka kasa mantawa tsayin shekaru?"

"Kai kake kallonsa a qanqanin abu, badan Allah ya kawo ka ka taimakemu ba a wannan rana bansan ya zamuyi ba. Ya bayan saduwa ya Kano? Kasan tun wannan ranar ban sake zuwa Kano ba amma duk idan naji wani zece sena bada sallahun a dubamun kai a wannan hanyar gashi bansan sunanka ba ballantana ko yan karkararku a tambaya" Alhaji ya sake fada. Audu ya jinjina kai cike da mamaki kafin yace

"Ikon Allah, nima yau Allah ya kawoni Kaduna shiyasa na taho da katin nan nace idan baka mantani ba na kiraka muyi zumunchi"

"Kace kana Kaduna?" Alhaji ya fada har yana miqewa, Audu ya nanata masa kafin ya fada masa yana Tashar Kawo tareda qaninsa, Alhaji be bashi damar sanar masa da abinda ya kawo su ba yace ya tambayi me wayar Adireshin gurin da suke ya kuma jira a nan ze tiro direba yanzu a kaisu masauki ai baqonsa ne shi. Haka ya zauna a gurin, ba'ayi ci mintina ashirin ba sega Direban Alhaji da sukaje Kano tare Audu na ganinsa ya gane shi ya qarasa gurin fuskarsa dauke da fara'a.

"My brother" ya fada yana buga kafadar Audu ko ba'a fada ba cike yake da farin cikin ganinsa. Shi ya daukar musu jakar kayansu suka tafi inda ya faka wata luntsumemiyar mota yayin waccen shekarar suka shiga Baballiya se zare ido yake.

Suka ringa ratsa titunan Kaduna da gine gine masu kyau da burgewa a nan kuma Audu ya tabbatar da cigaban da Kaduna tafi Kano ta bangaren tsarin birni wanda ake fada su zauna kasuwa suyita tafka musu yau gashi ya gani kuma ya yarda. Gine ginensu a tsare ga Titi ko ina Malam Baballiya ko kasa rufe baki yayi dan wasu ginin ma be taba ganin kalarsu ba saboda ko a Kanon daga makaranta se gida se ranakun hutu da Audu kan tafi Kasuwa tare dasu babu inda ya sani shiyasa Aljannar duniyar da yake gani yanzu ta mugun tafiya da tunaninsa. A unguwar Sarki inda katafaren gidan Alhaji Zakariyya yake kutsa cikin wani gida.

Gini ne na Alfarma wanda ko a yanzu kwaskwarima kadan za'ayi masa ya tafi daidai da zamani. Gurin da aka tanada dan ajiye motoci Direbam da yanzu Audu yasan sunansa Tunde ya faka motar. Seda ya dallewa Baballiya qeya kafin ya dauke idonsa daga kallon taswirar gidan tamkar kwayoyin idonsa zasu zazzago. Tunde ne yayi musu jagora har zuwa can gefen gidan inda sukaga qofofi guda hudu jere ya bude ta farko ya shiga suka take masa Baya Baballiya ne kan gaba Audu na daga baya saboda ya tsammaci bangaren matan gidan aka kawo su dukda sunbaro wancan qaton ginin me Bene qila na megida ne can amma ga mamakinsa cikin madaidaicin Falo yaga sun shiga. Tunde na murmushi ya nuna masa qofa dake cikin falon yace

"Ga daki nan, ku shiga kuyi uzurin da zakuyi bari a kawo Abinci" daga haka ya juya ya fita. Audu ya ringa kallon Falon dake malale da Kafet irin wanda daka taka qafarka zata lume a ciki ga wasu shimfida shimfidan kujeru na Alfarma, ya taba ganinsu sau daya a gidan wani Hamshaqi a Kano daya kaiwa Takalma wanda suma yana siyar dasu yanzu. Wani qamshi da sanyi ya ringa ratsasu, ya kalli Baballiya dake nan kamar gaula har digar da yawu yake tsabar kallo kafin ya zauna akan kujera kamar me tsoron ace ya tashi. Babu dadewa Tunde ya dawo da wani mutum a bayansa ya saka Apron da hular girki hannunsa dauke da wani qaton Try har mamaki ya kama Audu na tunanin yanda ya iya daukar wannan Try da hannayensa biyu ba taredaya nemi taimako ba.

"Ya naganku a nan ga jakarku ma baku kai ciki ba?" Tunde ya fada yana tsince jakar su Audu da Baballiya ya watsar a garin qauyanci. Cikin dakin ya kai musu Kuku kuma ta aje kayan hannunsa ya fita ya sake kawo wani madaidaici dabe kai na

farko ba daga nan ya fita ya barsu Tunde ma ya fita bayan ya jaddada musuga abinci nan suci su qoshi tamkar suna gida. Kiran la'asar da akayi ya saka Audu miqewa ya shiga dakin. Nan dinma lailaye yake da Kafet ga gado na Alfarma da sif irin ta cikin Bango se mudubi daga gefe. Qofar da yake zaton itace ta bayin ya bude ya shiga.

A zuwansa Lagos sun taba zuwa gidansu wani Abokin Yakubu da suke karatu tare a can ya koyi kunna irin famfon daya gani anan idan ba haka ba da yau an sha kunya. Ya kunna Famfo ya tara hannu da niyar Alwala yaji ruwan zafi sabanin na sanyi. Wannan dalili ya sakashi canza shawara, sosaiya ya gaji jikinsa na ciwon wahalar mota dan haka ya dakko soso dan yaga sabon sabulu a kwalinsa ya koma bandakin ya tara ruwa me zafi a bokiti ya sheqa wanka a bandakin yan gayu yayi Alwala ya fita. Tsaf ya shirya yana jinsa kamar yau ya fara wanka a rayuwarsa. Idanbeyi qarya ba fatarsa har wani sulbi tayi taji sabon sabulu. Anan yayi sallah seda ya idar ya tuna da Baballiya sukazo ya fito falon, nan ya ganshi Baje kan kafet yana bacci ga Abincin daya kacaccala nan ya barsu bude se zuba munshari yake kamar wanda yayi awanni da kwanciya baccin.

Tsabar takaici besan sanda ya kai masa hauri da qafa ba ya kuwa miqe a zabure ze kurma ihu Audu ya zare masa ido dole ya nutsu ya hau sosa inda ya haureshin yana tura baki girman Banza yake dashi amma ya ringa abu kamar qaramin Yaro. A gaba Audu ya tasashi seda ya tara masa ruwan wanka ya kuma zuba masa wani a Buta yaja masa kunne akan karya kuskura ya kunna musu famfo ya lalace kafin ya koma falon ya harde kamar gidansa ya shiga cikin Abinci yana ayyana abubuwa dayawa a ransa. Yana da manyan burika da yake fatan Allah ya cika masa.

Ze ginawa Bara'atu irin wannan Aljannar duniyar, ya hasko kansa yana tuqa mota irin wadda aka dauko su a ciki ha ma'aikata ko ta ina idan ya wuce su ringa zubewa suna gaishe shi dan shidin mutum ne me Izza yana so a girmama shi matuqa. Seda yayi damkafin ya tattare sauran gefe ya rufe, can dakin ya leqa ya hango Baballiya kan gado yayi rashe rashe yana bacci ya girgiza kai kawai yana murmushi, falon ya koma ya kishingide kan kujera bacci ya sace shi besan tsayin lokacin daya dauka ba sunansa da ake kira ya farkar dashi ya hau murza ido.

"Sannunku, na tayar dakai ko?" Tunde ya fada fuskarsa da Fara'a. Audu ya zauna sosai yana cewa

"Aa babu komai ina zaune ma bansan bacci ya dauke ni ba"

"Ai kun sha gajiyar hanya, daman Alhaji ne ya dawo sannan kuma anyi Magriba shiyasa ma yace a kirawo ku masallaci" Tunden ya sake fada. Audu ya kalli qaton Agogon dake jikin bango kafin ya miqe da hanzari ya wuce dakin Tunde kuma ya fita. Seda ya dalawa Baballiya dukan gaske dan ya gaji da kiran sunansa yana jijjiga qafarsa kafin ya miqe yana soshe soshe. Audu ya wuce yayo Alwala, a bakin gadon ya ganshi ya sake kifewa aiko ya kuma kai masa mari ya farka da gudu ya fada bandaki. A rayuwarsa zece be taba bacci me dadin na yau ba. Yana ganin babu wata Katifa data kai tasu ta gidan Yaya Audu dadi da laushi seda ya hau wannan yaji ashe shi akan sumunti yake kwana.

Yanda Alhaji ya ringa haba haba da Audu har seda abin ya bashi kunya, mamakin daya sake kamashi ganin tamkar duk mutanen gidan sun san labarinsa,

"Aboki nane na Kano da na gaya muku" abinda Alhajin yake fada kenan kowa se ya fara

"Ikon Allah shine sannu da zuwa ya hanya" a haka sukayo sallah suka dawo cikin gidan kai tsaye Alhaji dake riqe da hannun Audu ya wuce dashi Asalin ginin da suka wuce dazun.

Falo na Alfarma da ya qawatu da jere tamkar a qasar turawa. Alhajin ya zauna kan Kujera Audu yayu qasa ze zauna ya riqo shi yana cewa

"Haba zauna nan sama mana, kaima samu guri ka zauna" ya fada yana kallon Baballiya daya zubawa chandler ido kamar ze kamota. Qofar glass din dake cikin falon ta bude, wata farar Mace kalar Madara ta fito cikin kwalliya ta kece raini tamkar me tafiya biki qamshinta ya baza gurin ya hade da sanyin Ac dana freshner da aka saka. Fuskarta dauke da murmushi take takowa tamkar yanda shima Alhajin dake kallonta yake murmushin.

"Lale maraba da baqin Kano" ta fada tana zama gefen Mijinta. Audu ya zame ya shiga gaisheta ta amsa tana tambayarshi Hanya, seda ya mintsili Baballiya kafin ya shiga hayyacinsa ya gaisheta itama. Da daddaya yaran sa suka fara shigowa falon, Namiji daya fara shigowa wanda zasuyi sa'anni da Audu se mata guda biyar da suka biyo bayansa gaba dayansu farare ne tamkar Alhajin da Hajiyar gasu yan gayu abinda ya burgeshi dasu yanda suke da fara'a sunata haba haba dasu babu kyama ko nuna banbancin sun fisu matsayi.

A kan qaton Dining din gidan suka zauna duka sukaci Abinci dukda Audu yaqi da farko Amma Alhaji yace se sun zauna shima Dansa ne kuma baqonsa a dole ya dan tsakuri abincin dukda damab cikinsa a cike yake har sannan Baballiya kuwa be kwari kansa ba yaci iyakar geji, har addu'a Audu ya ringa masa a zuciyarsa ta cewar Allah rabashi da lalacewar ciki irin yanda ya zage yana narkar Abinci kamar kwancen Yunwa koda yake sabon dandano yaji a harshen sa. Seda suka gama cin abincin gaba daya suka koma cikin falon. Alhaji ya kalli iyalansa yana cewa

"Wannan shine bawan Allahn dana baku labari ya taimake ni a Kano, duk tsayin lokacin nan babu ranar da ba zanyi Addu'a Allah ya sake gama fuskokinmu ba se gashi ubangiji ya karbo Addu'ata"

"Aiko dai ranaku daddaya ne Dady bazeyi maganarka a gidan nan ba, babba da yaro dan gida da me aiki babu wanda be haddace Abokin Dady na Kano ba ni na dauka zanga wani tsoho irinsa ashe ma Dan Saurayi ne" Daya daga cikin yammatan ta fada wadda kuma da alama duk ta fisu kaudi da iyayi. Baze iya fadar ko ta nawa bace a jerin haihuwa saboda su biyar din kusan kansu daya, da gani irin haihuwar kwanika ce kuma da yake suna da garin jiki shiyasa suka tashi kai daya.

Namijin ya kalleta yace

"Kodai kin qyasa ne kike kiransa wani dan saurayi?"

"Kai Yaya" ta fada tana rufe fuska alamar kunya, Alhaji yayi dariya cike da nishadi ya nuna Namijin yana cewa

"Wannan shine babban Da na Jamal, likita ne ya kammala karatunsa shekara biyu data wuce a Jami'ar qasar Ingila harya fara aiki kuma ina kan kammala gina masa Asibiti nasa na kansa daze cigaba da kulawa dashi, wannan Sakina kenan ita take bi masa se Salima, Ummulkhairi, Mamana Binta se kuma Auta Munira" ya qarasa yana shafa kan Autar da ita ce bata kai girman sauran ba. Ya sake nuna Sakina,Salima, da Ummu yace

"Wadannan duk suna da Aure Sakina nada Yara biyu ragowar nada daddaya kaga jikokina hudu kenan, saboda zuwanka yasa duk suka zo Mamana da Auta kadai suka rage se Yayansu"

"Masha Allahu" Audu ya fada yana sake kallonsu gasu nan abin sha'awa. Sakina ce tace masa Mijinta yana zuwa Kano da akwai Yayansa acan yake zaune shi a unguwar goron dutse. Audu ya washe baki jin an an bato unguwarsu yace

"Wurin ina a Goron dutse? Ai anan nima gidana yake"

Da mamaki Alhaji ya kalle shi yace

"Oh daman a cikin Kano kake da zama?" Ya shafa kai yana cewa

"Eh a nan nake gwadago, da ina zuwa ina komawa gida amma yanzu bayan rasuwar Innarmu nayi qaura gaba daya da Iyalina muka koma cikin Kanon"

Take fara'ar dake kan Fuskar wadda aka  ambata da Binta ta bace, yanda ta hade ran lokaci guda yasaka kowa ya fahimci sauyin nata banda Alhaji da ke jajantawa Audu rasuwar Dada yayi masa ta'aziyya ya dora da cewa

"Kace kana da Iyali? Ikon Allah"

"Kwarai kuwa Alhaji, idan watan Sallar tsofaffi ya kama shekarata biyar kenan da Aure ina kuma da Yara biyu Maza"

Alhaji da Hajiya suka hada baki gurin cewa

"Ikon Allah ashe harda zuri'a, kai amma abu yayi kyau masha Allahu Allah ya raya yayi musu Albarka, wannan dai qaninka ne ana gani base an tambaya ba" ya fada yana nuna Baballiya dake zuba gyangyadi, bayan ci ai se a kwanta kuma a huce gajiya.

A fusace Binta ta miqe, Mamanta dake ankare da ita ta kalleta tana cewa

"Ina kuma zakije ana hira?" Tayi kwalwal da ido kamar haqaye zasu zubo mata tace

"Kaina ne yake ciwo Mama kwanciya zanyi" bata ko jira me zata ce mata ba ta wuce har tana hadawa da sassarfa saboda yanda take qoqarin fashewa a gurin, wani irin tuquqin bacin rai takeji data rasa na menene. Ta rasa gane meye hadinta da wannan dan qauyen da daga jin yace yana da mata zuciyarta ta fara kumbura wannan shi ake kira da daukar Dala babu gammo kenan.

Page 10

Qarfe tara na bugawa daya daga cikin ma'aikatan ya shigo cike da ladabi ya sanarwa da Alhaji Mijin Sakina da Mijin Ummu na waje Alhajin yace yayi musu iso.

Irin alaqar da ya gani tsakanin Alhajin da surukan nasa ya burgeshi. Wato su Yan boko komai nasu da birgewa yake (nada kenan da suka hada Boko da Addini se rayuwar ta zama me burgewa da ban sha'awa ba Yan Bokon yanzu da suka dauki fitsara a matsayin wayewa ba). Ya tuna lokacin da Mahaifinsu na raye, ko a masallaci baya hada sahun sallah da Mijin Mairo da Amina wai surukuta daga gaisuwa babu wata magana da take qara shiga tsakaninsu babu wata shaquwa a tsakani su kuwa bayan gaisuwar gashi har an zarme hirar aiki suna fadawa Alhan abubuwan da suke ciki. Ya nuna musu Audu wanda sun gaisa tun shigowarsu yace

"Ga Abdullahi nan shine baqon da matanku suka zo wa sannu da zuwa" aka sake maimaita gaisuwa data fi tada, matan kuwa tuni kowacce ta shige cikin gidan se gata da mayafi da jaka se yaga kamar har hoda da gazal suka qara da turare dan suna shigowa falon ya sake rikicewa da sabon qamshi, sukayiwa Iyayensu sallama suka fice harda Salima wadda su Ummu zasu sauketa dan unguwarsu daya, a yanda Yaji Mijinta Soja ne baya gari.

Bayan fitarsu Mama ta miqe itama tana cewa Mijinta bari ta shiga ciki taga koda abinda za'a qara kawowa su Audun, ta kalli Baballiya dake zuba gyangyadi tace

"Kaje ka kwanta abinka dan idan ba'ayi wasa ba Yayanka da Alhaji yau kwanan hira zasuyi"

Alhaji yayi dariya yace

"Kamar kin sani, a kawo mana shayi dan muji dadin hirar" ta wuce tana dariya. Alhaji ya kalli Audu yace

"Gaba daya murnar ganinka tasa na manta na tambayeka dalilin zuwanka Kaduna, ko kuwa dai ziyara kawai ka shirya kawo mun?"

Audu ya sosa qeya yana murmushi yace

"Kusan haka Alhaji, Allah ya nufi zamu sake haduwa shiyasa ya kawo mun tafiyar babu shiri" ya nuna Baballiya yaci gaba da cewa

"Wannan yaron ne ya dage akan aikin soja yake so yayi, nayi tambaya acan aka gayamun da akwai Jami'a ta karatun Sojoji da aka bude a nan Kaduna shiyasa na shiryo na taho dashi dan muji ya tsare tsaren makarantar yake".

Alhaji ya gyada kai cikeda gamsuwa yace

"Aiko kazo akan gaba dan suna cikin dibar dalibai ne idan banyi kuskure ba a cikin satin nan nakejin kamar zasu rufe ma dan haka gobe idan Allah ya kaimu zan hadaku da Tunde ya kaiku can NDA din, Abokina General Hanna Balogun shine mataimakin shugaban makarantar nasan babu matsala da kunje zeyi muku duk abinda ya kamata".

Murna ta cika Audu, wato ubangiji ya soshi da rahma shiyasa ya bayyano masa da katin Alhaji Tijjani, ya ringa masa godiya Alhajin yace

"Haba Abdullahi, ai tsakaninmu babu godiya Allah ne ya hadamu kaga kuwa duk abinda nayi maka ai banfadi ba domin kai ka fara taimako na".

"Binta ta shigo da qaramar sallama hannunya dauke da qaramin Try da aka fora butar shayi ta qarfe irin ta buzaye da qananan kofuna suma na qarfen guda biyu akai, Alhaji dake bawa Audu taqaitaccen tarihinsa shidin mutumin Paki ne tanan Kaduna Mahaifinsa haifaffen nan ne mahaifiyarsa Baturiya ce tun zuwan turawa Mahaifinsa suna cikin na farko farko da suka karbi Karatun Boko har ya samu damar tafiya qasar Ingila acan kuma ya hadu da mahaifiyarsa Janet sukayi Aure su uku suka haifa shine na biyu akwai Yayarsa Ketrina se qaninsa Muhammad, su biyun sun bi Addinin Mahaifinsu banda Babbar Yayarsu dukda daga baya dabda Mahaifiyar tasu zata rasu ta karbi Musulunci shekaru biyar da suka wuce kenan ta mayar da sunanta Fatima amma ita Ketrina Allah be nufa ba suna dai yi mata fatan karbar shiriya kafin mutuwa ta risketa.

Binta ta Ajiye Try Alhaji ya kalleta yace

"Sannu Mamana, ban lura ba dazu ashe kin tashi ba'a qarasa hira dake ba"

Ta dan yatsina fuska cikin salon sangarta tace

"Dady kaina ne yake ciwo shine naje nasha magani"

"Sannu Allah ya sauwaqe" Alhajin ya fada cike da kulawa Audu dake kallonta irin kallon qurilla yana hango siffar Turawa a tattare da ita se yanzu ya gano dalilin da yasa Yayan Alhajin har shi kansa suke kamar wanke hannu ka taba, jikin da suke dashi kuma gurin mahaifiyarsu suka gada kenan tunda a cike take qosasshiyar mace bawai irin shirgegeiyar nan da tsoka da kitse yayiwa yawa ba.

Tsakin data buga a daidai saitinsa ya maidoshi hayyacinsa, ya sosa kai, Alhaji dake ankare dash yayi murmushi kawai Binta ta wuce tana qunquni. Kadan yasha shayin dalilin Alhaji ya matsa masa suna sha yana tambayarsa Kasuwa da irin harkokin da yake tabawa.

"Har yanzu kana siyar da Man kuwa?" Alhajin ya tambayeshi. Audu ya kurbe dan saurab shayin cikin kofinsa yace

"Aa wlh, tunda na bar Bechi na saki harkar dan dama dalilin farata saboda haihuwa data zowa matar yayana cikin dare muka rasa wanda ze kaimu Asibiti duk masu Ababen hawa sukace basu da Mai hakan yayi sanadi har aka rasa jaririyar wannan yasa na fara sana'ar daman kuma Baballiya ne yake zama a gurin to yanzu muna tare babu wanda zeci gaba da kulawa dashi shiyasa na bari"

"Yanzu se bige bige kenan kakeyi?" Alhaji ya sake tambayarsa, Audu ya danyi jim kafin yace masa

"Eh" dan se yaji kamar maganar bata dace ba a tunani da izza irin tasa yana ganin sana'arsa ta wuce a kirata da Bige bige, shida yake da Jarin kusan Dubu dari tasa ta kansa a wancan zamanin banda na Gadonsu da yake juyawa gaba daya idan an hade kudaden da ya zuba a Kasuwa sun kai dubu dari uku ai kuwa ya zarce ace yana bige bige.

Alhaji ya nisa yace

"Yanzu dai ku gama da abinda ya kawo ku tukunna zamu san abinda ya dace ayi, meye matakin karatunka tunda naji jar turanci ka iya sosai?"

"Iyakacina Sakandire Alhaji" Audu ya bashi amsa, gani kamar ya gaji da hirar Alhaji yace suje su kwanta sa qarasa da safe, seda akayi da gaske kafin Baballiya ya tashi dan kan kafet ya baje yake jan Rago son ransa. Da sukaje kwanciya ya ringa tuna Bara'atunsa da yara suna can gashi babu waya ballantana ya kira ya sanar musu sun sauka lafiya da halin da suke ciki. Ya rufe ido, Binta ta shiga yi masa gizo.

A yanzu da yake qara shekaru da wayewa tareda sanin kan duniya kwakwalwarsa cike take da burika da mafarke da yake son cinma. Tun Asali yana da qawazucin auran mace me garin jiki, bawai qatuwa ba Aa cikakkiyar macen da babu qashi a jikinta. A irin shekarun da akeyiwa Mata aure a sannan kuwa yasan cewar baze samu irin kalar da yake da burinba, daga baya ya gane cewa se bayan Matan sun haihu jikinsu yake budewa su koma irin yanda yake kwadayin, tunda Bara'atu ta

haifi Babangida yake baza ido yaga ta fara qiba saboda Balaraba tun qibar ciki bata sace duka ba tana nan yar duma duma da ita ga Ikko data karbeta tasa ta qara wani kyau idan ka ganta ba zakace Matar Yakubu Bechi bace to hakan yayi ta fata daga gurin Bara'atuntasa sedaihar yau data yi haihuwa biyu tana nan tamkar yar matashiyar Budurwar daya aura qirjinta ne kadai zece abinda ya qara girma daga yanda ya aureta gani yake ma kamar qara qanqancewa takeyi idan suka fita se a ti ga dauka qannensa ne ita dasu Abdullahi wannan abin yana damunsa kuma iyakar dadi daze saka jiki budewa yana siyo mata.

Duk daren duniya se sunci Balangu ga fura da zasu dora da ita banda sauran cimaku masu rai da Lafiya amma sedai su suyi bindin bindin har Babangida idan ka gansu girmansu yafi shekarunsu amma banda ita kuma mahaifiyata nada qiba, Babanta kansa ba siriri bane ya rasa inda ta gado rashin Auki ita, ganin Binta ya tada masa da tsohon tsumi da kwadayinsa na Auran mace irinta. Sedai da yake wargima guri yake samu ita zuciyar batayi gigin hasaso masa ita a matsayin tasa ba, Aa yana lissafin samun wata me dama dama kamarta dukda yana matuqar qaunar Bara'atu baya kuma jin akwai wata mace da zata kamo qafarta a zuciyarsa sedai ya dibar mata wasu shekaru da muddin bata kai muradinsa ba ze qara Aure, badan baya sonta ba ko ya raina Halittarta Aa sedan kawar da qawazucinsa ya kuma kade hankalinsa daga kallon manyan matan da zuciyarsa take so.

Haka ya kwana yana mafarki harma ya qara Aure ya samo yar duma duma. Washe gari haka aka sake kiransu cikin gida sukayi karin kunallo tareda Iyalan Alhajin. Dankali kadai suka iyaci daga shi har Baballiyan se Burodi da ruwan shayi, tare suka fita da Alhaji seda Tunde ya sauke shi a gurin aiki kafin suka wuce NDA wanda Alhajin ya rigada ya sanar da Abokinsa zuwansu dan haka basu sha wahala. Anyiwa Baballiya duk wani sikirinin daya kamata sun karbi takaddunsa sun kuma gaya musu zasu sanar da ranar da za'a fara tirenin a gidajen Radio da kuma Talabijin dan haka su ringa saurara.

Da wuri suka koma gidan, A tsakar gidan suka tarar da Binta da Munira wadda da alama itama dawowarta kenan daga makaranta dan Uniform ne a Jikinta suka gaisa har yayi mamakin sakin fuskar Bintan yau sabanin jiya da tunda ta tashi da sunan ciwon kai taketa fushi har dazu da safe kafin su fita. Seda ya leqa ya gaida Mama tace za'a kai musu Abinci yanzun yayi godiya ya wuce masauki a ransa yana tunanin daya san da wuri zasu gama da sunyi sallama da Alhaji kawai sun wuce Kano, amma babu damuwa gobe zasuyi Asubanci da yardar Allah su tafi.

Da la'asar yana zaune gurin megadi suna hira Baballiya ana daki ana shan Ac tsabar tsiya hancinsa ya toshe saboda rashin sabo amma yaqi haqura wai idanya tafi babu tabbacin ya sake ganin ta. Binta ta qarasa gurinsu Audu tasha kwalliya da Atamfa dinkin tazarce, tana da tsayi da jiki ba qaramin kyau kayan ya mata ba ga kalar Atamfar da take da duhu ta sake haska farar fatarta tayi daurin gaban goshi, Audu besan kallonta yake ba seda Malam Saminu ya tabashi ya wayance da kallon qasa.

"Sannu Abdullahi hira kukeyi?" Ta fada bayan data tsaya kusa dasu. Audu ya daga kai ya kalleta ita dinma shi take kallo tana masa murmushi dan haka ya qaqalo murmushin shima ya amsa mata.

"Ko zaka dan rakani nan bayan layi zan karbowa Mama saqo a gidan qawarta?" Ta sake fada, kamar yace Aa danbega dalilin da zata jera dashi ba se kuma ya miqe ko ba komai ya sake zagawa ya bawa idonsa abinci.

Gwanin sha'awa suna tafe suna hira wadda Bintan ce take takalarsa har besab sanda ya ware ba yana maida mata har suka isa gidan qawar Maman ta shiga bata jima ba ta fito da Leda ya karba suka juyo.

"Kace sunanka Abdulwahab suna me dadi ya akayi ka bari aka bata maka suna wai Audu?" Binta ta tambayeshi, yayi murmushi yace

"Kinsan mu mutanen karkara ba kamar ku na birni bane"

"Ai kai bakayi kama da mutumin qauye ba ko kusa idan ba an fada ba, ni da Dady yace iyakarka Sakandire ma nayi mamaki amma ya akayi ka iya turanci haka?" Ta sake jefa masa wata tambayar yayi murmushi yace

"Kinsan ni ina da son kudi, da za'a kaimu Kano Almajiranci Abokina da yake karatun boko a can yace mun Malamansu sunce idan sukayi qoqari zasu tafi dasu ingila zasu samu kudi sosai, shiyasa dana shiga makaranta nafi mayar da hankali akan koyan turanci saboda idan naje ingila kinga bazan sha wahala ba na iya yarensu se daga baya na gane duk qaryace Ashe na watsar da Bokon na kama Kasuwa, amma Yayana da muka fara tare saura wata kadan ya kammala karatun Shari'a a Jami'ar Ikko"

Binta ta ringa dariya jin abinda yace, tace masa

"Wato Ingila kake so kaje, kaga ni kuwa ko yanzu naga damar shiga tikitin jirgi kawai zan yanke saboda inada katin zama yar qasa nacan"

"Haba dai?" Ya tambayeta kamar be yarda ba dan shaf ya manta da Mahaifiyar Alhaji kakarsu kenan Baturiya ce. Binta tayi murmushi tace

"Dagaske a can aka haifeni lokacin Dady yaje qara karatu kuma na zauna a gurin Mah seda ta fara rashin lafiya me muka da wo nan tare gaba daya harta rasu shekara goma kenan, idan kaima kana son zama dan qasar to ka Aurkjioieni Hawaii se Hawaiixna tafi dakai kaga shikenan zaka samu katin zama Dan Ingila"

Tuntube yaci, badan Allah ya taimakeshi wani takalmin dafaffen danqo ne sauciki a qafarsa da idan ka ganshi zaka dauka na fata bane da yasan babu abinda ze hana faratansa ficewa yau dukda haka seda yaji zafi ya dage qafar dayayi tuntuben da ita yana kada hannu Ledar daya ruqo mata ta fadi Binta ta dauke tana masa sannu, seda ya daidaita kafin sukaci gaba da tafiya, ita da bata san dalilin tuntuben nasa ba taci gaba da cewa

"Kaga shikenan ka zama baqin Bature, semuyi komawarmu can da zama dan ni daman nafi jin dadin can akan Nigeria, ko dan can nayi wayo shiyasa?"

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out  ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane  , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Rasa abinda zece mata yayi dan ya rasa zolaya ce maganar tata ko kuwa har ranta da gaske take? Idan zolaya ce to irin wannan maganar gaskiya bata dace ba domin dai sanin sa ba'a wasa da maganar Aure, idan kuma da gaske take to abune bame yuwu ba kai qarya ne ma me zatayi dashi baqauye da besan komai ba dan talakawa ita kuwa yar gata jikar Turawa gata nan son kowa qin wanda ya rasa kai wannan qanzon kurege ne kawai ba abune me yuwu ba. Zuciyarsa ta tambaye shi to idan da gaske take shin ze amince ne ko kuwa? Seya rasa amsar da ze bawa kansa dan haka yaci gaba da shiru har suka isa gida Itama da taji yayi shiru seta bar maganar, a Get ya sake zama tayi masa godiyar rakiya ta shige ciki Malam Saminu ya shiga zolayarsa yana cewa

"To kodai yar gida za'ayi da uwar masu gida da Baqon Alhaji?"

Audu ya kalleshi bedai ce komai ba Saminun yaci gaba da magana yana cewa

"Nayi mamakin yanda yarinyar nan ta shiga sabgarka, ka ganta nan sedauwar da uban suka tashi tsaye kafin ta saitu tabi hanyar kwarai farkon dawowarta saga Turai ma'aikatan gidan nan iska me dadi bama iya shaqa idan tana nan. Ta tsani Talaka a

yanda take fada da bakinta ta kuma tsani duk wani abu da ze hadata da takauchi. Juma'a Juma'a Alhaji na sadaka a qofar gidan nan zaka ga an cika danqam haka zata fito ta watsa mutane tayi musu rashin mutunchi seda uban ya zaneta wata rana kuma da quruciya lokacin yanzun dai komai ya lafa dukda dai bazan ce ta bar halinta kaf ba amma ta rage sama da kaso Saba'in a ciki yanzu dai babu ruwanta damu idan kaga tayi rashin mutunchi to sabgarta ka shiga da muke taka tsantsan da ita kuwa lafiya lau ake zaune dama bata gaida mu bamu isa ba mu muke gaisheta kuma uban duk cikin Yaran yafi sonta shiyasa ma da Mahaifiyarsa ta karbi shahada ya bata irin sunan ta".

Audu dai jinsa kawai yake sedai ko kadan be hango wani hali na rashin mutunchi da Saminun yace tana dashi ba domin kuwa tun zuwansa jiya tsaki kadai tayi masa wanda yanzu yake tunanin ma qila ba dashi take ba tunda gashi har ta nemi ya rakata guri sunje sub dawo suna hira idan da ta tsani talaka kamar yanda ya fada baya zaton ko kallo ya isheta tunda dai yasan Alhajin ya gaya musu inda ya sanshi, ya kuma kwatanta musu qauyensu to me ze saka tayi masa wasan ya aureta in har bata son talaka?

Suna nan Saminu nata bashi labaran gidan Alhaji ya dawo, Audu ya rakashi har bakin qofar falo kafin ya koma masaukinsu yayo Alwala saboda magriba da aka kira. Sanda suka zauna zaman cin abinci ya sanarwa da Alhajin gobe da safe zasu juya Kano, gaba daya mutanen gidan suka nuna rashin jin dadinsu. Alhaji yace

"Na dauka zakayi mana sati ko sama da haka? Ga tafiya da zanyi zuwa Rivers da ina cewa zamu je tare"

Audu yayi qasa da kai cikin ladabi yace

"Ai Alhaji saboda na baro abubuwa da yawa a can gidan kasan komai idan babu idon mutum ba lallai ayi yanda ya kamata ba"

"Hakane ga iyali kam an baro kodan saboda su yaci a Koma" Mama ta dora abinda ya qara dagulawa Binta lissafi kenan farko damuwar tafiyar da yace zeyi ga kuma zancen iyali da Mama tayi.

Miqewa tayi kamar jiya ta bar gurin, Alhaji ya kira sunanta ta tsaya

"Lafiya Mamana baki gama cin abincinki ba zaki tashi?" Ya fada cike da kulawa, ta kwararrabe fuska tace

"Dady kaina ne naji ya fara ciwo"

"Ke kanki baya tashi ciwo se ana maganar Audu kenan" Mama ta fada tana hararar ta, ta juya ido tana kallon Audun tace

"To ni ina ruwana dashi kawai kaina ne yake ciwo bari naje nasha magani" daga haka ta shige ciki Mama tace

"Kyaji da gulmarki dai"

Alhaji yayi murmushi yace

"Aa fa karki saka mun Mamana a gaba" ya juya kan Audu dake juya cikalo a kan farantin dayaci abinci yau tuwo akayi ya kuma san saboda su ne yaji naman kaji da man shanu yace

"Da zaka daure kayi satin da akwai dalilin da ya saka nake so ka zauna"

Audu yayi jumm, baya so yayi masa musu dan haka kawai yace

"Toh, Allah ya kaimu amma inaga zan tura Baballiya ya koma shi saboda Kasuwa"

"Hakan yayi kyau" Alhaji ya fada. Tun a daren ya cewa Baballiya ya shiya dan Asubanci zasuyi Tunde ne ze mayar dashi kamar yanda Alhaji yace. Baballiyan ya ringa qunquni ya baqin rai amma da yake babu damar wargi dole ya hada yan komatsansa yana tunanin yanda ze koma yaci gaba da kwana akan Katifarsu ta gida me kama da Dakin din sumunti idan aka hadata data gidan yan gayu. Washe gari kuwa qarfe shida suka dauki hanya Bayan Alhaji da Mama sun hada masa sha tara ta arziqi da tsarabar da ze kaiwa su Bara'atu.

Audu ya rubuta wasiqa ya bashi ya kai mata a ciki ya sanar da ita duk abinda ya faru da dalilin zamansa zuwa ranar da ze dawo. Shi yayiwa Tunde cikakken kwatancen zuwa inda yasan idan Baballiya ya gani ze iya kaisu gida kafin suka dauki hanya suna musu fatan sauka lafiya. A ranar tare suka fita da Alhaji gurin da yake aiki wato Matatar Mai ta Kaduna. Audu na zaune a office dinsa tsayin lokaci bayan Alhaji ya fita ya barshi sannan ya dawo ya same shi.

"Na barka kai kadai ko? Meeting muka yi" Alhaji ya fada yana zama akan kujera, Audu yace "babu komai ina ta kallon Talabijin ma bansan lokacin ya ja haka ba".

"Dalilin da ya saka na taho dakai saboda kaga gurin da nake aiki, ko ban fada maka ba kasan nan din ina ne, matatar Mai ce, itace Ma'aikata mafi girma da daraja da kuma kawo kudin shiga a Arewa baki tana kuma takewa ta Legas data fatakwat baya. Na so ace kayi karatu me zurfi ko da Diploma ce saboda a nan gurin takardar sakandire sedai a daukeka a matsayin lebura bawai babban Ma'aikaci amma dukda hakan bata baci ba, na dade ina so na bude gidan Mai a Kano, sedai rashin Ido ya saka ni daqile qudurin nawa amma yanzu dana hadu dakai ina ganin lokacin ne yayi ina so ka gwada harkar mai domin ana samun Alkhairi sosai da sosai a ciki"

Audu yaji abin ya masa girma, domin a sanda yake bunburutu yayi bincike cikin sabgar yaso ya shigeta da gaske amma irin maqudan da aka karanto masa wai a talauce ze zuba a matsayin jari bashi dasu baya kuma tsammanin nan da shekaru goma ze mallake su sedai kuma lamarin ubangiji babu yanda baya zuwa se gashi ya samu tayin shiga harkar daga sama duk se ya rasa abinda zecewa Alhajin. Sunyi maganganu sosai, Alhajin yace masa idan ya koma Kano ya nemi guri da yake ganin zasu fara bude gidan Man ze hadashi da wakilai da zasuje tare da zarar guri yayi za'a fara aikin ba tateda bata lokaci ba domin tuntuni ya samu lasisin yin hakan Allah ne bai nufa ba se yanzu. Suka yita hira Alhajin yana fada masa yanda harkar take, sirrikan kasuwar da yanda ake tafi da ita dashi kansa abubuwan daya mallaka a ciki da wadanda yake shirin mallakar. Se yamma lis suka koma gida cike yake da murna yana hasaso yanda zata fashe nan da wani dan lokaci Audu ze zama manajan gidan Mai.

Ya ringa hasaso nan da shekaru kadan shima ze mallaki nasa idan Allah ya yarda.

Seda yayi sati cif kafin ya shiryi tafiya Kano tareda wakilan da Alhaji ya hadashi zasuje duba gurin da za'a assasa gidan Mai, a cikin satin kullum se sun fita da Alhajin haka yayi ta sakashi cike ciken takaddu, ana gobe zasu tafin kusan raba dare sukayi a tsakar gida da Binta suna hira wadda ke cike da Alhinin rabuwa da juna. Wata irin shaquwa ce ta qullu tsakaninsu, shidai Audu a bangarensa babu wani abu face ya dauki Bintan a matsayin qanwa kuma diyar mutum mai daraja a gurinsa da yake shirin canza rayuwarsa. Sedai ita ba haka bane a bangarenta, duk yanda taso hana kanta ta kasa tilas ta amince da tana qaunar Audun kuma duk sanda ta tuna haka se taji kamar ta rufe kanta da duka tsabar takaici.

Bata san sanda haka ta faru ba, yaushe zuciyarta ta yanke mata wannan danyan hukunci dukbata sani ba kawai dai ta tsinci kanta dumu dumu a soyayyar Audu Bechi kuna ta gagara boye hakan ta nuna masa sedai sam yaqi nuna mata ya gane abinda ta ke ciki ita kuma ba zata iya karya bille ta zubda girmanta ta fada masa da fatar baki ba domin ta wuce da Ajin haka, zuciyace me aiki gaba gadi ta janyo mata

ba tareda tayi shawara da ita ba koda yake bataga laifinta ba, Audun Namiji ne ingarma irin zabinta. Dukda cewar be yi wayewar Azo a gani bata tabbatar zuwa gaba za'ayi Namijin gaske musamman yanzu da ta fara hango haske a gobensa saboda yanda Dady yake tsamo tsamo cikin Al'amarinsa, a kuna dan zaman da sukayi yanda yake bata labarin Harkokin da yake tabawa ta tabbatar Gobensa zatayi kyau. A tsarinta kuma tana so ta auri Namijin da zasu ginu tare suyi Arziqi tare ta yanda babu wanda ze bigi qirji yayi mata kankanba akan sa.

Haka ya tattaro ya dawo Kano, beko huta ba suka shiga neman lokashon inda za'a kafa gidan Man. A cikin kwanaki biyu aka samu, filin a bakin titi yake sukayi dace na Magada ne ana kan gabar yin rabo daman neman me siya sukeyi babu bata lokaci akayi ciniki suka karbi fili a bisa qololuwar darajarsa. Abinda ya qara bawa Audu mamaki hatta da Filin da sunansa aka yi takarda, be manta ba gidan man kansa Alhaji ya tambayeshi sunan da yake so ayi masa register dashi yace masa meze hana ya saka sunansa Zakariyya Paki amma Alhajin yace masa Aa, shiya bawa zabi daga qarshe BECHI ENERGIES akayiwa gidan man suna sannan ga fili an siya da sunan Audu.

Cikin qasa da watanni biyar aka bude gidan Man wanda ya kasance na farko a Kano mallakin mutum ba kamfani ba, dangi yan uwa da Abokai sunyi masa murna. Yan Bechi duk sunzo bude gidan Man dukda yana gayawa kowa bana sa bane na ubangidansa ne, ya kuma debi ma'aikata harda Yayan yayyensa silar barowasu Bechi kenan suma. A taqin lokacin Audu yaje Kaduna babu adadi, soyayya ce ta qullu tsakaninsa da Binta wadda besan sanda shima ya afkawa soyayyar tata ba. Abinda ze iya cewa kawai Bintan tayi daidai da tsarinsa, kuma ita ta bashi fuska shiyasa beyi shayi ko jin dar na amincewa da buqatarta ba dukda ya kanga kamar abin bame yuwuwa bane amma tabbas yana son Binta kuma in har ya samu dama ze aureta.

Page 11

Kamar da wasa magana ta qullu tsakaninn Binta da Audu, da kanta ta sanarwa da Mahaifinta wanda yayi matuqar murna da Al'amarin saboda shidai Allah ya saka masa qaunar Audub a ransa tamkar dan cikinsa haka yaje jinsa. Mahaifiyar ta dai saisa saisa, bata nuna qinta ga Al'amarin ba haka kuma batayi murna ba saboda a ganinta Audun barene. Haduwar hanya bata isa tasa Alhaji ya daukake shi haka bayan aminta dashi akan dukiyarsa kuma yace zero dauki Yarsa mafi soyuwa ya aura masa ba. Yan uwanta kuwa kaf da sukaji take suka nuna qin Amincewarsu.

"Allah ya sauwaqe, ke wace kalar wawiyace Binta? Kodai irin Asirin da yayiwa Dady duk ya rikice a kansa kema yayi miki? Daman qauyawan nan da surkulle suke wlh ban yarda da wannan Al'amarin ba Asiri yayi muku daga ke har Dadyn kuma dole mu tashi tsaye mu karya" Salima da take takewa Binta baya a fannin tsiwa ta fada aiko Bintan ta maka mata harara tace

"Idan ma Asirin ya mun meye naki a ciki? Ke zaki aure shi ko kuma ke zaki zauna dashi?

Da kika Auro Inyamuri waya ce miki qala seni da zan auri Bahaushe dan uwana. Ni bana fada muku dan ku yarda ko karku yarda bane kawai dai a matsayinku na yan uwana ya kamata ku sani Aure da Audu kuma babu fashi in sha Allahu" ta fada tana murguda baki.

Haka aka ringa dauki babu dadi, sun nuna qin Amincewarsu qarara Jalal ne kadai da yake Namiji beqi abun ba dukda be nuna dokinsa a fili ba tamkar dai mahaifiyarsu amma da yake Bintan ta kafe kuma Alhaji yayi na'am haka aka qulla magana.

A bangaren Audu kuwa sanda ya sanarwa da Yakubu da sukaje hutu maganar tashin farko shima ya nuna be yarda ba.

"Haba Audu, daga ka fara samun duniya sakayyar da zaka farayiwa Bara'atu da ita kenan ta qarin aure? Karka manta sadaukarwar da yarinyar nan tayi maka. Kwata kwata ma shekarun mu nawa da auran matan namu nawa suke? A bariki fa sa'anninsu har yanzu suna gaban iyayensu ana musu kallon qananan yara kai ko me yasa ba zaka barta taci arziqin da kuka tara tare cikin kwanciyar hankali ba?" Yakubu ya fada.

Audu ya karkace, shi fa a yanzu Jin Binta yake kamar daga sama aka yo masa wahayinta tsabar so. Ba wai ya dena son Bara'atu bane Aa, yanda Bintan ta iya magana da tattala Namiji idan yaje Kaduna har ya dawo Kano yayi satittika kafin ya sake komawa cike yake da bege da shauqin kalaman data ciko shi dasu. Ga tarin wasiqu datake rubuta masa masu dauke da kalamai masu gigita tunani, haka ze ringa dauka kullum yana karantawa idan sun qara ya ringa maimaitawa har se yaje ta sake hadoshi da wasu ya dawo yaci gaba da tisa karatun kalaman soyayya. Irin wadannan abubuwan yasa ya fara ganin baiken Bara'atu wadda bata san komai ba bata kuma iya komai ba se abinda ya koya mata ko ya nuna mata.

Ya kasa gane banbancinta da Binta wadda ta kereta a shekaru, sannan ta bangaren wayewarsu babu hadi Binta haihuwar cikin Turawa girman Kaduna zagaye take da gogaggun yan Boko yan uwa da qawaye baya ga haka ita din tana cikin mutane da Allah yayi masu dan banzan wayo da iya magana. Duk dakiyar mutum tana iya canza masa akala a cikin ruwan sanyi yayi abinda take so ba tareda ya ankare ba. Tana da wayo kamar me, ga kissa kamar rainon Tsofaffi da wadannan halayen ta sake kanainaye shi yanda take nuna masa yafi kowa a duniya ya kai matsayin da shi da kansa yasan qaryane be kai dinba kambama shi kawai take amma da yake shi mutum nr me Izza da kuma son a girmamashi a yabe shi hawa yake ya zauna kan duk abinda ta fada baya ko tunanin Izgilanci take masa domin ta fishi ta kowacce fuska amma take nuna masa ita din banza ce akan sa.

Gyara zama yayi ya kalli Yakubu da yayi shiru cikin mamakin abinda Audun yazo dashi yace

"To amma da farko akwai haramci a cikin abinda nazo dashine? Naga qarin auran nan halal ne. Dafa ba'a qara aure da ba'a haife mu ba domin mahaifiyarmu a ta biyu taje gidan Baban mu sannan ita Bintar nan ka san komai game da Alkhairin da mahaifinta yayi mun. Kana kallon laimar Arziqin daya lulluba mun a cikin watanni kadan na damu abinda na shekara goma ina fafutuka ban samu ba meye aibu idan na karbi tukuicin auran yarsa wanda ita tayi mun tayin haka da kanta baka tunin zan zama butulu mara godiyar Allah idan nace zan qita?

Tunda har su basu dubi matsayinsu da nawa ba suka amince zasu bani auran yarsu aikuwa ni bai kamata nace Aa ba kaima kuma be kamata kaqi abin ba domin Alkhairin da yake tattare dashi ba iyakar kaina ze tsaya ba gaba daya ya shafe mu. Kuma ni Bara'atu bani da matsala da ita, mun samu fahintar juna domin ban boye mata komai ba tun farkon maganar kuma ta amince dan haka yanzu abinda ya rage kawai zamuje can Bechi mu sanar dasu Yaya Baba idan yaso se a saka rana da zakuje ku nema mun auran. Ni yanzun duk bama wannan ya dameni ba, tunanin gurin da zan ajiyeta nakeyi".

Duk yanda Yakubu yaso fahimtar da Audu abu yaci tura dole ya haqura tunda dai kamar yanda Audun ya fada abinda yake shirin yi ba haramun bane sedai shima ba qarin auransa ne baya so ba, Audu qaninsa ne kuma Aboki koma yace Amini, duk wani sirrin junansu sun sani yasan da cewar Audu baze iya zama da mace daya ba kuma irin Bara'atu saboda tayi masa kadan sannan a tsari na halitta har yanzu bata kai cikar da yake fata ba amma yaso ace idan ma auran zeyi ya nemo daidai dashi ko a can gida ko a nan cikin Kanon amma dai ya samu yarinya yar Talakawa irinsa da zasu yi zaman lafiya ba irin wannan aure daya gingimo ba. Shi gaba daya ma

gani yake abin kamar da wani qulli ciki, tayaya mutum daga haduwar hanya ze ringa masa irin wannan hidima haka sannan har ya dauki ya ya bashi Aure bayan matsayinsa be wuci na me gadi ko share sharen gidansa ba.

Sanda yayiwa Balaraba zancen yanda ta firgice seka rantse ita aka ce za'a wa kishiyar, ta ringa masifa tana Bala'i wa Bara'atu daga qarshe dai dole ta barta tunda ita da za'ayiwa kishiyar ko a jikinta ina dalilintana daukar dumi?

A can Bechi ma haka Bilki ta ringa fada akan me Audu ze qara aure me Bara'atu tayi masa, amma tunda dai duk basu za'ayiwa kishiyar ba kuma me zama da ita tace taji ta gani dole suka haqura suka zubawa sarautar Allah ido.

Anje an tambayowa Audu Aure, Yaya Baba, Hashimu da Aminu se Yakubu sukaje Kaduna bisa jagorancin Audu. Tarba ta mutunchi akayi musu, basu taso ba seda aka tsaida ranar Aure watanni uku masu zuwa suka dawo kowa na jinjina gidan da Audu yaje neman auran. Hashimu ya ringa yawo a gari yana cewa Auran kwadayi zeyi tunda gashi tun be aureta ba ubanta ya gina gidan mai ya bashi gaba kuma ba'asan me zeyi masa ba. Takanas ya samu Baban Bara'atu akan seya tursasawa Audu ya sakar masa yarsa domin qarshe boyi boyi zata zama a gidan daya auro wannan yar Attajiran Azabatar masa da Ya kawai zasuyi hankalin Inna Hajara ya tashi sanda ta samu labarin irin Amaryar da ake shirin yiwo wa yarta, takanas ta tashi qanwar Bara'atun ta turata tace idan ta samu sarari tazo Bechi tana son magana da ita.

Haka kuwa akayi ta gayawa Audu yayi mata shiri kamar yanda ya saba duk sanda zataje gida ta tafi, Innarta ta ringa nuna mata qalubalen dake cikin auran da yake shirin yi amma se tayi murmushi tace

"Duk hasashe kukeyi Inna kuma Audu yana qaunata na tabbata babu wata mace da ze aura da zata zarceni a zuciyarsa sannan ita kanta da kuke magana tana da kirki. Tun yanzu bakiga yanda duk sanda yaje seta hadoshi da abin Arziqi ya kawowa yara ba dani kaina kuma ya fada mun sam bata da matsala dan haka kuyi mana Addu'a kawai Allah ya bamu zama lafiya" da haka ta kashe bakin Innarta da duk wani dake shirin saka mata rudu a zuciya.

Ba kuma wai bata damu ko kuma bata kishin Auran da Audun yake shirin yi ba, ta damu kwarai dan tana son mijinta, irin rawar qafar da yakeyi akan Amaryar tasa na daga mata hankali amma ta yarda da cewar Damuwarta ba zata saka a fasa abinda Allah ya hukunta ba sannan meye ribar ta tayar da hankali ta rasa mutunchinta da qimarta a gurinsa kuma daga qarshe yayi auran su zauna? Shiyasa ta maida komai

ga Allah shi take roqo kullum dare da rana akan duk fitinar dake cikin aura Allah ya kade musu ita ya sanya zaman lafiya da fahimta a tsakaninsu kuma wannan haqurin da tayi da ake mata kallon wawiya ko yarinta ce take damunta ya saka Audun ya mayar da ita Abokiyar shawara akan duk wani abu da zeyi ko yake shirin yi. Daidai da zancen muhalli ita ya tuntuba akan yanda take ganin za'ayi.

"Gurin saukar baqin gidansu kadai duk unguwar nan babu gida me kyau da tsaruwarsa, gaba daya abinda ya dameni kenan yanzu inda zan ajiyeta saboda kinga ko a shari'ance be kamata ace ka dauko Mace daga cikin daula ka muzguna mata a bangaren muhalli ku sauran buqatu ba" Audu dake faman lissafin kayan lefe ya fada, Bara'atu ta hadiye yawu tace

"Gaskiya idan hakane kuwa ya kamata ace kayi mata tanadi na musamman domin nasan ba zata iya zama a cikin gidan nan ba"

"A ina ma zan ajiyeta toh?" Ya fada yana kallonta, cikin iyakar gaskiyarta tace

"Na dauka zaka toshe qofar tsakiyar dakin nan seka huda mata qofa ta wajene mu tashi da falle daya"

Daya rasa abin ce mata kawai ya fashe da dariya, ya gama rubutunsa ya tattare takaddun ya fita.

Daya tuntubi Yakubu zancen gida ce masa yayi

"Ka sakata a bangarenmu kawai"

"To ku kuma fa?" Audu ya tambayeshi,

"Wannan ba matsala bane tunda kaga idan muka tafi yanzu se mun shekara ko fi kafin muzo, zuwa sannan se musan abinyi" Yakubun ya bashi amsa. Cike da rashin jin dadi Audu yace

"Wai dagaske kake ba zaka zauna ayi Bikinnan kuna nan ba? Wai me nayi da yayi maka zafi har haka ka qullaceni?"

"Bakayi mun komai ba Audu tafiya kuma ka sani ina shekarar qarshe ya kamata ace na ninka mayar da hankali akan Karatuna sannan itama Balaraba na gaya masa tana zuwa makaranta acan to sun koma kaga be kamatu daga farawarta kuma ta ringa wasa ba. Nidai abu dayane da yake damuna na rasa dalilin da sam auran nan be kwanta mun a zuciya ba, ina tsoron ka auro matar da zata wargaza maka zaman

lafiya, ta gurgubtar da kyakykyawan tushen daka soma ginawa. Haka kawai nake jin baka dace da matar Aure ba Audu amma Allah shine masanin gaibu ina kuma yi maka addu'ar Allah ya kawai da duk wani abun qi daga hadinku".

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Biki ya rage saura wata daya, ba qaramin raraka Audu yayiwa jarinsa ba ya hadawa Binta lefe na yar gata aka kai, be bar Bara'atu a baya ba dan itama seda yayi mata lefen dukda be kai na Bintan ba, ya kuma bada aikin sababbin Gado da kujeru daze chanza mata. Yakubu sun kwashe kayansu wanda Bechi ya aika dasu Bilki ta dauki Gado Aisha Kujera ragowar tarkacen yan uwa suka raba sun rabu da Audu akan ze nemi fili nan kusa a tayar masa da wani gini domin siyan bangaren Yakubun yayi dukda Yakubu yace Aa ai gida gaba daya na Audu ne dan da kudinsa ya siyi fili ya gina amma shi yace ba haka ba koda shi ya gina kyauta ce yayiwa Yakubun dan haka yanzun siya yayi kuma in Allah ya yarda kafin su zo Kano ze maida masa da wani.

Ya tada gyaran gurin, anyi toshe toshe da liqe liqe, maginin gaske ya dakko Injiniya akayi masa aikin se ga guri ya fito fes an fitar da Sef cinten daki biyu da falo a tsakiya harda bandakin tsakar gidan aka shigar mata a daki se kitchen aka lailaye ko ina da Torazo gida dai ya fito na zamani a ganin ba za'a kushe ba dukda yasan dai a matsayin Bintan tafi haka amma ai ita tace taji ta gani ko a bukka ze ajiyeta zata zauna. Bara'atu ma ta samu arziqi an saka mata torazo a dakunanta dana su Abdullahi da tsakar gidan, Gadonta ta maida musu can aka saka mata sabon da Audu ya mata ga kujeru da kafet harda kayan Kallo se danqareriyar firiza duk a kayan fadar kishiya ita kuwa me ta manta?

Audu nata doki da murna sanda yan uwan Binta sukazo ganin guri se kuma murna ta koma ciki. Babu kara suka ringa kushe gurin da yada maganganu akan an asirce musu yar uwa banda haka me Binta zatayi dashi balle har ta yarda ta zauna a gurin da ko Boyis kwatan su Albarka. Basu kwana a gidan ba kamar yanda ya shirya musu otal suka kama washe gari suka juya sukaje can sukayi ta cece kuce da fadar maganganu abinda ya saka Mamansu magantuwa kenan saboda yanda suka fasakta muhallin Bintan abin yayi muni. Tayi tsammanin yanda ya zage yayi lefe haka ze qerawa yarta gida kodan ya rage mata radadin auransa da bata so yar tayi, meye amfanin Kudin da Ubanta ya sakar masa domin tana da labarin qanin Kyauta yake bashi mai, idan an kai masa tanka goma kudin Biyar Alhajin yake karba haka tsayin shekara daya bata taba jin yace ga kudi Kaza na Ribar Mai da Audu ya kawo ba amma shine zeyiwa yarta wani Akurkin kaji a sakata a ciki.

Cikin fushi da tari Alhaji da maganar, takanas ya tashi Tunde suka tafi Kano kwanaki biyu bayan komawarsu su Salima a sannan Biki ya rage saura kwanaki goma se ganinsa kawai Audu yayi ba zata. Shidai Alhajin bega aibun gurin da suka ringa fada ba domin a abinda ta rasa a gidansu baze wuce girma da kuma taswirar gini ba dukda haka domin gujewa duk wasu surutai na matar tasa da bata taba qalubalantar wani hukuncinsa ba yasan tayi kawaici matuqa akan lamarin auran tunda har ta magantu yanzu tabbas abin ya kaita maqura dan haka yacewa Audu

"Me yasa baka sanar dani baka da gurin da zaka ajiye Mamana ba?"

Audu yaji wani iri, wato shima ya raina gidan kenan? Amma dai a qarfinsa sunsan yayi abinda ze iya harma ya zarta. Shiru yayi bece komai ba gudun kar zuciya ta kwashe shi ya gayawa Alhajin mara dadi dan be gama hucewa daga fushin cin zarafin da Yayansa suka masa ba daman.

"Ina ganin zan saka a duba gida ginanne idan yaso se a siya a sakata ciki ko ya ka gani?" Alhajin ya sake fada se sannan Audu ya daga kai ya kalleshi. Wato zancen Labahani gaskiya ne da yake cewa idan ka auri yar masu kudi rainin arziqi se abinda ka gani sannan su zasu ringa yi maka iko da gida to idan kuwa haka ne shi ba za'ayi akansa ba, baze bada qofa ba balle daga baya idan ya hana ace yayi Butulci.

"Kayi haquri Alhaji ba ina nufin raini a gareka ba amma maganar gaskiya wannan ne muhallin da nake dashi da zan saka Binta a ciki. Ka sanni ka san Asalina haka itama tun gabanin tafiya tayi nisa a tsakaninmu tasan komai a kaina kuma ta yarda da hakan zata zauna dani a kowanne. Kayi haquri ka barni na ajiyeta a inda Allah ya horemun a yanzu, ina fatan zuwa gaba na gina mata daidai da tsarinta amma a yanzu abinda ya sawwaqa kenan".

Badan Alhaji yaso ba gudun kuma karya takurashi yaga kamar ya masa kutse a cikin lamarin gidansa yasa ya haqura ya tafi kuma kamar yanda Audun ya fada ita Bintan taji ta gani dan ya zaunar da ita kafin a kawo kudin Aure ya tambayeta ta amice tace koda can Qauyensu ze kaita tana sonsa a haka zata aureshi.

Haka akayi Biki Amarya ta tare, iyayenta sun zuba mata abinda dakin ze iya dauka. Danma kuma babu laifi ginin an fitar da dakunan da baga dan haka sun dauke

gadajenta Biyu kantama kantama yan Dubai. Kujerune dai seda aka canzo ainin wanda aka siya mata saboda falon ya matse ga Divida bango guda yar waje kujerun ma irin bajaj din nan ne 1 sitter su takai girman two sitter matsakaitan kujeru dan haka suka matse matuqa dole aka mayar aka canzo mata wanda gurin ze dauka. Kwana biyu yan uwanta sukayi suka juya dalilin seda suka kaita Bechi wanda basu kwana ba ko banda ruwan gora da aka basu babu abinda suka iyaci na daga abincin tarbar Amarya yamma lis suka tada jaraba seda aka kaisu Kano gidan Amarya dan sunce ba zasu iya bacci a garin ba wannan Abu ya qona ran Yan uwan Audu ya ku.a darsa tsanar Binta a ransu duk da ba ita ta musu ba amma sun ce itama haka halinta yake kenan tunda bata hana yan uwan nata yar musu da magana da izgilanci ba

Audu kansa ya qara hasala wannan karon dan haka babu wata sallamar Arziqi suka koma Kaduna suka yita fadar qarya da gaskiyar abinda ya faru na wai an aura masa ita buqata ta niya ya fara musu rashin mutunchi. Todai babu yanda suka iya aure ya qullu Amarya da Ango na son junansu sedai fatan a zauna lafiya.

Sati gudan da Audu yawa Amarya Binta an barji soyayya irin wadda ya dauka a fina finan turawa kadai ake irinta. Baiwar Allah Bara'atu aikinta ta dafa abinci wanda take qure duk basirarta da abubuwan da Balaraba take koya mata idan sunzo tayi musu takai musu idan sunci ta debo kwanuka safe rana dare haka take wannan Bauta tsakaninta da Audu kuwa da safe idan ya dawo sallar Asuba ze shiga ya duba su shikenan se wata safiyar ko idan taje kai musu abinci baya fita ko ina yana daki suna barzar Amarci a haka ya kwashe sati dayansa gurin Amarya wadda zuwa sannan ba zatace ta mata wani abu ba tsakaninsu gaisuwa ce tana da Fara'a da kuma son yara dan kullum zata kira su Abdullahi ta basu abin dadi ita Bara'atun cema wani lokacin take hana su zuwa saboda karsu takurawa Babansu da kullum yana daka.

Sati daya Audu ya tara su yayi musu nasiha sannan suka raba girki kwana bibbiyu kuma kowacce girkinta zata ringayi. Hakan yawa kowacce dadi, a falon Binta akayi zaman dan haka bayan ya sallame su Bara'atu tayi mata seda safe ta tafi. Yara duk sukayi bacci ta sake gyarawa tayi kwalliya da wasu kayan bacci da ta siya gurin Maman Kabir Maqociyarta saboda wannan rana. Tayi gyaranta daidai gwargwado na cikin jiki dana fata ga sabon kitso da lalle da tayi dukda kullum ta kalli Amaryar tata Da take Jajir ga jiki duk madara da tsoka se taji kamar Audu ba ze sake yi mata kallon Mace ba wannan tunanin ya sakata damuwa har tayi yar rama daman babu jikin se ta sake komawa yar yarinya firit da ita.

Tana nan zaune falo tana kallon Tv da tsumayen Audu har bata san bacci ya kwasheta ba. Motsin rufe qofa ya farkar da ita, ta kalleshi kafin ta kalli Agogo, sha biyu da rabi a saninta tun Tara da mintina take zaune a gurin kusan awa uku kenan.

"Bakiyi bacci ba?" Tambayar daya fara jefa mata yana shigewa cikin daki, ya gotata qamshin turaren Binta ya bigeta yanda kasan yanzu ya shafashi. Ta yunqura tabi bayansa tana cewa

"Ina zaune bansan bacci ya kwasheni ba" ta dakata ganin harya kwanta. A tausashe tace

"Har zaka kwanta bakaci abinci ba?"

Fuskarsa washe da murmushi me kama dana rainin wayo yace

"Au na manta qanwarki tace kiyi mata aikin gafara ta bani abinci".

Tayi zukudi tana kallonsa kafin ta sauke ajiyar zuciya ta juya to me zatace?

Kwanukan Tuwon shinkafa miyar gyadar datayi wanda ciki ta dibarwa Bintan iyakar cikinta dan tun da safe yace a gurinta zeci abincin dare yanzu kuma ya canza shawara yaci a gurin Amaryarsa "to Allah yasa ya ishe su" ta fada a fili tana Adana abincin a cikin Fridge duk Balaraba ce ta koya mata tace a can miyar sati takeyi ta saka abarta a firinji sedai ta dumama idan zasuci haka sauran abinci duk adanawa takeyi shiyasa itama tunda ya siyo mata ta fara wannan dabarar da yake koda yaushe da wuta hankalinta kwance yanzu bata rasa abinda zata bawa yara kafin ta gama abinci.

Seda ta gama kintsa komai ta dauke Babannan da bata san sanda Abdullahi ya kawo mata shi falon ba dan ya saka rigima a gurinsu ze kwanta dukda bata yaye shi ba ta kaishi daki abin mamaki har Audu yayi bacci, jiki a sanyaye ta kwanta itama ranta cike da saqe saqe. Washe gari da safe tana hada abin kari ta jiyo sallamar Binta. Tun daga cikin kitchen din take jn tashin qamshin turarenta, gabanta ya fadi sanda suka hada ido. Kwalliyarta kamar me zuwa zaben sarauniyar kyau. Har qofar kitchen din ta qarasa fuska dauke da fara'a suka gaisa daidai nan Audu da gama wankan sa kenan ya shiga yana shiryawa dan yau ze fita aiki ya leqo haqoran nan a washe yana cewa

"Aa, wa nake ji kamar Amarya da sassafen nan?"

"Nice, na zo bikon Ango naji shiru har gari yayi haske baka leqa mu ba" ta fada cikin wani salo da ya saka Bara'atu sakin baki kwan datake soyawa akan wuta ya fara

qauri yayi baqi kafin ta ankare ta sauke. Abdullahi da Babangida suka fito daga daki suka gaida Binta, ta karbi Babannan tana masa wasa ta shige falon Bara'atun suka barta tsaye a kitchen. A sanyaye ta gama soya kwan ta fara shigar musu da abin karin. Ta jere komai a tsakiyar daki na Audu daban se nata dana yara daban. Abdullahi ta fara hadawa shayi shida ze tafi makaranta ta zuba masa wainar kwansa da Biredi ya dauka ya tafi dakinsu Babangida ya bishi dan haka ta zuba nasa ta bisu dashi ta bar Audu da Binta dake zuba hirar da bama fuskanta take ba dan rabi turanci sukeyi. Tana dawowa ta tarar sun baje suna karyawa tare.

Wani abu ya soketa amma ta daure

"Kin ganni da kwadayi ko?" Binta ta fada tana mata murmushi seta girgiza kai tana murmushin yaqe itama. Nata abin karin ta dauka ta shigar daki ta dawo ta dauki Babannan dake musu didifniya yana shirin zubar da shayi suka shige ciki. Binta na zaune har Audu ya shiga ya qarasa shirinsa kafin ta rakashi har qofar gida ya fita, ta rasa ma me zataji, haushi ko mamaki ko me?

Daga rakiyar Audu binta bata dawo ba bangarenta ta wuce. A sanyaye Bara'atu ta ringa ayyukanta saboda abinda ya faru daga jiya zuwa yau din. Da Asuba duk sun makara tashi shiyasa ma Audu be fita masallace ba. Daga gaisuwa wata magana bata hadasu ba ta fita hada abin kari shi kuma ya shiga wanka, tana Allah Allah ta gama idan sun zauna karyawar tayi masa magana Bintan tazo ta kasa ta tsare har seda ya bar gidan kudin cefane ma seda ta fito falo ta gansu a inda ya tashi ta daiji sanda yake ce mata gasu nan kafin ta fito kuma har sun bar falon to abinda take so ta fahimta shin abinda Bintana tayi da gayya ne ko kuwa dai tayine bada wata manufa ba?

Kasancewar Audu baya dawowa cin Abincin rana yasa se gurin uku ta tashi dora girki. Haka siddan Babannan ya tasa mata rigima, Babangida ya tafi makarantar Allo wadda akeyi nan cikin layinsu gida uku ne tsakaninsu qiriniyarsa tasa Audu kaishi dukda be cika shekaru uku bama sannan amma da yake yana da barage kuma bakinsa ya bude shiyasa seka dauka ya wuce shekarunsa. Ta rasa yanda zatayi da Babannan din ta goyashi yaqi ta aje masa kayan wasa duk a banza ga aiki ta dakko dan Funkaso take so tayi da miyar Tantakwashi se Zobo da Balaraba tace mata duk in tayi girki ta ringa hada masa Lemo ta kuma koyi kala kala su Jinja harda wani farau farau me dadi idan yayi sanyi.

Gaba daya kukan yaron ya hanata sakat gata ita bata iya aiki idan yaro yana mata rigima ba. Hijabinta ta zura ta dauki Babannan din da kayan wasansa ta doshi

bangaren Bintan, qofar a bude dan haka ta shiga da sallama tana kallon wurin tana qara sha'awarsa, kullum tayi sallah se tayi addu'a Allah ya qarowa Audu budi itama ya maida mata da gurinta irin haka komai a ciki. Tayi sallama shiru ba'a amsa ba daga inda take tana jiyo tashin kidan turawa qila Tv ce qila radio ta kunna kusan sallamarta uku dan haka ta tura qofar falon da itama ba'a rufeta ruf ba ta shiga da sallama.

Bintan na kwance kan kujera Idonta akan qofar ga Tv na aiki a ciki ake waqar da take jiyowa. Ta sake maimaita sallama tana fadada fara'arta, ba yabo ba fallasa bintan ta yunqura ta zauna tana kallonta ba tareda ta amsa sallamar tata ba. Kujrar dake dabda ita ta nufa da niyyar zama yanda Binta ta zaburo mata tana cewa

"Karki zauna mun a kujera" ya saka ta dage da sauri har tana shirin yarda Babannan tayi saurin dafeshi tana kallon Binta data miqe tsaye fuska a hade tamkar wadda aka aikowa da saqon mutuwa.

Page 12

"Karki zauna mun a kujera" ya saka ta dage da sauri har tana shirin yarda Babannan tayi saurin dafeshi tana kallon Binta data miqe tsaye fuska a hade tamkar wadda aka aikowa da saqon mutuwa.

Kallon kujerar tayi dan ta gani ko wani abun cutarwa ne akai da ya sakata hanata zama amma bataga komai ba seta sake kallon Bintan dake jifanta da wani kallo data kasa fassarawa. Cikin kaushin murya tace

"Meya shigo dake dakina?"

Mamaki da Al'ajabi suka cika Bara'atu, ita Binta take tambaya me ya shigo da ita dakinta? Matar da idan tazo kawo musu abinci take nacin ta zauna suyi hira itace take ganin rashin dacewar zaman musu ta tafi amma yau take mata magana haka cikin zafi da gatsali, tsawar data sake buga mata ta maidata hayyacinta, Babannan ya fasa kuka dan shi baya son Hayaniya tamkar Yakubu ne ya haifeshi. Qofa ta nuna mata tana cewa

"Fita, kuma wannan ya zama karo na qarshe da zaki tako qazaman qafafunki ki shigo mun daki, wato kinzo ki shafamun tsiya da talauci har da zaman mun a kan kujera? Wlh karki kuma idan ba haka ba sena banbance miki tsakanin aya da

tsakuwa fita" ta qarasa cikin sigar bada umarni. Kamar kazar da qwai ya fashewa a Ciki Bara'atu ta fita daga dakin tama rasa tunanin da zatayi, to me hakan yake nufi?

Haka ta goye Babannan yana kuka da komai ta shiga aikin Jiki babu kuzari ga rigimarsa ga mamakin Binta Allah ya taimaketa yayi bacci taje ta shimfideshi dukda yamma tayi taci gaba da aikin girkin. Bata samu ta gama ba seda aka kira sallar Magriba, su Abdullahi sun dawo dan haka shi ta hadawa wanke wanke yayi mata ita kuma ta kama Babangida da Babannan tayi musu wanka itama tayi, seda ta idar da sallah kafin ta shiga kwalliya. Tana zaune da yara suna cin abinci ita kuma ta zuraww Tv ido tana tunanin abinda ya faru tajiyo sallama daga tsakar gida, mamaki ya sake tiqe ta to me tazo yi mata kuma? Ko kuwa Tijarar da ta mata dazu ce bata isheta ba ta sake biyota nan?

Tsoro da fargaba ya kamata, ta san idan dukane tsaf Bintan seta babballata ta zubar ita bama zata iya takalar fitinarta ba kamar yanda tace karta sake shigar mata daki in Allah ya yarda anyi na farko anyi na qarshe to akan me kuma ita zata biyota.

Bata gama tunanin ba Binta ta daga labule ta shiga Falon, tayi kwalliya ta kece raini da Leshi ga qamshi tana bulbulawa fuskarta washe da fara'a ta sakeyin sallama.

Kasa amsa mata tayi se kallonta da takeyi a dan tsorace harta zauna akan kujera Abdullahi ya gaisheta sannan ta kalli Bara'atun tace mata

"Ina wuni Maman Baba? Ya yaran yau duk basu shigar mun ba"

Tsabar mamaki Bara'atu seta hangame baki ta kasa ce mata komai, Binta na shirin sake magana suka jiyo sallamar Audu a tsakar gida, Yaran suka fita da gudu tararsa Binta ta sake qyara zama Bara'atu kuwa tama rasa ya take har ya shigo dakin. Fara'arsa ta sake fadada ganinsu duka a gurin, ya zauna a kan two sitter kusada Bara'atun yana cewa

"Aa kace Uwargida da Amaryar duk suna nan me kuke tattaunawa haka?"

"Sirri muke nida Yayata" Binta ta fada tana fari da ido, Bara'atu kuwa a salube ta zame qasa tana masa sannu da zuwa tare da gaishe shi ya amsa cikin walwala. A fakaice Binta ta galla mata harara, ta gani amma idon Audun be kai ba yana qoqarin ciro alawa daga Aljihunsa ze bawa Babannan. Cikin yauqi Binta tace

"Barka da dawowa Ango, akwai idon yara da nayi maka maraba ta musamman"

Wani abu ya sako qirjin Bara'atu, shi kuwa kamar wani gaula haka ya bita da kallo yana cewa

"Allah ko, to ki ajiye mun bashi".

Hawaye taji sun zubo mata tayi saurin sharewa tareda miqewa ta fice daga falon dan kawo masa ruwa. Wannan ai cin fuska ne, a dakinta a kuma ranar kwananta zasu ringa irin wannan maganganun daman haka akeyi ko kuwa nata Mijin da kishiyar ne suka raina mata wayo?

Ta hado Ruwa da Zobo a Try daidai zata shiga dakin taji Bintan na ce masa

"Ai nan na wuni, can din yayi mun shiru da yawa shiyasa na taho muka sha hirar mu ina tayata ayyuka se dazu babu jinawa na koma nayi wanka"

"Kai amma naji dadi, Allah yaci gaba da hada kanku" Audun ya fada daidai nan ta kai ajiye Ruwan a gabansa mamakin Binta na neman ya sumar da ita. Tana ajiyewa tsulum Binta ta sakko tana cewa

"Bari na tayaki" ta zuba masa Ruwan a kofi daya ta zuba zobon a wani kafin ta dauka duka biyu tana kallonsa da murmushi tace

"Wanne zaka fara sha?"

"Bani ruwan" ya fada ta kai masa Bakinsa babu shiri Bara'atu ta miqe daga durquson da tayi tunda ta ajiye kayan tabi bayan yaran da Abdullahi ya hada kansu suka fita, yaron nada hankali da tsinkaye. Baya taba zama ya tisa su gaba sedai idan ita ta kirashi ko Audun.

"Haka fa ta ringa mun duk qoqarina na ta saki jiki dani taqi, ni kadai nayita surutu kamar lalatacciyar Radio se naga kamar bata jin dadin shigowar da nakeyi" Binta ta fada. Audu daya bi Bara'atu da kallo cikin ransa yana jin babu dadi ya kalli Bintan yace

"Haka take bata da yawan magana, kije dakinki zan shigo idan na dawo"

Yanayinta ya nuna bata ji dadin amsar daya bata ba amma da yake uwar kisisina ce seta wayance ta miqe tana cewa

"Shikenan, da wai zan jira muci abincin dare tare kaga ci da yawan yafi dadi amma bari naje ko shayine na tafasa nasha kawai daman ba yunwa nake ji sosai ba"

"To ki zauna idan munci abincin se ki tafi" Audu ya sake fada kafin ya miqe ya fita tsakar gida inda Bara'atu ke zaune daura da Kitchen ta zabga uban tagumi kamar wadda innarta ta rasu.

"Nan kika zauna kuma? To ina ruwan wankana?" Ya fada yana tsayawa a gabanta. Ta miqe a sabule ta shiga Kitchen, ruwan sata jona ta dauko ta kai masa bandakin. Yabi bayanta suka shige uwar daka kamar Binta ta bisu kota fizgo Bara'atun haka taji, a ciki kuwa duk qoqarin Audu nason ta hada ido dashi taqi. Ta dauko masa Jallabiyyar da yake shiga wanka da ita da tawul din goge jiki ta ajiye kan Gado ta dauki kwandon sabulunsa ta fita dashi ba tareda ta kalli inda Binta ke zaune ba.

"Nazo na tayaka?" Bintan ta fada cikin salon cusa takaici, taji diran abun amma bata tsaya ba seda ta dangana da bandaki, bata san meya ce mata ba se gashi ya fito yana dariya ya karbi kayan wankansa ya shige ita kuma ta juya dakin. Badan zata fidda masa kaya ba da a wajen zatayi ta zamanta.

"Bakiga komai ba yarinya da qafarki zaki fita ki bar gidan nan" Bintan ta fada mata daidai zata shiga dakin, bata tanka ba a ranta ta ringa jan A'uziyya tana roqon ubangiji da yayi mata tsari da wannan matar me fuska biyu a haka Audu ya fito daga wanka ya tarar da ita a dakin buqui tana kallon qofa tayi zurfi cikin tunani.

"Maimakon kije falon kuyi hira da yar uwarki kin barta ita kadai da Tv me yasa kike haka? Ita bata ji qyashin tazo inda kike ba kece zaki daure rai kuka kiqi kulata? Bana son irin haka kije ku zauna tare kafin na fito" Audu ya fada yana kallonta,

"Kayi haquri" ta fada muryarta na karyewa kafin ta miqe tabi umarninsa. Kamar ba dakinta ba haka ta samu guri ta rabe ita ko hamshaqiyar ta bararraje akan kujera tana jefa masa hira yana amsawa daga cikin daki seta fadi abu tace da Bara'atun "ko ba haka ba Maman Baba" ita dai ta zama kurman dole.

Ya gama shiri daidai nan aka kira sallar Isha Audu ya fito Binta ma ta miqe tana cewa

"Bari naje nayi Isha se na dawo"

"Nima fita zanyi" ya fada suka rankaya suka barta nan zaune tana ajiyar zuciya.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Alwalar ta fita ta dauro itama ta leqa dakinsu Abdullahi Jin shirunsu yayi yawa ta tarar da Babangida da Babannan sunyi bacci se Abdullahin yana duba takaddun makarantarsa.

"Ashe bacci sukayi?" Ta fada tana gyarawa Babangida wuyansa daya karkace

"Eh umma, muna gama cin abinci duk suka kwanta" Abdullahi ya bata amsa. Ta sabi Babannan tana cewa

"Ai gara suyi baccin, shi wannan da yayi wunin kuka daman dole yau yayi baccin wuri. Ka tashi kaje masallaci yau Baban naku ya manta ya tafi ya barka" daga haka ta wuce daki. Seda ta gyarawa Babannan inda ze kwanta tayi masa shimfidar Fitsari kafin ta tayar da sallah. Harta idar da shafa'i da wutri ta zauna zaman lazumi babu Audu babu labarinsa har ta jiyo an fara labaran qarfe tara abinda ya saka ta shafa addu'arta ta fito tsakar gida kenan ta leqa Abdullahi taga harya kwanta shima ya kashe musu fitila alamar ya dade da dawowa kenan.

Mamakin inda Audu ya tsaya takeyi, duk zamansu daga sallar Isha baya zuwa ko ina a gida ze zauna suyita hira har lokacin bacci yayi kuma da Binta tazoma be fasa ba daya dawo daga Isha ze garqame qofar gida to yau ina yayi kuma.

Zaure ta leqa, mamakinta ya ninku ganin qofar a kulle da sakata, ya shigo har ya kulle kenan to ina ya shiga

"Gurin Amaryarsa mana" zuciyarta ta bata amsa. Gabbanta suka qara yin sanyi ta koma ciki tana ayyana wato wannan ne abinda mutane sukayita hango mata amma wauta da yarinta ta hanata fuskanta, so da yardar da tayi da Audu yasa bata taba hasaso ze iya wofantar da ita akan wata mace ba koda yake Amarya ance kota Kare ce ana dokinta sedai shi nasa zirgillin yayi yawa bata tsammanin haka sauran maza da suka qara aure sukeyi tun ba'a je ko ina ba su fara nuna da uwargidansu da bola babu banbanci a gurinsu.

Yunwar data kusan wuni da ita tana aikace aikace ta sakata zuba funkason ta shiga ci badan dadi ba sedan maganin yunwa zuciyarta cunkushe da tunani. Wa zata kaiwa kukanta ya bata mafita dan ita a iya wayo da dabararta bata san me zatayi ta kaucewa afkawa wannan wawakeken ramin dake a gabanta ba. Makirci da tuggun da Binta ta tsiro dashi ga kuma megidan dataga alamar sam ba zasu daidaitaba. Domin bashi da fahimta, ta sani a koda yaushe hasashe da maganarsa itace daidai babu ruwansa da jin bangare domin yin alqalanci akan abu wannan halin ko akan

yaran yana gwadawa duk wanda ya fara kawo masa qara yakan bashi gaskiya ba tareda ya tsananta binciken bin ba'asin ainihin abinda ya faru ba ta sani yanzu koda zata fada masa abinda Binta tayi mata a bayan idonsa baze taba yarda ba, tunda bata san meta gaya masa dazun da har yake mata fadan ta barta ita kadai zaune ba.

Ta gama cin abinci ta matsar masa da nasa gefe ta fita da kwano ta daurayo bakinta kafin ta shiga shirin kwanciya itama. Tana tsaka da shafe jikinta da Addu'a ya shigo tayi saurin jan bargo ta rufa har kai a zuwan bacci take tana jinza yana kiran sunanta taqi amsawa saga kwancen da take tana iya shaqar qamshin turaren Binta tamkar jiya, wani abu me daci ya taso mata se hawaye suka shiga zubar mata ya fita daga dakin yana cewa

"Har kinyi bacci bari naci abinci toh"

Siririn kuka ta saki murya bata fita. Wannan wani irin abu ne? Sati daya da qara auren har zata fara karbar wannan wulaqancin haka, jiya be shigo da wuri ba da safe tazo ta kasa ta tsare bata barsu ko gaisuwar kirki sunyi ba sannan yanzu ta janye shi se yanzu ya dawo shin shi be san abinda yakeyi babu kyau ba idan ita tanayi da gayya da mugunta ne shi ya kamata ya biye mata su shiga haqqinta?

Tana sharar hawaye ya gama cin abincinsa da duk uzurin da zeyi kafin ya kwanta a bayanta. Wani kuka ya sake taso mata sanda ya jata jikinsa tana jin qamshin turaren Bintan a ainihin fatarsa da alama jiki suka hada. Ya dade yana koya mata abubuwa wanda se tayi da gaske take iya maida masa da martani saboda kunya yau kam bata da qarfin jiki dana zuciyar da zata kulashi. Tana jinsa yana zabga tsaki bayan daya samu nutsuwa, be ko jira ta saka musu ruwan zafi ba ya fice ko ya dumama koda na sanyi yayi oho ita dai seda ta fara jin saukar numfashinsa alamar bacci ya kwashe shi kafin ta fita ta saka ruwa tayi wankanta.

Tunanin abinda ya sakashi tsakin ta ringayi, duk sharrinsa bazece yaji wani abun daban tattare da ita ba saboda gyara gangariya Innarta tayi mata ruwan Ni'ima har diqa yake a jikinta kuma ko yanzun dukda jikinta be wani karbi abinda ya mata ba amma tasan taba da ruwan da ze bashi duk nutsuwar da yake nema to kodai shirun data masa ne ya bashi haushi dan yasha gaya mata baya so tana barinsa yana abu shi kadai. Da safe ma haka ya fita yana faman daure dauren fuska, qarfe biyar na yamma Babangida ya shigo da Biskit yace mata Babansa ne ya bashi ta tambayeshi yana ina yace yana dakin Amarya, be leqasu ba seda ya dawo daga sallar isha shima daga bakin qofa yayi mata seda safe ya juya daman ko qyallin idon Binta bata gani ranar ba.

Haka al'amura suka cigaba da gudana, a watanni biyu da auran Binta Bara'atun ta fita hayyacinta seka dauka jinyar shekara tayi saboda rama da baqin da tayi. Wani irin zama sukeyi mara kan gado, Audun gaba daya kamar wanda aka sakawa hannu ya fita a sabgarta tsakaninta dashi idan yana dakinta gaisuwa ce se ranar dayayi sha'awar kulata a shimfida yayi bayaga wannan idan kaji yayi doguwar magana da ita to qorafinta Binta ta kai masa yazo yanayi mata fada wanda bata iya ce masa komai illah ta bashi haquri, to ba se ta aikata abinda ake ce masa tayin ba sannan ne har zata kare kanta. Wata irin annamimiyar matace Bintan, rashin mutunchi da Tijara se kalar wanda ta manta ne batayi mata a gidan da zarar Audun ya fita yamma nayi ta daidaici lokacin dawowarsa idan yana dakin Bara'atun kenan kuna zata sheqo wanka tazo ta kame mata a falo harya dawo sannan ta hillace shi su tafi se sanda ta ganshi a hakan kuma ze zo ya rufeta da fadan Binta tace tayi mata kaza ko tace mata kaza babu bin ba'asi babu tambayar ya akayi yanda kasan wanda Bintan ta wanke gabanta ta bashi yasha haka yake shakkarta yake jin maganarta.

Ita kuwa Binta daman a shirye ta shigo gidan Audu, bata tsarawa kanta zama da kishiya ba dan haka ta shirya ta kuma tsara komai yanda zata ringayiwa Bara'atun gashin quma har se ita da kanta ta fita ta bar mata gida. Sanda tazo taga yar yarinyar a matsayin matar Audun ma abin dariya ya bata tasan ba zata sha wahalar kada taba, tayi amfani da nakasun Audun tayi galaba akansa. Ta karanci shidin mutum ne me son a riritashi, kalar soyayyarsa da wayewarsa har mamaki abin yake bata tamkar wanda ya tashi cikin Turawa ko wasu gogaggun mutane shiyasa take qure basirarta ta tabbatar da ta tashi kansa da nata salon wayo da dabarar. Da baki kadai idan ta zauna ta ringa tsara masa zance baya sanin sanda yake aikata duk abinda ta sakashi ta kuma fahimci Bara'atun wawiyace babu abinda ta sani se Biyayya wa Audun kamar zata kwanta masa irin abubuwan da Bintan take masa yasa gaba daya ya raina Bara'atun dan qoqarinta da yake gani a baya duk ya disashe, a yanzu kuma da damuwa tayi mata yawa tasa abinda take iya tabukawar ada ma ta dena Shiyasa ya fita a sabgarta.

A ganinsa baqin kishi ta saka a ranta shiya hanata walwa ta takura kanta shi kuwa bashi da lokacin da ze zauna yana lallashinta ko tambayarta me take so tu da dai be tauyeta da komai ba yanzu da budi ya qarar masa ma jin dadi da abubuwan mora rayuwa sedai suyi Kyautarsu amma dukda haka a maimakon ta saki ranta taci arziqi Aa se rama take tana qara qarmashewa tana ja masa zagi dan duk wanda ya ganta se ya zargi wani mugun abun sukeyi mata da ya saka ta fita hayyacinta.

Bara'atu bata sake shiga uku ba seda Binta ta fara laulayi, duk wata hidimar Bintan kanta ta koma bisa umarnin Audu, haka zata kwanta kamar ruwa idan yana gida tayita malele kuwa ita a dole ciwo take daidai da dan kamfai idan ta cire Bara'atun ce zata wanke mata girki kuwa se tayi kala uku a rana kuma taqi ci idan ya dawo tace masa ai ta fada mata abinda take so taci taqiyi haka ze hau kanta da fada da bala'i baiwar Allah sedai tayita kuka tana kuma kaiwa Allah kokenta gashi ya hanata zuwa Bechi a fadarsa idan ta tafi waze kula da Binta tunda shi yanzu sabgogi sun masa yawa dan har tafiye tafiye ya fara.

Wannan bala'i yasa ta qara figewa tayi zuru zuru. Ana haka ya tada zancen gyaran gida saboda ya samu isassun kudin da zasu gina masa abinda yake so. Sunyi shawara da Binta akan Bangaren Bara'atu za'a rushe tunda shine gefen hanya zefi kyau ya zama fuskar gida dan haka ya samu Bara'atu da zancen murna kamar ta fasa ihu sanda yace mata zata tafi Bechi ta zauna na wani lokaci kafin a gama gyaran gidan, a cikin sati daya suka tattara ita da Yaran suka tafi Bechi, cikin bangaren Yakubu na da suka zauna wanda Audun ya saka aka gyare shi daman idan sunje can suke sauka nan fa gulma ta ringa yawo a gari kan cewar auren ta ne ya mutu. Ramar da tayi ta qara bawa mutane abin fadi aka ringa yawo da zance kala kala kowa da irin abinda yake fadi.

Hankalin Bilki ya tashi da ganin Bara'atun, ita kadai ta iya budewa cikinta ta fada mata halin da take ciki a gidan dan uwanta dan hatta da Innarta duk yanda tayi da tasan me yake damunta qin fada mata tayi kawai tace mata rashin lafiya tayi amma ta samu sauqi. Ran Bilki ya baci da labarin da Bara'atu ta bata, ta ringa fada qarshe ta dora mata laifin cewar koma menene ita ta jawa kanta da tun farko ta basu damar yi mata rashin mutunchi.

"Akan me zaki zauna kinemi ki kashe kanki da damuwa? shi Yaya Audun mala'ika ne da bazaki iya kallinsa ki gaya masa abinda yake ranki ba. Kin zauna kin bari zuciyarki ta cika da tsoro mara dalili kina cutar da kanki to wlh idan kika cigaba da wannan salibancin kina ji kina gani seta rabaki da gidan kamar yanda ta fada" Bilkin ta fada cikin qunar rai.

Zamanta a Bechi se yafi mata kwanciyar hankali da nutsuwa, a qasa da wata daya ta fara maida jikinta ta murmure to bata da matsalar komai, ga kayan abinci nan jibgi ya ajiye musu haka kudin kashewa ya bata isassu tayi bacci cikin nutsuwa ta farka tayi abinda zatayi ta fita gurin Goggo Fadi suyi hira da Amaryar da Aminu yayi ya ajiyeta nan suke zaune tareda Goggo Fadin saboda qafa data sakata a gaba, idan kuma taji marmarin fita ta tafi gidansu ta wuni can dare yayi ta koma gida a haka suka ci wata daya sannan Audu ya je musu kwanansa biyu ya juya haka kuma

yaci gaba dayi duk qarshen wata zeje yayi musu kwana biyu har suka shafe watanni hudu a Bechi.

A bangaren Audu da Binta kuwa filin gida suka samu suna zuba sharafin soyayya babu kama hannun yaro. Ginin daya tayar kuma yayi nisa, ginin Bene ne akeyi na zamani taswira me kyau da qawatarwa qasan na Mandiya Binta ne se Benen da aka dora da zata zama turakar me gidan bangaren da Bintan take ciki yanzu kuma ya barshi akan Bara'atu seta koma can dukda Binta a ranta ta quduri cewar Bara'atun ta tafi kenan ba zata dawo mata cikin gida ba. Kwana biyu da yake zuwa yi musu qarshen wata seda yayi da gaske Binta ta barshi, Allah ya sani bawai baya son Bara'atu bane Aa mugayen halaye data tsiro dasu ne suke bashi a ganinsa Kishi ne yake damunta ya hanata walwala.



Gini ya kammalu har Binta ta tattara ta koma sabon bangarenta. Sababbin kayan daki Babanta yayi mata jere na garari irin wanda ba'a samu filin yi a wancan dakin ba se yanzu saboda wannan me yalwa sosai akqa debe su dan har rabin Filin maqocinsu da suke jingine ya siya ya shigo dashi shiyasa ta samu maka makan dakuna biyu ga Falo da kitchen da store, an rushe katangar tsakiyar bangarorin gidan ya hade se ya sake tada daki babba a tsakar gida guda daya aka kumayi Kitchen shima na tsakar gidan se Bandaki.

Tsaf aka fente ko Ina har inda Bintan ta tashi dukda babu abinda gurin yayi amma yaga be kamata Bara'atu ta shiga a haka ba. Ya sake aiya mata gado daya tunda daya take dashi nan kuma daki biyu ne yasa aka kwaso kayanta ta aka ajiye a store din gidan Alhaji Idi gidan qawarta qwara daya duk unguwar, da ita kadai ta iya sakewa ragowar dai idan sabga ta tashi aka gayyaceta zataje amma bata shiga gidan kowa suma tun suna shigo mata ganin bata sakewa yasa suka bari. Binta na zuwa suka ringa shishige mata duk suka zama yan korarta dan ta wuce da Ajin ace qawayenta ne, amma da yake yawancinsu gulma ce wasu kuma kwadayi ya sakasu neman qawancen haka suke jure duk izgilancinta suna manne da ita.

Ranar da aka maido kayan Bara'atu Binta bata tare suka fita da Audu ya ajiyeta a Gadon qaya dan ya siyi mota a tsukin. Gidan wani sabon Abokinsa Mustapha shima harkar Mai yake dan haka yanzu Audun yana mu'amala sosai da su dan qungiya guda garesu. A Asibiti suka hadu da Matarsa Baturiya gurin awo, hali yazo daya aka qulla qawance. Se daga baya suka fahimci sudin matan Abokanai ne shikenan

zumunchi ya qullu har ta gabatar da ita ga sauran matan Abokanan mazajen nasu dan suma guruf suke dashi kowacce naji da kanta Mijinta hamshaqi.

Data dawo gidan bata ma lura da an zuba kaya ba tunda qofar a kulle take, taci gaba da sabgoginta. Washe gari Audu yace mata gobe zeje Bechi. A fili tayi masa fatan zuwa da dawowa lafiya a zuciyarta kuwa tace

"A haka dai Auran ze balbalce badai ta dawo gidan nan ba".

Da Asuba bayan sun tashi kuma yace mata ta shirya kayanta kala biyu su tafi tare saboda duk sanda yaje se yan uwansa sunyi qorafin rashin zuwanta kuma ya manta Gobe daurin Auran Saleh Yaron Yaya Baba na Biyu. Rabonta da Bechin tunda aka kaita tana Amarya se zuwa daya da sukayi gaisuwar rasuwar Wan Baban Bara'atu shima a tsaitsaye ba kwana tayi ba watanni takwas kenan.

"Yanzu a sanyin nan kake so na tafi qauye?" Ta fada tana kumbura baki sanda yace ta shirya din, Audu ya kalleta yace

"Gida fa zamuje ba Jeji ba balle kice zakiji sanyi. Yaushe ma rabonki da can? Karki manta Bechi tushe na ne. Badan iyayenmu basu da rai ba kin san baki isa ki kwashi wata daya ba ba tareda munje kin gaishe su ba, ko yanzun ayyuka ne suke shan kaina su hanani zuwa ziyara akai akai amma ina ganin zan nemi direba wanda ze ri ga kaiku duk hidima Biki ko suna be kamata ace kuna qin halarta ba tunda ba kullum bane sannan tunanin da nakeyi zan gyara gidan mu nacan duk sallah mu ringa tafiya munayi tareda yan uwa"

"Tabdi" ta fada a ranta, a fili kuma ganin yanayin da yayi maganae kamar ransa a bace yake yasa tace masa

"Nima bawai ina nufin wani abu bane kawai dai saboda cikin jikina kaga ya girma be kamata na ringa dogayen tafiye tafiye ba"

"Kwananki nawa da dawowa daga Kaduna? Bechin ta kai nisan can ne? Ko da qafa zaki tafi? Kinga karki bata mun rai idan ba zakije ba ki zauna" ya fada yana ficewa daga dakin.

Ita da take neman hanyar da zata kama shi a hannu ina ita ina neman fitinarsa shiyasa ta tashi ta shiga shirya kayan kamar yanda yace a ranta kuma tana ayyana irin abinda zatayi idan taje. Ta tsani qauyen da mutanen cikinsa. Su ba kowan komai ba se Izza da girman kai ya yayan Sarakai wannan shegiyar Bilkin ko nan

Kanon tazo haka take mata rashin mutunchi Audun na kallo ba zece komai ba ti duk zatayi maganinsu. Ta shirya kala biyun kamar yanda yace sannan ta kwashi kayan shayi, Biskit da cincin din da Mero matar da ta samo tana mata girki tayi mata harda dubulan se Sauran Miya duk ta hada kamar me zuwa wata qasar. Audu be shigo ba se gurin takwas lokacin har tayi wanka ta karya da Mairo da Lantana ita kuma share share take mata duk da suka zo cewa tayi su tafi se bayan kwana biyu zasuje qauye. Ganin ta shirya ya saka shima shiga wanka a gaggauce ya shirya suka kulle gidan suka tafi.

Sun isa Bechi ana ta hidimar daurin auren da za'ayi washe gari. Gaisuwar ma kamar sun roqa haka tayiwa wanda taga zata iya. Wadanda ta raina kuwa ko kallon Arziqi basu samu ba. Bara'atu na cike da murnar zuwan Audu sedai ganinsa da Bara'atu ya saka duk karsashin ya barta, gabanta ya ringa faduwa dan ita tsoronta takeyi ko kuma tace tsoron kaidinta. Ita wlh daze barta a nan Bechin yaci gaba da zuwa koda ba duk sati ba zata yarda. A zaman da tayi harta murmure tayi tas abinta babu damuwar Miji babu ta kishiya kuma idan yazo mata kwana biyun sosai yake tarairayarta yana riritata sabanin a Kano da a suna ne kadai take da girki dan ko Binta ta barshi ya kwanta a dakinta to fa ba zasuyi bacci zur ba tareda tazo ta tashe su ba da sunan ciwo na damunta wanda se a ranakun girkin Bara'atun take ciwo. Audun da kansa yake ce mata idan a can yake watara ta kwanta ko farkawa batayi se Asuba.

A dakin Bara'atun Binta ta sauka kamar yanda ya tsaya. Ta haye mata gado tunda ta zauna Sallah kadai ke saukar da ita abinci da duk wasu tarkace dataci nan ta zubar sedai ta matsa gefe ta miqe qafa tana hura hanci mutane na tsakar gida ana hidimar girkin gobe, lokaci lokaci Bara'atu na leqata taji koda abinda take da buqata shara kuwa tayi takai sau biyar daga zuwansu Bintan. Tavi gyada, tasha rake taci goruba duk akan zanin Gadonta na kwalliya data shimfida mata saboda karramawa gashi me haske amma haka tayi daqal daqal dashi kamar yarinya dole ta canza wani da Bintan ta fita yin Alwalar Magriba.

Bayan tayi isha ne ita da kanta zaman dakin ya isheta dan haka ta fita tsakar gidan tana Kallon Faccalolinta dake hada miya suna hirarsu gwanin sha'awa. Babu wadda tabi ta kanta tubda suka zo se Laure uwar gidan Hashimu ita ta ringa shishshige mata ta kuwa yi mata qusa daga nan itama ta kama kanta. Can qofar dakin Sauda Amaryar Aminu ta zauna kan Tabarmar da aka shinfida, Bara'atu na kai tana bawa Babannan tuwo Goggo Fadi na daga qofar nata dakin itama kaca niyar tukwane da mata ta cika gidan.

"Yanzu nake so na qarasa bashi na kawo miki naki tuwon, ko a kawo nan tunda kin fito? Bara'atu ta fada kamar me tsoronta. Tayi wata yatsina tana kallon kwanon tuwon. Tuwon farar shinkafa ne da miyar gyada taji nama da kayan qamshi Bara'atu ce tayi ta dakanta saboda Bintan.

"Kawo" ta fada kamar bataso, ta miqe ta wanke hannunta kafin ta dauko mata fulasan data saka tuwo da miyar a ciki. Yaro yayi sallama ya shigo da qatuwar baqqar leda, Bara'atu ta karba jin yace inji Audu, dumi da qamshin tsire taji ta wuce dashi daki Idon Binta akan Ledar.

Seda ta raba tsaf ta zubawa Bintan wanda tasan duk hadanarta ba zata iya cinyewa ba, ta dibarwa Goggo Fadi ragowar ta fita dashi tabi duk Matan dake aiki kowa ta taba.

"Amma kinsan ni aka kawowa shine saboda tsabar iyayi da kadifiri kika bude harda rabawa mutane tsabar kwadayi su kuma suka karba, to ze shigo se ki fada masa wanda ya sakaki" Binta ta fada sanda ta ajiye mata nata. Bata tanka ba ta miqe, Bilki ce ta bata amsa tace

"Allah ya kawo shi din se ya daketa saboda ta baiwa yan uwansa tsire sunci"

"Ni banyi dake ba" Binta ta fada dan bata shiga sharafin Bilki, ta dameta a tijara kuma taga shi kansa Audun yana shakkarta shiyasa bata takakarta ko zuwar musu can tayi. Haka Iokacin kwanciya yayi dare dare ta haye nata Gado ita da yara qarshe se a qasa tayi musu shimfida suka kwanta. Washe gari aka tashi da hidimar daurin aure, shayi Bara'atu ta dafa mata da safe ta soya kwai dan an kawo Buredi tun cikin dare.

"Ko zakici Waina ko Tuwo a kawo miki?" Bara'atun ta tambayeta. Binta dake shiryawa bayan ta fito daga wankan da har bandakin ta kai mata ruwa tayi banza da ita ganin haka yasa ta fita itama ta shiga wanka. Daurin auran na safe ne, kafin goma gida ya cika danqam da mata harda Mazan ma masu shigowa yiwa Goggo Fadi Allah sanya Alkhairi. Binta tasha kwalliya da Leshi ta baza turare ta kafa kujera a tsakar gida tana kallon kowa daidai. Bara'atu bata daddara ba ta sake yi mata tayin wainar daurin Aure ko tuwo wannan karon tace ta bata.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Wainar Masara ce tayi kyau matuqa ta zubota ta ajiye mata ta tafi kawo miya. Ta rage miyar tuwon Jiya daman saboda Bintan dan ta san ba lallai ta iya cin wadda akayi ta taro ba, ta bincike Kitchen din inda ta ajiye babu miya se ganin kwanon tayi ma a wanke an ajiye bata da zabi dole ta debo mata ta Bikin.

"Ni zaki kawowa wannan miyar kamar ruwan wankin kan mahaukaciya ni zan ci miki wannan kawai kice kasheni kike so kiyi" Bintan ta fada a fusace sanda ta dire mata miyar, kamar me magana da Babarta Bara'atu tace

"Kiyi haquri, na rage ta tuwon jiya bansan waya juye ba. Ki gwada wannan dinma tayi dadi wlh zaki iya ci"

"Dama mana tayi dadi a bakin daya sbaa cin gabza dole kice wannan tayi dadi" Binta ta fada tana harararta, Bara'atu ta miqe jiki babu kwari mutane duk sun tsaya suna kallonsu ga Bintan bata magana a hankali, da qafa ta tunkuda kwanon miyar ya fallatsarwa Bara'atu a jiki tana cewa

"Zoki kwashe shiyarki banma san me kika zuba a ciki ba da kike ta nacin se naci".

"Amma kedai anyi yar marasa mutunchi, yanzu da miyar da zafi ta qona mata fata fa?" Hashimu daya shigo yana saba babbar riga ya fada, Binta ta kama qugu tana masa kallon banza, sedai ta gaza ce masa komai dan yanda yayi maganar cikin hayagaga ta tabbata ze iya rufeta da duka. Mata aka dauki surutu caaa kowa da abinda take fada. Hashimu nata bala'i yana qundumawa Binta da Iyayenta da basu san anyi ba zagi. Ya kalli Bara'atu dake hawayen wannan cin mutunchi data mata cikin taro, tacu kwalliyarta da Shadda Ruwan omo Bintan ta mata wankan Miyar taushe

"Ke kuma sakarya kin tsaya kina mata kuka, k wuce ki kwase me zafi a tukunya ki watsawa yar banza a wannan kodaddiyar fuskar tata" Hashimun ya sake fada daidai nan Audu ya shigo yana fama da tasa babbar rigar ya tarar dasu cirko cirko, Binta na ganinsa ta saka kukan zallar kirsa da makirci tana cewa

"Saboda ni ba yar cikinku bace shine zaku tsaneni? Me nayi muku? Wani abu ya taba hadani da wani a cikinku ne balle ku qwafeni kuke neman halakani"

"Wace irin magana ce haka babu dadin ji wa yake neman halakaki?" Audun ya fada yana qarasawa kusada ita. Ta sake rushewa da kuka tace

"Ina zaune kawai Bara'atu tayo kaina gadangadan da wuqa a hannunta, a garin na tureta ta taka kwanonmiyar nan ya fantsalar mata shine cikin su babu wanda yabi kadin ba'asin nufoni da tayi da wuqa sena miyar sata fantsamar mata suka hau zagina har wannan yayan naka yana cemun jinin shadanu" ta nuna Hashimu daya qame tsabar yau yaji wadda tafishi iya hada guri bashi kadai ba gurin kaf shiru sukayi suka daskare da mamaki, Audu ya kalli Bara'atu ya kalli wuqar dake yashe a gefenta ya sunkuya ya dauka yana nuna mata yace

"Me zakiyi da wuqa da kika nufota"

"Wallahi tallahi qarya take mun" Bara'atun ta fada tana saka kuka, Baba suwaiba wadda qanwace ga goggo Fadi ce tace

"Amma kedai wannan yarinya duk yanda akayi Abokanan wasa kuke da Shaidan, yanzu wuqar da ni kika tambaya na baki kika bare muruci shine zakice ta nufo ki da ita? Gaskiya bakya tsoron Allah yanzu ke ko kunyar idanun jama'a bakiji ba ki lafta wannan uwar qaryar da zata iya kashe Aure Allah wadaranki wlh tir da masharrancin harshe irin naki"

Nan aka sake daukar surutu kowa nayiwa Binta tofin Ala tsine. Audu ya kalli Bara'atun dake kuka kamar me sannan ya kalli Binta data sunkuyar da kai qasa kunya ta dabaibayeta kamar qasa ta tsage ta shige ciki takeji. Ta manta shaf a inda suke, Tsabar yanda idonta ya rufe tana neman dalilin da ze saka Audun sakin Bara'atu ya sakata hada wannan zancen da bata ma san sanda Dabarar tazo mata ba ta kwakwalwar kuma ta gaza kawo mata kalaman kare kai. Gaba daya sun kasa kunne suji hukuncin daze sauka akan Bintan da abinda tayi sabanin haka se ji sukayi yaja tsaki ya juya buguzun buguzun ya fice daga gidan.

"Kin shiga uku Bara'atu ke kuma taki jarabawar kenan a gidan Aure to Allah yasa ta zame miki kaffara"

"Bantan uba, yau naga abinda yafi qarfina ni yasu, Bara'atu dama haka kike zaune? Dole ki rame ai kinyi dakyau ma har yanzu kike cikin hayyacinki wannan makirci har ina?"

"Wlh bazan iya zama da irin wannan matar ba, dama ace Audun tsayayye ne da sauqi to da alama ta shanyeshi Allah sarki Dada Allah yayi bata da rabon shan takaicin suruka shiyasa ta mutu kafin a aurota dan wlh wannan tsaf zata raba Da da uwarsa kutusi"

Haka suka saka Bara'atun a tsakiya kowacce ta ringa surutunta, Binta kuwa jiki babu kwari kamar wadda aka kama da kayan sata ta shige dakin Bara'atun can qurya ta lafe a gado. Tana jiyo surutai ana zaginta amma babu damar tankawa ta rigada ta kwafsa. Haka ta wuni sir a daki ana ta shagalin Biki, Allah sarki Bara'atu, dukda abinda tayi mata haka ta zuba abinci da rana ta bawa Abdullahi ya kai mata bata daije da kanta ba. Bata ma sake shiga dakin ba dan ko kaya da zata sauya Bilki ce ta dauko mata ta kuwa yiwa Binta tatas kamar zata doketa dan bata gidan abin ya faru ta tafi gidanta ta dakko abu. Haka suka kwana.

Tun a daren ranar Abokanansa da matansu suka kai musu tsogwamin abinda ya faru suka tareshi da zancen,

"Gaskiya ka gyara gidanka Audu tun kana da hali. Wannan hanyar da ka dakko bazata bulle maka ba, idan baka dauki mataki yanzu ba kana ji kana gani gidanka ze ruguje, ba kuma iya matanka abin ze shafa ba harda yan uwanka seta rabaka dasu. Wlh banda qaddara ma wannan ba matar aure bace, mace babu komai a ranta se fitina da tada zaune tsaye? Wai me ka gani a gurin yarinyar nan harya rudeka Audu?" Shamsu Abokinsa ya fada. Audu yasha kunu yana kallonsu daidai dan kowa ya tofa ta bakinsa.

"Ana magana kayi shiru kana muzurai da hada fuska, mu nan babu wanda fushinka ze tsorata dan kar muke kallonka kasan mu mun sanka tun muna yawo babu wando, kuma gaskiya ce se mun fada maka ka dauka ko karka dauka wannan ruwanka mudai mu fita haqqin zaman tare" Iliyasu daya fi sauran zafi ya sake fada se sannan Audun ya budi baki yace

"To me kuke so nayi ko nace? Dani daku fa duka labari mukaji babu wanda abin nan ya faru a gabansa balle ya fadi haqiqanin gaskiyar yanda akayi"

"Amma Audu baka tsoron Allah, ta yaya Mutum sama da Ashirin zasu hada baki su fadi qarya? Idan duka matan gurin sun goyi bayan Bara'atu kana tsammanin Hashimu ma ze bi bayanta ne?" Iliyasun ya sake taso masa, saboda a bar maganar yace musu

"Naji, zan mata magana"

"Daga baya kenan, ai take a gurin ya kamata ka nuna mata kuskurenta ba wai daga baya ba yanzu ai ka bata qofar da zata taka koma wane tunda ko zakayi fada badai a gaban mutanen data muzanta wancan ba. Wlh ni mamakinka nake Audu, a tasowarmu idan wani yace ko a mafarki ya ganka Mace tana juyaka wlh duk se mun qaryata se gashi a gaske da ranmu muna gani ka zama solobiyon banza a gaban wadda ma bata isa ba" cewar Musa.

"Ya isa haka, nace zan mata magana ko, nifa ba wai wani abu yasa nake daga mata qafa ba. Idan na duba matakin dana taka a yanzu Mahaifinta ne sila, shi kuma a duniya bashida abinda yake so kamarta ya gayamun babu abinda zan yi na saka masa irin na kula masa da Binta wannan ne kadai dalili"

"Ai shikenan" kusan dukansu suka hada baki gurin fada tsabar takaicin da maganarsa ta qunsa musu daga haka suka watse suka barshi da Muzammilu shine be gaji da magana ba.

Washe gari kuwa da farar safiya Audu yace su fito su tafi. Bata san da su Bara'atu zasu koma ba seda taga ana loda kayansu a mota tayi qwafa bata dai ce komai ba dan babu fuska a gurin Audun, tun jiyan dai bece mata komai ba haka kuma be sakar mata fuska ba. Bara'atu dai duk a darare take har suka isa Kano ta wuce sabon dakinta har tsalle seda tayi saboda murna tayi dakin yan gayu. Haka aka cigaba da rarrafa rayuwa, sauqi daya ta samu shine na aikace aikacen Binta saboda masu aiki har biyu data tarar ta dakko wanda taja musu kunne akan ko gaisuwa ta shiga tsakaninsu da Bara'atun a bakin aikinsu.

Ko a jikin Bara'atu daman me zata saka suyi mata ita? Gaisuwa kuma babu dole a ciki ita a zauna lafiya babu ruwan kowa da kowa yafi mata. Lantana me share share itace Mara mutunchi a masu aikin ta kuma lura tafi fada a gurin Bintan sama da Mairo me mata girki wadda Bintan ta santa ta taba zuwa gidanta kitso sau daya can qasan layinsu take Lantanar ce bata san a inda ta kwasota ba. Matar sam batayiba, a suffa ma Astagfirulla kalar munafukai ne da ita kuma haka take a zahiri. Ita take zuba gishiri akan ciwon zaman su da Bintan. Yanzu da cikinta yayi nauyi ta kusa haihuwa tadan rage hayaniya da hayagagar da take mata shiyasa har take dan samun damar fita tsakar gida tasha iska.

Randa Lantana ta kunno Bintan kuwa ruwa ba zata barta ta hadiye da dadinrai ba, masifa zagi cin mutunchi da gori babu wanda bata mata, tun ba da Hadiza qanwarta tazo, ita take binta an mata aure shekara biyu baya zaman yaqi dadi suka rabu da Mijin nan ma babansu ya tasata gaba shine ta gudo gurin Bara'atun ta kwana biyu tareda Addu'ar ko Allah ze fito mata da Miji a Kano tayi aure ta huta da Fadan Babansu. Nan fa Binta ta samu nayi, gori da yana fita a jiki da bazasu samu sararin shan iska ba, sauqi daya da bata samu goyon bayan Audu ba da tace ya kori Hadizan, da haka zasu tattaro su cika masa gida to da yake har sannan ba a koma daidai ba tun abinda ya faru a Bechi dukda da fatar baki be mata magana ko fada akan abinda tayin ba kawai ya dan dauke mata wuta ne yanda yake rawar jiki yana mata abubuwa ya rage wannan ma na bala'in mata ciwo tadai barine zuwa ta haihu dan ta kanta take yanzun shiyasa ma take sararawa Bara'atun amma da zarar ta haihu zata qaddamar da shirin da tilas ta bar gidan da kareren qanwar tata data kwaso.

Kwanci tashi cikin Binta ya shiga watan haihuwa, lamari fa ya zarce nada dan kankat Audu ya tattara ya koma gurinta da kwana dukda daman kusan hakan ake, a girki hudu idan zatayi kwanaki takwas kenan da qyar ya kwana uku tareda ita dasun kwanta Binta zata doko qofa wai bata da lafiya daga qarshe ma tsakaninsa da Bara'atu sedai idan yana da buqatarta yaje da Rana ko da daren kafin lokacin kwanciya yayi daman saman sa Binta tace Turakarta ce ita kadai, daga qarshe dakin tsakar gidan aka gyarawa Abdullahi daya fara zama saurayi su Babangida kuma tare take kwana dasu a dakinta se dayan ya zama dakin Audun to a hakan ma ita bata damu ba tunda dai babu wata fitina ko a haka za'a cigaba da rakawa zata iya haqura.

Ranar da Binta ta haihu cikin dare naquda ta tasar mata, Audu baya nan ranar ya tafi Calaba dakko Mai a ranar dai suke saka ran dawowarsa amma har aka kwanta bacci shiru. Guraren sha biyu Ciwon gaske ya tasarwa Bintan, tun tana daurewa har abu yaci tura ta shiga kuka kamar yarinya. Abdullahi ne ya tashi fitsari ya fita tsakar gidan ya ringa jiyo kamar kuka daga dakin Bintan saboda darene guri yayi shiru kuma window dakin a tsakar gidan yake dan haka ya tafi da gudu ya bugawa Bara'atu qofa tana bacci taji bugun ta farka a gigice ta fito ya sanar mata da abinda yaji

Tunanin naquda take ne ya fara zuwar mata dan haka ta juya ta tafi dakko zani da Hajib idan yaso ta fita ta kirawo Baba Uwani maqociyarsu. Tana zuwa qofar dakin sukaci karo da Audu, bata gama mamakin sanda ya dawo ba tsaqarsa ta katseta.

"Ki kamata muje mota" ya fada rai a matuqar hade, jiki na rawa ta kama Bintan da tasan Azaba ce tasa ta yarda ta riqeta. Haka sukaje Asibitin murtala, kamar ana jira suna isa ko minti biyar ba'ayi ba Binta ta haihu ta samu Da Namiji. Yanda Audu ya ringa murna seka dauka haihuwar fari aka masa. A can suka qarasa kwana hardashi seda safe suka dawo gida Bara'atu ta ringa godewa Allah da zuwan Hadiza, shaf ta manta da batun Yara a gida seda sukaje Asibitin. Da ace Hadizan bata nan bata san ya zatayi ba qila sedai ta tako da qafa ta dawo dan ba zata barsu a gida suka kadai da daddare ba.

Kan jiki kan qarfi ta ringa hidima da Bintan da Jaririnta kyara da hantara kuwa babu wanda bata gani. Abinda yafi damunta yanda Audu ya shareta, ko magana ta masa a ciki yake amsawa hidima yake tayi da Matarsa da Jaririnsa kayan fitar suna ma ana saura kwana biyu Abdullahi ya shiga da qatuwar leda ta zazzage taga kayansu ne shida su Babangida ko dan kunne babu nata a ciki. Suna duba kayan ya shigo fuskar nan kamar hadari ya wuce dakinsa ta tashi ta bishi. Seda ta kai masa abincin dare ya gama ci kafin tayi masa godiyar kayansu Babangida da ya bayar ta qara da cewa

"Dan girman Allah idan wani laifi nayi maka kayi haquri ka sanar dani na gaji da wannan zaman gabar da mukeyi" ta tattara qarfin hali ta fada wanda Sadiya maqociyarta kuma qawarta guda dayace ta bata wannan shawarar ta cewa ta dena shiru, duk idan taga canji a gurinsa ta tuntubeshi suyi magana tunda tasan halin Binta baze wuce ta qulla mata wani abun a gurinsa bane koda ace baze yarda da ita ba in har ya gaya mata laifinta ta kare kanta shikenan ai ba makaho bane kuma ba kurma ba qin Allah ne ya saka idan an gaya masa abu yake hawa ya zauna ba tareda yayi bincike akai ba.

Seda ya mula kafin ya fara magana yana cewa

"Wato badan Allah ya kawoni ba so kikayi ki bar Binta ta mutu ba zaki fita ki taimaka mata ba? Koda yake dama tasha fadamun kince se kinyi Ajalinta da ita da abinda yake cikinta ba zata haifeshi ba. Wlh mamakinki nake Bara'atu, yaushe kika zama haka? Ko kuwa dama hakan kike kin lullubeni ne baki fito da ainihin kalarki ba is yanzu?"

"Ni ya kamata nayi maka wannan tambayar yaushe ka zama haka Audu? A zatona kaine mutum na farko da zaka fara bayarda shaida akaina amma kuma se zaton nawa ya zama ba gaskiya ba, koda ace ba zaka shaideni ba Audu yaci ace kasan me zanyi da wanda bazan aikata ba. A Bechi tace na nufeta da wuqa ka yarda yanzu

kuma tace ni nace zan kasheta da dan cikinta shima ka yarda wane mugun abu na aikata maka daya janyo irin wannan rashin yardar a tsakaninmu har takai ayi mun qazafin zanyi kisan kai kuma ka hau ka zauna? Nayi tsammanin ko Qadangarenta tace nace zan kashe zaka qaryata balle ran mutum ba dYa ba harda na Jaririn dabe iso duniya bama" Bara'atu ta fada cikinmatuqar qarfin hali hawaye masu dumi suna sakko mata.

Page 14

Hawayen ta suka qara gudu lokacin daya miqe ya fice daga dakin bayan daya antaya mata tsaki me qarfi. Ta dade zaune a gurin tana kuka, meta tsarewa Binta? Ita data shigo ta tarar batayi kishi ta tayar da hankalinta ba se itace zata yita hada mata tuggu da makirci a gurin Miji shi kuma sam babu bincike ya ringa zama kan magana da an gaya masa? Tana tsaka da wannan kukan Hadiza ta kwankwasa mata qofa, seda ta gyara fuskarta ta fita Hadizan ta gane tayi kuka amna tayi shiru bata tambayeta dalili ba kuka kuma ta gaya mata ta daura aure dashi tunda ba zata tashi tsaye akan wannan Kishiyar tata makira ba se ta zauna tayi musu kuka har hawayenta ya qare.

"Yace kije ga naman qauri can an kawo a gyara, banda rainin wayo ke zakiyi mata suyar qaurin ma ina yan uwanta sunzo? Dama ace zaman mutunchi kukeyi da sauqi amma keda bola banbanci kadan ne a gidan nan sann.."

"Ya isa Hadiza, muje ki kama min" Bara'atu ta katseta daga mitar data kwaso.

"Allah ya sauwaqe kedai da zaki iya bismillah" Hadizan ta fada tana zama akan kujera, tasan ba zatayi ba tunda ta fada dan haka ta fita rai babu dadi zuwa gurin gyaran Qaurin. Ta tarar da Mairo na hura ta dora yan ciki lantana kuma tana ware nama da qashi da alama hadosu masu gyaran naman sukayi.

"Barka da Rana Hajiya" Mairo ta gaisheta, fuska babu walwala sosai dalilin quncin zuciya ta amsa mata, Lantana kuwa ko kallon arziqi bata mata ba sema tahau waqar Habaici daga Mairon har Bara'atun babu wanda ya tanka mata daga qarshe ta nemi guri ta zauna dan Mairo tace ta bari zasuyi tana kallon Lantana nata jan qwafa da alama zataje tayi abinda ta saba na hadin masifa.

Suna kaskon qarshe yan uwan Binta biyu suka zo gurin ta gane Babbar ita tana dan zuwa dalilin akwai yan uwan Mijinta a nan Kanon me bi matan dai sau daya ta taba ganinta se yau na biyu. Dazu da suka sauka har ta fita zataje ta gaishe su suka

hadu da Binta a tsakar gida tace ko barandarta ta taka seta mata rashin mutunchi shiyasa ta fasa dan hakan yanzun ta gaishe su suka amsa kadaran kadahan. Robar da aka zuba Nama suka dauke suna barwa Lantana sallahun idan ankwashe sauran a kai musu.

"Ko me zasuyi dashi se Allah, a irin arziqinsu ai wlh nama dai yaci ya gunduresu yanzu amma Allah sa suma ba jida zasuyi su tafi dashi su aje qulli qulli a firiza yanda Hajiyar nan takeyi ba su basu ci ba su basu bawa wani yaci ya musu addu'a ba kai Hajiya Binta fa akwai Rowa alqur'an" Lantana ta shiga jero zance babu kai babu qafa. Yanda Bara'atu bata tanka ba haka Mairo kamar bata gurin, wannan nadaga abinda yasa take qara ganin girman matar. Ba ruwanta ta shiga sabgar da bata shafeta ba, aikin daya kawota gidan kawai take yi idan tazo da safe ta gama musu kalaci da wuri take dora na rana wata rana ma sha biyu ta gama data gama ta karbi rabonta zata tafi se kuma gurin qarfe uku ta dawo ta dora na dare shima tana saukewa zata tafi se kuma gobe da safe musamman yanzu da Binta tasa aka hade girkin tun zuwan Hadiza a yanda ta cewa Bara'atu ta dena girki da kanta, kwadayin Nama da Kazar daya kawo qanwar tata seta koma haka idan anyi girkin zata tsaya a raba ta kwashe duk abin arziqi ta hadasu da qasan tukunya ita bata ci ba ita bata bari wani yaci ba ta bakin Lantanar, ba kamar Mairo ba ita lantana idan tazo tun safe seta kai Taran dare har se Audu ya dawo Bintan ta fatattaketa sannan zata tafi yanda kasan bata da Miji balle Yara.

Haka suka gama suyar ko dandanon gishiri a harshenta ta koma daki. Washe gari tun sassafe aka ringa shigo da kayan cefane, guraren Goma Binta ta aiko kiranta, A falon Audu na sama ta sameta tasha kwalliya abinta ba zakace jego take ba. Ta gaidasu ta zauna tana satar kallon Audu da tun maganar jiya be sake ce mata komai a gidan ba dubasun da yake da Asuba ma beje ba yau. Kudi ya tura mata murya a daure yace

"Gashi nan, ki duba cefanen da aka kawo, abinda babu se a siya sannan su Bilki suna hanya bansan ko su nawa bane ki gayawa Mairo a saka abinci da yawa"

Tayi shiru a ranta tana mamakin yau kuma ita aka bawa kudin cefane sannan ita ake cewa ta fadawa Mairo a qara abinci abinda ko ran girkinta Binta ke fadar abinda za'a dafa.

"Shikenan na sallameki" ya sake fada seta miqe ta dauki kudin tana jin Binta cikin kissa murya qasa qasa tana ce masa

"Ko kaifa, ai ya kamata dai itama ta ringa jin matar gida ce ba wai ace komai sedai taga anayi ba kaga kar suzo a qara tafiya dani a baki ace na kankane komai"

Ta tafi tana mamakin Bintan a ranta, wato matar nan ko wagainiya Albarka shiyasa wani sa'ilin bata ganin laifin Audu saboda Bintan tamkar me rufa ido take. Bata taba mata Tijara ko cin mutunchi a gabansa ba, idan yana nan nunawa take nan dunita tafi kowa son su zauna lafiya da Bara'atu amma ita taqi bata hadin kai, da hakan take kanainayeshi kullum tana nuna masa laifin Bara'atu ne ita ce bata so su zauna lafiya, Bara'atu ce take fadawa yan uwansa mugun abu akanta shiyasa kowa baya sonta, Bara'atu ta tsaneta bata da buri illa na taga bayanta sannan ita kuma tayi ta nuna bajintarta da son jan Bara'atun da yayanta a jiki a gaban idonsa idan yana nan har kyautar abubuwa take kai mata ko yara yana fita tabi ta karbo abinta ta dora da Tijara shiyasa baze taba ganin cutar da take mata ba.

Maganar girkin kanta da farko ta hana ko gaidata masu aikin suyi da kuna ta canza ra'ayi ta karbe girki ita ta gaya mata ainin dalili amma shi se tace masa saboda Bara'atun ta huta ne hidima tayi mata yawa ga yara ga girki gara Mairo ta ringayi gaba daya tubda dai biyanta akeyi kuma dama kullum se tazo ko ba rabar girkin Bintan bane ire iren abubuwan da suke qara dagula zamansu kenan, shi tunda kunnene kawai se abinda yaji ba ruwansa da bin ba'asin ya akayi cikin kissa zata tunzuro shi ya dauki fushi da ita yanzu kuma da taso qulla wani abun shine zatace ya bata kudin cefanen abincin suna dan ta tabbata ba Alkhairi ya saka Bintan yin hakan ba.

Mairo taje ta samu tace ta duba kayan, data tambayeta me za'a dafa toh tilas ta koma ta sake tambayo Bintan tace mata Shinlafa da tuwo kawai zasuyi sauran abubuwan ta bayar da aikatau wannan yasa ta dan samu nutsuwa qila abincin iya jama'ar Bechi za'a bawa shiyasa ta barshi a hannunta. Tun rana suka fara rage aiki, su Bilki da Aisha da matansu Aminu ne suka yo gaba sauran dangi se gobe suna haka suka tasata gaba da tsiya harta rasa inda zata tsoma ranta wai daga dawowa harta tsomare a qauyen ma tafi kyan gani ta bari tsoron kishiya yayi tasiri a ranta.

Har an idar da Isha suka karbi baquncin mutanen Ikko, Yakubu da iyalansa Bara'atu ta rasa ina zata tsoma ranta saboda murnar ganin Balaraba. Suka rungume juna cike da kewa, Balaraba tayi kyau ta qara zama wata babbar Mace fata se walwali takeyi ita kuwa Bara'atu abin se godiyar Allah kawai. Daga gefe Aisha dake kallonsu tace

"Wato kwanciyar hankali duniyace, ku kalli dai idan daula da jin dadi ne Yaya Bara'atu tafi Yaya Balaraba samunsu amma kalle su ki gani banbancin kamar sama

da qasa kowacce da ka ganta base an gaya maka matsayin da take a cikin gidanta ba"

"Aisha kenan kedai da Allah yasa kike ke kadai a gun Mijinki kici gaba da gode masa domin ba zaki gane qalubalen me Kishiya ba se kina da ita duk abinda zaki fada ko ki bada shawara akai hasashe ne kawai tunda baki san ya ainihin matsalar take ba" Sauda Amaryar Aminu ta bata amsa.

Bara'atu kuwa a dakin Audu ta sauki Balaraba, ta fita ta kawo mata ruwa da abin tabawa tace

"Bari na dora muku abinci wannan bazata haka ace zakuzo ko Yaya Audu be sani ba"

"Wai injiwa? Audun da shi yaje ya dauko mu daga filin jirgi" Balaraba ta fada. Bara'atu ta gwale ido tace

"Filin jirgi? A jirgi kuka zo?"

Balaraba ta harareta tana dariya tace

"Ji yanda kika gigice kamar wnada nace miki da fiffike mukazo, jirgi muka hawo mana abin Allah in gaya miki yau se ga Balaraba a jirgi qiris ya rage na haihu saboda tsoro" suka kwashe da dariya gaba daya. Bara'atu ta sake cewa

"Amma shine be gaya mun zaku zo ba?"

"Ba zata yayi miki gashi ai kinfi yin murna da muka zo yanzun, ke ni ba wannan ba ya naganki gaka qashi da fata ko laulayi kikeyi?" Balaraba ta fada tana kallon Bara'atun, seta miqe kawai tana cewa

"Bari naje na dora abincin"

"Karki wahalar da kanki seda muka ci abinci muka taho tafiya a jirgi kamar wanda Aljanu suka ragewa hanya? Ni banma san minti nawa mukayi ba kedau Allah ya qara mana arziqi me amfani Allah kuma yasa badi mu lula muyi tafiya me nisa a Jirgin muje mu sauke farali" cewar Balaraba.

Dukda haka Bara'atu taqi zama tace to bari taje su gaisa da Yaya Yakubu daga haka ta tsere, bata so ta zauna tunda Balaraba ta fara zancen ta rame ko ciki ne da ita tasan yanzu magana zata sake dagulewa sedai tana fita Bilki ta shige ta samu

Balaraban ko kyakykyawar gaisawa basuyi ba dan tana sallah suka shigo yanzun taje ta gaida Yakubun kuma jira taje Audu ya matsa ra kwashe duk abinda ya faru da wanda yake faruwa ta gaya masa amma bari ta fara da Balaraban.

Tas ta labarta mata komai daya faru basa nan,

"Yanda kika san sallamammiya Bara'atu, na fada mata da nice wlh tun daga kan ginin nan gayyar zata watse. Hauka ma akeyi suci Talauci tare sannan dadi yazo ace ta zama yar kallo itafa da Boyi boyin gida babu banbanci. Idan anyi magana tace to ya zatayi? Na gaya mata taci abu ta kazan Yaya Audun tunda shi yake daurewa Bintan qugu tana mata iskanci kafin ta gangara kanta, ko Iskar qarya tayi ta musu rotse wlh duk zasu kiyayeta amma mata kamar Kazar da ruwa ya daka salaf salaf sedai tayita kuka in sun mata abu tana rama a haka fa kin ganta da kyan gani dalilin tajr Bechi kusan watanta biyar a can da ana gyaran gidan dawoqarta ne tayi wannan zabgewar to in aka cigaba a haka wata rana sedai azo a kwashi sauran qasusuwanta ai damuwa ta cinye tsokar tasa" Bilki ta fada cikin kumfar Baki.

Tsabar baqin ciki da takaici Balaraba kasa cewa komai tayi se qafa da take girgizawa, a haka Bara'atu ta dawo ta tarar dasu tana ganin Bilkin kuma ta tabbata ta gama kwaza komai. Fada Balaraba ta ringa mata kamar zata daketa da tayi tayi kuma seta koma banbaki da lallami dan lamarin Bara'atun ta rasa wannene ma zeyi amfani a ciki.

Banda kuka babu abinda takeyi ita kuma, haka suka kwana ko baccin kirki Balaraba bata iyayi ba, data rufe ido abin ze mintsineta ta tashi ta fara surfawa Bara'atun masifa can kuma tayi qasa tana lallashinta tareda bata dabarun kwatar yanci.

"Audu yana sonki, da ace baya sonki a yanda take wannan abun da ba zakiyi qarkon kawowa yanzu a gidannan ba. Wayo da dabara ne baki dasu, idan ta nuna miki wayewar Birni seki nuna mata ta qauye, akan me zaki ringa yiwa Kishiya kuka kin nuna mata kina tsoronta a fili ba dole ta takaki yanda taga dama ba, ai ko a ranki kina tsoronta ki dake idan ta fada ki mayar mata kar ki ganta wata zabgegiya kiji tsoron karta dake ki ai qarfi ba'a jiki bane idan kika qarfafa zuciyarki tsaf wlh zaki kaita qasa idan ma ta kaiku da dokuwa sannan shima karki raga masa tunda be dauki tsagin gaskiya ba. Wlh ki tashi ki kwatarwa kanki yanci idan ba so kike ki bata quruciyarki ki kashe kanki da kanki ba".

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Washe gari.

"Nifa wlh Ji nake kamar na rufeki da duka Bara'atu" Balaraba ta fada kafin taci gaba da cewa

"Banda tsabagen abin haushi Bintar me? Me akayi akayi wata Binta da zaki zauna ta shigo gidanki ta mayar dake yar kallo bayan ke kika ci wuyar Audun kika zauna dashi tun bashi da ko sisi har ya zama mutum ta ganshi ta aura na tabbata wlh a rayuwar da kikayi dashi Binta ko a me wanke mata kaya ba zata dauke shi ba. Amma shine kika zauna kika barta take zuba miki mulki a gida kin zama yar kallo jibeki dan Allah yanda kika qwanjale kika fita hayyacinki tamkar me wani ciwo ita kuwa tana walwala da farin ciki Miji na hannunta wlh tun wuri idan zaki farka gara, ki amshi Mijinki da matsayinki, ke kika sha wuya dashi dan haka yanzu kamata yayi duk wadda zataji dadinsa to a bayanki take".

"Kema dai kya fada Yaya Balaraba" Aisha ta tsoma musu baki taci gaba da cewa

"Koni da nake zaune a qauye wlh bazanyi sokoncin da Yaya Bara'atu takeyi ba banga wata kishiya da zanji tsoro ba, ba daga Kaduna ba ko daga Ingila ya aurota qarewar Bariki sena gwada mata nawa wayon qauyen dukda shima Yaya Audu da laifinsa ko nace ma yafi kowa laifi. Wancan zuwan da sukayi da Yaya Ummaru ya masa magana akan abinda tayi lokacin auran Saleh cewa yayi wai ayi haquri shi baya iya mata fada saboda idan ya duba yaga komai ya samu yanzu a rayuwa Ubanta ne sila kuma shi uban a duniya babu abinda yake so kamarta shi yasa yake mata lamuni kiji wani rainin hankali fa se kace wata diyar Qaruna ko kuma yanke Talauchi suka bashi".

Balaraba taja tsaki kamar zata tsinke harshenta kafin tace

"Saboda ubanta ya masa silar arziqi se akace tafi kowacce Mace ko yaya? Rabonsa ne a jikinsu kuma ko zasu bashi su haukace se yaci kawai tsabar mugun hali ne irin na maza matar da aka sha wuya tare da ita bola wadda zata diro rana daya itace abokiyar cin arziqi kuma wlh Audu ya bani mamaki a irin yanda kowa yasan yana qaunar Bara'atu ban taba tsammanin ko Gimbiya Elizaabeth ya auro ze fifitata akan Bara'atu ba"

"Abin ne nake ga kamar harda Asiri" Aisha ta sake fada Balaraba ta harareta tace

"Aikin kenan kullun ace Asiri, shin maza basa isakanci dole se an musu Asiri da yawa da haka suke fakewa ayita daukar Alhakin matan da basu ji ba basu gani ba ace asirce su sukayi, shidai Audu daman halinsa ne be fito ba se yanzu daman kuma kinsan kudi shi yake nuna ainihin kalar mutum ita kuma Binta tayi amfani da wannan damar take zuba sharafinta tunda shi ya bata qofa. Ni da Allah tashi kije ki karbo musu idan ba haka ba kuma naje da kaina" ta qarashe tana kallon Bara'atu data sunkuyar da kai idonta ya tara kwalla dalilin maganganun da sukeyi. Tun jiya Balaraba take mitarzancen nan, babu wanda ze fuskanci halin da take ciki kowa sedai yace mata wawuya ko sakarya ta kasa kwatar yan cin kanta ta sakarwa Kishiya ragamar gidanta daga zuwa to dan Allah base ta samu kwarin guiwa da Adalci daga gurin wanda ya ajiye su ba?

"Bari kiga na tashi" Balaraba ta sake fada tana yunqurawa dakyar saboda tsohon cikin dake jikinta nan Bara'atu ta zabura ta miqe tana cewa

"Bari naje, ni magana ce ban so wlh da kun barni yanzu se a dora musu wani tunda dai ta bamu iya rabon mu" da haka ta fice daga dakin tana jin Balaraban na zaginta. Yan Bechi na ganinta sukayi mata caa suna cewa

"Yawwa Hajiya Bara'atu, tun dazu muke jira a qaro abincin kinga yara se kukan yunwa suke wasu ko karin safe ba suyi ba muka fito". Da wani yanayi tace musu

"Kuyi haquri yanzu za'a kawo" ta fice daga falon zuciyarta na bugawa cike da taraddadin abinda ze biyo baya idan taje tace a qara musu abincin, dukda cewar su sukayi wahalar dafashi ita da wasu daga cikin yan uwan Audu da suka fara yowa gaba tun ana jibi suna. Seda suka dafe shinkafa kwano goma sha biyar, dambu kwano bakwai ga tuwon safe na kwano bakwai amma banda su Waina, Funkaso Alale da sauran tarkacensu irin na yan gayu da suka kai akayo musu daga waje amma a ciki tuwo Malmala goma suka basu se shinkafar da bata fi rabin kula madaidaiciya ba tun hantsi be gama dagawa ba kuma suka kusa cinye shi saboda ba'a karya ba duk suna jiran a kammala abinci sannan ga ma'aikatan da suka tayasu duk a ciki ta debar musu suka tafi dashi gidajensu gaba daya yan uwan Bintan suka lode abincin a Kuloli suka kai daki.

A hankali take gifta matan dake zaune tsakar gidan yan suna, wasu maqwaftansu ne wasu kuma qawayen Binta da matana Abokanan Audu wanda suke hulda da ita kadai duk kuma rukunin data wuce zata musu sannu wasu su amsa wasu suyi mata banza harta dangana da qofar falon Binta,

"Maman Baba" taji an kirata ta waiwaya fuskarta ta fadada da murmushi ganin Maman Kabir ce maqociyarta guda daya da suke sabgar Arziqi gaba daya sauran Binta ta kwace su ko tace sun koma gurin Bintan.

"Se yanzu zaki shigo mana" ta fada tana jan kumatun Kabir dake hannunta ya kuwa janye ya lafewa mamansa tayi dariya tace

"Maquyacin kawai"

"Tun safe naso na leqo baqi nayi wlh se yanzu suka tafi" Maman Kabir din ta fada. Bara'atu tayi murmushi tace

"Na sani tsokanarki nakeyi dazu Shamsiyya ta shigo ai tace Yayan Baban Kabir ne yazo, qarasa ciki to yanzu zanzo abu zan karbo gurin Binta".

"Ai gara na biki nima naga Jinjiri kafin na zauna" Maman Kabir ta fada hakan yasa suka shiga falon Bintan tare. Yayyenta na tsaitsaye a falon sun hada kai suna magana sallamar su Bara'atu ta sakasu zabura tamkar marasa gaskiya, Yaya Salima ta qaqalo fara'a ta yabawa fuskarta tana kallon Bara'atu tace

"Aa uwargida an leqo? Sannunku fa da aiki"

"Uhm" Bara'atun tace kafin kanta a qasa cike da taraddadi tace mata

"Daman yan Bechi da suka zo yanzu ne Abinci be isa ba shine nace ko za'a dan qaro musu"

"Aikin kenan abinci Abinci koda yake ba a saba ci ba, banda jaraba ma suna amma anyo gayya kamar wani Bikin fari wato za'azo aci banza to babu kowa ya nade yunwarsa ya koma da ita" Munira wadda take autarsu Bintan amma ta rigata aure ta fada cikin Fitsara se Yaya Saliman tayi saurin tareta tana cewa

"Haba ke kuwa Munira Abinci dai Allah na tuba abin aci ayi kashi kuma fa mutanen nan dangin me gidan ne idan ba'a basu ba to su za'a bawa? Barta dan Allah Bara'atu shiga ciki ki gayawa yar uwartaki se muji kamar Adadin da za'a zuba musu" ta qarasa tana nuna mata qofar dakin Bara'atu.

Maman Kabir da takaici ya quleta, ba abin tayi magana ba ta jawa Bara'atun ta juya kawai ta fita tana ce mata

"Bari naje an jima kan na tafi ma gaisa da ita" Bara'atu kuwa a sanyaye ta tura qofar dakin Bintan da sallama wanda tun zuwanta gidan shekara guda sau daya ta taba takashi randa aka kawota, ko ranar da zata haihu a qofar falo suka hadu ta taimaka mata suka tafi Asibiti. Zuciyarta duk babu dadi ta shiga, ita abincinma ko kalarsa bata dandana a harshenta ba da suka gama girkin shayi ta kada tasha

saboda yanda ta gaji sannan duk taron Jama'ar da suke iqirarin sunzo cin banza Jininta biyu ne a ciki Hadiza wadda dama tare suke zama se Ubaida data biyo yan zuwa suna saboda taga Yan uwan nata ragowar dukfa Dangin Audu ne, qanne da yayyensa da Matan yan uwansa se  Maman Kabir Qawarta tilo da ta shigo yanzu wadda tana da tabbacin harta fita be zama lalle ko ruwan fanfon gidan tasha ba.

Bata tarar da Binta a dakin ba motsin da taji a Bayi yasa ta ankare da tana ciki, Jinjirin daya ci sunan Babanta Binta Zakariyya na nade cikin showel ta matsa inda yake yanda aka kwantar dashi yayi kusa da bakin gado sosai, dukda cewar jinjirine amma ze iyayin motsi me qarfin da ze fado hakan yasa ta dagashi ta maidashi can tsakiyar gadon yana ta sharar bacci abinsa daidai nan taji muryar Binta akanta tana cewa

"Waye wannan? Uban me kikeyiwa Dana?"

"Gyara masa kwanciya nayi, naga an barshi a bakin gado" Bara'atun ta fada kanta a qasa. Binta ta galla mata harara ganin itace kafin tace

"Akan me zaki shigo mun har quryar daki me kike nema?"

"Daman maganar Abinci ce yan Bechi sun qaraso wanda aka bayar kuma ya qare shine nace ko zaki saka a qara musu"

"Babu, gayyar yunwa nace babu abincin ko kuwa ni na ce suzo balle na basu abinci?" Bintan ta fada cike da masifa. Bara'atu ta kalleta tace

"Yan uwan Yaya Audu ne fa ba wasu daban ba"

"Yana sama ai seki hau ki gaya masa ya sakko ya girka musu suci tunda yan uwansa ne ko kuma ke ki je ki sake dora wani amma ni abinci na ban dafa saboda wasu yan qauye ba na baqin dana gayyato ne dan haka malama maza fitarmun daga daki tun ranki be baci ba"

Kafin Bara'atu ta sake cewa wani abu burum Yaya Salima ta fado dakin kamar wadda ta labe daman tana jiran lokaci yayi ta shiga. Inda jinjirin yake ta nufa ta dauke shi tana cewa

"Bari a fita dashi mutane nata zuwa ganinsa se kuma ta zare ido ta kalli Binta data cire dankwalin kanta zata canza kaya tace

"Ke zo ki gani wane irin bacci yaron nan  yakeyi haka qirjinsa baya dagawa alamar numfashi?"

tana rufe bakinta Babbar Yayarsu Anty Sakina ta shiga dakin ta kallesu sunyi cirko cirko tace

"Lafiya kuwa meya faru?"

Salima ta miqa mata Babyn tana cewa

"Yawwa dubashi kiga Anty se naga kamar baya numfashi" da yake ita malamar jinya ce, nan ta tattaba yaron tayi salati tace

"Wannan ai ya rasu".

Maganar ta taja hankalin Bara'atu da har ta kai qofa ta tsaya, Binta ta finciki yaron daga hannun Yayarta tana duba qirjinsa babu alamar yana dagawa, ta kai kunnenta zuciyarsa bayan ta saka hannu a hancinsa bata ji dumin numfashi ba nan ma shiru seta sake shi Yaya Saliman tayi azamar tarewa kafin ya kai qasa kamar qiftawar Ido Binta ta dira gaban Bara'atu ta cakumeta tana cewa

"Kashe shi kikayi? Na rantse da girman Allah se kin bishi" nan ta shiga kai mata duka kamar me casar gero kururuwarta da ihun Bara'atun ya janyo hankalin sauran dake falo shigo gaba daya, tuni gida ya dauki hayaniya magana ta fasu Bara'atu ta kashe jinjiri gashi can Binta ta riqeta itama tace seta kasheta. Binta ko dukan Bara'atu take babu ji babu gani tamkar ma bata hayyacinta fadi kawai tace

"Wlh sena kasheki, sena bi kadin haqqin dana" ta shiga jibgarta tamkar Mahaukaciya ta kama yaron da yake tsokanarta saboda rashin Imani kuma yan uwanta kaf dake tsaye aka rasa wadda zata kwaci Bara'atun daga inda suke tsayen suke ce mata wai ta qyaleta ga gawar Jaririn a Hannun Anty Sakina.

Ihun Bara'atu na neman ceto da kururuwan Binta tana fadin seta kasheta ne ya janyo hankalin Yan suna. Hankali tashe yan Bechi suka duru darin, su suka taru suka danne Bintan har Bara'atu ta samu ta kubuta daga hannunta tayi mata jina jina fuska ta haye dan duka tasha ta ko ina.

"Meye haka? Kinyi hauka ne Binta zaki kama ta da duka?" Audu da suka sakko da gudu shida Jama'arsa da suka zo mata suna ya fada cikin tashin hankali.

"Wlh ban gama dukanta ba, idan anga na haqura to na kasheta kamar yanda ta kashe mun Da" Bintan ta sake fada tana zaburowa yan uwanta suka riqeta. Cikin rashin fahimta Audun yace

"Wace magana kikeyi haka? Wane dan aka kashe?"

Bayan wasu Awanni.

Ihun kuka da hargowar Binta kawai ake ji a falon,

"Na rantse da girman Allah yanda ta kashe shi itama seta bishi babu uban daya isa ya hanani daukar mataki akan wannan abun" taci gaba da sheqa kuka. Dazun da akayi jana'izar yaron sanda aka zo fita dashi qaramin hauka ta tayar ta riqeshi qam dakyar Maza suka bambareta ta ringa doke doke qarshe se a daki a ka kulleta se yanzun bayan Isha Audu yaje ya budeta da kansa ya tasa qeyarta zuwa samansa inda Yakubu yace ya tattaro su gaba daya aji abinda ya faru. Babu tsoron Allah ko tunanin bayan wannan rayuwar da akwai wata Munira da Salima suka bada shaidar Bara'atu ce ta kashe jaririn dan Munira cewa tayi ta leqa dakin ta hangota zaune an showel dinsa bata dai tsammaci yana ciki ba seda Salima ta shiga ta tarar da ya mutu.

Sakina dai tayi shiru, har ranta bata so abinda sukayi ba, magana ta gaskiya yaron ya rasu tun kafin Bara'atu ta shiga dakin, qus qus din da ta tarar dasu sunayi na taraddadin yanda zasu fada mata ne suma basu san menene silar mutuwarsa ba haka nan suka lura da babu rai tattare dashi shine suka shimfide mata shi a kan Gado ita kuma Bara'atu ta taka sahun barawo kuma tana shiga Salima ta kitsa ai kawai suce itace kuma har yanzun basu fadawa Bintan ainihin abinda ya faru ba.

Yakubu ya kalli Bara'atu data zama wata abar tausayi, fuskarta a kumbure ga duka ga uban kukan datasha. Cikin tausayawa yana kallonta yace

"Bara'atu menenr gaskiyar abinda ya faru?"

"Wallahi Allah shine shaidata ko taba yaron nan banyi ba. Ni daga haihuwarsa ma sau daya na taba riqeshi a Asibiti, sanda na shiga dakin na tarar dashi sun kwantar dashi a gefen gado abinda ya saka na matsar dashi tsakiya saboda naji tsoron karya motsa ya fado shine Binta ta fito ta ganni ko ita idan zata fadi gaskiya a tsaye ta ganni ban zauna mata a daki ba ga yan uwana nan a tambaye su da fitata daga daki zuwa sanda abin ya faru ya isa ace na zauna akan Jariri ya mutu har jikinsa yayi sanyi?" Bara'atun ta fada cikin dasashshiyar murya me ban tausayi. Yakubu ya gyada kai cike da aminta da zancenta ya kalli Audu yace

"Kaji daga kowanne bangare se kayi alqalanci bisa Adalci"

"Alqalanci? Shi ne ze yanke mun hukunci akan kadin ran dana da aka dauka? To billahillazi huwarrahamanu ba'a isa ba, ku barni na kasheta da hannuna ko kuma gobe na tafi kotu, ina da qwararan hujjojin da zasu saka a zaman farko Alqali ya saka a gillewa muguwa kai ta bishi, wlh ran dan baze tafi a banza ba" Binta ta sake zaburowa tana fada.

"Ya isa kiyi shirunki babu wanda yace ran danki ze tafi a banza" Audu ya fada, kafin ya kalli Bara'atu yaci gaba da cewa

"Dama ai kinyi furucin se kin ga bayan ta ita da abin cikinta. Allah be baki nasara ba tun yana ciki baki haqura ba seda kika aiwatar da shirinki yanzun ko Bara'atu yaushe kika zama muguwa me baqar zuciya haka? Ina tsoron Allan ki da har zaki iya zama akan Jinjirin kwana bakwai har seda ya daina numfashi me ya tsare miki a duniyar daya saka kika kauda shi?"

Shiru ne ya gifta gurin kamar kowa ya mutu koda yake da yawa daskarewa sukayi basa ma numfashi tsabar mamakin Kalaman Audu, Yakubu har zamewa yayi daga kan kujera yana leqen fuskar Audun ya kuma gaza furta komai. Audu yaci gaba da magana yana cewa

"Na gaji da wadannan mugayen halayen naki Bara'atu, daman simi simin mutum da yawanku mugayene, zuciyarku cike take da mugunta fal gashi kuwa kin fara fito mana da ita. Yau kin kashe Zakariyya, qila gobe Kan Bintan zaki juya idan aka kwana biyu kuma ki hau kaina na mutu ki gaje abinda na tara dake da yayanki ko ba haka ne shirinki ba shiyasa bakya so Binta ta haihu saboda ya zama yayanki kadai suke da gadona to bazan jure ba, ai se da igiyoyin aurena akanki ne idan na mutu zaki ci gado na ko? To kije kawai Allah ya hada kowa da rabonsa na Alkhairi na sawwaqe miki igiya daya".



https://chat.whatsapp.com/I8xKHGurk7EBf5ZqQdxHKG

"Allah ka gani babu saka hannuna a cikin wannan al'amarin, Allah karkasa haqqin baiwar Allan nan da suka dauka ya bibiyeni" Ummu ta fada bayan data gamajin abinda ya gigita mata tunani. Da safiyar sunan aka kirata daga gurin aikinsu, ita din

yar jarida ce kasancewar ta dauki uzuri ta tafi Kano se kuma wani aiki ya taso dan haka manajansu ya kira akan taje a maimakon ace se an taso wani daga Kadunan yazo tunda tana tareda abin nadar rahoto da sauran abubuwan buqata shiyasa ta tafi bata san badaqalar da aka kwasa ba seda ta dawo kuma da ace tana nan tabbas da bata goyi bayan abinda suka aikata ba dan ita din itace Mahaifinsu sak gurin dattako. Ta Jinjina abin ta kumayi matuqar mamakin yanda yan uwan nata suka iya aikata wannan ta'asa.

Idanunta dauke da hawaye ta kalli Babbar Yayarsu sakina da duk itama abin duniya ya isheta yace

"Yanzu Yaya harda ke? Kika bada shaidar zur? Kuna tsammanin idan Dady ko Mama sukaji maganar nan me zasu ce? Wannan wane irin zalunci ne yau koda ace dagaske matar nan ta aikata abinda kuka ce ai wlh ku masu rufa mata Asiri ne idan yaso ku barta da Allah ya kamata da haqqin ran data dauka amma bataji ba bata gani ba kun laqa mata sharrin da ze bibiyrta har yaya da jikoki sannan kunyi sanadin datse mata igiyoyin aure wlh ku kuka da kanku ku kuma shirya ta inda haqqin ta ze bibiyeku domin kuwa Allah baya bacci se ya saka mata kuma. Ke kuma( ta juya kan Binta) tun kina da sauran dama ki koma ga Allah ki bar wannan turbar da kika hau dan wlh babu inda zata kaiki se filin Nadama mara amfani da dana sani. Yanzu ba se anjima ba ki tashi kije ki gayawa Mijinku gaskiyar magana ki warware wannan qullin da kika yi, karki bari Yarinyar nan ta bar gidan nan dan wlh Binta ina jiye miki rayuwar da zakiyi a gaba wuyanki daure da haqqin ta, Kizo ki tarar da mata a gidanta ki gallabi rayuwarta ki hanata sakat da Mijinta meye ribarki a ciki?"

"Dan Allah Yaya Ummu ki riqe wa'azinki abinda ya faru dai ya rigada ya faru zance kuma Dady ko Mama sedai idan ke zaki fada musu kuma idan kika janyo suka mana baki kema se Allah ya saka mana akanki dan haka gara mu rufe maganar nan a inda ta faru Allah ya kiyaye gaba" Munira ta fada ganin sauran sunyi shiru har Bintan da Alama maganar Ummu tayi tasiri a zukatansu wannan ya basu qwarin Guiwa itama Bintan ta karkace tana cewa

"Allah ne ya kawo mun hanyar fitarta cikin sauqi babu abinda zan fadamasa wlh". Da dai Ummu ta tabbatar sunyi nisan da ba zasuji kira ba dole ta qyalesu, a iya saninta iyayensu basuyi musu kalar wannan tarbiyyar ba ba kuma tasan a inda suka samo ta ba tana kuma musu fatan shiriya a gurin Allah domin basu hau kan layin da ze bulle dasu ba.

A bangaren Bara'atu kuwa duniyar ta mata zafi, har ta dangana da cikin dakinta bayan jefa qafa take kawai badan tasan ina take zuwa ba. Ta zauna dabas a qasa, Balaraba da labari ya iske ta dan bata je zamanba itama ta zama kamar wata mutum mutumi saboda mamaki. Suna haka Hadiza qanwarta ta shiga dakin ta shiga sauke kayan Bara'atun tana zubawa a Jakunkuna cikin tsananin fushi.

"Wlh se sunga sakayyar mugun abunsu a kansu, shi kuma in sha Allahu har ya mutu yana nadamar wulaqantaki butulu wanda be san Halacci ba" haka Hadizan ta ringa fada tana zuba kaya ta hade mata komai tas dan daman kayan nata ba yawa ne dasu yanzu ba ta kwashe da yawan suturunta ta kyautar kamar yanda ta saba duk sallah kuma zeyi mata dinkuna masu yawan gaske to Bana da abin yazo a zamanin binta kala uku ya mata se lokacin Bikin Saleh nan ma ya mata uku.

Hadiza ta gama hada kayan Bara'atu ta fara hade na yaran se a lokacin Balaraba ta iya bude baki tace

"Karki hada kayansu ki barsu a gidan ubansu babu inda zataje masa da Da"

"Bazan iya barin Yayana ba ba zata riqe su ba" Bara'atun ta fada tana fashewa da kuka kamar wadda ake yankar naman jikinta. A mugun fusace Balaraba yace

"Ai ko kashe su zatayi se kin barsu, wlh ba zakiyi masa wahalar yaya ba yanda ya auro ki ke kadai ki tafi su zauna a gidan ubansu kuma dole ta wahalta musu, abinda tayi miki kuma Allah na gani seya saka miki ko ba dade ko bajima se taga sharrinta a kanta da ita da yan uwan nata gaba daya".

Haka aka kwana ana maida magana, washe gari Qarfe shida motar yan Bechi ta daga, Bara'atu kuma mota daban Yakubu ya nemo ta dauketa da kayanta tare dashi da Balaraba suka tafi banda yaran dan kamar yanda Balaraba tace ta barsu shima Yakubun da Asuba daya shiga yace a kira masa Bara'atun haka ya gaya mata ta zube masa Yayansa. Watsa watsa sukayi da Audu akan al'amarin, babu yanda beyi dashi akan ya janye furucinsa ba amma ya rantse akan baze maidata ba wannan tasa Yakubun barin gidan a cikin daren be kwana ba da Asuba kuma ya fita ya nemo mota aka balle kayan Gadon Bara'atun tas yasa aka lode su sannan ya samo qarama suka tafi a ciki zuciyarsa cike da baqin ciki da takaicin abinda Qanin nasa yayi. Ya kuma yi rantsuwar cewar babu shi babu duk wata sabga data shafi gidan Audu.

Abin seya zamarwa Bara'atu duka biyu domin kafin su isa wanda suka fara tafiya suna kai labari kamar wutar daji ya yadu cewar hassada tasa ta kashe jariri saboda yayanta kadai take so su gaji Audu. Mutane da abin mamaki wasu tamkar a

gabansu akayi se kace wani hawan sallah haka aka cika qofar gidansu ana jiran aga ta inda zata bullo tunda ance ya saketa ta hado kayanta tana hanya, aiko da suka isa seda Yakubu ya hada da dura Ashar abinda ba halinsa ba kafin matan da sukayi dandazo suka watse da sabuwar gulmar cewa magana ta tabbata gata nan harda kayanta gaba daya da alama auran ya qare saki uku yayi mata.

Seda tayi matuqar dagaske kafin ta iya shanye wannan jarabawa. Yanda mata suke musu zuruftu suna yada musu magana ita da mahaifiyarta har ciwo ya kwantar da Innar tata. Babanta kuwa nasa bala'in yafi na kowa dan da farko ma cewa yayi ba zata zauna masa a gida ba. Duk kuwa sa Yakubu ya sameshi qafa da qafa ya gaya masa komai daya faru amma mutumin nan ya hau kan qarya ya zauna ya dora mata laifi har yana cewa uwarta ce ta sakata. Watanta biyu a gida Audu ya tattaro yaran ya aiko mata dasu, tana zaune se gani tayi ana shiga da kayansu da buhunhunan abinci ta tambayesu su dawa sukace Direban Babansu ne ya kawo su a cikin kayansu taga kudi, kudade masu yawan gaske se farar takarda da gajeran rubutu a jiki.

"Kiyi amfani dasu gurin kulawa da yarana duk wata zan ringa aiko musu da abun buqata Aminu ze kai su makaranta a nan" abinda takaddar ta qunsa kenan. Hawaye suka wanke mata fuska, wato dagaske Audu ya cireta daga rayuwarsa kenan baze bata damar wanke kanta ba tana roqon Allah daya bayyana gaskiyar abinda ya faru badan tana so ta koma gidan Audu ba aa sedan ya cire zargin kisan kai daya dora mata a ransa.

*****************************

A gidan Audu kuwa duniya sabuwa Binta ta bude ta kori Bara'atu ciwon idonta yanzu bata da wata damuwa ta samu gida ta samu Miji yanda ya kamata musamman wannan abin daya faru yasaka yake qara riritata yana lallabata da sunan tausayinta yakeji akan abinda ya faru. Da farko da taga an bar yaran bata damu ba dan ta qulle a ranta ta samu bayi sedai yanda taga Audun ya ninka kulawar da yake musu sanda uwarsu tana nan yasa hankalinta ya tashi dan haka tasan yanda tayi Abdullahi ya tafi makarantar kwana wanda daman an gama masa shirin hakan tafiyar Bara'atu tasa Audu yace an fasa nan ta san yanda tayi ya tafi daman tare suke kwana dasu Babangida shine dawainiyarsu idan Mairo tazo ta karba babu abinda Bintan take musu se Audu na gida dan haka Abdullahi bayan tafiyar Abdullahi makaranta ya zaman yaran su kadai suke kwana a daki, sun saba ana tashinsu suyi fitsari ko basu ruwa da sauran abubuwa yanzun basu da meyi musu cikin dare haka Babannan ze tashi yayi ta koke koke sedai Audun ya sakko yaji dasu tana kwance se ta fake da cewar nauyin bacci ne da ita bama ta jiyo su, randa aka samu akasi suka mata fitsari a kwance ranar wuni zatayi yana gana musu Azaba idan ya fita in ya dawo kuma ta ringa cewa ita ta kasa gane kan yaran nan,

qana na dasu amma se nunkufurci tamkar uwarsu haka suke mata duk yanda take jansu sunqi sake mata.

Ya gasgata hakan saboda ko a gabansa ta jasu basa zuwa dalili kuwa Izayar da take musu idan baya nan kuma tace in suka fada seta yanka su, daya gaji da dawainiya dasu da dare baya samun bacci ya yanke shawarar a nemo me aiki da zata ringa kwana nan kuma tace bata yarda ba qarshe dai ya yanke shawarar mayarwa da uwarsu su tunda yasan itama ba a sonta ta barsu ba Yakubu ne ya tilasta mata wanda tunda ya koma a Lagos ko sau daya basuyi magana ba, fushi yake na gaske dashi shi kuma bega abinda yayi me girman da har Yakubu da sauran yan uwansa zasuyi fushi dashi haka ba. Basu dubi abinda ita Bara'atun ta aikata ba, idan daya bar Binta niyya tayi ta daga maganar zuwa Kotu sakin da yayiwa Bara'atu ne ya rage kaifin rigimar amma kowa be duba hakan ba laifinsa ake gani hatta da Alhaji Zakariyya Baban Bintan seda yayi masa fada sosai akan abinda yayi dukda ya fahimci da alama Alhajin be san musabbabin sakin ba.

Kwanci tashi har aka shekara da rabuwar Audu da Bara'atu a sannan kuma Binta ta sake haihuwa aka maida mata da sunan Babanta Zakariyya, rayuwa taci gaba da gungurawa, budi da Arziqi suna qara zuwarwa Audu a shekarar kuma yaje aikin Hajji tareda Yaya Baba babban Yayansu da Goggo Fadi, da Yakubu yaso suyi tafiyar amma yace ba zashi ba dan har sannan be sauka daga fushin da yayi da Audun ba, wannan dalili ya saka Audun bawa Yaya Baba kujerar ita kuma Goggo Fadi Yakubu ne yace ya biya mata, a cewarsa iyayensu Malam da Dada duk basuyi tsahon ran da zasuci arziqinsa ba dan haka yayi mata yasan zasuyi Alfahari dashi a inda yake ai kuwa taji dadi yayanta sunji dadi suka ringa masa Addu'a kamar me wannan abun da yayi ya saka Yan uwan zage jin zafinsa akan rabuwa da Bara'atu, dukda tafiyar ba'a son ran Binta akayita ba amma ba yanda ta iya tunda tana da danyan Jego a sannan haka sukaje suka dawo Audu ya koma Alhaji Audu.

Bayan dawowar Audu daga aikin Hajji ya tattara kudade daya dade yana tarawa tun bayan daya fara harkar mai. Kaduna ya nufa dasu ya samu Alhaji Zakariyya. Sanda Alhajin ya gama sauraron jawabinsa tsaf yana kallonsa yana murmushi. Shikam haka nan Allah ya dora masa qaunar Audun, tamkar sun hada jini ta wani gurin.

"Da gidan Mai, da jarin dana baka duk kyautace Abdullahi shiyasa hatta da filin da sunanka aka siyeshi haka nan na baka zabin sunan da za'a sakawa Kamfaninka. Ina fatan ya zame maka hanyar riqe kanka da Ahalinka gaba daya kuma Al'umar annabi su amfana da dukiyarka" Alhajin ya fada yana kallonsa. Haka Audu ya dawo Kano cike da mamakin karamci irin na Alhaji Zakariyya, wannan ya saka ya qara daura

aniyar kulawa da Binta domin yana ganin babu wani abu da zeyiwa Alajin ya biyashi tamkar kyautata mata.

Yanayin Budi da sana'arsa ta sakashi haduwa da sababbin Abokanai matasa masu tashen kudi kamarsa a lokacin, kamar kuma yanda rayuwa take a kowanne fanni mutum yakan hadu da Abokanai na kwarai dana banza, ya rage a karankanka kayiwa kanka Alqalanci kabi wanda Tarbiyya da dabi'arku tazo daidai to hakan ce ta faru da Audu yayi sababbin Abokanai da suka kasance Yan cikin kwaryar Birni wayayyu kuma yan Boko sun fantsama cikin harkar Man fetur domin sannan itace harka data bullo da akeyin kudi da ita a dare daya.

Alhaji Bashir da Alhaji Ali sune mutum biyu da suka fi shaquwa da Audu saboda koda tafiya ta kamasu zuwa inda suke dakko Mai tare sukeyi sannan suna wasu sabgogin Kamar fitar Kayayyaki irinsu Cocoa da Qaro zuwa qasashen dake da buqatarsu. Wannan shawarar Audu ce dan tun yana zaman bakin rimi yakan tsince hirar ana zuwa daga waje ana siyan wadannan Abubuwa. A yawace yawacen kasuwancins yasan duk inda ake samunsu dan haka suna haduwa da Alhaji Bashir wanda shi kuma yana da kyakykyawar Alaqa da wasu Turawa dan a qasar waje yayi karatu nan da nan aka qulla kasuwancin se Ali ya shigo ciki shi kuma ya nemo musu masu siyan Qaro nan da nan Kasuwa ta bude musu Arziqi kamar ana ruwansa ta ko ina zubowa yakeyi.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Audu be tsaya iya nan ba yana Noma, manyan gonaki ya siya a Bechi sannan a Gadonsu da yake juyawa an fitar kowa ya siya masa tasa Bilki da Aisha sun bawa Mazajensu suna kula musu da ita shi kuma ya karbi hayar ta Yakubu data Baballiya yana Nomasu, babu abinda baya Nomawa haka nan be yada saide saiden Kasuwa ba Shagonsa na kayan yara da mata na nan ya qara bunqasa ya zuba yara suna kula masa dasu.

Alhaji Bashir  shine me rawar kai a cikin guruf dinsu kuma shi ya fara diban Audu suna yawo a gari, shine rakashi gurin waccen yau gobe gurin waccan, tun yana zuwa rakiya kawai har ya zama shima ya fara kule kulen Mata. Dukda dai iyakar hirace take hadashi dasu sabanin Abokin nasa da yake taba shashanci da Matan. Ya kashe musu kudi su biyashi da Jikinsu bayan harkar mata har ruwa yana korawa kuma duk abubuwan da yakeyi yakan nunawa Audu hakan ba komai bane, a nan Nigeria ne ake daukarsu a wani Abu amma yej turai yaga rayuwa kuma menene amfanin neman da sukeyi idan ba zasuji dadin rayuwarsu ba?

Ali ma yana kula mata amma shima kamar Audun hirace kawai amma kuma su ukun ko da yaushe suna tare, duk yawon da Bashir zeje zasu rakashi su suka bude masa Ido da zuwa Hotels, su kama daki su wuni suna hira da yan mata a kashe musu kudi. A tun ana fitar rana har ta kai an koma ta dare. Idan ya dawo gida da Magriba ya gama uzurinsa ze salla wanka ya fita, Binta ta bararraje a gida hankali kwance ita kadai Babu Bara'atu. Bata wani damuwa da fitar tasa tunda tana samun duk wasu buqatunta idan ya zauna a gidan ma.me zeyi mata kuma a tunaninta be kawo mata cewar gurin Mata yake zuwa ba musamman data san yana harkoki da yawa yanzun.

A irin wannan yawaye yawacen Bashir ya kwashe su gari ya gari har kwantagora, basu san inda zasu ba seda suka gansu tsulum a gidan Karuwai, wai Ashe Ajo za'ayi shi kuma Bashir din da yake babban kwastoma ne kusan duk wata Karuwa data amsa sunanta a Kano yasan da zamanta to dalilinsa na zuwa kenan harya kwashi Abokanansa suka tafi tare. Ashe qaddarar Haduwa da Zubaida Yar Dagwas ce takai Audun Kwantagora, kyakykyawar yarinya Baqa me matsakaicin jiki yana ganinta Bara'atu ta fado masa a rai, idan yace be damu da rabuwarsu ba yayi qarya amma yakan danne zuciyarsa da cewar tayi abinda ya cancanci ya rabu da ita.

A yanda ya fahimta ko a cikin Karuwan Zubaida me Aji ce domin daga shigarta zuwa yanda take kamewa a gefe tanawa kowa kallon be isa ba ga Maza nata zuwa suna mata magana amma taqi koda yi musu kallo arziqi balle ta karbi tayinsu, bayan an tashi daga Ajo Bashir ya wuce sharholiyarsa Ali da Audu na zaune a dakin da suka sauka. Babu irin macen da Bashir be tura musu ba amma Ali ya kore su.

"Bana fatan na daukarwa Ahalina bashin zina dan ban san wanda ze biyashi ba, iya abinda mukeyi Allah ya yafe mana shima ina masa fatan ya shiryu ya dena abinda yakeyi" Ali ya fadawa Audu sanda yaga shaidan yana qoqarin ingizashi ya karbi tayin wata Kilaki datazo kansu tana duk wani abu data san zeja hankalin Namiji gareta, Alin ya mata korar kare.

"Nifa Ali da akwai yarinyar dana gani, kuma wlh ba sha'awarta nake ba ji nayi kamar sonta ya kamani a kallon farko" Audu ya fadawa Ali abinda yake zuciyarsa dan tunda ya zauna Tunanin Zubaidan yakeyi duk kuma macen data shiga se yayi fatan Allah sa idan ta fita ita ce zata biyo baya amma be ganta ba.

"A nan kaga macen da kake so? Ko kuma kawai kace mun kaima zaka fada ruwa" Ali ya fada yana gyara kwanciyarsa.

"Wallahi dagaske nakeyi, baka kuka da ita ba? Wata yar baqa haka ta saka jan kaya, dana kalleta se na ganta kamar Matata ta farko da muka rabu tunda na zauna a nan nake tunaninta" Audu ya sake fada. Ali ya juya masa baya yana cewa

"Lallai ka haukace Audu" daga haka yayi shiru. Audu kuwa be iya runtsawa ba se gabanin Asuba, tunanin Zubaida ya addabi ransa. Jin ta yakeyi a zuciyarsa kamar wadda ya shekara da sani abin tamkar Asiri a dan baccin da yayi kafin gari ya waye ma har mafarki ta yayi.

A daren ranar sun shirya washe gari zasu taho dukda Bashir be so ba sedai gari na wayewa Audu yacewa Ali su bari se gobe su tafi"

"Sedai na tafi na barku a nan dan ni banga abinda ze saka na qara kwana a gurin nan ba" Alin ya bashi amsa.

"To ka rakani na gwada sa'ata, idan ta kulani shikenan ko yau din zamu iya tafiya" cewar Audu. Kallonsa kawai Ali yayi dan lamarin Audun ya fara bashi tsoro. Ya tsoron kar maganar Hausawa ta tabbata da sukace zama da madaukin Kanwa na kawo farin kai, idan Audu ya dauki Halin Bashir to in beyi da wasa ba shima zasu jashi ciki dan haka ya kakkabe rigarsa ya fice daga dakin yana cewa shidai ya tafi ze hau motar Haya.

Qarfe goma suna tsaye bakin mota gaba dayansu, Bashir sunyi fada da Karuwar daya kwana da ita har taji masa ciwo da kwalba ya mata dukan mutuwa wannan fushin ya saka ya fasa qara kwanan da yayi niyya yace su tafi shi Ali daman harya fara cigiyar inda ze samu motar Kano yaga sun fito. Bashir na sallama da jama'ar sa Audu har ya shiga mazaunin Direba dan shi ze jasu saboda ciwon hannun Bashir sega Zubaida ta fito daga gidan taci kwalliya daurin nan kamar ze fadi saboda yanda ta tsikara shi hannu ta riqe da jaka madaidaiciya da zata ci kala a qalla Kala uku se qaranar jakar mata a daya hannun da alama wani gurin zataje kuma tafiyar kwana ce.

"Yar dagwas, an sauka daga sarautar kenan" Bashir ya fada yana kallonta, tayi far da ido, cikin yanga da iyayi tace

"Eh, ina kayi? Naga kamar tafiya zakayi ko?"

"Kano na nufa, kefa na ganki da jaka da alama balaguro zakiyi"

"Zan sauka a Zariya" ta fada tana wucewa motar, ta aje jakarta akan Boot ta wuce ta bude gaba ta shige kai kace motar tace. Bashir ne ya saka mata motar a Boot haka suka kamo hanya, duk yanda take daurewa seda ta biyesu ta shiga hirar, sun tsaya a hanya zasuyi sallah Audu ya samu damar yi mata magana shida ita.

"Kaga malam, nifa ba irin sauran masu Arhar da kuka saba tayawa bace" ta bashi amsa tana farfara ido ta wuce ta barshi a gurin yana murmushi kamar wawa. Dagaske sonta yake, irin soyayyar nan ma me zafi. Har qofar gidan da zataje suka sauketa a Zariya dukda tace su ajiyeta tun akan hanya.

"Nan ne sabuwar maboyar taki kenan? To sena rako Abokina" Bashir ya tsokaneta, ta harare shi kafin ta Audu tana taunar cingam qas qasa tace

"Nagode Samari, se wani jiqon"

"Shege Abokina wlh ka samu shiga, kasan uban nacin da nayi akan yarinyar nan kuwa amma taqi bani fuska? Kai bani kadai ba kowa mararinta yakeyi amma yarinyar nan yanda kasan kudi wahalar samu ne da ita, daga qusoahin gwamnati se Sarakuna take kulawa" Bashir ya fada yana dukan kafadar Audu.

Ali yaja tsaki yace

"Wlh kayiwa kanka fada karka kuskura ka bari shaidan ya maka ingiza me kantu nidai babu ruwana daga yau ma in sha Allah bazan sake binku fita irin wannan ba"

"Nifa na gaya maka sonta nakeyi dagaske" Audu ya fada bayan sun hau titi. Bashir ya ringa dariyar iskanci yana cewa

"A sannu dai duk zasu hau saiti, wato ina gaya muku dadin duniya a sha ruwa ga mata, kai Allah ka yafe mana kurakurenmu".

Haka har suka iso Kano.

Ba'a rufa sati ba ya kama hanyar Zariya ba tareda ya sanarwa da Abokanansa ba saboda yanda tunanin Zuby ya addabeshi, yaje gidan da suka ajiyeta wanda se sannan ya gane nan ma gidanmata masu zaman kansu ne, ya rasa ta inda ze fara nemanta. Har gurin Magajiyar gidan aka kaishi tace babu Zubaida a gidan haka ya haqura ya dawo Kano da qunar zuciya sedai duk yanda yayi akan ya yakiceta ya haqura da tunaninta abin yaci tura. Gaba daya ya shiga damuwa ya zaman har walwalarsa ta ragu. Da Binta ta matsa masa da tambaya se ya ce mata Asara yayi, aiko ta si ta fishi shiga tashin hankali ma dan Binta na son kudi, dukiyar Audu kuwa jinta take kamar tsokar jikinta a kullum zancenta Duk abinda yake dashi nata ne

tunda itace sila shiyasa take baqin ciki idan yayi Alkhairi wa wasu, ta bangarenta kuwa duk abinda take dashi ko take samu babu me ci, hatta a karan kanta mugunta takeyiwa kanta dan da wani ya mori abu tareda ita gara ta haqura da abun itama.

Wata biyu Audu ya kwashe yana dakon soyayyar Zuby, dayaga abin baze fita daga ransa ba tilas ya samu Bashir ya roqeshi akan ya nemo masa ita.

"Wlh sonta nake Bashir kuma da Aure" ya fadawa Bashir din.

"Amma dai Audu baka da hankali, to ai koni da nake cikakken dan Bariki iyakata da Karuwa na biya buqata ta mu rabu a gurin duk matan da suke yawo a garin nan ka rasa wa zuciyarka zata so se Karuwa? Hauka kake ko shaye shaye ka fara?" Bashir ya fada cikin madaukakin mamaki.

"Nidai idan zaka nemo mun ita kawai ka nemota Malam babu ruwanka ko Magajiya ce a hakan naji na gani kuma ina sonta in har ta amince kuma auranta zanyi" Audu ya bashi amsa cikin tsare gida. Bashir ya kunna sigarinsa yana zuga yace

"Babu shakka Haqqin Bara'atu ya fara dabaibayeka tun ba aje ko ina ba, ka saki yar gidan mutunchi me Cikakken Asali zaka maye gurbinta da Karuwa to Allah ya kyauta ka shirya gobe muje Zariyan, da kace musu Yar Dagwas da tuni an nemo maka ita sedai kuma idan suna ta canza a can dan halin matan Bariki ne basa amfani da sunansu na Ainihi.

Page 16

Kamar yanda Bashir ya fada suna isa suka tambayi yar dagwas se gasu a dakinta aka rakasu. Zubaidan na kwance kamar mara lafiya suka shiga, ta ringa kallonsu da mamaki dan bata gane Audu bama Bashir dai data fi waya shi ta gane.

"Lafiya? Tara ko bashi?" Ta fada cikin tsiwarsu irin ta yan Bariki bayan data miqe tsaye. Audu dai se binta yake da kallo Bashir yace

"Ai kya bamu gurin zama musha ruwa tukunna yar dagwas", tayi gatsine kafin ta dauki wani siririn mayafi ta yafa a kanta da babu dankwali ta fita tana tafiya a hankali.

"Duk yanda akayi dan Hau ta hadu dashi ya lakada mata na jaki shiyasa ka ganta haka" Bashir ya radawa Audu. Wani duumm yaji a zuciyarsa, shikam So be kyauta

masa ba ya rasa macen da ze zargo masa se yar bariki wadda jikinta bashida shamaki da Maza.

Zuby ta dawo da kwalabe uku a hannunta, biyu na Giya is Coca cola daya ta ajiye a gabansu.

"Ga naka nan wadannan nawa ne" Bashir ya fada yana tura masa Coke din. Seda ya zuqe kwalba guda kafin ya kalli Zubaida dake zaune daga gefe ta jingina tana kada qafa yace

"Tafiyar ta Aboki na ce, kwanaki ma yazo yayi ta bulayi ni ban ma san ya akayi yasan sunanki Zubaida ba yazo haka ya koma ba tareda ya sameki ba, bari na baku guri na dan nemi inda zan rage lokaci" ya fada yana miqewa da dayar kwalbar a hannunsa.

"Kaga jashi ku tafi ni ba lafiya ta isheni ba kuma ko qalau nake kasan tsadata ba haka nan ake fado mun ba kamar wata mara Aji" ta dakatar da Bashir din, se yayi murmushi yace

"Al'amarin da yake tafe dashi yafi wannan kedai ki saurareshi kawai" daga haka ya fita ya barsu.

Audu ya muskuta yana kallonta soyayyarta na qara huda zuciyarsa yace

"Bakida lafiya ne"

"Matsala aka samu nayi ciki, uban yace ze karba kuma naga kar daga baya yazo ya mun Akuya na zubar" ta fada masa kai tsaye kamar wadda ta aikata abin kirki, is ya kasa cewa komai ya zuba mata ido kawai zuciyarsa na bugawa.

Ina jinka fadi abinda ya kawoka dan kwanciya nake so nayi" ta sake fada tana gyara zama, zaman shima ya gyara ya fuskanceta dakyau kafin ya shiga zayyano mata abinda yake cikin zuciyarsa dan ya gaza dannewa,

"Kuma ni da Aure nake sonki, ina so ki bar wannan rayuwar ki koma gida gaban iyayenki wannan rayuwar bata dace da Mace kamarki ba, ki je kiyi Istibra'i zan aureki".

A duk maganganunsa fadar ta koma gida gaban iyayenta ne ya jefata a wani hali ya tado mata da tsohon mikin dake zuciyarta nan da nana hawaye suka wanke mata fuska. Kewar gidan da Mahaifanta ya taso mata se gani yayi ta hade kai da guiwa

tana kuka wiwi. Hankalinsa ya tashi da kukan da take ya kuma shiga mamakin me ya sakata kuka, shidai ba wa'azi yayi mata ba balle ace tsoron Allah ne ya ratsata kawai ya gaya mata yana sonta ne ze Aureta amma take wannan kukan kamar wadda zata mutu take.

"Ki dena kuka dan Allah" ya fada cikin rabewar murya.

"Ka tashi ka fita" ta bashi amsa cikin bada umarni. Ya tsaya amma tsaqar data buga masa tasa dole ya fita cike da mamakinta ya zauna a qofar dakin.

Zubaida kuwa tana kuka ta koma tunanin Baya, gida take tunuwa da mahaifiyarta tareda sauran yan uwanta da kuma dalilin daya fito da ita. Duk ranar da aka ambaci Iyaye ko Gida se tayi irin kukan nan, tana so ta sake ganin nata amma bata da hali. Kalaman Mahaifinta suka dawo mata sanda yake korarta daga gida.

"Ki tafi, idan kika sake waiwayarmu Allah ya isa iyakar abin kunyar da kika jamun ya isa ki tafi duk inda zakije Zubaida na yafeki daga cikin Yayana".

Cikin dare ya koreta, ba tareda yayi tunanin ina zataje ba wane hannu zata fada kuma ya gaya mata karta kuskura taje gurin danginsa kona mahaifiyarsu. Hatta da yan unguwa da suka tausaya mata suka so bata mafaka Tijara yayi musu yace ze hada duk wanda ya shigar masa hurumin gida da hukuma haka ya koreta se tasha taje ta samu mafaka duk akan dalilin Qaddarar data fada mata wadda shine sila. A dalilin kasa sauke nauyinsu da Allah ya dora masa na ciyarwa da sauran buqatu ya tilasta mahaifiyarta fara dora mata tallan shinkafa da wake tana kaiwa Bakin Kasuwa kuma a nan ne qaddara ta hauta wani Azzalumi yayi mata wayo yayi mata fyade, shekararta goma a sannan, ya gana mata Azabar data fitar da ita daga hayyacinta qarshe ta farka ta ganta a gidansu Kwance ga Mahaifiyarta na Kuka Mahaifinta kuma na Sababi kamar zeyi Aman wuta.

Yana ganin kuma ta farka be duba komai ba yace ta tashi ta fitar masa daga gida, a fadar sa daman an sha gaya masa ana ganinta a shagunan Maza, ko a sannan din be yarda Fyade akayi mata ba, a yanda wanda suka tsinto ta suka gaya masa wai ciki ta zubar, wanda ya bata maganin ya gudu se ita suka tsinto cikin Jini a wani kango. Babu dogon tunani babu komai Mahaifinta ya yanke wannan danyan hukunci na korarta a cikin dare. Beyi tsinkayen cewa a sannan ko Al'ada bata fara ba ballantana ace ta dauki ciki, yayi mata korar kare cikin rashin Imani, Mahaifiyarta da qannenta naji suna gani tabar gidan shekaru goma kenan kuma kamar yanda ya fada bata sake koda taka qafarta a qasar Kano ba da Asuba tabi wata mata Mai

siyar da Abinci a tasha daman ta santa idan ta kawo tallah tana gaisheta matar tasan abinda ya faru da Zubaidan dan haka data ganta cikin daren bata tambayi ba'asi ba kawai ta dauketa ta kaita dan dakinta na langa langa dake cikin Tashar. A nan ta gyarata tayi mata wanka ta kuma bata Abinci washe gari da Asuba suka hau mota suka bar Kano dan dama taga matar ta hada kayanta tsaf da alama zatayi Balaguro, bata tsinci kanta a ko ina ba se a Kwantagora, da fari Abinci suke siyarwa da giya a nan gidan daga matar ta ingizata zuwa ga wannan rayuwar da take nadama da dana sanin shigarta.

Takanyi kuka tace me yasa bata tsaya ba Babanta ya halakata tunda yace idan bata fita ba seya kasheta? Data sani ta zauna ya kashe ta ta mutu tun sannan qila da tana Aljanna abinta da wannan qazamar rayuwar data jefa kanta a ciki.

Audu na qofar dakin yana jiyo kukan ta daga ciki, kasa daurewa yayi ya koma ya tsaya akanta yana ganin yanda take kuka har jikinta na jijjiga.

"Dan girman Allah kiyi shiru, idanhar maganar so ko aure danayi miki ce ta sakaki wannan kukan na janye na haqura ke dena Kukan haka" ya fada cikin sigar lallashi. Bata bari ba, haka ya kai tsugunne ya ringa lallashinta da kalamai masu kwantar da hankali. Shida kansa yayi mamakin inda ya iyasu, be haqura ba har seda ta dena kukan tana ajiyar rai da jan majina.

"Kiyi tunani akan maganata" ya sake fada mata ba tareda ya sare ba.

"Ta yaya mutum kamarka me kamala, na fahimci ba halinka daya da Abokinka ba ya za'ayi kace zaka auri Karuwa kamata wadda bata da mutunchi ballantana daraja?" Ta fada hawaye na sake sakko mata.

Audu ya zauna da kyau ganin ta sakko tana so suyi magana yace

"Nima ban sani ba, amma na tabbatar qila Allah ne yaso dana zama silar fitar dake daga wannan rayuwar shiyasa ya doramun sonki. Sannan maganar Mutunchi ko Daraja, ban sanki ba bansan daga inda kika fito ba amma na tabbatar koma daga ina kike kin kasance Mace me Mutunchi da Daraja a baya, qaddara ce ta kawoki nan domin mata kadan ne suk shiga Bariki da son ransu, mafi aka sari Qaddara ce take afka musu wadda mutane suke kasa yi musu uzuri harsu ingizasu ga zuwa abinda yafi wanda ya same su a baya muni.

"Duk abinda dan Adam yake aikatawa muddin be mutu ba yana da damar shiriya ya nemi yafiyar ubangijinsa, kema lokaci be qure miki ba. Ki bar wannan rayuwar da babu komai cikinta se qasqanci, ki koma gida wlh da gaske nakeyi zan aureki bada wasa nake sonki ba".

"Mahaifina ya koreni, yace karna sake komawa gidansa idan har naje be yafe mun ba. Ina so naje, ina kewar mahaifiyata amma bana son na sake shiga wani fushin nasa akan wanda nake ciki" ta fada cikin sauti me ban tausayi.

"Ke din yar wane gari ce? Kuma meya fito dake daga gida?" Audu ya tambayeta. Bata boye masa komai ba na daga labarin rayuwarta ta gaya masa gaskiya, yaji tausayinta kwarai dagaske ya kuma ga baiken Mahaifinta. Irin wannan qaddarar ta fadawa mata da yawa, idan da ace iyaye suna taya Yayansu karban qaddararsu a yanda tazo musu da an samu raguwar masu fantsama Bariki. Da yawan iyaye Sukan manta cewar Abin kunyar da suke tunqahon yayan sun jawo musu har yasa suka kada su duniya kadan ne akan rayuwar da suke jefasu suyi, ga dakon zunubi domin duk abinda suka aikata na barna tare za'a raba musu Sakamakon da iyayen saboda sune suka turasu zuwa ga barnar. A tunanisa da a ringa zunden mutum ana cewa yarsa ta zama Karuwa gara a kira shi uban wadda aka tabayiwa Fyade ko tayi cikin shege ya barta a gabansa ta shiryu har ya aurar da ita wannan haqurin da mutum yayi se ubangiji ya dubeshi ya shirya masa zuri'a amma korar yara akan wata qaddara mara kyau ba daidai bane, su kansu Iyayen sunyi bankwana da kwanciyar hankali daga ranar da suka kori Yayan nasu basa sake samun nutsuwa.

Audu basuje Zariya da niyar kwana ba amma Alamun cin galaba akan Zubaida daya gani ya sakashi kwana a garin. Yayi mata alqawarin ze nemo mata mahaifinta muddin yana raye ze hada su kuma koya mutu ze maida ita gida gurin ragowar yan uwanta. Ya roqeta akan ta shirya su tafi Kano tare, ze bata mafaka har zuwa sanda zata daidaita da iyayenta amma taqi, tace dai yaje ba zata dawo idan har mahaifinta ya mata izini.

Haka washe gari suka dawo Kano gaba daya Audu bashi da kuzari, Bashir nata yi masa shaqiyanci da cewar shima ya zama dan hannu dan tunda suka rabu basu hadu ba seda safe da zasu wuce Kano dan haka besan duk abinda ya faru tsakaninsa da Zubaida ba.

A gida ya tarar da Binta cikin yanayi na neman tashin hankali dan yana shiga tambayar data fara jefa masa itace

"Daga gidan uban wa kake?"

A lokacin yanayin sanyin jiki da kuma martabar mahaifinta da ya wuce ya zageshi ya saka ya qi tanka maka amma kaitsaye zuciyarsa ta ringa raya masa ya gaya mata daga gidan ubanta yake ko da abinda zatayi akai. Bata haqura ba ta bishi har daki tana ihu da hargagi tareda fadar maganganu. Baturiya matar Ali ce ta gaya mata Audun sun tafi wani gari gurin Mata tareda Bashir itama tsintar zancen tayi a gurin Mijinta yana gayawa wani Abokinsa daya je gidan shine ta wanke qafa ta tafi gidan Binta ta gaya mata ranar bata iya runtsawa ba a tsaye ta kwana tana jiran taga ta inda ze bullo amma be dawo na se yanzun.

Duk kalar rashin mutunchin data ringa zazzagawa be tanka mata ba ya shige daki ya kullo qofa ya shiga wanka. A ranar yake so yaje ya fara binciken iyayen Zubaida data gaya masa ita din haifaffiyar unguwar Alkantara ce, sanda ya fito Binta ta sauka daga saman harya fita kuma beji motsinta ba ya dauki mota ya bi kwatancen da Zubaida tayi masa besha wahala ba saboda sunan Mahaifinta data gaya masa Malam Hassan Na'ibi yana fada aka kaishi har qofar gidan lokacin qarfe biyar na yamma rana tayi sanyi a qofar gidan ya tarar da Malam Hassan din da wasu dattijai guda biyu kan tabarma suna hira.

Ya ringa kallon mutumin, kamanninsa daya da Zubaidar, sedai yanayinsa ya nuna kamar bashi da lafiya saboda a kishingide ma yake be iya zama sosai. Audu ya qarasa kan tabarmar ya zauna suka gaisa duk suna masa kallon rashin sani.

"Gurinka nazo Baba, idan babu damuwa ina so zamuyi magana ne" ya fada yana kallon Malam Hassan ganin haka ya saka ragowar suka gane baqonsa ne.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

"To ai babu damuwa samari ina jinka ka fadi abinda yake tafe da kai wadannan ba baqi bane Aminaina ne koma menene yake tafe da kai ka fada suji" Malam Hassan ya fada. Audu ya kalli mutanen da ya kira da Aminansa kafin ya sunkuyar da kai, bashida tabbacin basa cikin wadanda suka zugashi harta kori yarsa tunda yace Aminansa ne su dan haka baze fadi maganar a gabansu ba balle su hanashi karbarta. Qara qasa da kai yayi yace

"Kayi haquri Baba amma daka daure munje gefe dan maganar da take tafe dani dakai kadai zan iya tattaunata"

"Ka je mana Malam kaji abinda yake tafe dashi" daya daga cikinsu ya fada, Malam Hassan yayi shiru yana kallon Audu kafin ya yunqura ya janyo sandarsa dake gefe ya tashi, Audu ma ya miqe yabi bayansa yana kallon yanda yake tafiya a gicciye tamkar wanda ya taba samun ciwon mutuwar barin jiki". A soron gidan suka tsaya, Malam din ya kwalawa wata yarinya me suna Surayya kira ta fito da sauri, kamarsu daya da Zubaida dan seda gaban Audu ya fadi daya ganta.

"Kawo mun kujerata" ya fada mata ta amsa da "toh Baba" kafin ta juya babu dadewa ta dawo da kujera me qafafu hudu irin ta qarfen nan doguwa Malam din ya dogara ya zauna akai yana nunaqa Audu wani tudu me kama da Dakali dake cikin zauren amma da Qaton dutse akayi shi. Audu ya zauna yana fuskantar Malam din.

"Ina jinka samari, meke tafe da kai?"

"Kayi haquri da abinda nazo maka dashi Baba sannan ina fata ka fahimce ni"

"Ka tafi kanka tsaye bana son wannan alayen me yasa kake son magana dani?"

"Akan Zubaida ne" Audu ya fada yana kallon Malam din dan ganin yanda zeyi reacting aikuwa ya zabura tamkar ze fado daga kan kujerar Audu ya tare shi. Jikin Malam Hassan ya dauki rawa ya qanqame Audu yana cewa

"Zubaida naji kace? Ina ka ganta? Kasan Zubaidata? Dan Allah tana ina daman tana tana raye?" Malam din ya fada cikin rawar baki tareda daga sauti abinda ya fito da yarinyar dazun da gudu kenan tana tambayar

"Baba lafiya?"

"Sunan Yayarku ya ambata, dan girman Allah ka gaya mun a ina kasan Zubaida tana ina?" Malam din ya sake fada babu tsammani se ganin hawaye yayi a fuskar Malam tamkar yanda Surayya ta fashe da kuka itama tana ce masa

"Ina Yayarmu? Dan Allah ka gaya mana a ina ka santa?"

"Kayi haquri Baba zan gaya muku amma se ka nutsu ka dena daga murya karka janyo hankalin mutanen waje" Audu ya fada yana zaunar da Malam din a kan Kujerar daya tashi.

"Muje ciki Samari wannan maganar bata zau bace muje ka sanar mun inda kaga Zubaida" Malam ya fada yana miqewa, Surayya ta dauki kujerar jikinta na rawa suka shige ciki Audu ya mara musu baya.

"Tausayin Malam da Surayya ya rufeshi ganin yanda suke kuka tamkar ransu ze fita bayan daya gama basu labarin inda ya hadu da Zubaida.

"Allah ka yafe mun, wlh sharrin shaidan ne da zuciya ya ingizani na kori yarinyar nan. A sanadiyyar haka abubuwa da yawa sun faru. Baqin cikin rashinta ya saka mahaifiyarsu kwanciya jinyar da har tayi Ajalinta nima kuma na gamu da hawan jini har mutuwar Barin jiki na samu seda na shekara biyu ina jinya bayan rasuwar Habiba kafin Allah ya bani lafiya, wallahi nayi nadamar abinda na aikata babu inda kuma ban shiga ba a garin nan ina cigiyar Zubaida, har gidajen Mata masu zaman kansun na ringa zuwa ko Allah ze saka na samu wanda ya ganta amma ba'a dace ba se daga baya wani bawan Allah ya sanar mana wata Mata ce ta tafi da ita amma besan motar garin da suka hau ba. Tu daga nan na fawwalawa Allah na ke kuma Addu'ar idan har Zubaida tana raye Allah ya gama fuskokinmu kafin na koma gareshi kona nemi yafiyarta, dan Allah Samari tana ina? Ka kaini naga yata karna mutu da haqqinta a wuyana" Malam ya fada yana sake rushewa da kuka.

"Kayi haquri ka kuma kwantar da hankalinka Baba, naso ace mun taho tare da ita amma taqi tace ba zata dawo Kano ba se idan har kai da kanka kace ta dawo dan bata so ta sake shiga wani fushin naka amma yanzu tunda anyi haka zan koma Zariya gobe idan Allah ya yarda a gidan nan Zubaida zata kwana" da wannan Audu yayi musu sallama tamkar Malam Hassan ze bishi haka ya ringaji, bayan ya fito daga gidan su Zubaida harya dauki hanyar gida ya fasa kaitsaye ya wuce gidan Mai. Full tank yayi, a nan ya tsaya yayi magriba ya dan ci abinci dan rabonsa da abincin kirki tun safiyar jiya kafin su tafi Zariya.

Musbahu ya dauka, Dan Yaya Baba ne daya dakko ya sakashi a gidan Mai yace yazo ya rakashi a daren ya dauki hanyar Zariya. Musbahu ya ringa zare ido ganin inda sukaje, to me ya kawo su nan kuma. Zubaida na bacci taji bugun qofa ta tashi ta bude mamaki ya cikata ganin Audu.

"Dama baka tafi ba?" Ta tambayeshi, ya kalli Musbahu kafin ya kalleta yace

"Ki hada kayanki Asubanci zamuyi na je na samu Baba kuma ya yarda ki dawo gida"

"Qaryane, yaushe kaje Kano har ka dawo nan?" Ta fada tana kama qugu, yayi gaba yana ce mata

"Qanwarki Surayya ta girma kamanninku daya tamkar Tagwaye"

"Innalillahi dagaske kaje gidanmu, kaha Innata me tace maka?" Ta fada tana fashewa da kuka tareda bin bayansa da sauri seya dakata yace

"Kije ki hada kayanki, mahaifinki na cike da zumudin ganinki na tabbatar yau baze iya bacci ba".

Washe garin kuwa Asubanci sukayi, shidai Musbahu bakinsa fal da tambayoyi amma babu me bashi amsa. Har qofar gidan Malam Hassan ya isa da mota, tun daga nesa ya hangoshi zaune kan kujerarsa ya rafka tagumi gefe Aminan sa na jiya na tsaitsaye.

"Ina ga shine wancan" daya ya fada yana nuna motar dake tun karo su, Malam Hassan ya miqe jiki na karkarwa, Zubaida ta fashe da kuka ganin da gaske Mahaifinta ne tsaye qofar gida yanayinsa kuma ya nuna ita yake jira.

Audu kasa jure wannan yanayi na haduwar Uba da Ya yayi bayan wasu shekaru, be ko yi mata sallama ba yaja mota suka tafi.

"Wlh idan naji zancen nan a bakin wani nida kai ne" ya fadawa Musbahu sanda ya sauke shi a Gidan Mai.

Gida ya wuce, yayi tsammanin tarar da yaqi saboda fita daya sakeyi ya kwana amma se yaga akasin haka. Bintan bata nuna damuwa kamar jiya ba daya shiga wanka ya fito ya tarar ta shirya masa abinci ya zauna kuwa ya nadi abinsa dan a yunwace yake yana ci amma zuciyarsa da kwakwalwarsa suna kan Zubaida ko me takeyi oho.

Binta kuwa abinda ya faru jiya bayan ya shiga wanka fita tayi ta tafu gidan Baturiya.

"Bari kiji, duk matar da kikaga ta isa to wayo, dabara, kissa da kisisinarta ya kaita. Karki bata wayonki a gurinsa bayan kin rigada kin fara kafa gwamnatinki. Wannan ihu da hayagagar baze saka ya fasa abinda yayi niyya ba amma cikin salo da dabara se kiga kin rabashi da koma wacece dan haka ki koma gida ki bashi haquri da sannu ki gano bakin zaren sannan muyi qoqarin daukar mataki, sannan banda abinki ai da kishiyar gida gara ta waje. Kinsan duk Namijin daya saba zama da Mace biyu ma wuyaci ne ya iya haquri da daya dan haka in har ba so kikeyi ya aurota ya kawo miki ku zauna tare ba ki rabu dashi yayi sabgar gabansa" abinda Baturiya ta

gaya mata kenan shiyasa ta dawo gida amma fa a zuciyarta bata jin zata iya jurewa kamar yanda tace mata amma zata gwada dauke kai dan kamar yanda Baturiyar ta fada tabbas da Kishiyar gida gara ta wajen.

Kusan sati daya da dawowar Zubaida gidansu kafin Audu ya sake zuwa, har cikin gida Malam Hassan ya saka ya shiga.

"Nayi ta neman inda zan zameka ashe itama ko sunanka bata sani ba, Yaro na gode, yanda kayi mun wannan Alfarmar ina fatan ubangiji ya jibanci lamarinka ya rabaka da iyayenka lafiya, nagode kwarai daka maidomun da Zubaida gabana, nagode daka zama silar barinta rayuwar barna" Malam Hassan ya fada daga nan ya basu guri shida Zubaidan dayaga tayi wani sanyi qalau tamkar ba ita ba.

"Nagode da abinda kayi mun Allah ya biya maka buqatunka na Alkhairi" tace daga nan sukayi shiru kamar kowannensu ya rasa abin fadi shi ya gaji da shirun yace mata

"Ina fatan abinda ya faru a baya ze wuce, ki cire komai daga ranki ki faro sabuwar rayuwa. Abinda ya faru qaddararki ce kuma Imanin mumini baya cika har se ya yarda da qaddara me kyau ko mara kyau sannan, ina fatan hakan ya zame miki kaffara. Sannan kuma ina nan akan bakana na neman yardarki, ina so da zarar kin kammala Istibra'i za'a daura mana Aure"

"Kayi haquri bana zaton na dace da nagartaccen Namiji kamarka, nagode da abinda kayi mun kuma in Allah ya yarda zan yita yi maka Addu'a Allah ya baka mace daidai da kai" ta fada cikin sanyin jiki. Babanta na cikin daki yana jiyosu yayi gyaran murya yana cewa

"Wannan wace irin maganace Zubaida, kana jina ko Yaro kaje in Allah ya yarda bata da wani Miji idan ba kai ba. Banda rashin wayo ki samu miji kamarsa har ki tsaya kinibibi ai yafiki sanin abinda ya dace dashi din kuma yace ke yake so"

"Shikenan Baba nagode, in sha Allahu kuma zan turo da magabata na e a tsaida magana".

Watanni uku bayan dawowar Zubaida gida, a hankali tun tana sharewa harta yarda ta sakarwa Audu fuska soyayya me sanyi ta qullu tsakaninsu, dukda tana matuqar jin kunyarsa kasancewar yasan komai na rayuwarta ta baya, ta kanga kamar wata

rana ze goranta mata bama shi ba babban damuwarta yan uwansa take zaton ya zasu dauketa idan har sukaji ita din wacece a baya gashi yace mata yana da mata ire iren wadannan tunanin yake sare mata guiwa taji kamar ma Auranta da Audun baze yuwu ba. Watanninsu hudu tare Malam Hassan yace ya turo magabatansa saboda yana so ya hada da Auran Surayya ayi gaba daya, su uku suka rage cikin yaya shiga da mahaifiyarsu ta haifa ukun sun rasu suma bayan rasuwar Mahaifiyar tasu se Surayya da Ibrahim Wanda yake bin Zubaida ne suka rage masa be kuma sake Aure ba tun rasuwar Habiba shekara bakwai kenan.

Babu damuwar komai Kai tsaye Audu ya tafi Bechi ya samu Yaya Baba ya gaya masa cewar zasuje nema masa Aure nan da sati daya, mamaki ya kama Yaya Baba saboda Yakubu yaje Bechi ba'afi sati daya da tafiyarsa ba kuma beyi musu zancen Auran Audu ba dukda yaga alamar kamar Audun ma be san yaje din ba, tun rabuwar Auransa da Bara'atu abubuwa sukayi zafi tsakaninsa da Yakubu.

Yakubun Yayi fushi me tsanani shi kuma Izza da ganin yanzu ya isa ya hanashi ya neme shi su sulhunta. Yaya Baba bashida ta cewa dan haka ya amsa masa da Toh, ya kuma sanarwa da sauran yan uwansu abinda ake ciki take Hashimu yace ba zashi ba. Aminu ya samu Audu ya tambayeshi Yakubu yasan da magabar kuwa yace masa Aa.

"Wannan abinda kukeyi sam be kamata ba, kaine qarami dan haka ka nemeshi ku sasanta. Me yasa kakeyin tufka kana warwara? Kayi nasarar hade kanmu sannan kuma ka koma ka bata da Yayanka da kuke ciki daya akan Mace wannan wane irin abu ne?"

"To ni Aminu menene laifina a ciki, Shi ya fiya damuwa ne kawai idan ba haka ba menene nayin fushi akan na rabu da Bara'atu nifa nake zaune da ita ni nasan matsalarta amma shi ne da fushi dan na saketa?"

"Saboda yafika hango abinda yake daidai ne shi yasa kai kanka kuma da zakayi duba na tsanaki zaka gane abinda ake qoqarin fahimtar da kai. Da ace zaka ji shawara da ka haqura da sabon Auran nan ka maida Bara'atu dakinta" Aminu ya sake fada. Audu yayi shiru kafin ya kalle shi yace

"To kai ka aureta mana ko kuma shi din ya aureta tunda kun fini sanin darajarta".

Badan Audu yaso ba sedan Yaya Baba dayace muddin ba sanarwa da Yakubu ba bazasuje masa neman Aure ba tilas ya kirashi ta wayar Landilayin wadda ya hada a gidansa shima kuma Yakubun suna da ita a Ofishin da yake aiki dan haka ya kirashi.

"Allah ya sanya Alkhairi yasa ayi a sa'a" abinda Yakubun ya fada masa kenan bayan daya shaida masa zancen Auran se kuma yaji babu dadi dan haka yace masa

"Amma zaka zo ko? Saboda ina tunanin a daura Auran kawai idan an kai kudin"

"Ina da Ayyuka da yawa a gabana bana jin zan samu halarta sedai daga baya nazo naga Amarya amma a ina ka samo matar?" Yakubu ya tambayeshi, Audu yayi shiru kamar mara gaskiya kafin yace

"Amm yar nan cikin gari ce unguwar Alkantara, yarinyar nada hankali da nutsuwa sosai se ka ganta ma"

"Amma da zan baka shawara ka dauka da nace kayi haquri ka maido da Bara'atu kodan darajar yayanta ka dubi rayuwar da zasuyi a Bechi babu wadataccen Ilimin Islamiyy ada Boko"

"To ya kake so nayi da wannan din bayan na sanarwa da Iyayenta zan turo so kake na zama qaramin mutum?" Audu ya fada a dake dan ya gaji da maganar ya maido Bara'atu da suka dameshi da ita, Yakubu yayi murmushi yace

"Bance ka fasa ba kana iya hadasu su ukun ai Alhamdulillahi Allah ya hore maka abinda zaka iya riqe su nidai yaranka nake dubawa saboda zuwan nan da nayi na gansu banji dadin yanda suka koma ba gashi sun fara tasawa"

"Naga muma a Bechin nan aka haifemu muka girma, yanzu kai bada shekarunka ba harda Aure ka kammala sakandire ka tafi Jami'a? Suma idan sun girma sun kai munzalin da zasu iya wahaltawa kansu se su dawo nan gidan su zauna yanzu dai ba wannan maganar mukeyi ba ka daure dan Allah kazo kasan dai nan duniya bani da kamarka" Audu ya fada. Yakubu yayi dariyar takaici yace

"Zanyi maka Addu'a daga nan kuma da ace abinda ka fada da gaske be baka da kamata da baka qi karbar shawarata ba muddin ba cutar da kai nayi niyya ba, yanzu ina aiki ne zamu sake magana idan na samu lokaci" daga haka ya ajiye waya ya bar Audu sororo da waya a hannu seda ya kashe ma sannan ya tuna dayar maganar da yake so ya masa ta jin dalilin daya saka ya dauki Baballiya ya tafi da shi Lagos zeyi hutu ba tareda su. Sanar masa ba seda sukayi magana da Alhaji Zakariyya yake gaya masa dan a gidan Baballiyan yake zama idan sun samu hutu yanzu haka yana ma yana shekararsa ta qarshe shirye shiryen fita sukeyi.

Duk yanda Audu yayi da Yakubu akan yazo Auransa qi yayi dole ya haqura badan yaso ba kuma har ransa yaji rashin jin dadin hakan saboda bashi da tamkar Yakubu sannan ya rasa abinda yasa Yakubu ya dauki wannan fushin dashi. Yanzu kenan yana so ya nuna Bara'atu ta fishi a gurinsa kenan?

Haka nan ya tura su Yaya Baba da wasu Abokananansa sukaje masa neman Auran wanda ba'a tashi daga gurin ba seda aka daura shi. Yana gida ranar be fita ba yana tsammatar dawowarsu Binta natayi masa gwalgwaso ta aje wannan ta kawar da wancan surutu kuwa har kunnensa ya gaji ga babu halin yace tayi shiru ko ta fita ta barshi ya huta.

Lantana ce ta kwankwasa musu qofar saman, rawar kan matar ya zarce misali seda Binta ta taka mata burki sannan ta dena zirgillin shigar mata turakar Miji. Bintan ce ta bude qofar ta leqa fuska a hade tana cewa

"Meye? Wai sau nawa zanja kunnenki akan tako benen nan ballantana kiyi tunanin shiga dakin nan? Ke wace irin daqiqiyar mace ce ne Lantana?"

"Kiyi haquri Hajia, baqi kukayi shine nace bari nazo na sanar miki" Lantana ta fada cikin qasqantar da kai amma a ranta zagin Binta takeyi.

Binta ta yatsina fuska tace "Baqi kuma daga ina? Ni yau babu wanda babu wanda nayi da ita zatazo"

"Ai Hajiya Maza ne ba mata ba kuma kamar yan Uwan Alhaji ne dan naga wasu suna yanayi dashi"

Tsaki me qarfi Binta taja, ta tsani wannan zaryar maukar da yan uwan Audu suke musu. Ba'a rufa sati se wani yazo daga Bechi badan ta taka burki bama har kwana

suke so su ringayi amma duk zatayi maganinsu dan ba zata dauki wannan abun ba suzo su dabaibayeshi su cinye musu dukiya to bada ita ba. Ciki ta juya ba tareda tacewa Lantana komai ba, Audu na kwance kan kujera tace

"Kayi baqi"

Da gaggawa ya miqe kamar wani mara gaskiya, be ko tambayeta su waye ba ya shige daki ya zuro rigar wandon jikinsa ya sauka qasan seta bishi da sauri dan se anyi komai a gabanta. Haka take duk sanda yan uwansa suka zo seta kasa ta tsare komai zasu fada ko ya basu seta gani idan akayi dace kuwa saqo ya biyo ta hannunta daman se abinda mutum ya gani. Qannensa Mata dai da suke ciki daya tun fitar Bara'atu babu wadda ta sake taka qafarta gidan se yan dakin Goggo Maryo ne suke zaryar zuwa ko gajiya basayi da wulaqancin Binta dan Mazan sun fisu kamewa da wadatar zuci muddin sukaje to dole ce ta saka ko kuma maganar Gonarsa wadda Aminu da Yaya Baba ne suke kula masa dasu yanzu.

Bayan Audu ya sauka qasa a tsakar gida ya tarar da Baqin nasa a tsaitsaye.

"Bismilla muje can falon" ya fada yana musu jagora zuwa falon da Bara'atu ta fita can ya gyara ya saka kujeru yake sauke baqinsa amma haka Binta zata bisu har can din. Suna zama tana shiga ko gyale bata yafo ba ta dirirce ganin harda Yaya Baba ko babu komai shidin babbane a cikinsu yanayin rayuwa yasa take ganin kamar ma ze girmin Dadynta dan wahala tasa tsufa ya masa sammako banda yanzu da Al'amura suka fara daidaitar musu ya dawo hayyacinsa dalilin Alkhairan da yake samu daga kula da Gonar da yakewa Audu amma da kam anji jiki ga tarin iyali ga Abinda suka Dogara dashi na Noma Hashimu ya ringa Ha'intarsu yana Azurta kansa su da wahala amma shine cikin walwala da jin dadi wannan ya saka suka yada makaman yaqinsu suka rungumi su Audun hannu bibbiyu gashi kuwa suna sharbar romon damakaradiyya har ya sauke farali a dalilin hakan.

"Au kune sannunku da zuwa ina wuninku?" ta fada tana jada baya tareda sunne kai, suka amsa mata a tare, ta tsaya daga qofa bata fita ba bata shoga ciki sosai ba Audu ya kalleta yace

"Kawo musu ruwa mana"

"Ayyo toh, bari a kawo" ta fada ta juya tana dannan masa Ashar a ranta. Mairo ta kwalawa kira ta gaya mata ta kawo ruwa tayi sauri ta koma bakin qofar ta labe.

"Munje kuma Babanta ya sanar mana da daman kun gama magana shiyasa bamuyi gardama ba dayace a Daura auran, to Alhamdulillahi anyi komai kamar yanda

shari'a ta koyar yanzu ya rage kuma ka saka ranar da matarka zata tare, Allah ya sanya Alkhairi ya sa Abokiyar arziqi ce" Yaya Baba ya fada.

Ihun da Binta ta fasa ya hanshi yin magana se ya miqe da sauri ya fita suka rufo masa baya kowa da tunanin abind aya sameta, tana tsaye ta dora hannuwa biyu a kai, ganinsu yasa ta qara fashewa da ihu me firgitarwa da tayar da hankali har tana dira qafafu kamar qaramar yarinya.

"Lafiyarki? Meya sameki? Ko kunama ce ta harbrki?" Audu ya jera mata tambayoyin cikin rikicewa yana qoqarin riqeta amma taqi tsayawa, ihu take tsalawa duk qarfinta kuma taqi magana haka nan bata dena dire diren ba.

"Kodai shafar jinnu ne tana dasu?" Yaya Baba ya tambaya yana ja baya, takaici ya qume Audu na abinda takeyi ya juya yana ce musu

"Muje dan Allah lafiyarta qalau wulaqancine da rashin son a zauna lafiya ya sakata haka" seta ruqo rigarsa ta baya cikin gunjin kuka tace

"Wlh baka isa, idanna yarda shegiya uwata ta haifeni aure? Aure fa naji suna zancen an daura maka ni zaka munafunta kayi mun kishiya da kudin ubana har yaushe ka nemi auran ban sani ba? Na rantse da Allah kayi kadan" ta fada tana cukuikuye masa riga, bayaninta ya fahimtar dasu dalilin kukan, Yaya Babba ya baza riga yace

"To mu bari mu wuce dan me motar daya kawomu yana waje dama yana jiranmu, Allah ya zaunar lafiya ya kade fitina idan an tsaida ranar Biki ka sanar mana mu shirya a can ai za'a kai Amaryar kamar wannan itama ko?" Ya qarasa yana nuna Binta.

"Ku koma ciki Yaya bamu gama magana ba ke kuma sakeni" ya fada yana qoqarim banbare hannunta daga rigarsa amma ta qara riqewa tam tana qara tabbata masa idan ta sake shi shegiya take.

"Kaga ka kashe wannan wutar tukunna bari muje Allah ya rufa Asiri" daga haka suka fice suna waiwayen Binta dake ihu tana qara maimaitawa Audu be isa ya mata kishiya da kudin ubanta ba.

Mari me kyau ya kwasa mata bayan fitarsu daya saka ta sakeshi babu shiri. Ya nuna ta da yatsa yana cewa

"Kinyi na farko kinyo na qarshe ni ba sakarai bane da zaki cimun kwala a gaban mutane, Aure kuma nayi, ba'a qaro mata ke na Auroki ko ba wata kika tarar a gidan ba? To ki kiyayeni wlh" yana gama fadar haka fuuuu ya wuce cikin gida ya barta a tsaye taba sharbar kuka.

A haukace ta zari mayafi tabar gidan bata ko dauki Zakariyya ba ta tafi gidan Turai can ta tarar da ita a wani birkitaccen yanayi dan itama gyale ne a hannunta da alama fita zatayi qiris ya rage suci karo kowacce taja baya. Binta ta fashe da sabon kuka tana shigewa cikin falon Turai tabi bayanta tana cewa

"Gidanki zani"

"Ai gani nazo, Turai ni Audu ze wulaqanta a duniyar nan ni ya tozarta yayi mun kishiya ban sani ba da kudin ubana?"

"Danqari, Binta amma Audu ya shammace mu kuma wlh ko a bakin Ali banji zancen auran nan ba se yau, to ya akayi haka? Kin ma san wadda ya aura wai?" Turai ta fada cikin Tashin hankali. Binta na sharar hawaye da Majina tace

"Ina na sani, badan nabi bayansa bama da yan uwansa sukazo da qila sedai naji ana gafara za'a shigo da Amarya ki taimaka mun Turai ya zanyi? Wlh bazan dauki wannan wulaqancin ba Audu be isa ya tozartani a duniya ba yayi kadan har marina fa yayi yanzun me kike tsammanin zeyi mun idan matar ta shigo".

"Uhm Binta kenan, nifa Auran Audu bashi ya daga mun hankali ba kamar wadda ya auro din, Kilaki fa ya kwaso miki a matsayin kishiya, idan har Auran nan ya tabbata ai kin gama yawo Binta wlh kashinki ya bushe kishi da Karuwa"

Sakare Binta tayi kukan ya tsaya mata kamar anyi ruwa an dauke kafin ta lailayo wata Ashariya me maiqo ta maka tana cewa

"Kilaki? Ni aka aurowa karuwa a matsayin kishiya? Ashe barinkin Audu har tayi qaurin da ze auro Karuwa ya kawo cikin gidana? Lallai kuwa be siyo zaman lafiya ba ze kuma san ya tsokana tsuliyar Dodo, na rantse da Allah daga ita harshi se sun gane kurensu, zasu san ni Binta ba kanwar lasa bace" yeeyeyey ta cigaba da kuka.

Turai ta sauke tagumi tareda yin Ajiyar zuciya me qarfi tace

"Qawata wannan Al'amarin fa ya zarce yanda kike tsammani, duk fa iya kissa da manaqisarmu bamu isa mu kama qafar matan bariki ba. Ke iya qoqarinda tayi har ya Aureta ai kinsan ba qaramar kai bace wannan tararta se anyi babban shiri" ta matsa kusada Bi ta dake kuka ta dafata taci gaba da cewa

"Kina ji qawata, yanzu dai tunda me afkuwa ta rigada ta afku mataki biyu ne zamu iya dauka a kai,ta siyasa zamu bullowa abun kuma ba mu zamuyi yaqin da kanmu ba, na tabbata yan uwansa basu san waya aura ba dan haka farke mata laya zamuyi duk wanda ya isa ya fada aji a danginsa ki sameshi ki gaya masa wacce Audun ya auro sannan ki sanar da iyayenki abinda ake ciki da kuma abinda ya miki ki qara maggi da gishiri ke kice dukan mutuwa ya miki ma sannan na biyu dole mu binciko ko wacece mu bi ta qarqashin qasa mu watsa auran tun a waje babu yanda za'ayi ta tare a gidanki" Turai ta fada. Haka suka ci gaba da kitsa yanda za'ayi har dare Binta na gidan kafin ta koma wujiga wujiga fuska ta kode saboda kuka ido yayi luhu luhu. Ranar bata ko kalli qafar benen Audu ba, cikin daren ta hada kaya daman Turai ta shirya mata direban da ze kaita Kaduna ai kuwa washe gari Asubar Fari tana jin Audu ya dawo daga masallaci ta dauki Jakar kayanta ta saba Zakariyya a baya ta fice.

Can inda sukayi da Direban ze tsaya taje ai kuwa ta tarar dashi babu bata lokaci suka yanki hanya se Kaduna. Yanda ta wuni ta kwana da yunwa ga tashin hankalin da take ciki ya saka duk ta fita hayyacinta, inda Audu ya mareta yayi shati abinka da fuskar Ajebo, saboda iya sharri har kanta ta buga a bango yayi quli ta karci wasu gurare a jikinta da farce saboda ita kadai tasan meta shirya zata fada idan taje gida.

A Makeken compound dinsu ta kwanta tana malelekuwa wai ba zata iya takawa ba bayan isarsu, Direban kansa bude baki yayi tsabar mamakin kaidin wannan matar. Qalau suka taho da qafafunta sau biyu suna tsayawa a hanya harta fita tayi uzurinta amma shine da zuwansu zatace bata iya tafiya lallai mata ababen tsorone.

Mamansu na Kitchen tana bada umarnin abinda za'a girka na rana ta jiyo ihu da kururuwa a waje babu shiri ta fita tayi tozali da Binta kwance a qasa tana wannan ihu qurjinta ya buga, abinda ya fara zuwar mata shine mutuwa akayi dan haka jiki na rawa ta qarasa ta kamata.

"Na shiga uku na lalace Mama wayyo Allah na" abinda take ta fada kenan sanda Maman suka shigar da ita ciki da taimakon Munira qanwarta. A falo suka barta ta sake kwanciya qasa har wani numfashi take ja tamkar wadda ake zarar ranta.

"Dan Allah kiyi shiru kimun bayanin meya faru Binta, karkisa ka zuciyata ta buga ki gaya mun meya samu Mijin nako" Maman ta fada cikin tashin hankali.

"Meyake faruwa haka? Ke Mamana menene? Accident kukayi ko wanine ya mutu acan?" Alhaji Zakariyya daya taso daga bacci dalilin kuwwar Binta data isa ko ina a gidan ya fada yana isa gareta, ganinsa yasa ta qara rikicewa ta shiga qoqarin miqewa tana miqa masa hannu ya riqota jikinsa har rawa yake saboda tashin hankali

"Kiyi magana Binta, zakici ubanki wlh idan baki mana shiru kin fada mana abinda ya faru ba" Mama ta fada cikin tashin hankali ta jimqe hannayenta da suke fitar da zufar fargaba.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh Iallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

Dakyar ta iya nutsuwa dukda ba sosai ba ta shiga kora musu qaryar data tsara ta haddace dangane da Auran da Audu yayi ba tareda saninta ba kuma akan ta masa magana yayi mata dukan kawo wuqa dakyar ta kwaci kanta shine ta gudo. Yanda ta tsara labarin babu wanda ya isa ya qaryata ta musamman ga shaida nan jikinta ya nuna. Mamaki madaukaki ya kama iyayenta musamman Alhaji daya ringa dubanta kamar me son ya tabbatar da dagaske take ko qarya takeyi.

"Wlh bazan koma ba, sedai ya zaba koni ko ita haka kawai bazanje su shafamun cuta ba kuma idan ya zabi zama da ita Dady ka gaya masa ya maido maka da duk wata dukiya daya samu ta dalilinka ai daman saboda ni ne kuma idan ya sakeni dole ya bayar tunda bata ubansa bace" Binta ta fada cikin gunjin kuka. Alhaji Zakariyya ya wuce bangarensa ba tareda yace mata qala ba ya kasa yarda da abinda ta fada, meya hada Audu da matan banza har ya gano matar Aure a cikinsu sannan da gaske Audu ne yayiwa yarsa gudan jininsa wannan dukan babu kara balle ya taci arziqinsa to kodai shaye ya fara toh?

A can falo kuwa da Mama ta gaji da ihu da kururuwar Binta ta daka mata tsawa tace

"Ki rufe mana baki, Audun ai ba mahaukaci bane da ze kamaki da duka haka kawai waye be san halin tsiwarki ba a gidan nan kuma Aure daman kin sani a rubuce take zeyi, ba wata kika tarar a gidan ba dan haka ba zaki fitar da ran kema za'a kawo miki wata ba. Abinda na jiye miki tun farko a Auran Tifical Bahaushe kenan wanda be yi Ilimin Boko ba balle ya waye da yanda rayuwa take, irinsu Audu a kullum tunaninsu be wuci su samu kudi su tara mata da Yaya ba basu damu da jin dadinsu ba balle walwala ko yanda zayuwarsu zata kasance, ke kikace kinji kingani dan haka

yanzu babu wani dalili da ze saka kice zaki dawo mana nan, Munira ma Addu'ar Allah ya kawo wanda zero dauke mun ita nakeyi ballantana ki kaso Auranki ki dawo mun".

"Kai Mama ya zakice haka bakiga abinda ya mata ba se kace ba yarki ba, kuma ko auran zeyi ya rasa wa ze auro is Karuwa haba mana wannan ai ba abune me yuwuwa bama" Munira ta fada aiko ta juya kanta tana cewa

"Idan na sake jin bakinki a nan sena gwabjeki shashasha ai kema ba sanin ciwo kanki kikayi ba

"Ya isa haka Firdausi, ke kuma Mamana ki shiga ciki kiyi wanka Munira ki rakata clinic a dubata, ku dauke yaron nan daga qasa sannan wanda ya kawoki tafiya yayi ko yana nan?" Alhaji Zakariyya saya sake fitowa shirin shirin fita ya fada. Se sannan suka lura da Zakariyya dake kwance qasa abinsa yana bacci Direban ne ya shigo mata dashi ya watsar dashi a qasa tareda jakar kayanta. Ta miqe tana dingisawa Munira ta dauki Yaron suka wuce ciki.

KANO

Rai fes Audu yayi bacci babu damuwar komai tattare dashi illah mafarkin Amaryarsa daya kwana yanayi tareda shirya yanda tariyarta zata kasance nan da sati biyu masu zuwa shima saboda ya bata damar yin shirye shirye ne daga bangarenta dan shi a shirye yake fenti kawai ze saka a sakewa dakin can tazo ta zauna. Rashin zuwan Binta dakin be dameshi ba saboda yasan koda taje qarshe rigima zasuyi, da ya dawo daga sallar Asuba har ze shiga ya dubata kuma ya fasa dan yana so ya koma bacci  yasan kuma muddin ya shigan bacin rai ze kwaso dan haka ya bari akan sa hade idan gari ya waye sosai.

Bugun qofar gidan da ake kamar za'a ballata ne ya tayar dashi. Ya ringa sakin tsaki yana tunanin wanene haka? Jallabiya ya saka ya sakko yana mamakin Ina Binta ta shiga ake irin wannan dukan qofar bataji ba ko itace ta fita qofar ta kulle ta waje. Takaici ya qumeshi ganin Lantana me aiki, ya tsani matar saboda kana ganinta kalar munafukai ne da ita. Ta durqushe a qasa kamar zata kwanta tana gaishe shi ya amsa a dake yana cewa

"Wane irin abu ne haka zakizo kina dukan qofar mutane"

"Kayi haquri yallabai kasan dokar Hajiya qarfe bakwai nake zuwa gidan nan to Nazo tun bakwan na buga ba'a bude ba na tafi shine na dawo na sake bayi bugun da qarfi ne ko bacci take kar nayi laifi tace banzo da wuri ba"

Tsaki yayi ya juya ciki, harya fara hawa sama ya dawo jin tanata qwanqwasa qofar Bintan shiru ba'a bude ba, ta matsa ya isa jikin qofar ya kwankwasa kana ya murda handle din qofar. Fahimta da yayi a kulle take yasa ya zagaya ta window ta da yake a tsakar gidan ya zuge ya leqa ciki, kayana da ya gani barbaje suka fahimtar dashi bata nan, se abin ma ya bashi dariya a fili yace

"Yaji tayi kenan"

"Ki tafi na manta zataje zata fita yau ta fita da wuri ina bacci" ya fadawa Lantana, kamar zata fasa kuka haka ta ja qafa tana waiwayensa, kamar tace masa zata zauna ta jira tunda ko fita Bintan zata yi tana barinta tayi mata jiran gida gashi ta kwaso yunwar safe ta saka rai zatazo taci me kyau kuma ace bata nan.

"Alhaji Mairo tazo ne? Kuma zuwa yaushe Hajiyar zata dawo?" Ta fada tana sunkuyar da kai,

"Idan ta dawo zata saka a kiraki ba yau ba ba gobe ba, kija qofar ki tabbatar kuma ta rufu idan kin fita" ya bata amsa yana juyawa tilas ta fita taja musu qofar gidan. Audu kuwa kasa komawa bacci yayi, tunanin inda Binta ta tafi ya shigayi, qila ba zata wuce gidan Baturiya ba dan bata da yar uwa a Kano bare yace gurinsu zataje Baturiyar itace yanzu babbar Qawarta ko yace Aminiya indai ba gidanta taje ba to Kaduna ta tafi.

Zabura yayi ya miqe yana salati, idan Kaduna ta tafi ya Alhaji zero dauki maganar? Ze goyi bayansa ko kuma ze goyi bayan yarsa ne? Idan Alhaji ya goyi bayan Binta yace ya sakar masa yarsa ya makomarsa zata zama kenan dan dai Alhajin shine abin tunqahonsa, duk abinda yake ganin ya tasarma zama da bazar Alhajin yake rawa.

A gurguje yayi wanka ya shirya, kai tsaye gidan Ali ya fara zuwa suka hade a waje Alin na shirin fita ya kuma tabbatar masa Binta bataje gidan ba dan babu inda zata buya da ze kasa ganinta.

"Dan girman Allah kazo ka rakani Kaduna" ya roqi Alin

"Kai yanzu? Ina babu wannan magana, ai yanda ka tirko rigimarka se ka san ta yanda zaka kasheta. Amma fa ban taba dauka da gaske kaci kai ba Audu se yanzu, duk matan da suke garin nan yayan mutunchi ka rasa wadda ta burgeka se wannan yarinyar? Kodai Asirinsu tayi amfani dashi ta zarge zuciyarka?" Ali ya fada yana tsareshi da ido. Audu yaja tsaki kafin ya shige mota ya daga ba tare da ya bashi amsa ba

Yau dinma Musbahu yaje ya dauka suka tafi Kaduna, seda ya isa qofar gidan kuma ya fara tunanin me zece musu idan ya shiga? Seda sukayi sallar La'asar da Magriba da suka riskesu a hanya kafin ya saka kai cikin gidan. Ko ina tarwai da haske, Tun daga Get suka fara gaisawa da ma'aikatan gidan harya isa qofar falo. Ta ciki Munira ta hangoshi, ta kwasa da gudu tayi daki ta fadawa Binta da tunda tayi wanka taci abinci take rama baccin da batayi jiya ba.

"Wlh ko me za'ayi karki koma ai raini nema kamar ke ace a miki kishiya bayan duk fafutukar da daukar hakkin da mukayi muka fitar da waccen shine za'a dakko miki alaqaqai to babu wannan maganar" Muniran ta qara zugata.

Tun daga yanda Alhaji ya amsa masa gaisuwarsa yaji guiwoyinsa sun qarayin sanyi dama Mama tana musu iso a tsayw suka gaisa ta shige ciki, yau ko Kayan Alatun da ake tarbarshi dasu be samu ba Ruwa da Lemo ma Alhajin ne yayi magana aka kawo musu.

"Bansan ta taho ba Alhaji, na dawo daga sallar Asuba kawai na tarar bata nan" Audu ya fada bayan dogon shirun da sukayi kowanne kamar ya rasa abin fada.

Alhaji ya nisa yana kallonsa yace

"Me ya hadaku da har yasa ta baro gidan ba tareda saninka ba?".

Be boye masa komai ba ya bashi labarin Auran da yayi wanda yake ganin shiya tunzurata ta baro gidan, ya rufe da qaryar cewa

"Bansan cewa zasu daura Auran ba saboda tambaya kawai akaje".

Shiru Alhaji ya sakeyi yana kallonsa kafin yace

"Menene gaskiyar maganara data fada na cewar Yarinyar Karuwa ce?" Seda ya daga kai ya kalli Alhajin saboda kalmar daya fada din se yaga kamar tayi girma musamman ana maganar matarsa ne ina laifin yace tsohuwa, wannan ya tunzuro

zuciyarsa ta raya masa ci masa mutunchi Alhajin ya tashi yi amma ya danne dan ko ya masa qarya bashida amfani tunda har magana ta fito amma a ina Binta taji wannan batun?

"Kayi shiru" Alhaji ya katseshi, kansa na qasa yace

"Gaskiya ne, amma ban aureta ba seda na maidata gaban iyayenta tayi Istibra'i kamar yanda shari'a ta tanadar"

"To akan me ka daki Mamana har kaji mata ciwuka a jiki?" Alhajin ya fadi ainihin abinda yafi damunsa a duk cikin maganar, se Audu ya daga kai da sauri ya kalleshi jin abinda ya fada.

"Wlh Mari daya nayi mata, shima kuma cin kwalata tayi a gaban yan uwana da sukazo fadamun an daura aure ta labe harta tsinci maganar shine ta shaqemun wuya nace ta sakeni taqi ni kuma zuciya tasa na mareta bayan nan ko yatsa ban nuna mata ba wlh" ya fada cikin kare kai. Alhaji bece komai ba yaja Intercom ya kira cikin gida kan Binta tazo, ba'a dauki lokaci ba ta fito tana jan qafa fuskar nan kamar dafaffen Kunu ta zauna kusada qafar Alhajin tana hararar Audu wanda ke kallonta yana mamakin abinda ya karceta a fuska kamar sunyi dambe da Mage.

Ce mata yayi ta maimaita duk abinda ta fada cewar Audu ya mata, tana kuka ta shiga shiryosu harma da abinda dazun bata fada ba na cewar daman Audun ya dade yana yawon ta zubar dinsa har kwanaki yake tafiya yayi acan in ya dawo kuma tayi magana ya zageta koya hada mata da duka qarshema tace idan ta fita har gidan yake kawo mata shidai kasa cewa komai yayi saboda mamaki, maganganunta kuma babu yanda za'ayi ace qarya takeyi tunda tabbas yana yawace yawaceb har yaje ya kwanan amma ai ba abinda take fada yakeyi ba sedai kuma waye ze bada shaidar hakan?

Shidai Alhaji na jinta yana kuma kallon Audu daya kasa rufe bakinsa seda tayi shiru kafin ya kalleta yace

"Kinaji ko Mamana, duk wani Aure da kika gani tattare yake da qalubale muddin kuma ba ma'aurata sun bude cikinsu ba bazaka taba sani ba dan haka kowa haquri yakeyi kamar yanda kika faro haqurin kici gaba dayi kuma tunda ya auro yarinyar

da take dauke masa hankali a wajen ai magana ta qare se ayi fatan kuma Allah ya hada kanku ya bada zaman lafiya. Kaikuma abinda nake so na gaya maka shine ka tabbatar kayi na farko kuma kayi na qarshe da zaka dora hannu da sunan duka a jikin Mamana, zan manta da duk wata alaqa dake tsakaninmu na maka ka a Kotu domin bana hada kowa da yayana, ban daki yar kowa ba dan haka babu hujjar da zata saka wani ya dakar mun yata. Idan tayi maka laifin da ba zau iya sasantawa a tsakaninku ba ka kawo mun qararta nizan hukuntata amma bazan lamunchi duka ba ina fatan ka gane?"

Kunya, nauyi da takaici suka rufe Audu gaba daya ya rasa ma abinda zeyi, Alhaji yaci gaba da cewa

"Idan Allah ya kaimu gobe yanda kikazo da sassafen nan ki tattara ku koma aje aci gaba da haquri kuma na kashe maganar nan, Aure kuma dakayi Allah ya sanya Alkhairi ya baka ladan Jihadi"

"Wlh bazan koma ba, babu yanda za'ayi nayi zamab kishi da Karuwa Dady kawai kace masa ya saketa idan ba haka ba bazan koma gidan ba" ta fada cikin kuka tana bubbuga qafa.

Page 18

Ki bude kunnenki dakyau kiji abinda zan fada, dukiya da kike tutiya akanta ta Abdullahi ce, duk abinda nayi masa kyautace halak malak dan haka ko ki bishi ki koma, ko ki dage ya sake ki zabi ya rage naki amma ki sani sisin kwabo baze maidamun ba dan ya rabu dake ko wani abu saboda dama badan ya aureki na bashi ba, tashi ki bani guri karki qara mun ciwon kan da yake damuna" Alhaji ya dakatar da Binta dake ihun kuka.

Sanin halin mahaifin nata kaifi dayane yasa ta tashi ta koma ciki tana cigaba da kukan ta labartawa Mama yanda sukayi.

"Ahto seki shirya ki koma daman duk tsuntsun daya ja ruwa ai shi ruwa ze doka, ke kika zabe shi dan haka dole ki jure duk wasu tazgado dake tareda zama dashi kishiya kuma naga wata kika tarar kowa da halinta zata zauna ai ba kuma kanki ze ajiyeta ba" abinda Mama ta sake gaya mata kenan haka tana ji tana gani suka kama hanya da farar Asuba ba tareda ta hadu da sauran yan uwanta ba wadanda su ta saka ran zasu bata shawarar yanda zata yida wannan Al'amari, da Munira

suka sake tattaunawa da dare ta qara masa karatun yanda zatayi ta hana Amaryar shigo mata gida dan basu hasko ma ta shigo balle ta zauna.

Haka suka sha tafiyar bata ko kula Audu sedai shine yake tankata lokaci lokaci daya gaji da yanda ta shareshi yayi shiru har sukazo Kano, yana Ajiyeta ya fita itama bata zauna ba jakarta kadai ta shigar daki ta fice gidan Turai.

"Wlh Turai ko a jikinsu, babu fa wanda ya daga maganar Asalin matar daya aura din kamar ma basu fahimta ba haka suka share zancen har a gabansa Dady yana wani jaddadamun duk kudin daya bashi ba Aro bane kyautace kuma ba saboda ni ya masa ba, wlh da na shirya rabuwa dashi amma wannan dalilin yasa na fasa. Babu yar iskar dazan tafi na barwa gida tazo ta wataya da kudin ubana".

Duk da yanayin jimamin da suke ciki seda Turai tayi dariyar maganar Bintan ta kuwa sake harzuqa tace

"Au ga mahaukaciya ko ina magana dariya ma kike mun"

"Ba haka bane, ke dince da abin dariya waini in tambayeki Binta tsakaninki da Allah Audu kike so ko kuma Dukiyarsa?" Turai ta fada tana kallonta.

Ta zabga tsaki kafin tace

"Duka gaba daya, kinga Audu yayi mun daidai da tsarin Mijin da nake burin na Aura cikas dinsa daya rashin wayewar Boko amma abinda yaja hankalina harna yarda na Aureshi saboda yanda Dady ya ke labarinsa na san gobensa zatayi kyau zeyi Arziqi. Turai ina son kudi ina so kuma na auri me Kudi, dukda nayi samari masu kudi yayan masu kudi abinda yasa na zabi Audu a cikinsu saboda shi be waye ba, zan iya masa wayo na samu abinda nake da buqata a gurinsa sannan na hana kowa rabar sa ya zamani ni kadai zan moreshi se yayana, ba qaramin takaici naji ba dana samu labarin yana da mata harda yaya kuma tun sannan na daura Aniyar seta fita ta barmun gidan, bayan nayi nasara sannan ga Arziqi nan yana qara habaka se kuma na bari wata tazo ta tayani ci? Wlh baze yuwu ba dole koda tsiya koda Arziqi matar nan ta koma inda ta fito babu yanda za'ayi na zauna da kishiya a gidan Audu".

"Yanzu dai plan A ya ruguje se mu tafi ga shiri na biyu, kuma ina so ki kwantar da hankalinki qawata shi yaqi akace fan zambo ne, yanda kikayi da Bara'atu haka zakiyi da wannan ma koda ace ta shigo cikin gidan, yanzu abinda zakiyi, lambo lambo zaki masa ki nuna masa kinyi nadamar abinda kikayi ki bashi haquri kisan duk yanda zakiyi yabyarda dake ta haka ne zaki yi komai ba tareda ya zargeki ba,

kamar dai lokacin Bara'atu ai kinga kin nuna masa kina sonta harta fita be taba sanin irin gallazawar da kika ringa mata ba" Turai ta fada

"Turai! Wannan fa ba Bara'atu bace, kefa kika ce mun kilaki ce ta ina zan iya goga kishi da yar Bariki Turai?" Bintan ta fada cikin yanayin dake nuna tabbas ta tsorata da Amaryar da Audun yayiwo mata. Turai tayi murmushi tace

"Dadi na dake Damusar takardace, ga tsoro ga ban tsoro, yanzu har akawai wata kisisina da matar bariki ta iya waddda mu bamu iyata ba? Meye a cikin barikin ne da har zata naki tsoro? Kinga fa yaqin nan dole se kin dage idan ba haka ba kina zaune zata shigo kuma ta kwace Mijin"

"Allah ya rufa asiri, wlh ko zan mutu bazan bari naga wannan rana ba" Binta ta fada tana fashewa da kuka Turai tayi dariya tace

"Bama zaki mutu ba sedai ita me shirin yi mana kutse ta mutu, yanzu dai kamar yanda na gaya miki kije ki lallabashi ku daidaita, da an kwana biyu kic zaki Bechi ki gaishe su a can zaki kwarkwance komai ki gaya musu wacece ita son samu ki fara sanar da Yayansa na Lagos nasan ko beji maganar na qauyen ba shi baze qijin ta tasa ba" da wannan shawara suka rufe ta koma gida ta yi matuqar qoqarin danne zuciya tayi duk abinda Turai tace.

Kuka wiwi ta ringayi tana bashi haquri da rantsuwar ba zata sake ba yanzun ma sharrin shaidan ne tayi iyayinta har seda ya sakko shima ya bata haqurin yanda Al'amuran suka kasance a qaryarsa wai besan za'ayi haka ba.

"Amma banji dadin yanda kika kwanceni a gaban Dady ba, na dauka ko abinda kika fada gaskiya ne ke me rufamun Asirice a ko ina" ya fada in relevant to zancen yawonsa data gayawa Dady. Kanta na qasa tana share hawayen kissa tace

"Kayi haquri, wlh bansan abinda ya shiga kaina ba kan yafemun Mijina kaji dan Allah"

"Ya wuce, Allah ya yafe mana gaba daya sannan in Allah ya yarda nan da kwana Goma Zata tare, ina so ki lissafa duk abinda kike da buqata da wanda za'ayi amfanin yinin Biki a can Bechi"

Wani abu ya caki ranta amma ta shanye tace

"Shikenan zan lissafa, yaushe zamu tafi Beechin toh?"

Da mamaki ya kalleta jin yau anyi zancen zuwa Bechi salin Alin ba ta fadi mara dadi ba, ransa ya qarayin fari yana qara gasgata da gaske tayi nadama dan haka yace mata se saura kwana uku zasu tafi da anyi yini yau washe gari au dawo gaba daya da Amarya ta amsa da Allah ya nuna mana a Ranta tana ayyana Bura'ubar da zata tafka a Bechi idan sunje.

Haka ko akayi, tana kallo aka ringa fenti aka shigo da sababbin kayan gado da kujeru aka saka a tsohon dakin Bara'atu baqin ciki kamar ya murqusheta ta mutu wato cikin dukiyarsu yayiwa Tsinanniyar Amaryar kayan daki, takaicin kanta ya sake rufeta datayi wautar cewa ya barshi bata buqatar komai duk a salon wanke kanta gurinsa. Ranar Laraba suka tafi Bechi ita da Direba daya hadata dashi tareda kayayyakin amfanin girkin da ba za'a samu a can ba, Juma'a za'a kai Amarya can ayi yini su Kwana Asabar su juyo.

Wai se ga Binta na bi gida gida daki daki na yan uwan Audu da sunan taje su gaisa abin dariya ita ce har gidansu Bara'atu. Duk gidan data shiga bata fitowa seta kwance Amaryar Audu ta fada musu tsohuwar kilaki ya auro, Bilki da tun sakin Bara'atu ta fita a sabgar Audu da gidansa farko cin mutunchin Binta taso tayi da ta je mata gida amma zancen data kai mata ya tayar mata da hankali. Me yake damun Audu? Wace hau ce ta haushi da ze auri Karuwa? Hankali tashe ta tafi gida ta samu su Yaya Babba duk sun tattaru dan kowanne na komawa gidansa da yamma ya samu saqon da Binta ta bari shiyasa suna idar da sallar Isha suka tattaro suka taho gidan gaba daya ita ko Binta tana masaukin su da aka qara gyareshi, rabon su duka ya siye banda na Yakubu dan nan yake sauka idan yaje se ya qara fadada nasan yayi dakuna manya da bandaki a ciki.

"Nifa tun ranar da mukaje neman auran kun tuna sanda na fita zagayawa a lokacin naji wasu suna qus qus din wai anya wadannan sun san labarin Yarinyar suka zo nema dansu aure? Basu dai fadi komai ba amma wannan magana tasu ta jefani a wasi wasi sedai tunda shi ma'auri wakilci kawai ya nadamu shi yasa nayi shiru bance komai ba" Yaya Baba ya fada, Aminu yace

"Haba Yaya, menene amfanin girman idan ba zaka ga abin da ba daidai ba ka gyara mana? Yanzi da kaji wannan magana ai ko a tsakanin mu seka gaya mana idan yaso mu basu kudin Aure mu tafi ba zamu yarda a daura ba har se an bincika munji dar din maganar halin nata, na tabbatar shima be sani ba yanzu ya za'ayi?"

"Amma ku kuna ganin gaskiya wannan yarinyar ta fada, kun manta sharrin ta kenan?" Hashimu da be manta kitimurmurar Binta ba ya fada. Bilki tace

"Bana jin qarya ne, tunda ga Yaya Baba ma yace yaji wata magana, yanzun dai mu jirayi Yaya Yakubu ya iso gobe idan Allah ya kaimu in yaso se mu san abinyi kafin Audun ya qaraso shima" inji Bilki, haka taron ya tashi, washe gari ko da Rana Yakubu da Iyalansa suka sauka Bechi. Binta batayi qasa a guiwa ba ta shige ko gajiya bata barshi ya ware ba yana aje haqarqarinsa a kujera ta zube a gabansa ko kallon inda take Bakaraba batayi ba ta taja yaranta suka shige daki.

Bilki tayi turus da kayan abinci a hannunta tana kallon Binta dake rusa kuka a gaban Yakubu tana masa bayani se ta fara jin anya maganar nan da gaske ce kuwa kodai wasan kwaikwayonta data saba ne ta hadashi?

"Yanzu saboda Allah ba zaki barshi ya ko huta ba zaki tasashi a gaba da wannan maganar?" Bilki ta fada taba hararata.

"Zauna Bilki" ya bata umarni kafin yaci gaba da cewa

"Menene gaskiyar abinda ta fada?"

"Yaya muma ita tazo mana da maganar, amma Yaya Baba yace..." Ta fada masa abinda Yaya Baba yaji sanda sukaje neman aure.

"Shikenan tashi kije, zamuji ta bakinsa idan ya qaraso"

"Dan girman Allah kar kuce masa ni na gaya muku"

"Dama ba zamu fada ba tashi kije abinki" da haka ta fita rai fes dan koda Yakubu beyi wata magana ba daga fuskarsa ta fahimci ya kadu da maganar.

Tana fita Balaraba ta fito daga daki tace

"Yanzu kun yarda da maganar wannan annamimiyar matar? Matar data laqawa wata sharrin kisan kai sena Bariki ne ba zata dorawa wata ba? Koda yake Allah ya kawoshi gara yaji abinda ta hada ko idonsa ze washe ya gane da wadda yake zaune ai".

Yamma Lis Audu ya isa Bechi, seda sukayi sallar Isha kafin Yakubu ya tareshi a wajen dan baya so sauran yan uwan su fara masa magana ta yanda laifin Binta ze fito. Cikin siyasa da kwarewar aikinsa ya saka masa maganar a baki, yana da labarin yawace yawacen da yakeyi da wannan yayi amfani yace an gaya masa acan ya hadu da Amaryar tasa.

"Haka ne, amma ban aureta ba seda na maida ita gidansu tayi Istibra'i tukunna" ya bashi amsa kai tsaye. Yakubu ya ringa kallonsa ya gaza cewa komai, dakyar ya iya bude baki yace

"Amma yanzu na tabbatar da Audu baka da tunani sam, duk matan duniya ka rasa macen Aure se karuwa ko kuma asiri tayi maka?"

"Ni babu Asirin da tayi mun kuma ka dena cewa Karuwa tunda ta tuba ta bari sannan babu inda Shari'a ta haramta Aurena da ita tunda dai tayi tsarki sannan ni ina sonta a haka kuma nasan har a gurin Allah nayi aikin alkhairi jihadi babba nayi" Audun ya fada cikin yanayin ko in kula,

"Haka ne" Yakubu ya bashi amsa daga nan yasa kai ya shige gida ya bar Audun a tsaye.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Tabbas yasan wannan lokacin zezo shiyasa yake yawan nunawa Dada rashin amfanin baiwa Audu damar yanke duk hukuncin da yayi masa ba tareda ya shawarci kuwa ba. Ita ta bashi wannan damar, shi a matsayinsa na babba bata taba daukar Maganarsa da muhimmanci ba domin a sannan tana ganin Audu ya fishi wayewa da sanin rayuwa, yasha gaya mata hakan bashida kyau domin idan ya yanke hukuncin daidai qata rana ze yanke akasin haka kuma baze taba ganin cewar yanayin abinda ba daidai din ba tunda ya saba cewar akoda yaushe shi yake bada

shawara ba dai a bashi ba, yau da ace ta gina su akan turbar su shawarci junansu sannan su yanke hukunci akan duk wani al'amari na rayuwarsu ya tabbatar koda Audu na da taurin kai da kafiya tilas a wani bangaren yayi yanda ake so, gashi yanzu yana yankewa kansa danyan hukuncin da idan ba'ayi wasa ba se yayi nadamar su a gaba.

Tamkar dai Yakubun dmsanda su Yaya Baba suka tareshi suma tabbacin gaskiyar maganar ya basu be kuma saurari komai daga bakinsu ba ya shige daki inda Binta ta kasa kunne tana jira ta jiyo magana ta tashi amma shiru, washe gari Juma'a yan uwan Amarya Zubaida suka yiwa Bechi tsinke, su biyar se ita ta shida, dayan dakin dake kusada na Binta aka shigar da ita Mata nata turuwar zuwa ganin fuskar Amarya amma babu dama dan a rufe take daman gulma da munafunci ne kawai ya kaisu suga fuskar tsohuwar Karuwa. Binta na cikin Dakinta a kwance abin duniya ya isheta ta kasa fita har sanda aka fito da Amarya tsakar gida inda akayi shimfidu aka zaunar da ita Bilki ta shiga ta kira Bintan saboda Al'adace za'a danqa amanar Amarya a hannun uwargida.

Daurewa tayi ta qara barbada hoda, daman Leshi tasa me kyau daya qara fitar mata da suffar ta gaba gaba ta tura dauri gaba ta fita tana qoqarin danne shadan dake raya mata data fita ta cakumi Amaryar ta mata dukan mutuwa. Haka ta ringa yaqe har aka gama komai aka bude fuskar Amarya, ganinta tayi yar yarinya da kadan ta fi Bara'atu cika amma kyakykyawace kwarai duk da baqace, kaso ashirin na fargabarta taji ya ragu dan ta saka ran ganin matar da idanunta kadai zasu firgitata amma se ta raina zubinta.

"A haka dai gata kamar salaha amma wai tsohuwar kilaki kai jama'a Allah ka tsarkake mu ka tsarkake mana zuri'a" wata da bakinta bashida birki wadda kuma ta fita danyan kai ta cafe tana cewa

"Kedai bari Tsahare, aini abinda yafi bani mamaki ma Audun daya dakko wannan aba, anya ba juyar masa da hankali tayi ba dan dai wannan al'amari beyi kama da na wanda yake cikin hayyacinsa ba sedai aikin sihiri" seka rantse su kadai ne a gurin yanda sukayi maganar hankali kwance babu wata damuwa tattare dasu kamar wadanda aka saka maganganunsu kuma sun isa kunnen kusan duka mutanen gurin, Zubaida ta sake sadda kai qasa kuka na neman kwace mata, abinda take gudu kenan wanda ta tabbatar da seya faru, shi yasa bata tsarawa kanta yin aure ba koda ace ta bar rayuwar bariki sedai komai ya faru kafin ta farga, haduwarta da Audu, komawarta gida ga kuma aure ubangiji ya fita sanin hikimar yin hakan kuma koma yayane ta godewa Allah daya tsamota daga mummunar rayuwar data fada ba kuma zata butulce masa ba zatayi haquri ta jure duk wani qalubale da

zata fuskanta amma tabbas tana tausayawa kanta tana kuma tausayawa Yaran da zata haifa a gaba dan ta bar musu abin gori har jikokinta idan ba'ayi wasa ba.

"Meye haka Jamila? Ke Tsare wace irin magana kukeyi haka saboda Allah?" Goggo Fadi ta tsawatar musu, a maimakon maganar ta mutu se ya zama abin cece kuce, wanda a kunji kunji sukaji labarin suka gasgata qus qus ya tashi ko ace qaramar hayaniya kowa na tofa albarkacin bakinsa masu fadar Alkhairi nayi masu tofin ala tsine sunayi wannan ya tilastawa Zubaida da qanwarta Surayya fashewa da kuka sauran yan uwansu kuwa jikinsu yayi laqwas tamkar an watsawa Kaza ruwan zafi. A can Kano a unguwarsu ba kamar yanda ake taammata ba Zubaidan bata samu qalubalen kyara ko hantara ba domin har wanda basu santa ba labarinta suka samu a sanda ta dawo sun karbeta hannu biyu saboda wannan ya taimaka mata gurin sakewa ta fara manta rayuwarta ta baya ta fuskanci gaba.

Sun dauka yanda suka manta komai haka sauran Al'umma zasu manta sedai basu san wasu yanzu nema suka samu abin jajantawa da gorantawa. Yanda maganganu suke tashi ya saka dole aka maida Amarya daki tana rusa kuka kamar me domin babu shamaki suke aibatata, tamkar Binta zata taka rawa saboda murna, gumu yayi gumu, masu tsawatarwar basu da yawa dan haka maganar taqi mutuwa har seda. Maza suka shigo ciki, Tsahare uwargidan Yaya Baba data fara tada zancen seda ta karbi Tukuicin saki daya, Jamila matar Aminu data tayata dai ya aikata gida itama amma be furta saki ba, wannan yasa washe gari Asubar fari Audu ya kwashe su suka bar Bechi bayan ya kaftawa Matan Yayyen nasa da sauran Jama'a dake gutsiri tsomar warning, Yan uwanta dai saboda mutuwar jiki basu ko iya rakata dakinta sukace da Direban daya kaisu ya maida su inda ya kwaso su, saga ita se Audu da Binta suka wuce gida.

Kwanakin Amarcin Zubaida dai basu zowa Audu a yanda ya tsara su ba dan abinda ya faru a Bechi ba qaramin tabata yayi ba gaba daya ta rasa nutsuwarta balle ta samar masa da tasa. Abin yawa Binta sugar har ta ringa ganin wautarta da tun farko bata hasaso haka ba, data sani Bechi ta tafi tun farko ba Kaduna ba, qila da yanzu gori ya saka Zubaidan neman saki da kanta amma yanzun ma ta samu nayi, ba duka ba zagi amma In sha Allahu da kanta zata tafi dan ba zata barta tasha ruwa a gidan ba. Yanda Angon duk yake a wani sukurkuce ya qara bata damar kafa kanta da nuna masa ita ta Allah ce har a gabansa ta ringa tausar Zubaidan tana gaya mata ta cire komai a ranta ta bar ta mutane. A haka Audu ya gama kwana ukunsa ya komawa Bara'atu kafin yayi kwana biyu ya dawo Qanwar Mahaifiyar Zubaida ta kai mata ziyara. Ita tayi mata maganar data maido da ita hayyacinya, ta gaya mata damuwa ko kuka ba zata mata maganin komai ba qaddararta ce a haka kuma me afkuwa ta afku dan haka ta manta baya ta toshe kunnenta daga jin duk wasu

munanan Kalamai ta kuma maida hankali ta gyara gidan Auranta domin a yanzu bata da kowa bata da komai se Mijinta da gidan Auranta, ta dage ta nemi Aljannarta ta kuma tabbatar da cewa tayi tuba na gaske, abubuwan data aikata a baya da suke laifi yanzu lada zata samu akansu dan haka ta dage ta kama Mjinta.

Wannan ya zaburar da ita randa Audu ya koma Dakinta Binta bataviya bacci ba saboda lukutin tashin hankalin daya sameta, a garin muguwar dabi'arta ta labe ta jiyo abinda ya kusa zauta mata tunani. Ta yi qoqarin shiga dakin ta dakatar dasu daga abinda sujeyi amma qofar a kulle dole ta wuce dakinta tana kuka wiwi qarin takaici da baqin cikin yanda Audun ya bude baki yana ihu tamkar farin shigan Hauka yanda kasan yau ya fara sanin Mace, washe gari kuwa taga qarshen bariki dan bata tsammatar Audu ya fita sallar Asuba kuma bataga kyallin idonsa ba se yamma lis shima tareda Amarya suka fito suna raha da dariya hannayensu sarqafe da juna yanayin shigarsu ya nuna mata cewar fita zasuyi.

"Idan na yarda Allah ya tsine mun albarka" ta fada yana miqewa tsaye harda cire dan kwali tayi damara.



"Idan na yarda Allah ya tsine mun albarka" ta fada yana miqewa tsaye harda cire dan kwali tayi damara.

Duk su biyu suka dakata suka kalleta, fuskar Zubaidan dauke da murmushi harda rausayar da kai tace

"Ina wuni Yaya Binta?"

"A gidan ubanwa na zama yayarki? Ni zako gwadawa Karuwanci? Koda yake na manta sana'arki ce ai ba a qasa kika tsinta ba" Bintan ta fada murya a sama,

"Meye haka ne Binta? Ke baki iya magana a hankali bane dole se kin daga murya kamar meyi da mutanen sama sannan wannan damarar da kikayi ta mecece haka?" Audu ya fada yana kallonta se kuwa ta shiga qara tamke damararta tana cewa

"Ba shakka dole ka tambayeni me nakeyi haka wato kaima an dora maka darasi irin nasu na tsofaffin kilaki ko? Saboda tsabagen rashin Adalci tun daren jiya rabona dana sakaka a ido, haka ka kwana kana kurma ihu a gidannan kamar wanda ya samu abinda baze qare ba sannan yau ko kyallin qeyarka ban gani ba se yanzu zaku fito cikin shiri da alama ma waje zakuyi wato ga banza jaka ka ajiye wlh ba zan

yarda ba" ta qarasa maganar tana qoqarin fashewa da kukan takaici saboda tuno daren jiya da tayi.

Wani murmushi me tafe da qaramar dariya Audun yayi ya kalli Zubaida data sunkuyar dakai, Karuwa da Binta ta kirata ya soki ranta amma tayi shiru tana qoqarin danne damuwarta tareda hana kanta karaya a gaban Bintan,

"Ashe dagaske kike da kika ce duk maqota suna jina yanzu yaya zan kalli mutanen waje idan na fita bayan na tafka abin kunya qato dani ace yar yarinyar kamar ke ta sakani ihu a daki? Gaskiya mu koma an fasa fitar nan gara na hada kunyar jiya data yau gaba daya gobe na fita dan bazan fasa ihu ba"

Da Binta ta rasa abin fadi se kawai ta fasa kuka me kama da ihu ta juya ta shige daki, Zubaida kuwa dariya ta fashe da ita tana kare fuska saboda kunyar maganar tasa,

"Mu koma ciki" ya sake fada yana kama hannunta ta zame tace

"Babu ruwana kaje ka rarrashi Yaya Binta kar kasa ta qullaceni"

"Ki barta zan lallasheta gobe dan bazanso abinda ze sosa mun rai ba bare harya hanani ware murya dakyau nayi ihun dadi"

"Allah ya isa tsakani na dake yar iskar Karuwa, idan ma kuma Asiri kikayi kika shigo gidan nan na rantse da Allah sena karyashi zaki gane dani kike zanje" Binta data fito da Hijabi a jirkice ta fada cikin kuka kafin ta fice daga gidan ko ina zata se Allah,

"Ka bita mana kana kallo ta fita" Zubaida ta fada cikin yanayin damuwa, ko a jikin Audu ya juya ciki yana cewa

"Duk inda taje ma zata dawo" daga haka ya jata suka koma ciki fitar da suka niyyata aka fasa.

Binta kuwa bayan fitarta rasa inda zata nufa tayi, Turai bata nan ta tafi Gumel suna Yayarta ta haihu kaf Kano kuma ita kadai ce qawar da take kaiwa kukanta. Haka nan tasha kwana ta tasamma gidan Lantana wanda tunda ta fara mata aiki shekara uku kenan sau daya ta taba zuwa sanda Salisu Babban dan Lantanar ya rasu se yau data rasa gurin zuwa kawai zuciyarta ta raya mata taje can. Lantana da makwaftanta biyu na tsakar gida sun baza faifan Binta suna caccaka, haka nan

kullum aikinsu kenan yanzu labarin kishiyar da aka mata dake neman zauta ta take basu

"Ai in gaya miki alqadarinta ya karye, badai ta kori ta Allah ba ai gashi nan an hadota da wadda zataci ubanta ta kowanne fanni, kilaki fa akace yo har a gaya mata iya kissa da kisisina" daya saga cikin matan ta fada, Lantana ta buga cinya ta bude baki zata bada sharhi Binta ta doko sallama suka zabura gaba daya daka kallesu kaga marasa gaskiya

"Hajiya, kece?" Lantana ta fada bayab data miqe tana sosa kai kamar me kwarkwata, Bintan ta kallesu irin kallon raini kafin ta nufi wata Farar Kujerar roba dake ajiye a tsakar gidan,

"Allah yasa lafiya dai Hajiya keda kanki kika zo gidan nan idan wani abu ne aida se ki aiko a kirani" Lantanar ta sake fada. Cikin muryar qunquni ba tareda ta kalleta ba tace

"Lafiya lau, zaman gidan ne ya isheni shine na fito"

"Ai to barka, kuma ke kikace na taho da wuri yau ai da yanzu ina can na tayaki hirar to ina wuni?" Cewar Lantana sauran matan da se sannan suka iya magana duk suka gaisheta.

"Bari naje Lantana inaga su Shamsiyya sun taso daga Allo yanzu, mace daya ta fada se dayar ma ta miqe tana cewa

"Bari na biki ki lallabemun kan nan nawa, Lantana Allah bamu Alkhairi"

"Duk tafiya zakuyi? To ku gaida gida nagode" Lantana ta fada ta na miqewa ta taka musu. Binta na zaune tana qarewa tsakar gidan Lantanar kallo yanda kasan wani filin baje koli can kwanukan wanke wanke can kayan yara sun cire sun zubar a qasa harda zannuwanta ga abinci da akaci aka zubar ba'a kwashe ba banda tiqar rake da qutsirarrun Kara gurin murhunta kadai abin kallonne.

"Bari na kawo miki ruwa Hajiya" Lantana ta fada Binta ta kalli Randarta ta kalli Lantanar kafin ta zabga tsaki tace

"Kika ce mun Mijinki yana aikin Malanta ko? Yana ina? So nake a karyamun duk asirin da waccen tsinanniyar tayiwa Audu a yau nake so ba se gobe ba ta yanda ze mata korar kare ta tafi gidansu komai dare"

"Tirqashi" Lantana ta fada a zuciyarta a fili kuwa seta gyara zama tace

"To yanzu kin hau saiti kenan Hajiya"

"Da ba a saiti nake ba? Karki gayamun magana Lantana saboda kinga nazo gidanki, ki kiramun shi ayimun aikin da yake gabana ba surutun banza nazo muyi ba"

"Allah ya baki haquri Hajiya nima ba surutu nake miki ba, amma yanzu dai Malam baya nan ya tafi qauye kuma kwana uku zeyi a can, da ace jiya kikazo da zaki tarar dashi amma da akwai Mijin qawar nan tawa da suka fita yanzu shi yana nan a gida Malam me makarantar Allon nan ta kan kwanar shigowa idan kina so yanzu sena rakaki gurinsa duk abinda Malam zeyi miki shima irinsa yakeyi" Lantana ta fada cikin ladabi. Binta tayi shiru na wani lokaci, zata so ace a yau din nan an karya mata duk wani Asiri da Zubaida tayiwa Audu amma kuma bata son terere, shima Mijin Lantanar data zo gurinsa saboda tasan zatayi komai cikin sirri ne Lantanar ba zata fitar mata da sirri ba wannan da take fada kuwa bata da tabbas a kansa dan haka ta nisa tace

"Jibi kikace ze dawo ko?"

"In Allah ya yarda Hajiya"

"Shikenan, bari naje na dawo" ta fada tana miqewa tsaye, Lantana taso ta jata da wata maganar ta zauna ko Allah zesa taji yanda ake ciki dan daga ganin idanun Bintan da kuma kawo kanta da tayi gurin Mijinta da tayi mata Qaryar yana aikin Malanta tun farkon fara aikinta a gidan tasan banza bata kao zomo Kasuwa kuma duk abinda ya koro Kifi daga ruwa ya fada wuta toh tabbas yafi wutar zafi, zata so taji komenene dan ta samu na yamadidi a unguwa kamar yanda ta saba raba zancen Bintan lungu da saqo a unguwar amma yanzu babu fuska dole ta haqura ta rakata zaure tana jaddada cewar Jibi da Malam ya dawo zata sanar mata.

"Ko na biki na tayaki zaman ne Hajiya?" Bata dai sare na ta fada, Binta ta mata Banza tayi gaba. A maimakon ta tafi gida kai tsaye seta bige dabi ta wancan lungun ta bulla wancan seda taji ana kiraye kirayen sallar Magriba kafin ta kama hanyar gidan ranta na quna da tunanin me zataje ta tarar, tana shiga Soro hawaye ya balle mata, wai yau ita Binta ce gidan Audu ya gagareta zama har ta fita tana garari a titi

saboda qata Mace? Wlh bata isa ba, taci alwashin seta tozarta Zubaida, yanda ta kori Bara'atu Salin Alin haka itama zata fita ta bar mata gida, Audu da duk abinda ya mallaka nata ne wata mace bata isa tazo ta mata katsalandan a sabgarta ba.

A tsakar gida sukaci karo ya fito da Alama masallaci zeje,

"Kin dawo? Ga Alhaji can an maidoshi bakya nan yana gurin Yar Dagwas" Audun ya fada mata kafin ta bashi amsa ya rabeta ya fice daga gidan dan har an tayar da sallah. Kamar kububuwa ta doshi dakin Zubaidan babu sallama.bare neman iso ta bankada labule ta fada ciki.

"Wane Dan abu ta kazan ne ya baki izinin taba mun yaro? Dana tsarkakakke zaki shafa masa Dattin zina? To bari kiji karki dauka kinga gurin zama a gidan nan, yanda kika shigo da qafa biyu idan bakiyi wasa ba sedai a kwasheki a wilbaro dan sena karairayaki na zubar. Se kinyi nadamar auran mun Miji, sena illataki yanda ko kin koma yawon Karuwancin naki ba zaki samu masu tayawa ba, bani Dana, kuma ki fito ki doramun abincin dare yanzun ba se anjima ma".

Zubaida na tsaye da goyon Zakariyya wanda yake ta rigima tunda wata yarinya ta kawo shi daga gidan da Binta take kaishi raino yana ganin Audu ze fita kuma ya saka kuka wannan yasa ta goyashi harya rufe ido da alama daman rigimar bacci ce hargagin uwarsa ya tadashi. Kwanto mata danta tayi ta direshi kan Kujera, Binta ta fizgeshi ya saka kuka saboda yanda taja hannunsa ko tsoron yaji ciwo batayi ba ta fara jansa tana cewa

"Kinji abinda nace ai karki bari na maimaita miki"

"Bana tsammanin yace miki ya miki bayanin ni wacece a gidan nan, to idan beyi miki ba ni yanzu bari na gaya miki. Yanda kike matar aure da aka auro da sadaki nima haka nake, matsayinmu daya na yar aiki ko me dafa abinci aka kawo miki ba dan haka ke baki da qarfin ikon da zaki sakani na dafa miki abinci a gidan nan kici, idan kinga haka ta faru to Mijina ne ya bani umarni wannan kuwa zanyi saboda shidin shugaba nane, kuma neman Aljanna ya kawoni gidansa bazan tsallake umarninsa ba muddin be sabawa shari'a ba" Zubaidan ta bata amsa kafin ta angizo daurin dankwalinta gaban goshi tace

"Karuwa kuma bakiga komai ba daga cikin halinta, ki saka ido ki gani, tsakanin nidake za'aga wadda zaman gidan nan ze gagara" tana gama fada ta wuce cikin daki tana kada jiki tabar Binta tsaye baki a sake, seda ta bugo qofa kafin Bintan ta

farga ta fara dura mata Ashar tana cewa idan ta isa ta fito ta gani seta sauke mata rainin da take taqama dashi yau, ta gama hayagagarta taja Zakariyya suka wuce daki tana cigaba da bala'i kamar tsohuwar karya.

Zubaida kuwa Alwala ta daura tanayi tana kuka, a duk sanda aka kirata da Karuwa takanci ciwon abin yanda bata taba tsammata ba. A sanda take cikin rayuwar Alfahari take da sunan amma yanzu tana jn muninsa fiye da misali. Yanzu haka za'a ringa alaqanta yayanta da wannan mummunan sunan?

Bayan ta idar da sallah bata tashi ba har akayi Isha'i ta dora shafa'i da wutri tayi addu'a kana ta nade abin sallar ta tashi. A gurguje tayi wanka ta shirya, cikin irin dinkunan da Kilallu irin tane a wancam zamanin ta saka riga da siket daya matuqar kamata ta baza qamshi ta ko ina sannan ta kafa dauri a gaban goshi.

Audu ya gaya mata kartayi girki ze shigo musu da abinda zasuci dan haka ta dora ruwan shayi baqi ta zuba kayan qamashi sannan ta dauki Kankanar data hada tun yamma tashanye ta koma falo ta zauna bayan ta kunna waqar Aliko makaho tana bi hankali kwance tana gyada kai.

"Baki a washe kamar wawa Audu ringa binta da kallo sanda ta karbi ledojin Kaji da kayan Marmarin daya shigo dasu,

"Aa kaga yar dagwas, irin wannan Ado haka gaskiya kinci sunan naki na yar dagwas" ya fada yana washe mata haqora. Ta dan bata rai irin na shagwaba dukda tace

"Nace maka bana so ka canza mun wani sunan amma banda wannan" har ranta ta tsani sunan a yanzu amma bata so ta nuna masa hakan cikin fushi ko fada, ya zauna yana sake ce mata

"Barni kinji, dadi sunan yake mun. Je ki kawo faranti muci Naman nan tun da zafinsa".

Ta wuce Madafa tana juya mazaunanta da basufi rabin na Binta ba amma da yake ta iya sarrafasu bala'in dauke masa hankali take idan tana tafiya. A da gani yake ba Macen data kai Binta iya gwalangwaso da kisisina wannan abin ya qara dakusar da Bara'atu a idonsa yaji sam ta dena birgeshi saboda bata ko kamo qafar Bintan ba babu abinda ta iya se wanda ya koya mata amma yanzu daya auro Macen gaske se yaga ashe duk wani sanaben Binta sharar fage ne, wato jiya yaje cloud 9, yaga

abinda ya dauka a gurin Hurul'ayni matan Aljanna kadai ze samu yanzu ita kanta Bintan ganinta yake kamar shi dan yanzu ne ya tabbatar ya auri Mace.

Yana can lissafin ta dawo, yanda take duqawa ta ajiye kayan ma abin birgewa ne sannan ta kalle shi tayi masa wani farrr da ido se yaji kamar ze suma dan dadi.

"Ina na Maman Zakariyya? Kona kirata muci tare?" Ta fada tana bude ledojin.

Ya sauka qasa ya zauna yana cewa

"Ai tana da Kaji a firinji, kema gobe za'a kawo miki saboda ajiyar Danyan Nama da sauran kayan amfani" ya bata amsa yana daukar kofin data tsiyaya masa baqin shayi a ciki kurba seta shagwabe fuska tace

"Haba dai, ya za'ayi muna gida daya ka siyo abu muci mu kadai banda ita da yaronmu? Aa gaskiya bari na dibar mata dan wannan ai ya mana yawa Kaji biyu Manya ina zamu kaisu" taja faranti ta fara dibar Naman, wata qaramar Leda da taji dumi ta bude taga Tsirene a ciki ta aika masa hararar qasa tace

"Harda tsirema duk a wane cikin zamu zuba mu kadai?"

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

Ta cika faranti da Kazar da tsire ta lullube da takarda sannan ta bude kayan Marmarin suma ta diba a Leda tana kallonsa tace

"Bari na kai mata". Da kai ya amsa mata ta dauka ta fita ya bita da kallo yana tuna lokutan baya a zamanin Amarcin Binta. Kullun ta Allah se sunci Gasashshiyar Kaza da tsire da wani damun fura me shegen dadi da yake siyo musu suci su biyu ko takardar Naman Bara'atu da Yaranta basa gani balle suji qamshi. A sannan ma yakan siyo hardasu amma indai ya fara shiga bangaren Binta dashi to ya zama haramiyarsu daga baya ma ya dena siyowa dasu ta cusa masa ra'ayin ai suna ci a Miya kuma sanda tana Amarya itama an mata dan haka yanzun lokacinta ne taci ita kadai shiyasa yanzun yayi amfani da maganarta ya siyo musu shida Zubaida kadai itace Amarya ai itama tana ci a Miya.

Zubaida kuwa a qofar dakin Binta ta tsaya ta rafka sallama, Bintan na zaune ta zabga Tagumi, abin duniya ya isheta taji sallama, bata dauka Zubaidan bace ta amsa harda bada izinin a shiga. Ta shiga tana qara wata qaramar sallamar ganin

itace ya saka Binta zabura tana binta da kallo tundaga sama har qasa, dukda kyashi da hassadarta daya cika mata zuciya seda ta yabi kyan da shigarta tayi to ina ga Audu?

"Ke bakida hankali koM meya kawoki dakina? Da izinin ubanwa kika shogo?" Ta fada cikin hargowar data zame mata jiki, Zubaidan tayi murmushi tace

"Seda nayi sallama fa kika amsa kafin na shigo, kuma ba wani abu ya kawoni ba, kazar Amarci Mijinmu ya sake siyomun shine nace bazanci ni kadai na na raba na kawowa Dana" ta dangwarar mata da Farantin a qasa ta juya tana tafiyar yanga Binta tayi kukan kura ta kai mata cafka, a yanda ta cakumeta Allah ya dubeta kamar jifa sega Audu ya fado dakin badan haka ba ta tabbatar da tace seta ballata ta zuba a wilbaro tabbas abinda tayi niyya kenan.

"Baki da hankali Binta meye haka zaki kamata da dambe?" Ya fada yana janye Zubaida da zuciyarta ke buga tsalle daga hannunta. Bata dauka jarabar Matar nan takai haka ba, ita ko doguwar cacar baki ba iyawa tayi ba ina dmga yar bawa hammata iska kuma ace da wannan qansamemiyar basamudiyar ai wata rana murus zata kasheta idan akace suyi dambe.

"Dole kace bani da hankali mana wato kai ka aikota tazo tamun cinikinta Abinda aka saba ko? Ni zaka wulaqanta Audu da abinda zaka sakawa ubana kenan bayan duk halaccin da yayi maka a duniya? Karka manta mahaifina shi yayi maka rigar da har ka ringa yawo a gari ka kwaso wannan karuwar, to wlh bazan zauna baqin ciki ya kasheni ba tattarawa zanyi na bar maka gidan ka idan yaso ka auro irinta goma ka ajiye gara na koma gidanmu inda ake sona" tayi bal da farantin kazar da aka kai mata ta shige daki tana kuka wiwiwi, diri diri yayi ya rasa me zeyi, ya bita ne ko kuma su fita su bar mata dakin?

"Ka bita mana karfa ta jiwa kanta ciwo kamar watsi take da kaya" Zubaida ta fada jin Binta na zubar da kaya a qasa se ya tafi solo solo ya shiga dakin ita dai Zubaida ta juya ta fice har sannan jikinta be dawo daidai ba daga tsoron shan suburbuda a hannun Binta. Bata san ya suka qare ba dan har bacci ya fara fizgarta kafin ya shigo ransa duk babu dadi ganin haka yasa daman tayi shirin bacci a kwance take tana jiransa se kawai ta gyara kwanciya dakyau tayi baccinta shima ya gama abinda zeyi be nemeta na duk yanda yake cike da zumudin kebewarsu amma ya gagara yin komai, yanda Bintan ta ringa kuka tana fadin zata tafi kawai ta shiga duniya yana wulaqantata ne saboda yaga Dadynta ya goyi bayansa sanda ta koma gida ita kawai gara ta tafi koma inane tunda babu me qaunarta ya shiga tsakaninta da

Iyayenta kuma yazo yana wulaqantata akan Matar daya hadu da ita daga baya tasan baya qaunarta tun sanda aka kashe mata Da amma be dauki matakin komai ba.

Haka ya kwanta ransa duk babu dadi sedai da Asubahi da yar dagwas ta kaishi gari me nisa tuni ya manta da wata Binta da Emotional blackmail dinta. Tana can ta saki baki tana jiran ya bugo Asubanci yaci gaba da rarrashinta dan jiyan Data gama surutai bandaki ta shiga ta kulle yayi yayi ta fito taqi tace ya fitar mata a daki in ba haka ba zata kwana a ciki sannan ya tafi to ta dauka daya dawo masallaci ko kafin ma ya fita se shiga ya dubata amma taji muqus har gari ya waye tarwai se Tara saura na safe suka fito da Amarya yayi shirin fita, tana zaune kan barander dakinta Lantana na share tsakar gidan suka fito ta zube tana gaishe su.

Kamar jiya yauma harda dan risinawar Zubaida ta mata ta gaidata, bata tanka ba ta zabga tsaki bata dai yi masifar data sababa shirun nata kuma se yaji babu dadi dan haka yacewa Zubaida yana zuwa.

Falon Bintan ya shiga ya tsaya a tunaninsa zata bi bayansa amma shiru, ya leqo ya mata magana nan ma ci kanka bata ce masa ba wannan ya hasalashi ta wulaqantashi gaban me aiki dan haka ya fice fuu ko Adawo lafiyar da Zubaida take masa be amsa ba.

"Zaki san ni ba sa'ar wasanki bace wlh yau se kin gane kurenki badai jiya ya ceceki ba? Yau naga ubanda ze kwaceki a hannuna" Binta ta fada tana miqewa bayan data tabbatar Audu ya fice daga gidan tabi bayan Zubaida data qarawa tafiyarta sauri jin abinda take fada, gudu ta saka ganin dagaske kamata take shirinyi tana fadawa daki ta turo qofa Binta ta saka hannu zata dannata ciki bisa tsautsayi ta datse mata yatsa da qarfi take ya fashe ya fara jini.



"Akan me zaki kulle qofa? Dukanki zatayi ko cizo da ze saka ki kulle qofa har ki hada da hannunta ki matse?" Audu ya fada cikin kaushi yana duban Zubaida dake durqushe gabansa kanta a Qasa Binta kuma na daga gefe tana yarfe hannu yatsanta data datse da qofa ya kumbura idanun nan sunyi fici fici da alamun tasha kuka ba kadan ba yau din. Audu na yin sallama Lantana da bata tafi ba ta zube a gabansa tana fada masa uwar dakin nata babu yanda take tana daki, hankali tashe

ya doshi Dakota n nata can ya tarar da ita tayi zaman dirshan a qasa tana yarfe hannu tana kuka harda majina, shiri sukayi da Bintan akan hakan dukda dagaske take jin azabar ciwon yatsan amma tuggun da take so ta hada da faruwar hakan shi ya saka ta sake rakwarkwabewa ba iyakar zafin ciwon ba.

Daya tambayeta ya akayi taji ciwon take ta gaya masa Zubaida ce, akan ta bita daki su sulhunta kamar yanda ya roqeta jiya akan tayi haquri ta kwantar da hankalinta su zauna lafiya to bayan tafiyarsa tayi tunani akan hakan kuma taga ya kamata ace tayi shine yau taje dakinta da niyyar ta bata haquri akan abinda tayi mata jiya a maimakon ta saurareta se kawai ta hau zaginta tace ta fitar mata a daki, data tsaya ta dafa qofar shine ta hada harda hannuta ta datse shi kuma kamar fulawar da aka zubawa Yeast ya shiga kumbura ya tafi fuuu ya kira Zubaidan nan gaban Binta ya titsiyeta yana tambayarta ba'asin dalilin rufe qofa.

"Ni ba a sanina na bigeta ba kuskure ne" ta fada cikin sanyin murya, Binta ta zabura tace

"Wlh qarya takeyi tana sane ai Lantana na gurin ka tambayeta kaji"

"To a tambayi Lantanar mana in har zata fadi tsananinta da Allah ko ita ta san ba ina sane na bige miki hannu ba, sannan ni bani na nace ki shigar mun daki ba bare har ki saka hannunki qofa ta datse ki" Itama Zubaidan ta katseta

"Ke! A gaban nawa ma rashin kunya zaki mata? To bari kiji daga yau koda wasa karki sake kullemun qofa tunda dai gida nawane ba na wani ba, sannan dukanku matana ne babu wadda nayiwa shamaki daga shiga dakin wata a cikinku, yanzu kalli ciwon da kikaji mata ji yanda hannun ya kumbura fisabilillahi hakan da kikayi yayi kyau?" Audu fada yana zare mata ido, Zubaida sadda kai qasa saboda kukan dake shirin bada ita tace

"Amma dai tsakani da Allah ba haka ya kamata kayi ba, seka tambayeni abinda ya hadamu tunda dai kaji daga bangarenta"

"Ke zaki tsara mun abinda zanyi a cikin gidana? To banyi hakan ba nace banga damar yin hakan ba koda abinda zakiyi?" Ya hayayyaqo mata seta fashe da kuka saboda takaici tama rasa abinda zata kuma ce masa

"Tashi kije" ya bata umarni yana wani dauke kai dan kukan nata ya tabashi amma shi a dole ta masa laifi shiyasa ya dauke kai. Cikin kuka guiwoyinta a sanyaye ta wuce dakinta. Zubaidan na fita itama Binta ta fashe masa da kuka tana cewa

"Yanzu shikenan ta jimun ciwo taci bulus iyakar abinda zaka ce mata kenan sannan saboda makirci ta fita tana kuka kamar ita aka zalunta?"

"To ya kike so nayi, so kike na rufeta da duka ko kuma na riqe hannunta ki rama abinda tayi miki? Ina kinji dai tace kuskurene?" Audun yayi kanta a fusace, yanda yayin yasa tayi shiru bata kuma cewa komai ba wato tuggunta be samu shiga ba so tayi ya rufe Zubaidan da fadan koma ya falla mata mari koya rufeta ma da duka amma dai ko banza hakan ma babu laifi tunda ya sakata kuka a gabanta da haka zata cigaba da nunawa Zubaidan ita din ba kowa bace a gurinsa Audu, kuma duk yanda ta dama haka za'a sha. Qarawa kukanta volum tayi babu ko dadin sauraro Audu yaja tsaki yace ta tashi suje gurin wani wanzami dake qasansu a duba hannun.

"Wlh ba zani ba idan ba zaka kaini Asibiti ba sedai na zauna da hannun haka kuma gobe karka saka ran zaka fito ka tarar dani a gidan nan Kaduna zan wuce" ta fada cikin kuka. Wannan tasa ya kaita Asibitin suka bata magu gunan rage radadi bayan an mata allurar kashe kwayoyin cuta sannan suka dawo gida lokacin goma harta gota, seda taci abinci tasha magani kafin ya wuce dakin Zubaida.

Tana zaune a falo ta kunna Tv amma hankalinta baya ga abinda ake nunawar tayi nisa cikin tunanin da tunda ta baro dakin Binta takeyinsa. Se taga kamar shari'ar ta Audu ba haka ya kamata ya gudanar da ita ba, tambayarta ya kamata yayi abinda ya hadata da Binta har wannan tsautsayin ya faru bawai ya dora mata laifin matsewa matarsa hannu haka nan ba kuma da yake maganar kowa tana iya shigar dakin yar uwarta babu shamaki a ina ake haka fusabilillahi?

Yanda ya shiga fuska a daure haka tayi masa sannu da zuwa jiki babu karsashi guiwoyinta suka sake sanyi da Al'amarin Audun, to fushin na menene kuma? Ba an gama magana ta wuce ba? Ya gama uzurirrikansa data bashi abinci yace ya qoshi, bata sake tsinkewa da lamarin ba seda ya juya mata baya da sukaje kwanciya a ranta tace lallai abin babbane.

"Kayi haquri in dai akan abinda ya faru jiya ne kake fushi wlh ba ina sane na matse mata hannu ba ita ta biyo ni tana zagina tace zata dokeni ni kuma tsoron haka yasa na shigo na tura qofar bansan ta saka hannunta a ciki ba" Zubaidan ta fada hawaye na saukar mata sanda Audu ke shirin fita da safe ba tareda ya ko kalli kayan karin data jera masa ba.

"Oh, bayan abinda kikayi shine kina da bakin sake magana harda sharri zaki mata a yaushe ta zageki harta biyoki zata dokeki?" Ya fada yana dakatawa daga fitar dayayi niyya. Hawaye suka balle mata na takaici, wato sharri tayi mata? Ita Bintan Allah kadai yasan abinda ta fada masa wato natane gaskiya se ita data fadi ainihin abinda ya faru shine zece ta mata sharri?

Muryarta na rawar kuka tace

"Akan me zan mata sharri? Sannan ai kaima zaka iya bada shaida akai dan ba shibe karo na farko data zageni ba ko tayi yunqurin dukana a gabanka ma anyi shekaran jiya ba kai ka kwaceni daga hannunta ba?" Ta fada tana tsare shi da ido. Yayi jummm alamar ya gasgata abinda ta fada din amma saboda qi fadi da rashin son gaskiya irin nasa se ya murje yace

"Rashin kunya zakiyi mun har kina tsareni da ido kamar wani sa'anki? To bari kiji muddin kina neman zaman lafiya a gidan nan dole ki zauna lafiya dani da kuma matata. Mu bamu saba fadace fadace da kuka iya har ana fidda jini ba a gidan nan dan haka ki san a inda kike" daga nan yasa kai ya fita ya barta tsaye kamar ya dasata tana juya kalamansa.

Ita da suwa suka saba fadace fadacen da zubar da jini?

"A bariki mana yake nufi" zuciyarta ta bata amsa, dabas ta zauna dafe da kunci hawaye suka shiga mata tsere, wato abinda yake nufi kenan, a fakaice yana gaya mata cewar nan ba irin gidan daya dakkota bane kenan da suka saba Fada kamar Kaji suna jiwa junansu rauni Yau Audu da kansa yae goranta mata wani al'amari daya shude a rayuwarta kenan.

Wannan abu yasa gaba daya jiki ta yayi sanyi, sararin data samu ta fara baje kolin sharholiyarta duk karsashin ya barta shima kuma be bi takanta ba yana ta tattalin Binta da hannu ya saka a gaba har ya saukar mata da zazzabi me zafin gaske seda ta kwana uku a kwance kullum kuma is Zubaidan ta shiga ta dubata safe da dare

idan yana nan zata amsa cikin sakin fuska idan baya nan kuwa har Lantana samun damar yaba mata magana take suce mata mayya wai ta kama mata hannu to kurwarta kur. Ita Binta ko abinda take mata ma sam be dameta ba irin na Audun, qiri qiri yaba ganin gaskiya amma ya take yabi qarya shin wane irin mutum ne shi haka?

Ya za'ayi rayuwa ta yuwu a haka ace duk abinda aka gayawa mutum walau shine gaskiya walau qaryane se ya hau ya zauna kuma idan ya gano gaskiyar daga baya girkan kai da izza su hana shi karbar kuskurensa ai ko baze furta da baki ya karbi gyara ba se ya nuna hakan a aikace amma shi babu daya daga ciki da yakeyi sedai ya dora fushi wannan ai ba daidai bane. Data lura da gaske fushi yake da ita kuma bashi da alamar sakkowa dan har ranakun girkinta da suka zagayo bacci ke shigar dashi dakinta safiya nayi ze fice dole ta sauke nata fushin ta sake samunsa ranar ta tattara duk wata wayo da dabarar da take dasu ta wanke kanta a gurinsa ta hanyar karban laifin da bata aikata cikin sani ba ta kuma tabbatar masa da ba za'a sake ba har da kukanta tace kuma ya rakata a gabansa ta baiwa Bintan haquri sukaje ta bata haqurin ganin idonsa yasa Binta tace ta haqura ai ita komai ya dade da wucewa a gurinta daman wannan tasa ya sakko daga fushin da yake suka koma zamansu lafiya abinda yayi mugun batawa Binta rai.

A zaman tsamar da sukayi ba qaramin qara samun kan Audun tayi ba, a wayo da dabara take dada kwarkwarashi shi kuma dake kan keke ne ya hau daram ya zauna. Shiryawarsu da Zubaidan se ya zama silar warewar nata shirin musamman da taga kamar Zubaidan ta ganota duk irin tuggun data hada mata a gurin Audun ta dena musawa zata amsa laifinta ta durqusa har qasa ta bashi haquri tana hawayen munafunci a cewar Bintan shi kuma me son girma kansa ya sake fasuwa shikenan kome ta shirya ya wargaje.

Tun daga wannan kuma Zubaidan ta hankaltu duk laifin da Binta ta dora mata zata amsa ta bashi haquri tunda ta fahimci abinda yake so kenan babu ruwansa da jin ainihin magana yanda take hakan kuwa da takeyi ya sama musu zaman lafiya se a dade ba'aji kansu ba idan ba kuma Bintan ta shammaceta ta tunzuro shi ta yanda harta gaza kare kanta ba.

A haka aka kwashi watanni biyar da Auro Zubaida a kuma wannan yanayi ta fara laulayi wanda yazo mata da zafin gaske ga Amai ga Zazzabi lalurori dai iri iri ba qaramin Jiki take ji ba, wannan cikin ya sake gigita Binta, wato Zubaida zama tazoyi ma kenan tunda gashi har tayi ciki ita tana me haka ta faru yama za'ayi Mata suyita

haihuwa a gidan Audu Bara'atu tayi biyu ita tana da daya kamar rai kuma a auro wata a bayanta tazo ta goga da ita wannan baze yuwu ba ta shiga takalar masifa kala kala fatanta Zubaida ta tanka mata ta samu dalilin lakada mata na jaki ta yanda cikin zebi rariya tun be gama samun gurin zama dakyau ba sedai bata samu hakan ba, Zubaida da ko a baya bata biye mata ba balle yanzun da take ta kanta.

Abin ya hadewa Binta biyu dan Audun shima yanzu duk ya maida hankali kan Zubaidan sosai wannan yasa ta kasa jurewa ta fiddo haukarta fili take baje musu ita watarana ya tanka mata wata rana kuma ya qyaleta a haka abinda ya sassuta lamarin ganewar da tayi itama tana da shigar ciki saboda batan wata da tayi amma tayi shiru bata gayawa Audu ba sannan kuma cikin Zubaida yayi watanni uku a lissafinsu na daga sanda ta fara laulayi kenan ita kuma nata yana wata daya.

Koda Zubaida sukaje Asibiti likita ya tambayeta yaushe rabon da tayi Al'ada ce masa tayi watanni uku, tayi lissafi da watan data fara laulayi dukda maganar gaskiya ba zata iya cewa ga lokacin da tayi al'ada ta qarshe ba tun zuwanta gidan sau daya tayi watanninbaya da suka biyo idan Al'adar tazo kwana daya ne kuma dan kadan ba kamar yanda ta sabayin kwanaki Bakwai ba kuma ba se qarshen wata ba ko yaushe tana iya ganinsa kuma ya dauke har ta fara zaton ko Sanyi ne ya kamata to tunda tasha magani kuma jinin be sake zuwa ba babu dadewa kuma ta fara laulayi.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane ,

magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

Bayan tabbatar da lafiyarta data abinda take cikinta aka bata sati hudu ta dawo daga Asibiti, kafin zagayowar sati hudun nan tamkar wadda aka bugawa iska cikinta yayi wani girma na ban mamaki. A watanni ukun da tayi muddin ba wanda ya karanci yanayi na masu ciki ba shine ze iya tantance samuwar cikin a jikinta dan idan ka cire Laulayi babu wata halittarta data canza kota nuna samuwar wani abu tattare da ita. Cikinta na nan yanda yake be qara tudu ba haka nan batayi qiba ba se gashi a sati hudu cikin ya bude yayi girma haka jikinta da fuskarta duk sun sauya idan ka ganta seka dauka in kun rabu yanzu anjima za'ace maka ta haihu.

Binta bata nan ta tafi Kaduna sanadin jikin Alhaji Zakariyya daya motsa harya kwanta a Asibiti dan haka suka tafi tareda Audu ya kwana biyu ya barota a can kuma zuwan yayi daidai da bikin yaye su BabaIliya da akayi dan haka suka hada tafiyar harda Yan Bechi duk sunje sun duba jikin Alhajin kuma a gidansu Bintan aka

musu masauki suka kwana biyu suka juyo tare aka baro Binta a can satin ta uku kafin ta dawo Kano.

Ranar da Binta ta dawo ita kuma Zubaida bata nan taje gidansu yini se dare Audu ya dakkota koda suka shigo kuma bata ma san Bintan da dawo ba dan be gaya mata ba se da ya shiga tareda Zakariyya wai yaje mata sallama sannan ta sani ta kuwa cika da mamaki amma batace masa komai se fatan wayewar gari lafiya tayi kwanciyarta ita kadai. To washe garima bata fita ko tsakar gida ba dan a yanayin da take yanzun tafi ko yaushe buqatar samun hutu da nutsuwar zuciya bata shirya dibar hauragiyar Binta ba dukda tana so taje su gaisa tayi mata yame jiki amma ta bari akan se da dare idan yana zaune seta shiga ko ganinsa ze rage kaifin duk rashin mutunchin data so yi mata.

Hakan kuwa akayi, bayan isha ta shirya taje Audu na zaune yana cin abinci tareda Zakariyya Binta na cikin daki tana buruntu tayi sallama ya amsa yana tsokanarta da cewa

"Uwar biyu kin shigo?" Haka yake ce mata tunda cikin ya fara wannan girma me ban mamaki yace kodai yan biyu ne shi yasa wata hudu cikin ya ninka girmansa se tace masa to qilan tunda ita ba sanin ya cikin yan biyun yake tayi ba.

"Baquwa mukayi?" Binta data fito ta fada tana zama akan kujera idonta akan Zubaidan, Audu ya murmusa yace

"Baki ganeta ba? Kallarta dai da kyau kiga dawa tayi miki kama?"

Ta zuba mata ido tana so ta gano wacece din kamar yanda ya ce, tai fici fici da ido se ko ta zabura sanda ta gama ganota ta nunata tana cewa

"Ke..meye wannan? Me zan gani haka?"

Yanda tayin ba Zubaida ba hatta Audu seda ya bushe da dariya yanda kasan wadda taga wata fatalwa haka rikice tana jera mata tambaya yace mata

"Kinga abin mamaki ko? Yanda kika san cikin nan na jira ki tafi ya fara girma qila da baki dawo yanzu bama sedai kizo ki tarar ta haifeshi"

"Au Namiji ma zata haifa?" Maganar ta subucewa Bintan, Zubaida ta kalleta Audu da be gane inda maganarta ma ta dosa ba yace

"Yan tagwaye ma kuwa muke tsammata dan wannan cikin daga ke har Bara'atun ban taba ganin wadda tayi me girmansa ba" ya furta sunan Bara'atu a fili karo na farko tun bayan rabuwarsu da ita.

"Zancen banza ma kenan, ita zata haifi yan tagwayen a gidan nan? Wlh baze yuwu ba" ta idasa kwancw qullin haukarta. Zubaida ta gyara zama ganin cin kan Bintan gaba yakeyi tace

"Yaya ina wuni? Ya aka baro yan gida? Ya me jiki kuma? Ubangiji ya qara afuwa yasa kaffara ne" daga nan ta shiga yunqurin miqewa tsaye tana jin Bintan dake kallon Audu tace

"Lallai ma wannan rainin wayo ne qarara kuma wlh bazan dauka ba, ni za'a mayar mahaukaciya cikin da be ko cika qata hudu bane zeyi wannan girman sannan saboda jaka ce ta raineni na yarda ai kuwa ba'a isa ba"

Zubaida bata tsaya sauraronta ba ta wuce dan dai kamar maganar bata shafeta ba haukanta da bata gajiya dashi ne ya motsa ga Mijinta nan seta sauke shi a kansa amma ba ita ba ciki kuma dai ba mutum ke bayarwa ba balle tace zatayi fito na fito da wanda ya bata dan haka tana zuwa daki taci abinci tasha saiwoyin data jiqa jiya dataje gida Baba Zayya Amaryar da Malam Hassan Babanta yayi watanni biyu kenan ta hado mata saiwoyi wai na taimakon sauqin naquda ne da rage zaqi a yanda Baba Zayyan tace wai cikinta ya nuna alamun ta kusa haihuwa ta ringa dariya tana cewa Baba Zayyan kace a kanta za'a fara haihuwar hudunni kenan ita kuma tace mata to su daura tsakanin su za'a me gaskiya dan bata yarda da lissafin Asibiti ba ko makaho yaga cikin Zubaida yasan ya haura zuwa watanni bakwai ko takwas.

"Idan kika lissafa watanninki a daki ai cikinki ya kusa isa haihu ina watan Sallar Tsofaffi akayi Bikin wata na takwas fa kike ciki yanzu ai dab kike da ki haihu" Baba Zayya ta nanata mata. Ita dai bata dauki batun da muhimmanci ba, wata hudun nan shi take lissafawa kanta dukda girman cikin da motsin da takeji abin dubawane, ba wannan ne cikinta na farko ba ciki biyu tayi a rayuwarta ta baya sedai dukkansu baau kai matakin da aka busa musu rai ba ta ciresu dan haka ba zata dorar da komai game da yanayin girma ko sanda yake fara motsi ba. Ta dafe cikin da hannu

biyu tana jin wani yanayin nadama mara misaltuwa yana shigarta. Yanzu fa Al'umma zasu iya ringa jifan abinda zata haifa da rayuwarta ta baya ko?

Washe gari Audu na fita Binta ta fice itama, daren jiyan basu kwashe shi qalau ba, Bintan da tayar da bala'i babu rufa rufa tace Audu ya raina mata wayau, watau ciki yayiwa Zubaida a waje can gurin tambadarsu shine ya aurota dan su rufawa kansu Asiri kenan ko to billahillazi ba zata yarda ba seta bankada kowa yaji wannan aika aikar da sukayi baze gurbata musu zuri'a ya hada yayansu da yan uba Shegu ba ta ringa masifa tana bala'i seda ya zabga mata mari ya korata dakinta kafin ya samu sa'ida hayagagar da take masa akai da safe kuwa ko leqata beyi ba dan tayi bala'in bata masa rai akan maganar tata Zubaidan kanta daga bakin qofa suka gaisa ya fita shine Bintan najin fitarsa daman ta shirya itama ta tafi gidan Turai.

"Yanzu ke meye abin daga hankali a nan yanzu? Wannan ai abinda zaki koma gefe kiyi dariya kisha kallo ne idan ma da cikin ta shigo ke ai gaba ta kaiki dan magana na fita dayan biyu ne dole ya sawwaqe mata ta tafi ta nemi uban cikinta idan ma nasa ne dai ta saku tunda dai ba'a Aure da ciki to ai gaba ta kaiki gobarar Titi a Jos Qawata" Turai ta fada bayan da taji bayanin Binta.

Ta numfasa tace

"Zancenki gaskiya ne amma ta yaya kike tsammanin haka zata faru? La shakka idan cikin ba nasa bane wannan kuwa na san ze iya sakinta amma muddin na sane kema kinsa babu inda zataje kuma zama sunyi auran ne daman saboda kauda idon mutane da kuma zargi"

"Banyi muku katsalandan ba Hajiya amma watan auran nan da kuke magana akai nawane tukunna?" Barira me Aikin Turai dake ta goge goge hankalinta na kan hirar su Bintan ta fada. Turai ta harareta tace

"Wai sau nawa zan hanaki tsoma mun baki idan ina magana da mutane? Aiki kikeyi dama ko kuwa zaman gulma shiyasa kika maqalw gaban Tv tun dazu kin kasa gama gogewa kenan?"

"Kiyi haquri hajiya ba gulma bace ba maganar gaskiya ce wanda a ganina duk abinda zaku shirya dole ya zamani kunyi akan saitin da ba za'a ruguzaku ba. Akwai

hanya me sauqi da zakubi ku heganta cikin nan kona Alhajin ne tunda dai an samu tangardar lissafi girman ciki ya zarta watanninsa" Barira ta sake fada bayan ta saki duster da take goge goge da ita ta juya ga abinda tafi iaywa wato hada tuggu da munafunci, abinda ya kaso mata aure kenan kuma ya korota daga qauyensu saboda an mata tambari duk wata Masifa data taso tsakanin kishiya da kishiya a garin In sha Allahu se kaji sunan Barira a ciki ita ta qullota kuma lafiya lau take zaune da nata Mijin tsabar yanda kawa qara da zuwa shari'a gaban me gari akanta yaqi qarewa yasa ya sallameta shine wata qawarta da ta fito Aikatau Birni ta janyota itama suka taho a gidansu Turai waccen take aiki dan haka da sukazo ita kuma tata me aikin sannan ta tafi gida se Mamarsu tace ta dauki Bariran dukda bata so ba dan bata son me aiki babba kodan irin Mazansu ido a mata amma ganin ta iya aiki kuma dai ta ganta kalar gidadawa kamar ba zata yarda da irin wannan abin ba yasa ta karbeta kuma se take jin dadin zama da ita dan Barira badai ladabi da duk cikin iya takunta.

Bi ta da Turai suka shiru sunasauraronta ita kuma ganin sun bata hankali yasa taci gaba da cewa

"Ina itace naji kunce tsohuwar kilaki?" Turai ta gyada kai alamar haka ne, Barira ta gyara zama tana buga cinya tace

"Yo Allah na tuba kwace goruba a hannun kuturu ai shiyafi komai sauqi, ai kamar yanda Hajiya tace miki ki koma gefe kihya kallo to haka zakiyi amma kafin nan se kin basa bam din da ze tayar da kowa, abu daya zafi fada da ze maida Alhaji hayyacinsa in ma cikinsa ne in ma ba nasa bane kawai kice masa kin gano da cikin ta shigo, zuwa sukayi aka kwantar dashi se yanzu da suke ganin ta dan kwana biyu aka tashe shi kina fada masa hala kija gefe kiyi zamanki kawai ki saka ido, in cikinsa nema zaki gane idan ma na wani ne kin haska masa hanya duk ma yanda akayi ze binciko"

"Amma Barira kanki yana kawo haske, to tsaya dagaske ana kwantar da cikin kar kuma mu fadi abinda ba haka ba" Turai ta fada tana jinjina tunani irin na Barira.

Barirar ta sake washe baki tace

"Kai Hajiya yo wannan har wani abun mamakine ko a nan cikin Binni ai anayi. Mu a karkarar mu kihiya tanawa kihiyarta asiri a kwantar mata da ciki se kiga Mace ta hekara goma da ciki ayita cewa Aljanune nan ba asan Asiri aka mata ya kwanta ba in ta dage da neman magani se kiga ya tahi an haife dan to haka idan Yara suka dakko abin kunya hima zuwa ake a kwantar hi se an kwana biyu a daki lissafi yayi daidai se tayar dahi kiga yarinya ta haihu qalau babu me cewa komai"

"To amma ai ita watanta takwas yanzu fa" Binta ta fada bayan data gama hada lissafi akanta. Barira ta sake sheqewa da dariya irinta shegun qauye tace

"Kai Hajiya yane muke ta maimaita magana amma kamar baku ganewa. Dama ai kintatar lokaci akeyi se a daga cikin kinga in ta haihu nan da sati ko biyu ne ai babu me cewa komai tunda ta shiga wata na tara a daki to amma idan kika bullo da wannan maganar ko shekara tayi kanta haihu kin saka kokwanto a zukatan jama'a musamman da daman tana da tambari sannan shi kansa me gidan kinga lissafin da yakeyi na cikin ai be kai asalin watannin qiyasin girmansa ba ko?"

Page 21

Rai fes Binta ta koma gidase da tayiwa Barira kautar Naira Dari biyu tukuici. Ita kadai ta ringa sakin murmushi a hanya harta koma gida nan ta tarar da Lantana rabe qofar daki tana jiranta.

"Ai nazo tuntuni ashe kin fita, Mairo ma tazo ta tafi kin santa ita ba zata iya jira ba" Lantanar ta fada bayan data karni muqullin daki ta bude mata.

Binta ta shiga tana cewa

"Eh ai ita da yake ta fiki tunani tana kuma da abinyi a gida shiyasa ba zata zauna ba tunda babu aikin da zatayi"

"Kai Hajiya" Lantanar ta fada tana yaqe dan taji zafin maganar Bintan kullum haka take yaba mata su da tana da zuciya yaci ace yanzu ta haqura da aiki a gidan gaba daya.

Binta ta shimfide Zakariyya tana miqa tareda wash

"Ai yaci ki dena goyashi haka Hajiya kar ku ringa danne na cikin, in fita ta kama ki ringa cewa na turo miki Aisha ta mana tana tayaki da daukarsa" Lantana da bata daddara ba ta sake fada, se kuma akaci sa'a Bintan ta yarda da shawarar tace zata ringa yin hakan. Tana zaune a Falo tana ayyana yanda maganar nan zata tashi Lantana na share share sega Audu kamar an jefoshi ya fado falon, ta miqe da sauri tana tambayarsa lafiya kuwa yace

"Babu lafiya, yanzu Suleiman ya dawo daga Bechi yake shaidamun Allah yayiwa Babansu Bara'atu Rasuwa, ki shirya yanzu zamu tafi can dukda dai nasan ba zamu samu jana'iza ba amma gara muje din in yaso ma dawo gobe".

Binta taja tsaki bayan data koma ta zauna tana cewa

"Shine ka shigo a gigice har kana fadar mun da gaba na zata ma qata asarar ce ta fadawa Dukiyarmu? To Allah ya jiqan musulmi amma babu inda zani da ranar nan fatsar fatsar".

Zubaida na bacci bacci ya shiga itama ya shaida mata rasuwar, iyakar abinda ta sani kan Bara'atu tsohuwar matarsa ce ba'a fi watanni biyu bama data san itace uwargidansa ba Binta ba a bakin Mairo mewa Binta Girki ranar ta roqeta ta koya mata yanda akeyin Gero da wake shine tace ai Maman Baba ma tana son Abincin a sannan ta tambayeta wacece ita tace mata Bara'atu uwargidan Audun tayi mamaki kwarai jin har yara biyu ne tsakaninsu dan be taba gaya mata ba data yi masa zancen kuma har yajin kwanaki ya mata saboda tace be kyauta ba dakyar suka shirya bayan yaja mata kashedin babu ruwanta da sabgarsa wadda bata shafeta ba, bata san meya rabashi da Bara'atu ba dan haka karta kuskura ta tsoma kanta a ciki shiyasa kidimewar da yayi yanzun da ya gaya mata rasuwar Baban Bara'atun ta bata mamaki, matar daya cire daga rayuwarsa ita da Yayan da suka haifa tare na menene ze dawo dan ta rasa mahaifi?

Haka ta cicciba ta hada abinda zata buqata a yar jaka tana hasaso yanda yan Bechin zasu karbe ta wannan karon, bata sake zuwa ba tun bayan da aka kaita wancan Al'amarin ya faru haka suma A matan Aisha ce kadai tazo babu dadewa tana ciwon Nono Audu yace tazo Kano taga Likita ta kwana hudu a dakin Zubaidan kuma dai lafiya lau babu abinda ya hadasu har suka rabu ta koma.

Bata san banda Binta za'ajwe  ba seda yaceta fito su tafi, ta kulle qofarta tana tsaye jikin dakin Tsakar gida wanda Abdullahi yake kwana ciki kafin a kaishi makarantar kwana tun daga nan kuma idan anyi hutu Bechi yake tafiya da Audu ya tambayi ba'asi yace babu komai be matsa ba ya qyale shi kuma dai be fasa yi masa komai ba tamkar yana gidansa ze aikawa da Aminu kudin komai nasa ayi masa.

"Ba tare da Maman Zakariyya zamuje ba?" Ta tambayeshi jin yace suje,

"Badani za'aba uwar azagwai" Binta dake tsaye kan Baranderta ta turo dauri gaba irin wanda Zubaidan takeyi ta fada kome ta tuna kuma se tayi saurin sakin fuska ta matso kusada ita tana cewa

"Yauwa kar in manta, idan kun dawo daga Qauyen nan akwai taimakon da zakimun. Wlh in gaya miki qanwar qawatace Ibtila'i ya hauta wani shege ya dirka mata ciki, to kuma ta samu Miji Aure nan da wata biyu wannan abu ya faru shine nace ko zaki taimaka ki kaimu inda kuke zuwa a kwantar muku da ciki a samu asiri ya rufu ayi Auran nan idan yaso intayi wata kamar biyar a tayar dashi ko kinga sahu a likafa babu me cewa wani abu".

Sak Zubaidan tayi tana kallonta har ta kai qarshe yanda take doka murmushi kadai ya isa yasa ka gane babu Allah a ranta makirci ne zallah ta hado, waiwayawa tayi ta kalli inda Audu yake tana fatan ace ya rigada ya fita beji wannan maganar da Bintan takeyi ba amma se taga yana tsaye ya zuba mata ido tamkar yanda Bintan take kallonta tana murmushi.

"Kinyi shiru baki ce komai ba" Bi ta ta sake fada har tana dafata fuska dauke da murmushin makirci se ta saka hannu ta tureta tana cewa

"Bani da lokacin Amsa shirmenki"

Binta tayi shewa harda rangada guda tace

"Allah nawa Annabi na uwata, yarinya ba kecw bakida lokacin amsani ba nice bani da lokacinki, kuma shirme da kikace a tsakaninmu za'a tantance wadda take shirme kwanannan, kiyiwa Bara'atu gaisuwa injini kinji Allah ya jiqan Babanta" daga haka ta juya tana kada Mazaune tana waqa abinta.

Zubaida na tsaye inda take ta kasa motsi har seda Audu yayi mata magana kafin ta shiga daga qafa dakyar har suka fita. Seda suka dauki hanya sosai motar shiru babu me cewa qala kafin ya yanke shirun ta hanyar yi mata maganar data saka qirjinta bugawa dam kamar ze fashe.

"Sanda kikace kin zubar da ciki dagaske kike ya fita ko kuwa qaryarku ta yan bariki kikayimun?"

A razane ta kalleshi, hankalinsa na kan titi fuskar nan a hade tam kamar ta shanu. Shiru tayi zuciyarta na tsinkewa, takalarta yakeyi da masifa ita kuma bata shiryawa hakan ba bata da kalaman da zata kare kanta dasu a yanzu ta tabbatar matarsa ta rigada tayi masa famfo shiyasa ta tayar da wannan maganar a gabansa qila kuma ta rigada ta fada masa abinda take so ta fada wannan da tayi fami ne ta barbadawa ciwo gishiri.

"Ba magana nake miki ba kin mayar dani dan iska kinyi shiru" ya fada cikin masifa harda buga sitiyari, Zubaidan ta zabura saboda tsawar ta shigeta amma a maimakon tayi magana se kawai ta fashe da kuka. To me zata ce masa dan Allah?

Kwafa yayi be sake ce mata komai ba har suka isa Bechi, sun tarar da Anyi Jana'izar Babansu Bara'atu, a qofar gidan suka tsaya daman ya fice ya barta a motar ya tafi gurin Maza masu karbar gaisuwa Tilas ta fita ta shige qofar dataga Mata na shige da fice. Bata san kowa ba dan haka ta tsaya tana raba ido,

"Ashe tare kuke" taji an fada daga bayanta ta waiwaya ganin Aisha yasa ta saki ajiyar zuciya a qalla taga wanda ta sani.

"Muje ciki" ta sake fada mata se tabi bayanta suka ratsa matan dake zaune ta gaishe su tareda yi musu ta'aziyya kafin suka dangana da Rumfar Inna Hajara.

Anan taga Bara'atun tana rakube gefe ta sake zama fiyat da ita ga tashin hankalin mutuwar data riskesu ta farat daya idan ka ganta gwanin tausayi. Aisha ce ta gabatarwa da Bara'atu da ita. a matsayin Amaryar Audu, suka sake gaisawa kafin Aishar tace su koma tsakar gida dan yafi iska. Bayan su. Zauna Bara'atu da kanta ta fito ta kai mata ruwa da Kunun Tsamiyar da aka kawo na sadaka tace

"Ki dan sha wannan kafin a sauke abinci"

"Nagode" Zubaidan ta fada a sanyaye badan zata iya sha ko cin wani abu ba dan jiki da zuciyarta gaba daya batajin dadin da zata iya saka wani abu a bakinta a halin yanzu. Sunyi jugum jugum Aisha tace

"Itace matar Yaya Audu ta farko, Makircin Binta ne ya fitar da ita daga gidan ta qulla mata sharrin wai ta kashe mata Jariri ranar suna"

Qirji Zubaidan ta dafe tana zare idanu, tuna a inda suke yasa ta saisaita kanta cikin kaduwa tace

"Kashe jariri?"

"Wlh fa, kuma sharri tayi mata dan wlh ko kiyashi Bara'atu ba zata kashe da gangan ba balle mutum sahun barawo ta taka yaron dama ya rasu shikenan suka liqa mata sharri daga shiga dakin shi kuma Yaya Audu babu binciken komai ya yanke hukunci dalilin mutuwar Auranta kenan shekara Uku yanzu".

"Uhm" kawai Zubaida ta iya cewa, wato ashe nata tuggun da take shirin qulla mata me sauqi ne akan na Bara'atun kisan kai fa kuma na rashin Imani ace Jariri ka kashe wannan ai tayi mata tambarin da ba kowanne Namiji ne ze iya dauke kai ya aureta ba wadda ta iya kashe dan Jinjiri babu tausayi ai kisan babban mutum qaramin abu ze zama a gurinta.

Haka ta ringa jimanta maganar jikinta ya qarayin sanyi qalau da Al'amarin gida Audu, taga Babangida da Babannan sun girma Masha Allah musamman da suna da garin jiki irin na gidansu se suka tashi kamar yan biyu sedai duk su biyun suna nan a hargitse yaran qauye dai sak to uwarsu bata da nutsuwar zuciya balle ta iya samun damar kulawa dasu yanda ya kamata, Manema uku ta samu bayan rabuwarta da Audu biyu duk ba yan garin su bane amma da sunyi zuwa daya biyu za'a samu wani annamimin da zeje ya soke maganar sedai taji shiru ba zata sake jin duriyarsu ba wannan abin yasa ta shiga damuwa matuqa ga tunanin Audu da soyayyarsa data qi barin zuciyarta sedai ta sani ya mata nisa bama ta yiwa kanta fatan komawa gidansa Addu'arta daya ce a kullum ubangiji ya warware mugun qullin da Binta tayi mata ya wanketa a idon Audu da duk wanda ya yarda da sharrin da aka mata.

Se Yamma Aisha da Zubaida suka bar gidan rasuwarz babu motar Audu a waje hakan ya tabbatar musu ya wuce gida dan haka ta rakata can kafin ta wuce gidanta itama dan Magriba ta kawo kai.

"Kace badan wannan rasuwar ba qila da sedai kuzo kawo mana Jariri ko Jinjira" Goggo Fadi ta fada sanda Zubaidan ta shiga dakinta gaisheta ta tarar da Audu a ciki. Bece komai ba itama bata amsa ba se kanta data qara yin qasa dashi.

"Ya kamata ka ringa qoqartawa Iyalanka suna zuwa gida akai akai cikin dangi, kaga dai Amarya rabonmu da ita tun randa aka kawota kuma kai kana zuwa koda ba ka kwana yaci karinga tahowa dasu a haka za'a saba sosai ai" Goggo Fadin ta sake fada se sannan Audun yace

"Za'a gyara in sha Allah, bari naje an fara kiran sallah" ya miqe ya fita Zubaidan ma fita tayi ta dauro Alwala tayi sallah nan dakin Goggo Fadi Saude ta kawo mata tuwo bayan ta sauke ta dan tsakura saboda yunwa ta fara sakadarta tana nan zaune Goggo Fadi na janta da hirarraki duk a takure take ta gaji tana so ta kwanta amma

bata san inane masaukinta ba bataga kayanta a dakin Goggo Fadi ba balle tace a nan zata kwana shi kuma tunda ya fita be dawo ba balle ta tambayeshi.

Be shigo gidan ba se da goma ta gota lokacin ta gaji ta kwanta a dan gadon Goggo Fadi da take tayi mata tayin tun da taga tana gyangyadi daga zaune amma taqi hawa tana kwanciya kuwa bacci ya kwasheta se ji tayi yana tashinta sukayiwa Goggo Fadin sallama tana biye dashi har bangaren dake gefe wanda aka kaita randa sukazo Bechi tana Amarya. Daki daya ya bude ya shiga tabi bayansa, dakin da aka sauketa ne wancan lokacin se yanzu ta kalleshi da kyau cikin dakin ba zakace a qauye kake ba tamkar Dakunansu na Kano Bango yasha Fenti haka qasan dakin Malale da Kafet ga bandaki a ciki har wayarin din ruwa da akwai.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Fita yayi ya barta a dakin, ta shiga bandaki tayi uzurin da zatayi ta fito ta bude jakarta data gani ta canza kaya kafin tabi Lafiyar Katifa bata sake motsawa seda aka fara kiraye kirayen sallah ta farka ta ganta ita kadai Babu Audu a dakin yanayin gurin kwanciya kuma ya tabbatar mata da ita kadai ta kwana kan katifar dan babu shaidar an kwanta daya barin to Ina ya kwana? Data tuna da wani dakin a gurin seta bar zancen a ranta tana jinjina wato lamarin yayi tsamarin da baze kwana daki daya da ita ba kenan ai shikenan. Tayi wanka bayan da tayi sallah ta shirya tsaf abinta be shigo ba seda gari yayi haske lokacin har Saude ta kai mata abin Kari Ruwan shayi a fulas se wainar kwai da qaton Burodi ta fita kawo mata Madara da Bonbita ya shiga dakin yana wani cin magani ta gaishe shi ya amsa a daqile yana gaya mata tayi sauri da wuri zasu tafi.

Haka suka kamo hanya bayan sun biya gidan Rasuqar sun sake musu gaisuwa, tana zaune cikin mota tana leqensa suna tsaye da Bara'atu daya saka aka masa magana da ita, bata san me suke cewa ba hankalinta yafi tafiya ga Yaran da suka zagaye shi amma daga nesa kowanne ya tsaya irin suna son zuwa gunsa amma babu shaquwa ko fuskar yin hakan se taji wani iri a ranta, to su kenan ma da aka rabasu da ubansu ta qarfi da yaji inaga ita da Ake shirin sheganta abinda zata haifa ta yanda ma baze samu ko Alfarmar kiran kansa jininsa ba?

Kwalla ta ziraro mata tayi saurin dauketa ganin ya nufo motar, taga sanda ya bawa Bara'atun Kudade masu kauri amma ta girgiza kai taqi karba kana taja yaranta suka

shige cikin gida da alama wannan abun ya sake tunzurashi dan motar kanta fizgarta yake kamar zasu tashi sama ita dai ta qanqame jikinta har sukaje gida babu wanda yacewa dan uwansa qala.

AUDU

Tunda suka baro Kano abin duniya ya taru yayi masa yawa haka nan maganganun Binta suka samu matsuguni a zuciyarsa dukda ba kaitsaue tayi magana dashi ba amma se ya ringajin kamar saqo ta bashi, girman Cikin Zubaidan ya jefashi a kokwanton da sam be taba shiga ba se yanzu da Binta ta soko wannan maganar sannan tambayar da yayi mata akan Cikin datace masa ta zubar a baya da shirun datayi ya sake jefashi cikin rudani wannan tasa bayan sun Isa Bechi yabkasa zama har seda ya nemi qarin bayani akan Kwantar da ciki da tayarwa da yaji a zancen Binta.

"Falalu ya fara tara da zancen a gurin zaman makoki da suka hadu a maimakon ya bashi amsa se kawai yayi dariya yace me ya hadashi da shirmen Mata a bakinsu yake jin wani Kwantaccen ciki amma shi be yarda da akwai shi ba. Shaidan ya rigada ya samu abinda yake so yayi kane kane a zuciyarsa haka nan ya jefa masa wasi wasi kala kala, sam ya kasa nutsuwa shiyasa daya fita salkar Magriba kai tsaye ya wuce gidan Bilki dukda ba shiri suke a yanzu ba tun bayan abubuwan da suka faru amma da yake buqatarsa ce yau ta tashi se gashi a gidanta. Tasna Yazo Bechi dan tun rana Labari ya isar mata ta bar gidan raauwar babu dadewa su kuma suka shigo daman kuma Audu na shiga Bechi labari ze karade ko ina kafin Alkhairin kyautar sa ya isa gida gida wannan lazim duk zuwa zeyi rabon abinda ya samu wa jama'ar gari musamman a baya zamanin da suke tare da Bara'atu sunfi zuwa garin sosai yanzun yakan jima beje ba amma duk in ya shiga dai zeyi Alkhaiti daidai yanda hali ya bayar.

A dakin Bilki ya zauna ya rafka tagumi yana sauraronta bayan da yayi mata tambaya akan gaskiyar ana iya kwantar da ciki tsayin wani lokaci sannan a tayar dashi sanda ake so?

"To zancen gaskiya anayi dukda dai ban tabayi ba kuma ban taba ganin wadda taje akayi mata ba amma na samu labarin mutane da yawa da hakan ta faru dasu, kaga babu nisa nan gidan Malam Ado ai kasan Ila Abokin Baballiya ta shima ba'a jima ba anyi irin wannan dambaruwar gidansa yayi Aure matar watanta shida ta haihu. Yar Umarawa ce ya aurota daman dai tun lokacin bikin aketa surutai akan yarinyar kamar magana ta dakko shine iyayenta suka tada auranta babu shiri, hatta dakin da

ya sakata fa ubanta ne ya bashi kudi ya qarasa ginashi saboda yace be shirya Aure ba basu karbi Lefe ba kuma karka so kaga uban kayan garar da aka hadota dashi bana tsammacin sun qare har yanzu.

To a yanda Zainabu dai take cemun (kishiyarta) kasan Qanwarsa ce yayan Maza suke wai Amaryar watanta biyar sega Ciki ya fito qato kamar zata haihu gobe, kuma sunce sudai lokaci daya sukaga wannan abun mamaki da fara laulayinta da girman cikin befi watanni ba tofa ciki nayin qato daman akwai qanwarta da aka hadota da ita ta shirya ta tafi can garinsu satinta daya sega Babarta tazo ganinta wai ya akayi ya akayi ta tattarata suka tafi gida wai bata da lafiya za'a nema mata magani ba'a rufa wata ba akace ta haihu, su Zainabu sunje sun gano yar ance musu bakwaini ce to tace Aradun Allah wannan ya idan ka kalli idonta ma zakace ta shekara a ciki kuma qatuwa da ita tabarakallah in taqaita maka zance dai anyi wata uku da haihuwar yanzu Auran yake da wata tara tana can gidansu har yanzu bata dawo ba".

Wannan labari na Bilki ya sake bashi tabbacin maganar da Binta ta fada ana haka kenan, amma wace hujja ze kama ta cewar Zubaida ta shigo gidansa da ciki? Sannan wane tabbaci yake dashi akan kwantar da ciki tayi ta shigo masa dashi gida? Dole ya tsananta bincike ya gano koma menene amma yanda al'amarin ya kasance lokaci daya ciki yayita girma kamar na Aljanu ya bashi mamaki shi kansa. Be gayawa Bilki dalilin tambayar ba duk nacin data yi masa ya tattara ya tafi amma ya kasa komaqa cikin gidan can wani guri ya samu ya zauna yana ta lissafin ya zeyi idan ta tabbata da ciki Zubaida ta shigo masa ba nasa bane ba?

Seda yaga dare ya farayi ya koma gidan ya rigada ya cusawa ransa wani abu na daban shi yasa ya kasa koda kwana daki daya da ita ya bude dakin da Binta take sauka ya kwana a ciki. Har mamakin kansa ya ringayi yanda ko sau daya be taba tunano rayuwarta ta baya yaji ya qyamaceta ba ko ya kasa mu'amalantarta amma yanzu yaji ta fita a ransa akan abinda be gama tabbatarwa ba. Haka suka dawo Kano nan kuma zamansu ya dauki sabon zama ya fita a sabgarta tsakaninsa da ita ya ajiye mata kudin cefane idan ya kwana a dakinta kenan in tayi abinci bayaci gaba daya ya birkice saboda rashin nutsuwa daya sakawa ransa.

A bangaren Zubaida kuwa gaba daya ta maida hankalinta gurin Ibada ne da kuma kula da lafiyarta data abinda yake cikinta tayi matuqar qoqari gurin ganinbata bari damuwar Audu tayi tasiri a ranta ba haka duk iskancin da Binta zata mata bata daga kai ta kalleta yanda kuma be sake mata tambayar da yayi mata randa sukaje

Bechi be itama bata daga maganar ba a haka suka kwashi tsayin sati biyu cikin wannan hali. Da safiyar ranar Asabar tana zaune daga bakin qofarta ta cire saiqoyin data jiqa ta shanya su kafin ta gama shanye ruwan daya jiqun seta maidasu, tana zaune kan Tabarmar data shimfida da yar Radionta a gefe tana sauraro ita kadaice a gidan tun safe Audu da Binta suka fita kamar yanda taji a bakin Bintan tana bawa qawarta da taje gidan labari Audun ya biya mata Aikin Hajji fitar da sukayin tana kyautata zaton duk cikin shirye shiryen tafiyar ne dan abin ya matso a kwanakin kusan kullum se sun fita.

Taja Qaton kofin robar dake cike da ruwan magani ta kurba ta ajiye ta saka hannu biyu tana shafa cikinta da taga kamar yayi qasa sosai kuma ya dan rage girma, sam bata ji shigowa ko sallamarasu ba saboda ta nitsa cikin tunani se maganar Binta taji akanta tana cewa

"Ahaf, ka gani ba? Wasu jiqe jiqen aka qara kawo mata bana gaya maka wannan tsohuwar Matar Babanta ce take mata safara ba kullum tana tafe gidan nan yau ta kawo wannan gobe ta kawo wancan gashi nan kuwa cikin ya fara komawa za'a sake danne shi qila ace mana anyi bari se wata shekarar a haife shi tunda mun ramfo wannan wayon ko?" Bintan tayi maganar tana zuba mata ido fuska a washe irin duniya ta mata dadi babu abinda yake damunta duk da cewar bata tsammaci za'aja lokaci ba wannan Bam din data dana be tashi ba amma kamar yanda Turai ta gaya mata tabi komai a hankali dai kar suyi gaggawa to tana zuba ido taga yanda wasar zata kaya.

Audu bece komai ba ya wuce samansa, jiki a sanyaye Zubaida ta miqe ta shiga tattara abubuwanta Binta natsaye tana zubda mata habaici,

"Ke kin dauka zaki kawo mana shege wato kici bulus bamu gane ba? To qaryarki tasha qarya wlh tun wuri ma ki nemo farkan daya dibga miki ciki ki nana masa abinsa badai a gidan nanba kar muke kallonki"

"Wlh Binta ki tsoraci gamuwarki da Allah" Zubaidan ta fada hawaye na sakko mata, Binta tayi shewa tace

"Nan da sati i yanzu ina gaban Ka'aba yarinya in shafata in roqi Allah yayi gaggawar tona miki asiri ki tattara ya naki ki barmin gida gayyar tsiya gayyar na'ayya"

"Allah baya bacci" Zubaidan ta sake fada daga haka ta shige dakinta. Tana zaune Audu ya shiga ya zauna akan Kujera yana fuskantar ta, irin zaman da yayi yass gabanta ya shiga faduwa, cikin kaushin murya yace

"Zan sake tambayarki bana buqatar qarya ko wani alaye ki fada mun gaskiyar magana Cikin da kikace kin zubar dagaske kike ko kuwa kwantar dashi kikayi?"

Kuka ta fashe dashi ba tareda ta sgirya ba tace

"Yanzu ka dauki maganar da take fada dagaske kenan? A ina ka taba ganin an kwantar da ciki? Idan ma anayi tayaya ciki ze kwanta tsayin sama da shekara daya a Jikina ace baka lura ba wai me yasa akai baka amfani da kwakwalwarka se abinda matarka ta kitsa maka ba tareda bincike ba ka hau kai kawai ka zauna?"

"Nine bana amfani da kwakwalwata?" Ya fada yana nuna kansa, a duk maganganun babu abinda ya tsinta se wannan, ta miqe cikin kuka tace

"Kwarai, kwakwalwarka hotoce Audu domin bata aiki se abinda wani ya kitsa maka dashi kake tunani. Ya za'ayi ka kasa tantance gaskiya da qarya? Se yaushe idonka ze bude ka gane tuggu da makircin da matarka take shirayawa a cikin gidan nan? Ta laqawa uwargidanka sharrin Kisa shine zata shegantaka maka Da ko Ya ka hau kai ka zauna?

To wlh na gaji bazan iya wannan rayuwar ba, ba zan zauna da mutumin da besan daidai ko abinda ya kamata yayi a matsayinsa na Namiji ba, bazan cigaba da zama ace Kishiya ita zata tsara mun irin zaman quncin da zanyi a cikin gidan aurena ba.

Ka fito fili ka fadi abinda yake ranka ka fadi cewar kana kokwanton cikin jikina karka sake sakayawa ko ka titsiyeni da tambayar abinda ya shafi rayuwata ta baya, ka fadi kai tsaye Matarka ta kitsa maka cewar cikin jikina ba naka bane kuma ka hau ka zauna babu abinda zance maka kuma banida amsar da zan baka a yanzu se dai nace maka mu jira lokaci, ubangijin daya wanzar da samuqar cikin ze qarware duk wani qulli da ake qoqarin laqaba masa amma kafin nan ka sani bazan iya cigaba da zama da kai ha Audu gidanmu zan tafi zanje na qarasa rainon cikina a can har Allah ya saukeni lafiya abinda na haifa ya raba gardamar zargin da kake neman laqabamun" tana gama fadar haka ta shige daki tana Kuka ta hau hada kaya.

Laqwas yayi akan Kujera kamar kazar dataji ruwan zafi, ya yunqura ze miqe kenan Burum Binta ta fado dakin tana cewa

"Babu shakka daman ance tabarmar kunya da hauka ake nadeta kana zaune tayi maka wasan kwaikwayo da salonso na Tsofaffin kikali ko? To ai idan kina da gaskiya fitowa zakiyi ki kare kanki baqai ki hau koke koke kina hada kaya ba kaga magana ta tabba da ciki aka shomigo mana so take ta tafi se ta koma inda za'a rufe maka baki ruf ka kasa cewa komai koda yake yanzun ma naga kamar bakin naka a rufe yake ai"

"Banida lokacinki ki kuma jirayi sakamakonki komai nisan tsahon zamani" Zubaida data fito da jaka ta fada tana gotata. Tana fita Audu da Bintan suka rufa mata baya Binta na shewa kamar sabon shigan hauka tana tafa hannu.

"Subhanallahi me yake faruwa haka" suka tsinkayi muryar Yakubu da shigarsa gidan kenan yana fada, Zubaidan taci burki kuka yana sake kwace mata Binta ta gyara tsayuwa murya a sama tace

"Me fa ya faru Yaya Yakubu? Abin kunya tayi asirinta ya tonu kuma shine take mana qaramin hauka".

Zuciyar Yakubu ta tsinke ya tafi wani tunani na daban seya kalli Audu dake nan tsaye qato dashi kamar wanda kwakwalwarsa ta bata se zare ido yake yace

"Me ya faru? Ban fahimci abinda take cewa ba?"

"In maka gwari gwari Yaya Yakubu, ciki. Shege tayo take neman laqawa qaninka ta gurbata muku Zuri'a" Binta ta sakeyin caraf ta amshe tamkar sunanta ya koma Audu.

"Hasbunallahu wani'imal wakeel, Audu dagaske ne abinda take fada?" Yakubu ya fada yana ja da baya dan ya samu balance sosai jin wannan babbar magana.

Page 22

Wuta ta daukewa Yakubu sanda Binta ta gama rattaba masa abinda ya faru dan ita ta zama bakin Audu yau. Ya ringa kallon Audun yana jira yaji ya qaryata ko ya fadi akasin abinda Bintan ta fada amma yaga yadauke kai gefe yana wani cin magani se ya maida kallonsa kan Zubaida dake irin kukan nan da meyinsa ya gaji dayi, tausayinta ya rufeshi gefe daya takaici da tsanat Bi ta me girma tareda qyamatar Hali irin na dan dan uwansa suka kamashi.

"Ku Fita ki bamu guri" ya fadawa Binta da Zubaida.

Zubaida ta miqe ya kalleta yace

"Kar kije ko ina ki koma dakinki" ta juya ta fita Binta ko ta gyara zama, cikin kaushin murya yace mata

"Zaki fita ko sena kwasa miki mari a nan gurin?"

shidin ba ma'abocin zafi bane amma bashida wasa musamman a gurinta sam basa ga maciji yanda kuma ya hade gida ya tabbatar mata ze iya kwasa mata mari idan bata tashi ba kamar yanda ya bara umarni dan haka ta miqe tana qunquni.

"Nayi maka uzuri domin bayan Kaidin Mace Jahilci da duhun kai suna dawainiya dakai Audu lokaci yayi daya kamata ace ka koma Makaranta Both Islamiyya da Boko" Yakubun ya fada bayan fitar Binta wadda ta labe a bakin qofa ta kasa kunne tana jiran taji me zasu tattauna. A zabure Audu ya kalle shi yace

"Ni kake kira jahili?"

"Qasurgumi ma kuwa" Yakubun ya bashi amsa idonsa fes a kansa kafin yaci gaba da cewa

"Banda kai wawane wanda bashida tunanin kansa se abinda aka kitsa masa kuma Jahilci yana dawainiya da kai ta yaya Mace zata zo maka da irin wannan maganar shirme wadda ko yaro qarami aka gayawa dariya zeyi amma ka hau kai ka zauna harka sheganta cikinka da kanka wane kalar wawanci ne yake damunka Audu? Binta ce ta auro maka Zubaida da zatayi maka lissafin cikinta ka yarda ko kuwa? Watanta nawa yau a gidanka? A lissafin watan sama auranku ya shiga wata na goma ma kaga kenan cikinta har yazarce watannin da Da yakeyi kafin a haife shi kuma da zata ce maka Da ciki ta shigo kwantar dashi tayi kai mahaukacine da ka kwashe tsayin lokaci tare da Mace da ciki amma baka gane ba ko kuwa akanta ka fara Aure balle kace baka san yanda alamar ciki take ba?

Wato ita da yan uwanta sun laqabawa Bara'atu sharrin kisan kai sunci banza shine yanzu ta sake fitowa da wannan sigar kai kuma ga Raqumi se yanda aka juya akalarka ta fada ka hau ka zauna akai..."

"To ai ba qarya Binta ta fada ba hakan zata yiwu tunda ita Zubaidan da bakinta ta gaya mun tayi ciki tun kafin na dawo da ita gidansu kuma ni ban tabbatar da tace ta

zubar dagaske ne ko qarya takeyi ba. Sannan ba Binta kadai ba har Bilki seda na tambaya ta tabbatar mun ana iya kwantar da ciki yafi shekara sannan a tayar dashi idan ba haka ba tayaya za'ayi ace ciki yayi wannan girman a wata daya" Audun ya fada a fusace zuciyarsa na tafarfasa na yanda Yakubun ya zageshi ya kirashi Jahili. A fusace shima Yakubun yace

"Ta yanda Allah ya rangwanta maka hankali da tunani kake kasa banbance tsakanin daidai da rashi Sa ta haka yayi ikonsa ya girmar da ciki a wata daya, Kai wane irin mutum ne Audu? Anya kwakwalwarka a daidai aka dasa maka ita kuwa?"

"Karka sake zagina kuma karka sake dangantani da hauka" Ya fada yana miqewa tsaye,

"Idan na kuma zaginka zaka rama ne? Na fada kai wawane shashasha wanda bashida tunanin kansa se abinda waccen yar iskar Yarinyar da idan tayi wasa ba zataga annabi ba ta shirya maka. Ka auro shaidaniyar Mace tana neman ta Halakar da kai, to bari kaji ka farka tun kana da sauran lokaci idan ba haka ba kana ji kana gani zaka tafi lahira yanda haqqi ze kaita wuta haka zata kama hannunka ku shiga tare...."

"Na shiga uku ni kake kake cewa yar wuta Yaya Yakubu?" Binta ta fado musu hannu aka tana kwakwazo, cikin daga murya Yakubun yace

"Ke munafuka ce, munafuki kuma Allah da manzonsa sun rigada sun fada mana makomarsa idan har ya mutu be tuba ba. Cikin Halayan manyan munafukai wannene bakiyi?

Qarya, Ha'inci, Zalunci, Annamimanci sannan ga tulin haqqin mutane da kika dauka dana Aure da kika lalata kina tsammatar idan baki nemi yafiyar wadanda kika zalunta ba zaki wanye lafiya da duniya ne?

To dakai da ita kar ku fasa duk abinda kukeyi duniya ce gaku gata nan kuma kanku kuke rusawa, Zubaida kuma babu infa zataje a gidan nan zata haife abinda yake cikinta tunda kai baka san shari'a ba bari na gaya maka koda ciki ta shigo gidanka muddin ta yi watanni shida kafin ta haihu Shari'a ta baka Dan koda kana kokwanton ba naka bane balle kuma wane tabbaci zamu samu idan ma da cikin Tazo ace ba naka bane tunda a yawon tambadanci daman kuka hadu? Baka ga komai bama

tukunna Abdulwahab kabi duniya a sannu idan ba haka ba ranar kuka na tafe" yana gama fadar haka ya fice daga falon.

Seda Binta ta tabbatar da ya sauka qasa kafin ta kalli Audu tace

"Lallai wannan shi ake kira ga Mari ga tsinka jaka, yanzu shi Yaya Yakubu saboda qin Allah shine ze ringa fadar maganganun nan saboda ba shi ake shirin liqawa shege ba? Ni anya kuwa cikinku daya da Yaya Yakubu nan?"

"Karki kuskura ki zagarmun Dan uwa babu ruwanki duk abinda ya fada a kaina dan ya isa ne" Audun ya dakatar da ita cikin kaushi idanunsa sun kada sunyi jajir saboda bacin rai, ta sunkuyar da kai irin na shahararrun Makirai tace

"Allah ya baka haquri ai ba wani abu nale nufi ba kawai dai gani nayi kamata yayi ace ya tayaka qyamatar wannan abin ba wai ya goyi bayan a cuceka ba amma kayi haquri idan ba bata maka rai" sum sum ta fice daga dakin itama zuciya fari qal dan tasan ko iya tijarar da Yakubu yayi masa dalilin Zubaida ta isa ta qara tunzurashi tunda shi mutum ne me Izza da tsananin son girma.

Bayan fitar Yakubu daga Bangaren Audu dakin Zubaida ya nufa, tana zaune bakin qofa tayi tagumi bata ko bude ba balle ta shiga cikin ta zauna kamar yanda ya ce mata ganinsa yasa ta miqe tsaye a yanayi na bacin ran da yake ciki ya ce mata

"Bude qofar ina son magana dake"

Ta bude suka shiga ya zauna akan kujera ita kuma ta zauna a qasa sukayi shiru na dan wani lokacin kafin ya nisa yace

"Ina so ki gaya mun tsakaninki da Allah shin da akwai wani abu da kika aikata da har ya sakawa Audu kokonton cikin jikinki a ransa"

Tayi raurau tana shirin fashewa da kuka, abin ya hade mata biyu ga damuwa ga yanayi na ciki Yakubun yayi saurin cewa

"Ki bar koke koken nan haka kodan lafiyar abinda yake cikin ki kiyi mun magana kawai"

"Allah shine shaidata babu abinda nayi wanda har ze cefa kokontona a zuciyar Audu. Haduwata da shi zuwa maidoni gida da yayi gaba daya ya faru a dan taqin lokaci shi shaidane akan cewar tunda na dawo gidan mu nayi tuba na gaske babu inda nake zuwa babu wanda yake zuwana wata magana bata qara hadani da Namiji ba idan ka cire mahaifina she shi Audun ballantana har wani mugun Al'amari ya faru har aka daura mana aure na tare a gidansa, kuma a cikin gidan nan ma nayi Al'ada balle yace da ciki na shigo kuma har sanda cikin ya bayyana duk be nuna wata damuwa akai ba seda Matarsa ta dawo daga gidansu sannan abubuwan suka canza"

"Ita ta kitsa maganar kenan, Binta! Binta! Wannan yarinya anyi shaidaniya amma babu komai karki saka damuwar komai a ranki ki kyalesu daga shi har itan kici gaba da kula da kanki da abinda yake cikinki. Idan kinji gidan ya miki qunci ki taho gidanmu tare mukazo da Balaraba kuma zata jima a nan dan zan tafi na barsu se na dawo sallah sannan zamu koma baki daya sannan dan Allah maganar nan ta tsaya ikar cikin gidan nan karki gayawa kowa in sha Allahu komai ze warware kansa kinji" Yakubu ya fada mata cikin lallashi. Ta share kwalla tace

"Shikenan zan zauna kamar yanda kace zan kuma cigaba da roqon Allah daya zabamun mafi Alkhairi, tabbas nayi dana sanin Auran Audu saboda bansan haka yake ba. Ban taba tsammanin bayan tsamoni da yayi daga rayuwata ta baya ba kuma zeyi amfani da hakan ya rusamun rayuwar dana ke qoqarin ginawa a gaba. Yanzu idan yaqi karbar dan da zan haifa ya zanyi? Da wane ido duniya zata kalleni?"

"Karki sake fadar haka babu abinda ze faru da kuma halastacce da ne da kansa ze amshe shi ba tare da wani ya tilasta masa ba, kedai Allah ya sauke ki lafiya kawai kinji kiyi haquri kuma kici gaba da Addu'a" daga haka yayi mata sallama ya tafi ta maida jakarta daki amma bata bude ta ba domin har zuciyarta bata aminta zata iya cigaba da zama da Audu ba. Bata shiryi qare rayuwarta cikin qunci da baqin cikin Miji da kishiya ba. Ta sani daman dole zata riski qalubale masu tarin yawa a rayuwarta amma bata tsammaci ta haka zasu bullo mata ba.

Shiru shiru ta tsammaci Audun ze shiga ya mata masifa amma har wayewar gari bataji duriyarsa ba haka suka kwana biyu ko qofar dakinta be leqa ba se a kwana na uku da dare tana zaune ya shiga ya tsaya daga bakin qofa ya miqa mata takadda fara a linkife fuska babu Annuri ta karba ta bude bata iya karatun boko ba dan haka ta mayar ta rufe ta ajiye a gefenta ba tareda ta tankashi ba.

"Baki ce komai ba, ko bakiga abinda yake rubuce a ciki bane" ya fada cikin murya me kauri, ta daga kai ta kalleshi irin kallon nan na daidai nake da lokacinka kafin tace

"Ka rubuto mun da Ajami idan kana so na gane abinda yake ciki har na baka amsa". Yaja tsaki ya koma inda ya fito. Tun randa Yakubun yazo yake auna daya da biyu akan yuwuwar ya amince da cikin jikinta amma ya kasa, Shaidan ya rigada ya yi kane kane a zuciyarsa yana raya masa abubuwa kala kala ga qaramar shaidaniyar dake nan gefensa tana qara ingizashi, duk yanda yaso daya daure yayi mata uzuri ya kasa musamman idan ya tuna dalilinta Yakubu ya yaba masa baqaqen maganganu ya kirashi jahili se yaji babu abinda zeyi ya huce irin ya saketa kawai hakan ko yayi ya rubuta mata saki har biyu a takarda ya linke ko Binta bata san da ya rubuta sakin ba se da kuma ya bata sannan yaji cewar yayi wauta data bude yaga babu damuwa ko kidima a fuskarta. Tuna masa da tayi bata iya karatu ba ya sanyaya masa zuciya kenan bata san me takaddar ta qunsaa ba da wannan sanyin ya juya ya tafi yana ayyana ze dawo ya dauke takardarsa kawai ya fasa.

Safiya nayi ta shirya ranar Asabar baya fita da wuri kuma da yake yanayin sanyi ya fara kankama kowa na daki yayi luqui a ciki. Ta dauki jakar kayanta da takardar daya bata ta kama hanya, tsakaninsu da gidan Yakubu babu wata tazara me nisa dan dayan tsallaken Titin Audun ya maida masa da filin sa daya karba yayi madaidaicin gida. Ta zabi da taje gidan Yakubu ne saboda ko babu komai shidin ya jibanci lamarinta sannan tana tsoron yanda Mahaifinta ze karbi wannan Al'amarin idan taje tana buqatar wanda zeyi masa bayanin da ze sauqaqa masa tashin hankalin da komawarta gida da cikin da ubansa yake kokonto ze jefashi a ciki.

Balaraba na tsakar gida tana kauda kayan wasan yara da bata samu ta kwashe jiya da suka gama wasan ba taji ana qwanqwasa Get ta bude ganin Zubaidan ya bata mamaki sedai labarin da Yakubu ya bata na abinda ke faruwa a gidan Audun ya kauda mamakin nata ta matsa mata ta shigo tana mata sannu kafin ta karbi jakar hannunta. Bayan sun nutsu a falo, ta kawo mata Ruwan shayi da su madara da burodi tace

"Bari na soya dankali, bari nayi da se sun tashi a bacci tukunna"

"Ki barshi wannan dinma ya isa" Zubaidan ta fada a sanyaye amma Balaraba ta wuce kitchen tana ce mata yanzu zata gama.

Daidai wanda zataci ta soyo mata da kwai ta kawo, ta kalli kayan shayin na nan yanda ta ajiye su tace

"Na dauka kin hada shayin ya sarara kafin ma gama? To bari na hada miki"

"Baqi mukayi ne?" Suka jiyo muryar Yakubu dake fitowa daga daki yana tambaya. Balaraba ta amsa da cewar

"Baquwa dai" ya qaraso ciki yana kallon Zubaidan sam beyi mamakin ganinta ba domin yasan halin taurin da kafiya irin na dan uwansa. Yayi mamakin da har aka kwana hudu ma sannan ya ganta a gidan nasa.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh Iallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

Seda suka gaisa kafin ta zaro takardar da Audu ya bata ta miqa masa ba tareda tace komai ba, ya bude ya karanta yayi shiru kamar ruwa ya cinye shi kafin ya ninketa yana sauke ajiyar zuciya ya miqe tsaye.

"Ki gyara mata dakinki seta zauna ciki kafin muga abinda Allah zeyi" ya fadawa Balaraba ya shige ciki. Balaraban ta miqe a sanyaye tabi bayansa ita kuwa Zubaida Fulas taja ta shiga hada shayi daidai wanda ze isheta ta tabbata dai saki ne a cikin takardar, ita kuma a kullum ta tashi Addu'a bata mantawa da neman zabin Allah a dukkan lamuran rayuwarta dan haka duk abinda ya sameta zata karbeshi da kyakykyawan Ikilasi.

A dakin Balaraba tayi masauki tana ta jaddada mata ta saki jikinta tamkar tana gida. Bayan da su Dada da qannenta biyu suka tashi daga bacci su suka ringa debe mata kewa harta manta da damuwar data kawota gidansu ta ringa jin zumudin itama dan cikinta ya fito duniya ta tabbatar koshi ya isa ya ringa bata nishadi yana debe mata kewa. Ta tuna sanda tayi cikin da bayan zubar dashi Audu ya maidota gida a lokacin taso ta bar cikin ta haifeshi saboda ta shirya barin rayuwar Bariki. Ta so ta haife dan ta raineshi da yaqinin wannan abin ya saka ta samu rangwame a gurin ubangiji na daga tarin zunuban data dibarwa kanta sedai daga baya tunanin irin rayuwar da Da ko yar da zata haifa da qalubalen da zasu fuskanta yasa ta kasa idar da qudurinta.

Sanda wannan cikin ya bayyanar mata tayi murna kwarai musamman dataga irin tarin murna da Zumudin da Audun ya ringayi shima ta ringa hasaso yanda zasu

raini abinda zata haifa tare ashe duk mafarki takeyi zanen qaddirarta daban abinda take tsarawa a zuciyarta daban.

Bayan fitar Yakubu har ya dauki niyyar zuwa gidan Audu se kuma wani tunani yasa ya fasa hakan, a karo na biyu kenan daya sake yanke danyan hukuncin da yake ganin hakan daidai ne a rayuwarsa.

A bangaren Audu seda hantsi ya daga kafin ya shirya ya fito ya nufin dakin Zubaida dan ya karbo takardar jiya. Ya tura qofar dake a bude ta sakayata yana sallama ciki ciki shiru babu motsi Tv da Radio da take yawan kunnawa duk a kashe dan haka ya dauka bacci takeyi seya wuce uwar daki nan ma qwalam bata nan. Tsaf ya bincike ko ina be ganta ba kuma bega takardar ba, yanayin dakin da be nuna alamar an dauki wani abu ko an hada kaya ba yasa yayi tunanin ko maqota ta leqa amma wannan ba halinta bane musamman da duk maqotan yan fadar Binta ne dukda haka ya qaddara wani gurin ta leqa seya koma daki da niyyar kafin ya gama shiryawa ta dawo.

Binta ta kawo masa abin kari yau din jinta take kamar wadda akawa Bishara da Aljanna. Lantana ce tayi mata albishir din taga Zubaida a hanya da jaka sanda take tahowa ta gaji kenan ta tafi ba kuma zata dawo ba. Tana so ta zungureshi da maganar taji ko ya sani amma dai tayi shiru harya karya ya fito ta rakoshi ta ringa dariya qasa qasa ganin ya doshi dakin Zubaidan yana kwazara mata kira nan ma shiru bata amsa ba.

"Wai ina wannan yarinyar ta tafi?" Ya jefawa Binta tambayar ta watsa hannu tace

"Yo ka bani ajiyarta ne da zan san inda zataje?"

"Shikenan sena dawo" ya fada daga nan ya fice yana mamakin ina zataje dan sam be kawo gida ta tafi ba tunda ai bata san abinda takardar daya bata ta qunsa ba, haka ya dawo gida da yaqinin ze tarar da ita amma wayam bata nan, ya diririce, ta tabbata gidansu ta tafi kenan amma me yasa zata tafi to? Ya jefawa kansa tambayar rainin wayo.

Bayan Isha ya shirya tsaf ya cewa Binta zeje wata unguwa, gidansu Zubaidan ya tafi zuciyarsa ta ringa tuhumarsa me ze kaishi gidan amma hakan nan ya zungura kai yaje. Malam Hassan ya rasa ina ze sakashi saboda murna bayan sun gaisa ya tambayeshi Iyali yace

"Dazun Babarsu take cewa gobe In Allah ya kaimu zata leqa ta ganota kuwa jiki yayi nauyi har tana cewa ko zata dakkota tazo gida tunda haka akeyi a Al'ada haihuwar fari"

Cikinsa ya bada wani sauti quuuu, bata zo nan ba kenan? To ina yarinyar nan ta tafi kardai fa ta hefashi a masifa in duniya ta sake shiga ai da seta bari seta zo gidansu ta gayawa Mahaifinta komai sannan seta tafi amma yanzun ta ina ze fara yi masa bayanin shima nemanta yazo?

"Aa bafa abin dole bane idan baka so ta dawo gidan se tayi zamanta dan naga fuskarka ta canza daman matane da Al'ada kasansu basa wasa da ita" Mala Hassan ya katse masa tunani a zatonsa zancen dawowarta gida ne ya canza fuskar Audun besan Al'amarin yafi gaban haka ba. Tilas ya masa sallama a gurguje ya taho bayan ya ajiye masa na goro.

A gida ma rkicewa Binta yayi da tambayar ina zasu nemo Zubaida ina ta tafi?

"Ya wuce ta koma inda ta fito ne, wai kai meye ma naka na damuwa ina ka saketa duk ma inda zataje taje mana kana da matsala da ita ne?" Ta fada cikin jin haushin yanda yake ta safa da marwa cikin damuwa. Washe gari da farar safiya ya tafi gidan Yakubu ya ringa buga musu qofa kamar za'a tashi duniya Yakubun ya fito yana ganin shine ya shiga surfa masa fada shima yana tambayar ba'asin wannan bugu kamar ya masa sata. Daya masa bayanin abinda ya kawoshi qiris ya rage Yakubun yayi dariya amma ya kanne a ransa yayiwa Allah tasbihi wato tun ba'aje ko ina ba aiko ze gane kuskurensa domin baze fada masa tana gidan ba.

"Ni meye nawa a ciki yanzu Audu? Kashedi nawa kamun akan na fita daga sabgar gidanka? Ashe da nace kayi haquri ka bar maganar nan baka daddara ba to ka saketa ta bar maka gida meye kuma abin damuwa a ciki ko daman ka dauka zata zauna ne kuci gaba da ci mata mutunchi kuna aibatata kaida matarka?" Yakubun ya fada yana tsareshi da ido. Audu yaja tsaki yace

"Ni bance ta zauna ba amma data tashi tafiya ai seta tafi gidansu ko amma yanU naje jiya bata can yanzu me take so na gayawa mahaifinta idan suka zo ganinta basu sameta ba?"

"Se ka gaya musu ka saketa ita kuma tana tsoron ta tayarwa da mahaifinta hankali idan ta koma gida shine ta sake shiga duniya, ni dana san wannan shirmen ne ya kawoka wlh bazan bude qofata ba haka nan ina bacci na me dadi ka daga mun hankali da bugu. Ka tafi ka nemo yarinyar mutane dai kafin iyayenta su farga, kaga daman ba'a jima nayi wani case Mata ta bata Iyayenta sukace Mijin ne ya siyar da ita yayi kudin jini AAllah ya tsareka kaima kar suce kayi kudin jinin da ita daman an fiyi da masu ciki" yana gama fada masa hakan ya maida qofarsa ya rufe ya bar Audu cikin tashin hankalin daya ninka na farko akan maganar da yayi ta karshe.

Daman a Bechi ana rade radin qungiyar Asiri ya shiga yayi kudi farat daya da yawa sun qaryata cewar wai sirikinsa kuma ubangidansa ne ya buda masa yake samun kudi haka? Su kance shi din har nawa ya mallaka da yake bawa Audun kudi haka? Zancen da akeyi yanzu rabi da kwatan Gonaki da filayen da suke a Bechi mallakinsa ne saboda duk wanda ya daga fili ko gona ze siyar da an tallata masa ze siya a farashi me daraja kuma shiyasa wasu ma haka nan suke siyar masa suje wani gurin su sake siya ragowar kudinsu susha shagali yanzu idan wannan magana taje Bechi ace matarsa ta bata da tsohon ciki la shakka cewa zasuyi yayi tsafi da ita kawai.



Sati guda ya shude Audu na bulayin neman Zubaida sedai sama ko qasa babu ita babu kuma wanda ya ganta bare asan labarin inda tayi. Har Zariya sukaje da Bashir gidan daya dakkota suka tarar an tashi gidan ma gaba daya titi ya biyo ta kan hanyar haka suka juyo Kano babban abinda ya qara daga masa hankali ya bazama nemanta zuwan da Baba Zayya tayi akan taje duba Zubaidan Allah ya taimake shi yana gida ranar, daya rasa abin fada mata dole ya rangada mata qaryar Zubaidan tana Bechi, kuma daman yaso yaje ya sanar dasu tana can har se bayan ta haihu zata dawo Kano to Allah be nufa ba. Dake akwai yarda da Amana sam Baba Zayya bata kawo komai a ranta ba tunda ana hakan mace ta tafi garin su Miji haihuwa dan haka tayi musu sallama ta koma gida ta shaidawa Malam Hassan yanda akayi.

Wannan dalili ya qara zaburar da Audu ga neman Zubaidan, nadama mara amfani ta dirar masa biya hukuncin daya yanke ba tareda zurfin tunani ba. Haka ya ringa raba kudi wa malamai akan ayi masa Addu'a Allah ya bayyana Zubaidan ya kuma kareta a duk inda take. Cikin wannan yanayi Alhazai suka fara tashi, Binta taje gida tayi sallama da danginta ta dawo tana ta shirin tafiya sauke farali bacci ragagge takeyi saboda jiran ace su fito. Ita sam ta manta ma da wata Zubaida balle batun ba'a ganta ba, yanda Audun be cika nutsuwa ba a lokacin yasa ta tsahirta masa, ita

kadai take ta shirinta tunda dai ya sallameta ya bata Guzuri me auki ita kam ya gama da ita se jiran ranar tashi kawai takeyi.

Acan gidan Yakubu kuwa hankali kwance Zubaida ke zamanta, tsakanin Balaraba da Yakubun ba zata tantance wanda yafi tattalinta ba. Duk wani abu da zata buqata suna mata haka nan basu barinta ta zauna shiru balle ta fada tunani ko wata damuwa a koda yaushe cikin hikima sukanyi mata nasiha akan rayuwa da qalubalen da yake tattare da ita. A dan taqin zaman ta fahimci banbance banbance masu tarin yawa da suke cikin rayuwar Haske data duhu ma'ana rayuwar da akeyinta cikin sani da wayewa ta Addini da kuma rayuwar Bidin bidima irin wadda tayi a baya ta koma dora yinta a gidan Audu.

Yakubun jajirtaccen Namiji ne wanda yake tsaye akan lamuransa dana iyalinsa. Ga daishi be tara dukiya tamkar dan uwansa ba amma rayuwar gidansa ta zamo abar sha'awa wadda duk me hankali idan aka bashi zabin kudi ko nutsuwa irin ta gidan Yakubun tabbas baze tsallaketa ba.

A kullum da Asuba seya dorawa matarsa da Yayansa karatu haka bayan sallar Isha'i idan sun zauna a maimakon hirarrakin banza na duniya sukan yi tasu hirar ne akan karatuttukan da sukayi. Ya tambayesu su tambayeshi, hatta da Qaramin dansu Tijjani me shekaru uku a sannan Alqur'ani ya fara zama a bakinsa, haka qananan Hadisai da ake dorawa Yayinsa yana tsinta har idan Yakubun yana tambayarsu sukayi kuskure Tijjanin da suke kira da Alhaji ze gyara musu ga wayewa ta boko turanci yafi hausa Nuna a bakinsu kodan inda suke zaune yaren da suka fi amfani dashi kenan? wannan abin ya matuqar birgeta ya kuma zaburar da ita kan cewar itama bata makara ba tana da damar da zata nemi ilimi tana kuma burin abinda zata haifa ya tashi cikin irin wannan rayuwar ta ilimi ba irin ta gidan ubansa ba.

Zata iya bada shaidar Audun yana salloli na farilla kuma yana qoqarin yinsu akan lokaci kuma cikin jam'i, a zamansu daya tasamma shekara a watan Azumi kadai zata bada shaidar yana zuwa sallar Tarawi da kuma Qiyamullaili tun bayan daya shude kuma a ranakun girkinta dai bata sake ganin yayi ba bata sani ba ko idan yana dakin Binta. Dama shi bame jurar Ibadar Azumi bane domin Ramadanan ma da qyar yake kaishi, bayan Alqur'ani bata tsammaci ya karanta wani littafi ba bata taba ganinsa dashi ba haka ko a magana ba zatace ga inda ya kawo misali daga cikin Hadisi ko wani littafi na Addini ba. Ba zata manta ba akwai sanda ta taba shawartarsa shiga karatun Asuba da akeyi a masallacin dake cikin layinsu wani

baqon babban Malami ne yazo yake bada karatun Fiqhu da Hadisi se Tauhidi take yace mata ai ya gama karatu, seda ya shekara biyar yana qolanta to wane karatu ya rage masa da beyi ba kuma?

Da tace ita zata ringa zuwa gurin matar Malamin da take karantar da Mata a cikin gida harya yarda bata san ya akayi ba ya dawo yace babu maganar ta tambayi dalili kuma yace babu dole ta haqura badan taso ba domin Allah ya sani tana sha'awar ta nemi ilimi shiyasa yanzun data samu wannan damar tayi amfani da ita.

Dada take ja tana biya mata karatun, dayake tasan baqi dan haka karatimu da takardar Alqur'ni be bata wahala sosai ba dukda tafi gane rubutun warshu amma da yake ta saka kanta se gashi tana ganewar in ta biya mata kuma ta ringa nanatawa kenan har seta haddace. Balaraba ce ta sameta akan ta ringa fitowa suna daukar karatun tare bayan da Dada ta sanar mata tana yiwa Inna Zubaidan qarin karatu, daga nan itama ta zama yar Aji ta kuma maida hankali sosai akan abinda ake koya mata. Irin nutsuwar da take tsintar kanta a ciki ta qara tabbatar mata da cewar tabbas akwai banbanci me tarin girma tsakanin rayuwar da akeyinta cikin sani da kuma ta jahilci.

Satinta uku a gidan wata safiya ta tashi da naquda, kafin nan sunje Asibiti har sau biyu Yakubu da kansa ya kaisu tareda Balaraba an dubata an kuma tabbatar da lafiyarta data abinda yake cikinta suka basu kwana goma daya zagayo suka koma kwanaki biyu kenan da zuwan nasu da safiyar ranar Laraba ta tashi da naquda nan da nan suka wuce Asibiti da ita, daman Yakubu yana nan ya jinkirta komawarsa Ikko saboda yana taraddadin ya zasuyi idan haihuwr tazo mata cikin dare gida babu Namiji daga ita se Balaraban dalilin daya saka ya daga tafiyarsa kenan saboda a Asibiti zuwansu na farko sun bashi tabbacin ba zata qara sati biyu nan gaba bata haihu ba gashi kuwa kwanaki goma sha biyu kenan da wanacn zuwan haihuwar tazo.

Cikin taimakon Allah bata dauki lokaci mai tsaho ba ta sauka, ta haifo wasu runtuma runtuman tagwaye wanda ko a Da guda daya aka haifi wannan tabbas se an jinjinawa wadda ta santaloshi se gashi har biyu ubangiji ya bata a sauqaqe cikin Aminci. Lokacin da aka nunawa Yakubu yaran kasa cewa komai yayi se tasbihi daya ringayi a zuciyarsa. Duk wanda yasan Ahalin gidansu baya buqatar a fada masa yaran tsatsonsu ne ze iya cewa ma ba'a taba haifar Jarirai masu kama da Mahaifinsu Malam Tijjani Kwabo da kwabo irin wadannan ba har hasken fatarsa basu bari ba abinda ya banbantasu da Audu kenan saboda shi yana da duhu kadan.

Ya rasa ta ina ze fara ma, Balaraba nata murna ta kasa tsayuwa guri daya shi kuwa tunanin waze fara shaidawa zancen haihuwar yake tayi. Gadai Arziqi Allah ya basu wadannan ne tagwaye na farkoba zuri'ar gidansu amma haihuwar su tazo cikin rudani. Seda ya tabbatar babu abinda ake da buqata a Asibitin kafin yacewa Balaraba zeje ya dawo.

Can kamfanin da Audu yake ginawa inda kuma nan su Musbahu suke zama ya nufa. Yaci sa'ar tarar da Musbahun be tafi gidan Mai ba, bayan sun gaisa yace yazo ya rakashi gidansu Zubaida Amaryar Audu babu musu ya hau mota suka tafi a ransa yana mamakin meyake faruwane domin a kwanakin nan gaba daya sun lura da Baba Audu baya cikin hayyacinsa dukda be fada musu komai da yake damunsa ba amma ko gidan Mai seya kwana biyu be fito ba aikin Kamfanin ma an dakatar dayi kamar yanda ya fada yana cikin wani dan uzuri ne.

Da suka isa gidan a Mota ya bar Musbahu ya qara qofar daya nuna masa a mazaunin ta gidan Malam Hassan. Yayi sallama cikin sa'a Malam din ya fito ya amsa a shirye yake da alama wani gurin zashi, be taba ganin Yakubu ba amma jini da kamannin fuska yasa ya gane dan uwan Audu ne dan haka yayi masa iso cikin gida bayan ya saka Baba Zayya tayi musu shimfida ta kawo masa ruwa a mutunce suka gaisa suna tambayarsa iyali.

Cikin nutsuwa da kuma sanin makamar aiki irin nasa ya warwarewa Malam Hassan duk abinda ake ciki be boye masa komai ba hatta da sakin da Audun yayiwa Zubaida da zamanta a gidansa zuwa yanzun data haihu be rage komai a ciki ba. Malam Hassan yayi shiru cikin tsantsar jimami kafin yace

"Tabbas nayi zargin wani abu ya faru saboda irin zaryar da dan uwanka ya ringayi a gidan nan kuma alamu na rashin gaskiya sun bayyana tattare dashi sedai na kyautata masa zato na cewar koma menene nasan baze cutar mun da Zubaida ba na saka a raina dai wata matsala ce qila da yake jin nauyin sanar dani. Hatta zuwan da zayya tayi ni na turata domin taje ta ga halin da suke ciki qila mu iya gano bakin zare sedai ya tabbatar mata da cewar ya tura Zubaidan can garinku, tabbas wannan maganar ta tayar mana da hankali hat shaidan yaso yayi wasa da zuciyata ya darsa mun zargin wani al'amari na daban amma na yaqe shi da qarfin addu'a ban kuma gusa ba kullum cikin yinta nakeyi ina roqon ubangiji da koma menene yake faruwa ya bayyana mana ya kuma sauqaqa mana.

Na godewa Allah da Jarabawar ta tsaya iyakar haka, na kuma gode maka da kayi mun wannan arziqin na riqe Zubaida a hannunka harta haihu ubangiji ya wanketa daga zargin da dan uwanka yakeyi mata na taje masa gida da Dan da ba nasa ba. Yanzu data haihu a hannunka ze iya tantance kamanceceniyar da take tsakaninsa da abinda aka samu kuma ya iya nutsuwa yayi lissafi na kwarai sabanin idan ana nan ta haihu tunda har ya rigada ya yarda da cewar Boka ko Malamin tsubbu na iya aikata komai la shakka yace itama kamannin dake tsakaninsa da abinda aka haifa qirqirarta akayi".

"Hakane Baba ina kuma qara baku haquri akan abinda ya faru In sha Allahu ma komai ze daidaita base har Zubaida ta dawo gida ba daga can gurina zata sake komawa dakinta da yardar Allah kuma abinda yasa nazo na sanar muku da abinda ake ciki saboda ku mahaifantane kuna da haqqi akanta be kamata kuma ace mun rufeku akan babban Al'amari irin wannan ba" Yakubu ya sake fada. Malam Hassan yayi murmushin daya fi kuka ciwo yace

"Kayya yaro dena wannan magana kuma ai zancen kome babu shi Aure ya qare sedai muyi fatan ubangiji ya musanyawa kowannensu da Mafi Alkhairi a gareshi. Kamar yanda rayuwar data faru a baya ta shude muka yarda da qaddara wannan ma mun dauka, rabon wadannan bayin Allah yayi sanadiyyar wannan Auran, tsakaninmu da Abdullahi kuma har abada babu abinda zamu ce masa sedai fatan Allah ya dubeshi ya saka masa da Alkhairi kwatankwacin wanda yayi mana. Maidomun da Zubaida gida da yayi ya isheni komai a duniya wlh kuma wannan al'amari daya faru baze goge tarin Alkhairinsa na baya a idona ba, wata Jarabaqar ce daga ubangiji kuma idan munyi haquri zamu cinyeta".

Yakubu be ja maganar da nisa ba yayi masa sallama bayan ya roqi Baba Zayya data shirya su tafi Asibiti tare ya kuma sake roqar Malam din da maganar ta zama sirri tsakaninsu. A hanya Baba Zayya ta samu bakin zazzage masa buhun bala'in da bata iyayi gaban Malam Hassan ba kai kace shine Audun, shidai be tanka mata ba domin sunada duk wata dama ta suyi fada dan an bata musu.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

AUDU

Shirye shirye suke tayi saboda a daren ranar suke saka ran tashin su Binta. Gaba baya ta hargitse gidan ta hada faggon jakunkuna tamkar me zuwa yawon bude ido ba Ibadah ba. Addaba masa tayi akan seya qara mata kudi,

"Kaga fa a can nake so nayi siyayyar kayan haihuwar nan, dan abinda ka bani me naci a ciki me nayo tsaraba sannan duk ciki kake so nayi siyayyar kayan jaririn?" Binta ta fada tana matse fuska sanda yake jaddada mata sisi baze qara mata ba.

Kudade masu kauri ta karba a hannunsa, banda guzurinta ga wanda Babanta ya bata amma a haka take hanqoron se ta sake waftar wasu a hannunsa ya rasa bala'in son kudi irin na Binta kuma ba abin Mamaki bane taje ta dawo daga ita se jakar hannunta dan ya dade da gane Binta bata iya tsinanawa kanta ko waninta da komai a zamansu daga kan sutura zuwa wani abin amfani na gida sabo sedai idan shi ya siyo ko kuma aka mata daga gidansu amma a karan kanta batayi ya kan tuna Bara'atu zamansu duk Azumi zatayi yan kaye kaye ta fitar da tsoffin kayan amfaninta ta maida sababbi banda Bintan.

Data ishe shi da surutu shi kuma ya rantse sile baze qara mata ba se kawai ya shirya ya fita, Gidan Mai ya tafi, mamaki ya kamashi yanda yaransa suke ta yi masa barka da Arziqi Allah ya raya bayan sun gaisa haka ya shige ofishinsa ransa fal da mamakin barkar me ake masa.

Sallama Musbahu yayi ya bashi izinin shiga bakin nan nasa kamar ze taage saboda fara'a ya gaida Audun kana yace

"Yanzu naje na gano yan tagwaye, wlh Baba kamar kayi kaki ka ajiye, duk yaran gidan nan ni banga wanda ma yayi kama da kai kwabo da kwabo kamar su ba".

Kallon Musbahun ya ringayi kamar be fahimci abinda yake fadi ba, so yakeyi ya tambayeshi waya haihu amma kuma ya qiyin hakan a maimakon haka seya miqe yana cewa

"Muje na gano su"

Maganar tasa ta bawa Musbahu mamaki dukda daman yanda ya ganshi tamkar be san da zancen haihuwar ba ya bashi mamaki sannan ya sake shiga duhu akan lamarin, tabbas akwai abinda yake faruwa tun daga daukarsa da Baba Yakubu yayi sukaje can gidan Malam Hassan bayan nan sukaje Asibiti a can din yayi tsammanin

tarar da Baba Audun ko matarsa amma yaga akasin haka Inna Balaraba ce kadai se Baba Zayya da suka tafi da ita tare.

Shidai bece komai ba har suka isa Asibitin wanda shi yake tuqi yana gaba Audu na biye dashi a baya har suka isa dakin da aka kwantar Zubaidan tana hutawa. Wani tsalle zuciyar Audu ta buga lokacin da idonsa yayi arba da jinjiri a hannun Baba Zayya tana jujjuyashi, idonsa fes akan yaron ya shiga cikin dakin sosai se ganin mutum sukayi sangangan akan su. Balaraba ta buga tsaki kamar zata tsinke harshenta kafin ta miqe tana cewa Baba Zayyan

"Bari na zagaya"

"Nima bari na biki nasha iska warin magani duk ya cika mun ciki" daga haka ta ajiye jaririn hannunta Musbahu yayi zuruf ya daukeshi suka fice suka barsu a dakin.

Idanu Zubaidan ta rufe tana qara gyarawa yaron data gama shayarwa kwanciya a jikinta, Audu na tsaye tamkar wanda aka sarewa guiwoyi ya kasa gaba ya kasa baya jinin jikinsa ya tsinke haka bugun zuciyarsa ya qaru kamar wanda yake kusa dashi ze iya sauraro. Musbahu ya ajiye yaron hannunsa bayan daya gaka jujjuyashi bakin nan yaqi rufuwa ya fita ganin kamar suna da buqatar sirri. Fitar Musbahun ta dan saukar masa da qwarin guiwa har ya qara taku biyu ya isa gaban gadon sosai yana kallonta tareda yaran da kunyarsu tayi masa lullubi.

Ko a rufa ido aka shafa fuskarsa aka shafa ta yaran an sana halitta dayace balle a kalle su ido biyu, bayan kamannin fuska qirar jiki da kammani na jini duk sun bayyana tattare dasu, ya kai hannu ze sauki wanda Musbahu ya ajiye a ba zata yaji ta daka masa tsawa tace

"Akul ka tabamun yara" ta fada har tana nuna shi da yatsa. Yanda tayi maganar cikin sauti me nuna bacin rai matuqa hakan kuma ya nuna a idanunta tilas ya janye hannunsa daga daukar yaron da ya bude ido yana kallonsa tamkar ya sanshi. A sanyaye kai a qasa tamkar ba Audu uban yan Izza ba ya matsa dab da ita cikin karyayyen sauti yace

"Kiyi haquri ki yafe mun, wlh sharrin shaidan ne".

"Babu wani shaidan face kai da Annamimiyar matarka, ni yanzu babu wani abu daya rage tsakanina dakai ubangiji ya gama mun komai daya wankeni daga zargin

da kake neman laqabamun, ciki dai gashi na haifeshi watanni goma sha daya a gidanka cikin qudura ta ubangiji kuma ya bani Yaya masu kama da kai kaga duk iya sharrinku da kaida matarka baku isa ku barranta wadannan yayan da Ahalinku ba, fatana kar Allah yasa su gado mugun hali irin naka. Wlh nayi dana sanin Auranka Audu, da ace na san haka can cikin zuciyarka yake baqiqqirin da ban amince da kai ba.

Ka gwada mun hali me kyau, ka yaudareni da Kyakykyawar Dabi'a. Nayi tsammanin na samu Bangon da zan jingina, jigon da ze tallafi rayuwata ya gyarani ashe kai kayi shirin qarasa tarwatsa rayuwa tane. Rayuwata ta baya ta zama tariyi kai kuma ka niyyati shafamun baqin fentin daya fi na baya muni, shin bakayi tunanin halin da mahaifina ze shiga ba idan yaji wannan mummunan abun daka zargeni dashi?

Anya kai ko da zuciya a qirjinka Audu? Me yasa baka tunani da kwakwalwarka ka sakarwa zuciyarka Linzami?

To wlh ka farka tun kafin lokaci ya qure maka, wannan rayuwar da ka dauka ta rashin tunani babu inda zata kai ka illah Nadama da dana sani mara amfani.

Ita kuma matarka ka gaya mata tabi a sannu, ina tausayawa rayuwar da zatayi a gaba haqqi dabaibaye da ita. Se yanzu na fahimci yanda kuka taru kaka kassara rayuwar Bara'atu kuka laqa mata mata mugun qazafi to wlh haqqinta kadai ya isheku a duniya idan har baku nemi yafiyarta ba ina kuma fatan yanda Ubangiji ya wankeni itama ya wanketa ya bayyana gaskiyar duk wani mugun qulli da kukayi akanta" tana gama fadar haka ta gyara kwanciya ta jera yaranta a gabanta bayan ta bashi baya ta rufe ido zuciyarta na tafarfasa tsanar Audu me tsanani tana hudata.

Badan kar tayiwa Allah butulci ba da tace inama ya jinkirta bata wannan gwalalon kyauta a wani gidan inda yafi na Audu Alkhairi? Amma dukda haka ta godewa Allah ta sake gode masa bisa ni'imar da yayi mata.

Tamkar wanda lakarsa ta tsiyaye haka ya ringa jefa qafafu harya fice daga Asibitin, ya manta da Musbahu sukaje hakanan beyi tunanin mota ba ya ringa taka qafafunsa bude ido kawai yayi ya ganshi a qofar gidansa tundaga Asibitin Murtala, tafiya yayi wadda rabon da yayi irinta a qafa dai ze iya cewa tun Zamanin yana Audu qolo. Binta na zaune a tsakar gida da jama'arta da suka zo yi mata Sallama makwafta da kuma Turai da Mardiyya Wata sabuwar qawa da tayi babu dadewa.

Yanda Audun ya shigo ya saka duk matan binsa da kallo kamar ma be lura dasu ba haka ya tsallaka ta tsakaninsu ya wuce sama, Turai ta kalli Binta kafin tayi mata alama da ta bishi ta miqe tana murmushin yaqe ta sallami maqwaftan ya rage Turai da Mardiyya kafin ta haye sama gurin Audu.

Yana zaune akan kujera yayi irin zaman nan na balance ya bude qafafu da hannayensa kana kallonsa kasan da akwai abinda yake damunsa. Cikin salo da kissa ta bude firji ta dakko ruwan sanyi ta matsa gabansa ta tsiyaya masa tana cewa

"Lafiya dai ka shigo kamar baka cikin hayyacinka?"

Seda ya kwalwale ruwan ya miqa mata kofin kafin ya yunqura ya gyara zamansa yana kallonta dakyau yace

"Zubaida ta haihu"

"An ganta kenan, a ina? To mema ya shafemu da ita ko haihuwar ta? Halan gurin farkan nata ta je ta haihu acan ko?" Ta yi maganar tana yatsina fuska. Miqewa yayi ya nufi daki yana tafiya a hankali yace

"Ta haifi tagwaye duka maza, kamanninsu daya dani"

"Me kake nufi?" Ta miqe a zabure qirjinta na dukan dubu dubu kunnenta na mata amsa kuwwar Tagwaye Maza da ya fada, se ya waiwaya ya kalleta yace

"Karmu fara wannan maganar ma. Kin cuceni kin rabani da matata, waima meye dalilinki na sheganta mun Yaya Binta? Me yasa kikayi haka?"

"Ni na sheganta maka yaya? A yaushe akayi haka? Tsakaninka da Allah ni da kai mun taba magana nace maka cikin Zubaida shegene? Hasashena nayi na fada kai kuma tunda kasan da walakin goro a miya ka tabbatar haka ne to kuma se kazo kace na cuce ka dana maka me? Da kake wannan babatun ma me kake nufi ka karbi cikin kenan ko Yaya?"

"Ciki daman nawane" ya bata amsa yana shigewa ciki dan in ya tsaya din be san me zece mata ba. Gaskiya ta fada magana tayi me harshen damo shi kuma ya hau

ya zauna daram wato ta tabbata ya zama wawa kamar yanda Yakubu ya fada Bintan ta karanci rashin tunani irin nasa shiyasa tayi amfani da wannan ta cusa masa tunani a kwakwalwarsa harta kaishi ga yanke danyan hukunci yanzu gashi tun ba'aje ko ina ba ya dawo yana dana sani mara amfani dan yasan ya rasa Zubaida ba zata sake yarda ta komo gidansa a matsayin matar aurensa ba.

Daren ranar Binta ta wuce Saudiyya cikin tashin hankali bayan sun rakaya dasu Turai sunje Asibiti sun ganewa idanunsu Tagwayen da akace Zubaidan ta haifa. Kuka wiwi ta ringayi kamar wadda kanta ya kwance wai ya za'ayi tazo a bayanta ta haifi tagwaye kuma Maza kenan yanzu ta fita kasafi cikin dukiyar Audu kenan. A Saudiyyan haka tayi Ibadar rabin Addu'arta ta Allah ya sa tayita haifar Yan biyu Maza ne bayiwa kanta wata kwakwkwarar Addu'a ba balle Yayan da take roqon a bata haka aka sauke Hajji ta dawo kamar yanda Audun yayi tunani daga ita se Kayan data tafi dasu yar tsarabar data yiwo bata kai kota kashi goma cikin uban kudin data tafi dasu ba.

Bayan dawowarta ta tarar da an kwashe kayan Zubaida wannan ya dan rangwanta mata damuqar data saka kanta a ciki. Daman daga Asibiti Zubaidan gidansu ta wuce kamar yanda Mahaifinta ya buqata Yakubu yayi iyakar roqon da ze iya amma Malam Hassan yace yayi haquri kawai. Ran Yakubun ya sake baci matuqa ya dauka Audun zeyi Nadama ya kuma nemi su sasanta ta koma dakinta amma seyaga akasin haka. Ya dai siyawa Jarirai kayan na Alfarma haka itama Maijegon ya hada da ita da Manya manyan Ragunan suna dana Qauri ranar kwana biyar da Yan Bechi suka zo wanda suma Yakubu ne yaje ya sanar dasu suka kai kayan Barkar.

Da aka kwana biyu har ya koma Ikko ya sake dawowa wata daya bayan haihuwar kenan ya sake tarar Audu da zancen ya suke ciki sun daidaita zata dawo idan ta yada wanka ko kuwa kai tsaye babu boye boye yace masa

"A gaskiya ni bazan iya zuwa nayi bikon wata mace ba, zan bata lokaci harta huce daga fushin da takeyi, idan ta nuna buqatar cigaba da zama a gidana se mu daidaita".

Yakubu ya rasa abin fada ya ringa kallon Audu kawai yana jin kamar ya rufeshi da duka. Ya dade yana ganin marasa hankalin mutane amma Audu leader ne, cikin tsantsar takaici yace

"Abinda ya hanaka ka maido da Bara'atu kenan tunda bata furta da bakinta tana so ta dawo ba ko?"

"Ka gane ashe, ai Allah ya kallo duk wani abu daya kamata ace nayi da ze nunawa Bara'atu ta dawo dakinta nayi. Kana kallo dawainiyar gidansu kaf har abinda be zama dole na ba yi musu nakeyi, duk wata se nayi mata aiken kudi da kayan abinci kuma idan naje Bechi ina zuwa naga Yaran to me kuma ya rage da zanyi ya nuna mata Biko nakeyi? Sena zubarda girmana na roqeta ta dawo bayan Alfarma zanyi mata naci gaba da zama da ita bayan laifin data aikata mun?

Itama Zubaidan ai koda ina da laifi nata yafi yawa a ciki, me yasa bata tsaya tayi mun bayani yanda zan fahimce ta ba amaimakon haka seta ringayin abubuwan da zasu qara tabbatar mun da zargina akanta ni kuma shine ya tunzurani na yanke hukunci. Kuma ai ita har haquri na bata da naje Asibiti tace babu ita babu ni kuma ta hanani taba Yayana shine kake so naje gidansu nace ta dawo salon ta samu damar rainani ko to ni bazan iya wannan aikin zubarda mutunchin ba" Audun ya fada cikin dagawa.

Mamaki, takaici hade da baqin ciki sukayiwa Yakubu rubdugu lokaci daya amma ya rasa kalmar da zeyi amfani da ita gurin zagin Audun dan haka ya kada kai kawai ya wuce ya barshi yana jinsa yana masa magana akan ya tsaya mana ina zashi be ko waiwaya ba. Duniya dai akace tafi bagaruwa iya jima, tabbas yana jiyewa dan uwansa randa muguwar Ta'adarsa zata bibiyi rayuwarsa.

Page 24

Rayuwa ta miqa, kwanan Binta Talatin da bakwai da dawowa daga Aikin Hajji ta haihu ta sake samun Da Namiji da yaci suna Naziru, yafi babu wai Agwai da baqin Da yanayin da ta nuna kenan domin ta gama sakankancewa da Addu'ar data ringa zagaye Ka'aba tanayi akan Allah ya bata yan Biyu Maza ta karbu to dayan ma babu laifi tunda yanzu sunyi kai daya su ukun gaba daya kowacce tana da Yaya Maza Biyu kenan, amma ba ta sare ba za kuma taci gaba da addu'a Allah badi war haka tayi yan uku ma ba biyu ba kuma duka Mazaje dan babu yanda za'ayi wata mace ya fita kaso a cikin Dukiyar da ubantane silar samunta.

Ko kaza bata zo mata barka ba daga Bechi balle suna haka sukayi bidirinsu da ita da yan uwanta se qawaye da makwafta shi kansa Audun tun bayan abubuwan da

suka faru zamansu ya canza salo dan gaba daya ya daura mata laifin itace silar Rabashi da Zubaida ita kuma ta nuna sam ba haka bane ba. Da fari bayan dawowarta ta biyeshi zaman ya zama babu dadi sedai bayan da suka tattauna da Turai da kuma sabuwar mashawarciyar da suka samu wato Basira se abubuwa suka canza daga bangarenta.

Basirar ta qara tunasar da ita cewar muddin fa tana son biyan buqata seta kwantar da kai. Tilas ta maida kanta banza a gurin Audun, tunda har ta fahimci shi mutum ne me matuqar son girma da son a nuna ya isa to tayi amfani da wannan damar gurin kaishi matsayin da Allah be kaishi ba. Ta ringa nuna masa nan duniya babu yashi, duk kuma abinda ze fada karta kuskura ta musa masa ta barshi akan komai yayi daidai ne baya kuskure.

"Hajiya sufa Maza kamar qananan yara suke wlh, fahimtarsu kawai zakiyi me suke so menene basa so shikenan ku zauna lafiya. Kuma a yanzu abinda ya kamata ki mayar da kai gurin yi shine ta yanda zaki kafa kanki da Yayanki a gurinsa yanda zakiyiwa duk wata mace da zata shigo rayuwarku Zarra" Basirar ta fada taba durqusar da kai irin na shahararrun munafukai. Binta ta hura hanci tace

"Ai ba se kin fada ba, haihuwa dai an haifesu amma naci alwashin muddin ina raye yaya nane zasu zama kan gaba a komai na dukiyar Audu, baze tuna yana da wasu yaya ba bayan nawa, duk wanda yaci Arziqin Audu to ni naso"

"Ina yinki qawata fada da cikawa wannan aikinki ne" Turai ta fada tana bata hannu suka tafa. Haka suka yita qulle qulle da shiri na yanda za'ayi yanzu da nan gaba. A haka har lokacin haihuwar tata yazo bayan anyi suna da kwanaki Turai taje ta sameta da zancen rashin zuwan yan Bechi.

"Ni se nake gani ko dai babu dadi yaci ace kina sabga dasu, saboda dangin Miji ba qananan Munafukai bane, kinga idan suka kafawa mutum qahon zuqa Allah ne kadai ze kubutar dasu. Kina kallo dai yanda nake zaune da nawa duk sharrin mutum be isa yace na masa mugun abu a fili ba kuma na sani sun sani basa qaunata nima bana qaunarsu amma tunda ban bada qofar da zasu wulaqantani ba kinga qalau muke zaune dan haka kema dole ki gyarota dasu, ki jasu a jiki musamman ma naki da suke Fuqara'u Ahalin tsiya. Kamar kajine kina watsa musu tsaba na tabbata zasu biki ko wannan ma ze qara miki fada idan kika kame yan uwansa kinga koda ace kin

samu tangarda dashi ba fata ba yan uwansa zasu zame miki makamin da zaki gyara komai" cewar Turai.

Binta ta numfasa tace

"Turai baki san yan uwan Audu ba musamman yan dakinsu. Yanda yake da wannan kafaffiyar zuciyarfa iwa ta mutanen farko haka suke. Bana tsammatar kudi ze saka su soni kina kallo ko shi din da yake musu shine jigon komai nasu akan Wannan shegiyar Bara'atun duk suka masa tawaye, yanzu an kuma na biyu sun nuna sunfi qaunar Karuwa akaina shiyasa duk suka qi zuwar mun Barka amma ai na samu labarin su sukazo suka kaikayan suna suna gidansu Zubaidan.

Tsinanniyar Bilkin nan tun ranar sunan Dady na farko bata qara tako qafarta gidan nan ba gara Aishar tazo jinya kwanaki can Mazan kuwa tunda suka zo fadar Baqin labarin Auran Karuwa basu dawo ba hatta Baballiya tunda aka Auro ni sau daya ya tako qafarsa gidan nan sedai fa idan naje can Kaduna na ganshi ya samu guri ya baje kamar gidan ubansa yanzu nan Yakubu ne kadai yake zuwa idan cin mutuncibsa ya tashi kuma daman duk ciki Audun ma shi yake shakka shi kadai ne yake tsayawa ya gaya masa magana son ransa kuma ya shanye baze iya mayar masa ba a yanda ya tsaneni kuwa ko duniya da abin cikinta zan bashi baze qaunaceni ba haka Annamimiyar matarsa ni ko kamanninta bazan iya tunawa bama yanzu. Kai na tsani Yakubun nan iyajar raina wlh" ta qarasa tana cizon yatsa tsanar da tace tanawa Yakubu ta nuna qarara akan fuskarta.

"Dukda haka dai ance se an tsaga ake ganin jini, daurewa zakiyi ki cusa kanki cikinsu ko basa qaunarki ta hakane fa zaki ringa sanin wasu abubuwa da suka shafi shi kansa Audun, hatta da dukiyar tasa kince duk abinda ya samu acan yake narkata, filaye gonaki duk ya tattara acan to idan kika qwafe a nan kin bar musu komai can ta yaya zaki san me kuke dashi? Irin hakane kina zaune kina lissafin dokin Rano se anzo ranar kasafi kiji abinda ba haka ba ita Bara'atun da take cikinsu tsaya mata zasuyi taja rabo me tsoka ga wannan itama tunda sun nuna tafi musu ke duk mara musu baya zasuyi a barki da lissafi. Amma idan kika shige su ta yanda ba za'a layance miki komai ba kin sani shima kuma ki matseshi ta yanda duk abinda yayi ko zeyi seya gaya miki"

"Yana ma gayamun in dai ya siyi abu ze fada mun tunda wannan matsiyaciyar ta fita ne dai kinga yanda abubuwan suka koma"

"Se haquri ki kuma cigaba da lallabawa daman ai ba kullum ake kwana a gado ba dole wata rana a samu yanda ake so wata rana kuma aka sin haka sannan ba yanzu muke dubawa ba gaba zamu gina lokacin Jin dadib ai be ma zoba tukunna qawata kedai Allah yayi mana tsahon rai musha shagali" Inji Turai. Binta ta murmusa tace

"Ai ni dole ma nayi tsahon rai dan munyi Gadonsa"

"Ke karkiyiwa Allah gatsali wlh yanzun kijiki a rami" Turai ta fada tana zare ido, Binta ta rufe baki tace

"Uffararan Allah na tuba ba haka zance ba, dangin mu dai sunyi Gadon tsahon rai kinga nima zanyi" ta sake sakin wani shirmen Turai ta miqe tana cewa

"Bari kiga nayi nan iskancina be kai shiga hurumin Allah ba, to mutuwa dai ba ruwanta da gadon tsayin rai ko gajartarsa in lokaci yayi dole a tafi" da haka hirar ta watse saboda Binta tace kan me kuma ana hirar arziqi zata sako musu zacen mutuwa.

Bayan ta yada wanka ta cewa Audu zataje Bechi ta kwana biyu, wannan yasa ya sassauto daga daure dauren fuskar da yake fama dashi tun rabuwarsa da Zubaida. Ya shirya mata tafiyar Ado sabon Direban daya dauka yake jigila dashi ne ya kaita Bechin niqi niqi da kayan tsarabar data loda dan Hajji Kam taje tayo tsince tsincen su Zam Zam, Dabino Bagaruwa su kallo kallo na yara da sauran tarkacen tsaraba ta tafi.

Kadaran kadahan suka karbeta musamman da basu san da zuwanta ba dan haka babu wani tanadi da akayi mata ta bude dakinta ta shiga a ranta tana tsine musu babu wanda ya bita ko suce zasu tayata kimtsa guri sun dai karbi Naziru yana can hannun Sauda Amaryar Aminu. Ta gama kakkabe dakin ta kimtsa abinda zata kimtsa kafin ta bude jakar tsaraba ta shiga kasawa gida gida.

Yara ne sukayita shelar zuwanta garin, Aisha ta biya gidan Bilki akan tazo suje yiwa matar Yayan nasu Barka da zuwa amma tace babu inda zataje. Haka ta tafi ita kadai ta tarar da Yaya Mairo da Yaya Amina da matan Yayyensu duk sunzo Goggo

Fadi ta aika an gayo musu. Kamar yanda Turai ta fada kuwa duk wadda ta shigo fuska a murtuke dan ba a son ransu suka zo din ba dan dai bazasu tsallake kiran Sirikarsu bane amma data miqa musu qullin tsaraba se kaga sun hau washe baki suna godiya daga nan se a shantake a fara hira kuma wannan tasa Aisha ta tarar da dakin cike da Mata suka gaisa ta karbi yaron da daman shine maqasudin zuwanta bawai ganin Bintan ba tana tambayarta Yayansa tace mata Yana Kaduna tunda suka zo suna suka tafi dashi. Bata jima ba tayi musu sallama tace se gobe zata dawo.

Bayan Isha Jamila Uwargidan Hashimu ta sake dawowa da Langa tuwo da miya data sakowa Binta abincin dare. Tana daki bayan ta lallaba Naziru yayi bacci, qullin uban Nama ne a gabanta da damammiyar fura take ci Baballiya ne ya kawo mata bada jimawa ba tayi mamakin ganinsa a Bechi wato ya zo Kano amma koya leqa can gidansu da tayi masa tsiya yace mata ai yaje Kanon amma a Kamfani suka hadu da Yaya Audu dake ba jimawa zeyi ba anyi posting nasa can qasar Kudu yazo yiwa yan gida sallama ne shiyasa be shiga can gidan sun gaisa ba ya ajiye mata saqon ya wuce ta bishi da kallo tana mamakin girman da yayi, idan ba'ayi wasa ba zefi Audu tsaho da qirar qarfi yanzun.

"Sangangan kenan sudai sunyo gadon girmaz wai yanzu haka nawa Yayan zasu tashi kenan kamar dakarun yaqi? Allah yasa dai su kwaso hankalin wancan me baqar zuciyar Wan uban nasu dan ta nan ya banbanta da sauran" ita kadai take sambatu tana danna lomar Nama abinta Jamilan tayi sallama. Tsaki taja qasa qasa kafin ta amsa, babu damar ta boye abinda take ci dan ta rigada ta shigo dan haka ta hade fuska dan ba zata sammata ba.

"Aa, Hajiya irin wannan rabasha haka kice gashin Haladu aka kawo miki" Jamila ta fada tana kallon ledar kamar ta dumbula hannu yawunta ya tsinke dan qamshin naman ua cika dakin duka. Yaqe kawai Binta tayi ba tareda tace komai ba a ranta tana mamakin meya maido matar nan kuma? Yan cikin gidan ma sun barta ta huta kuma se ita zata kwaso jiki tazo ta isheta a daren nan daga zangar ta dan basu fuska dazu.

"Daman Tuwo na kawo miki, yo ahe ke tuni kin makari da babban yanka" Ta sake fada tana bude Langar tuwo da miyar data jere a qasa. Warin daddawa da kuka suka daki Binta a ranta ta danna Ashar tace

"Ni zanci wannan baqin tuwon da miya kamar yawun Kaza?"

"Zabuwa Babansu yace a yanka a zuba miki a miyar" Jamilar ta sake fada tana karkato mata da kwanon miyar dan taga Namomin da suke ciki wanda qarya takeyi ba Hashimu ne ya bada ba satar mata Zabo tayi tasa aka yanka tasan kuma da zarar labari ya isa kunnensa gobe akwai bala'i dan da tace masa Bintan tazo ma seda ya kora mata ashar yace ina ruwansa da wata Binta.

"Allah sarki aiko nagode, bari na ajiye da safe se a dumamamun nayi kari dashi"

"Aiko daman yafi dadin ci dumamen" Jamila ta sake fada tana gyara zama. Hira ta shiga sokowa Binta kamo nan kamo can, da taga bata da niyyar tashi dole ta bude naman ta mata bismilla aiko ta dirar masa seka rantse bata ci a gida bayan iyakar qoqari Mazajensu sunayi da wuya ayi miya lami a gida. Seda suka tada naman tas wanda Jamila ce ta cinye Rabi Binta ta janye Furarta gefe dan wannan kam ba zata bata ba.

"Uhm bari na tashi dare ya fara nisawa, nace da safe in Allah ya kaimu nazo na rakaki ki gano gidan ummarsu Babangida ko?" Jamila ta fada yana miqewa tsaye da shirin tafiya.

"Wace Ummarsu Babangida kuma?" Ta tambayeta cikin rashin fahimtar wa take nufi.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana

rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

"Au, Bara'atu zance miki ko zaki fi ganewa. Juma'a idan tazo mako uku kenan da tarewarsu, kinga gida badai gida ba tamkar naku ba Birni, ai gaskiya Alhaji Audu yayi karamci ya kuma kyauta saboda dangin uban nan nata tasamma ci musu mutunchi sukayi wlh, kinsan basa son uwarta ta fa daman akace. To yana mutuwa suka tada bala'i wai gidan da yake ciki gadonsu ne su goma ya hana a raba ya ke zaune ciki dan haka se su fitar musu a gida a raba sannan su san kasonsu, kinga dan taqin da akace sun cire musu a matsayin rabon baban nasu? Ai badan Alhaji Audu ba a garin nan bamu san Ina Inna Hajara da yayanta zasu tsoma ransu ba shine fa ana gaya masa ya aiko aka far....."

"Ya isa haka dan Allah, kije Allah ya kaimu goben se kizo ki rakani" Binta ta dakatar da Jamila daga zubar da takeyi tamkar famfon daya lalace. Jamilar ta fice bayan ta mata sallama tana dariya kamar wata wawiya tana fita Binta ta mayar da qofa ta

rufe, wani kalar tashin hankali ke rufzo mata dukda yanayin garin babu zafi amma ita zufa ce take keto mata ta kafofin gashin jikinta. Ta ri ga safa da marwa a dakin tana huce ita kadai tama rasa ta ina zata fara tunani, Audu ya ginawa Bara'atu gida yaushe akayi haka bata sani ba kuma akan me?

To kodai sun maida Auransu ne bata sani ba tana can gaho? Ta jefawa kanta tambayar seta zabura a fili tace

"Kut**uba kenan ma ai kuwa da anyi yaqi duniya ni za'a yaudara a ninke baibai?"

Kukan da Naziru ya sakane ya ankarar da ita hayagagar da takeyi ta daukeshi taci gaba da zaga dakin tana jijjigashi, wato mutanen nan anyi qungurumayen munafukai, ashe da Jamila bata gaya mata ba haka zata gama zamanta ta tafi ba tareda ta samu wannan mugun labarin ba aikuwa zasuga tatura, seta nuna musu ta fisu iya tashanci wato uta zasu hadewa kai?

Tabbas Turai tayi gaskita da tace tana can Bihim zasu rabe komai a barta da zare ido gashi kuwa an fara.

Daren ranar bacci barawo ne ya saceta dakyar aiko tayishi da mafarkin wai Audu ya mutu an kwashe komai an bawa Yayan Bara'atu da Zubaida ita bata samu ba. Da safe kuwa dakyar ta iya zama jiran Jamila da ace tasan gidanta ma da ba zata iya zaman jira ba gara taje su wuce daga can. Wadanda suka dawo washegari son zuciya ganin yanayinta yasa suka watse dan a dare dayan ciwon qyashi da Hassadar data dorawa kanta ya zabgeta kai ka dauka kwana tayi tana gudawa.

Jamila bata zoba se bayan La'asar dalili kuwa Hashimu na gida ranar bayan ya gama Tijarata akan Zabonsa data dauka tayiwa Binta Miyar da ko dandanata batayi ba da safe da Sauda ta kai mata kayan Karin Kumallo tace ta dauke tuwon a bawa Yara. Seda ya fita kafin ta samu ta kammala duk abinda zatayi gudun kar sukai Magriba kafin ta fito. Tinqis tinqis se gasu a sabon gidansu Bara'atu Jamila nata zuba mata dan banzan Surutu ita ko Ruhinta da gangar jikinta suna ga su isa taga gidan da Audu ya ginawa Bara'atu.

Tun daga qofar gidan yanda aka lailayeta da fulasta tasha fenti yanayin tsari da taswirar ginin kai ba zakace a cikin Bechi yake ba. Wani abu me daci da maiqo ya taso mata har seda ta dafe qirji tana kallon qofar gidan dake garqame da kwado

alamar basa nan. Jamila ta qarasa tana shafa qofar ta juyo ta kalli Binta da taje tunga tace

"Kinga basa nan, ko ina suka tafi se Allah amma babu komai gobe ma ranace se mu dawo" tana rufe baki sega Qanin Bara'atu ya shawo kwana ta washe baki tace

"To qila ma gasu nan kinga qaninta".

Ya qara gurin ya gaishesu a mutunce Jamila tace

"Ina mutanen gidan mun tarar qofa a rufe? Ka ganta can ka ganeta ko Matar Alhaji Audu ce tazo muku Allah sanya Alheri".

"Ai kuwa kunyi sabani dan basu koyi Minti Ashirin da fita ba sun tafi Rano" ya bata amsa. Ta dafe qirji tace

"Rano? Kai sun luluqa da nisa, to kuma yaushe zasu dawo?"

"Gaskiya ban sani ba" ya bata amsa cikin qaguwa da maganarta ya fara tafiya ta tareshi tana cewa

"Aida ka bude mana to taga gidan tunda kaga ita ba mazauniyar nan bace balle ace ta sake dawowa idan sun dawo, qaraso Hajiya ya bude mana mu Shiga" ta fada tana kallon sashen da Binta ke tsaye sedai wayan bataga kowa a gurin ba. Ta hau waige waige qanin Bara'atu me suna Isah yace

"Indai wannan Hajiar ce ai ta dade da tafiya tun sanda nace miki basa nan" daga haka shima ya wuce ya barta tsaye tana cizon yatsa. Bawai da zuciya daya ta sanarwa da Binta wannan maganar ba so tayi ta hada bala'i ta kuma so ace sun tarar da su Bara'atun dan ta tabbatar da Binta bazatayi haquri ba se tayi musu tijara da rashin mutunchi iyakar qarfinta.

Cike take da qyashi da hassadar ya za'ayi ace dukda Bara'atu bata tare da Audu kuma taci gaba da kere masu ta kowanne fanni na rayuwa? Shekaru Aru Aru suna zaune gidan qasa lokaci daya Audu yazo ya tadawa Bara'atu da Iyayenta ginin Jan

bulo ya danqara musu gida kamar na wani sarki Alhalin su suna fama da jar laka? Shiyasa ta kwazawa Binta maganar tunda ta lura bata sani ba yanzun ko tasan inta koma Birni wacce za'ayi se Allah ita dai fatanta Audun ya kwace gidan kawai tunda dai yana tsoron Binta.

Farar safiya Binta ta kammale kayanta tsaf tasa a nemo mata shatar mota zata tafi gida. Goggo Fadi ta ringa tambayarta abinda ya faru data tashi tafiya gagaga haka Alhalin sati guda tace zatayi bata da abin fada mata a matsayin dalilin tafiyarta dan haka kawai ta laqawa Danta ciwo tace shine bashida lafiya gara su tafi ta kaishi Asibiti. A wata mota da Jaki ya fita dadin hawa da saurin tafiya ta kamo hanyar Kano, ita ma din da dakyar aka samo mata ita dan masu motocin daukar kaya tuni kowa ya fita ai kuwa taji jiki kafin taje gida, baya da qafafunta sun fada dan jinjirinta kansa ya gane kurensa a wannan tafiya seda sukayi jinyar gaske ita dashi ga qarin baqin ciki ta tarar Audu baya gari seda taje gidan Turai a kwana na uku bayan taji dama dama sannan ta gaya mata ai sun tafi Legas tareda Ali zasu dakko kayansu.

"Karki tareshi da hayaniya kibishi ta siyasa idan kika gano bakin zaren sannan musan abinyi" Turai ta fada mata bayan data shaida mata zancen gidan da Audu ya ginawa su Bara'atu. Haka kuwa akayi, tayi matuqar qoqarin boye tashin hankalinta da damuwa akan Al'amarin harya dawo daga tafiya seda ya kwana biyu ya ware gajiya kafin ta tada masa da zancen ai taga gida akace shiya ginawa su Bara'atu.

"Badan Bara'atu na gina musu gida ba nayine saboda Yarana, ya za'ayi ace da raina ban mutu ba a watsarwa da Yayana da uwarsu kayansu a waje bayan ina da halin da zan iya siye garin gaba daya ma ba iyakar gidan da suke ciki ba (kuji fariya). Shiyasa na yanke shawarar yi musu gini na Alfarma irin wanda babu shi a kaf garin da makwafta" ya bata amsa. Binta tayi murmushi a qoqarinta na boye tashin hankalinta tace

"Gaskiya hakane amma dai basu kyauta ba suma se kace ba yan uwa ba? Kuma naji ma kamar nace fin qarfi kawai suka gwada musu amma tun Baban nasu yana da rai ya fitar da kowa ya bashi kason kudinsa?"

"Oho musu wannan su ta shafa tunda na rigada nayi abinda nayi, gidan ma kuma zan siyeshi na mayarwa dasu Bara'atun se naga ta tsiyarsu ko?" Ya bata amsa, ta zabura se kuma tayi saurin daidaita zama tace

"Aiko dai, ka barwa su Bara'atu ko ka barwa su Babangida?"

"Ita dasu ai duk dayane kuma duk abinda zanyi mata Alfarmarsu take ci ko iya ruqonsu da takeyi ai tayi qoqari Alhalin ubansu nada rai kuma ina da yanda zanyi"

"Uhm hakane, ni da zakayi haquri ma ka yafe abinda ya wuce daka maido su munci gaba da zamanmu kawai hankali kwance. Duk se naji rashin dadi saboda mutane zasuyi ta kallona a matsayin wadda tayi silar raba Yaya da Mahaifinsu" Bintan ta zartar da hukuncin da take ganin shi kadai ne ze datse alaqar Audu da Bara'atu, tunda dai yace saboda yara yake mata komai to gara a kwaso mata yaran suzo suyi ta dabdala a tsakar gida da dai uwarsu tacigaba da morar Audun.

Wani kallo ya watsa mata me ma'anoni da yawa fuskarsa ta nuna mamaki qarara yace

"Dagaske kike ko wasa? Kina nufin kin yafe mata abinda tayi miki su dawo muci gaba da zama tare?"

Seta rausayar da kai ita ala dole gata Allah tace

"Abinda ya faru ai ya rigada ya faru na dauki qaddara tunda Allah ya qadarta Yaron bame doguwar rayuwa ko bata silarta ba ze mutu, kuma yara ai basu suka mun laifi ba itan ma kuma na yafe mata Albarkacinsu"

"Amma naji dadin wannan magana matuqa in sha Allahu nan bada dadewa ba kuma zan shirya dawowarsu, harkin wankemun baqin cikin abinda ya faru kuma kin qara daraja a zuciyata saboda ba kowa za'ayiwa babban laifi irin wannan ba ya yafe harya cigaba da zama da mutum" Audu ya fada cikin madaukakin farincikin da shi kansa besan dalilinsa ba.

Ta maka masa harara a fakaice kafin tace

"A kullum burina kenan na faranta maka rai, inda na san wannan ze saka naga farin cikinka haka da tuntuni an aiwatar dashi amma yanzun ma lokaci be qure ba".

Daga haka suka tashi daga maganar da kowannensu da kalar manufarsa akan abinda yake fadi.

Binta tana maganane akan Babangida da Babannan, su take nufin Audu ya dakko su dawo gidan saboda kar Bara'atu taci gaba da cin arziqinsa ta dalilinsu yayinda shi kuma tasa kwakwalwar ta fassara masa Maganar ta a matsayin ya maido da Bara'atu taci gaba da zama da Yayanta a gidan wannan ne ya sanyashi farin cikin da beyi tsammani ba. Allah ya sani bazeyi qarya ba ba kuma ze iya boye tarin qaunar da yakeyiwa Bara'atun ba saboda ita ya fara so har kawo yau kuma be dena sonta ba Halayen dara tsiro dasu daga baya ne sukayi tasiro gurin ruguza zamansu wanda yake fatan a yanzu ta hankalta ta gane kuskurenta.

Abu na biyu daya qara masa jin dadi shine ya san maida Auransa da Bara'atu ze gyara alaqarsu da Yan uwansa data gurgunce musamman Yakubu da Bilki, wannan farin cikin kadai ya hanashi bacci ranar, washe gari kuwa yayiwa Bechi tsinke sedai ya tarar da su Bara'atun har sannan basu komo ba.

Izza da girkan kan dai yana nan, ya saka a ransa Mace tayi kadan daya je bikonta, Hayatu Abokinsa ya barwa sallahu akan idan Sun Dawo yaje ya tuntubeta yaji ra'ayinta akan komawa gidansa.

"Kai yanzu Audu kana nufin kafi qarfin ka tare ta baki da baki kuyi maganar nan?" Hayatun ya tambayeshi cikin mamaki.

"Ga Amsar nan ka bawa kanka ai, ko yanzun saboda Yayana zan mayar da ita bawai dan ta cancanci na maida itan ba" ya bashi amsar da har ransa yasan qarya ya fada.

"Ai shi kenan, girman kai dai rawanin tsiya, kuma shi ya halakar da mafiya yawan Magabata" Hayatu ya bashi amsa.

Page 25

Wasa ya wasa, qaramar Magana ta zama gaske, kamar yanda Audu ya barwa Hayatu sallahu ya isar da saqo dan Bara'atu na dawowa gida ya doma sallama kofar gidansu, ta fita suka gaisa, batayi mamakin ganinsa ba saboda Abokanan Audunna Bechi sukan leqa sa'i da lokaci suga Yaranta. Sukance Audu ya musu rana dan haka bazasu yada yaranshi da suke kusa dasu ba dan idan ka ture halin Audu na Rashin

son gaskiya da shegen girman kai yana da kirki, kuma abun hannunsa be rufe masa ido ba daidai gwargwado yana kyautatawa Yan uwa da Abokanansa.

Bayan sun gaisa da Hayatun ta tambayeshi jikin matarsa datayi samu da jijjiga lokacin haihu da yake abun a gida ya faru se daga baya aka kaita asibiti abin se yaso ya taba mata kwakwalwa dakyar dai da taimakon Allah aka samu kanta dukda har yanzun  dai bata koma yanda take a canbaya ba.

Seda suka gama gaishe gaishe kafin ya amayar mata da ainihin abinda ya kawoshi, tayi shiru tana sauraronsa harya gama kafin tace

"Shi Audun da kansa ya gaya maka ko kuma aike yayi maka?"

"Dakansa yazo lokacin baku gari shineya barmun sallahu akan nazo na tayashi biko da banbaki kafin ya dawo".

"Ya yardada gaskiyar ban kashe masa Da ba kenan yanzu?" Ta tambayeshi cikinkar yayyar murya, tausayinta ya kama Hayatun, Bara'atu mace ce me nutsuwa da matuqar haquri, sun taya Abokinsu baqin cikin rasata kuma a cikinsu da akwai wadanda sukayi niyyar neman Auranta se dai sanin waye Audu da tabbacin da suke dashi na cewar be dena sonta ba yasa suka gaza aiwatarda nufinsu saboda Tijarar Audu abar gudu ce tun zamanin yarintama balle a yanzu da karansa ua kai tsaiko.

"Bamuyi wannan maganar dashi ba, amma na tabbata a zuwansa baya raba nasaba da warwarewar komai, ta yiwu ya samu gamsuwar cewar baki aikata abinda aka zargeki dashi ba shiyasa ya dawo ku daidaita. Nidai abinda zan iya ce miki kiyi haquri ki mayar da komai ba komai ba ki koma dakinki kodan saboda rayuwar Yaranki. Kowa ya sani Audu be kyauta ba kuma shikeda laifi cikin duk al'amuran da suka faru amma kin sanshi, qi fadinsa baze barshi ya nuna gazawarsa ba sedai na tabbata ko be furta da baki ba zakiga Nadamarsa a aikace dan haka karkiyi wasa sa damar da ubangiji ya baki, kiyi tunani ki yankewa kanki hukunci".

Ta koma gida tana ta juya maganganun Hayatu, Inna Hajara bata ce mata komai ba dukda chanjin yanayin da ta ganta ciki se tayi tunanin kodai Hayatun yazo mata da Maganar Aure ne saboda irin zaryar da yakeyi tuntuni tasa tayi tunanin hakan.

Har aka kwana biyu da zuwan Hayatu Bara'atu bata sake ba, walwalarta ragu ainun, wani irin cakudadden yanayi take ji na farin ciki, damuwa da kuma zullumi. Farin cikinta Bikonta da Audu yayi domin ba zatayi qarya ba Allah ya sani tana qunar Audu ba kuma ta tsammanin zata iya zama da wani Namiji a duniya ta soshi bayan Audun wannan dalili yana daga abinda yasa zamanta a gida babu marshinshini be wani dameta can ainun ba,

Damuwarta kuma tunanin idan ta yarda ta koma wace kalar rayuwa zatayi a gidansa Alhalin Binta tana nan?

Zullumin da take ciki kuma shine na tunanin shin Audu ya gane cewar Binta sharri tayi mata ne da har ya nemi ta koma ko yaya? Zata so ta san amsar tambayar nan domin itace zata qara mata qwarin guiwar Amincewa buqatarsa ko akasin haka. Zata so su hadu dashi suyi maganar nan kafin ta kaiga yanke hukunci,

"Nikam lafiyarki Bara'atu? Yaro na tsaye kanki yana magana tun dazu kamar me bacci kin masa shiru alhalin idanuwanki a bude suke?" Inna Hajara data leqo daki dalilin maganar Babannan da take jiyowa yana ta maimaita abu daya, Gidan kitso Bara'atun tace yaje ya tambayo mata tunda ya shiga dakin yake fada mata matar tace taje yanzu bataji ba balle ta bashi amsa tayi zurfi cikin tunani har seda Inna Hajar tayi magana da qarfi kafin ta ankare.

"Banji shi bane Inna, me kake cewa kai kuma?" Ta fada tana gyara zamanta. Inna Hajara ta shiga cikin dakin da kyau tace

"Ai daman ba zakiji shi ba, kai yi tafiyarka wasa, ki fadamun me yake damunki tun randa Hayatu yazo gidan nan na ke lura dake yanayinki ya canza".

Barin maganar a ranta baze magance mata komai ba kuma a wannan gabar tabbas tana buqatar Abokin shawara wannan abun yasa ta fuskanci Inna Hajarar ta shiga fada mata yanda sukayi da Hayatun ranar da yazo.

Baki ta saki galala tana kallon Inna Hajara wadda ta taqarqare ta rangada guda kafin ta daga hannu sama tana cewa

"Allah na gode maka daka sa zanga wannan ranar da raina ban mutu ba, Allah na gode maka daka karbamun Addu'ata. Dama bangaya miki ba? Ba a banza Audu ya jibanci lamuranmu fiye da da ba, tun baroqarki gidansa ban taba yin salla na tashi ba tareda na roqi ubangiji daya bankada sirrin duk wani Azzalimi daya qulla miki wannan mugun shairin ba gashi kuma Allah maji roqon bawansa ya amsa roqon mu. To meye abin damuwar daya kika kasa walwala? Wannan ba abin kiyi rawa kiyi shewa ki godewa Allah ne amma shine kika tsangwami kanki kwana kusan uku bana tsammatar kinyi dariya? Ko kuwa bayan Batun komen akwai wata maganar ne?".

"Babu wani abu bayan wannan amma ni abinda ya dameni Inna banida tabbacin cewar Audu ya zabi ya maidani saboda gane gaskiyar abinda ya faru a baya ni nafi kyautata zaton zeyi hakan ne saboda Yayansa. Sannan Inna karki manta har yanzu fa Binta tana cikin gidansa, kina dai ji har ta kori Amaryar da yayi kin kuma ji rade radin da akeyi a gari kan itan ma wata qullalliyar ta qulla mata kenan bata canza zani ba tana nan da halinta babu abinda ya sauya" Bara'atun ta fada a sanyaye cikin karayar zuciya.

Inna Hajara ta galla mata harara tace

"Ai bari kiji, wlh wannan karon kika kuskura kika tsaya tsoron kishiya yayi tasiri a ranki se kinci ubanki. Ai maciji baya saran mumini a guri daya sau biyu, kin zauna da ita kinsan duk wani salon tuggu da munafuncinta dan haka kema seki shirya irin naki da zaki goga da bata hanyar cuta ko Ha'inci ba. Sannan da kike cewa saboda yayansa ne koma saboda menene dai abu daya ake fata kuma ya tabbata idan baki koma gidansa ba zaki cigaba da zama hakane babu Aure tunda dai kina kallo cikin Garin nan da kewaye labarinki babu inda be ratsa ba wanene ze Aureki?

Gidan san dai da kika gogo baqin fentin acan zaki koma ki wankeshi karma ki kuskura naji kin tado da wannan maganar balle har dalilin haka yasa ya janye muradinsa idan ma besan gaskiyar ba. Ko iya komawar da zakiyi ta isa ta karya Alqadarinta saboda ta dauki haqqinki ne saboda tayi silar ki fita daga gidan yanzu kuma Allah ya nufa zaki koma dan haka ma shiri zamu fara, yace da zarar kin amince yana zuwa za'a maida Auranko? To ki aika a kira Hayatun yau ki sanar masa kin Amince, in sha Allahu bazaki rufa qarshen watan nan cikin gidan nan ba zaki koma dakin Mijinki yan hassada da baqin ciki da masuyi mana dariya sedai su mutu Allah yayi abinda basu isa su hana ba".

Duk yanda taso fahimtar da Inna Hajara buqatar taja lokaci Audu yazo da kansa su tattauna kafin qulluwar kowacce magana qi tayi, daga qarshe ma takans taje ta samu Qanin Babansu ta sanar masa da cewar Mijin Bara'atu yazo biko bata ko tunanin maganar ta rushe tunda dama ba wani ginuwa tayi ba. Malam Sadi wanda yake cike da wulaqancin da Audu ya musu ya ginawa su Bara'atun sabon gida sannan ya siye gidan da sukaso tozartasu akanshi sedai kuma tsoron Tijarar Audun daya tuna furucinsa na cewar duk seya siye gidajen da suke ciki in suka bata masa rai sanda suka goranta masa cewar meye hadinsa da Bara'atun da har ze siya musu gida? banda Rashin zuciya matar data kashe masa Da ze dawo yana bibiya take ya kora musu gargadi sun kuma san ze aikata domin cefane Bechi yake tayi yana siyan gidaje da filaye tamkar wasu yan tsaki tuna wannan tasa yace babu komai duk sanda suka shirya suzo.

Dataga Bara'atu ba zata nemo Hayatu ba dakanta ta tura aka kira mata shi suka qulla magana ba'aja lokaci ba yayi takakkiya yaje ya sanar da Audu abinda ake ciki.

"Ashe har yanzu Bara'atu tana sona tana kuma muradin zama dani?" Audun ya fada kamar wani soko sanda Hayatu ya gaya masa yanda ake ciki. Hayatu ya karkace yace

"Bana tsammanin haka, domin munyi magana da ita kuma ban fahimci wata alama taso ko muradi a tattare da ita ba se Damuwar data nuna mun ta son sanin ka yarda da ita ko kuwa har yanzu kana mata kallon Mara Imani Azzaluma?"

"Bana son maido da wannan maganar tunda har wadda ta zalunta ta yafe mata magana ta qare a gurina" ya bawa Hayatu amsa yana wani dauke kai kamar bashi ya gama shauqi yanzun nan ba, Hayatun ya sake cewa

"Kenan har yanzu kana kan bakanka? Dagaske Zuciyarka ta aminta da cewar Bara'atu ta aikata abinda Binta ta zargeka dashi?" Hayatu ya tambayeshi yana tsareshi da ido, seya miqe tsaye yace

"Ya za'ayi kazo ka tsitsiyeni kamar wani yaronka kana tambayata? Wannan fa abu ne daya shafeni nida Iyalaina kuma ni nake zaune dasu duk wani wanda ze bayar da shaidar Halin Bara'atu bafa ze kai kamar ni da nayi zaman shekaru sama da biyar da ita ba, ku sanin zahiri kukayi mata ni kuwa na santa har badini dan haka ba ku

zaku ringa gayamun abinda zatayi da wanda zatayi ba. Saqo na baka ka isarmun na gode kwarai kuma zan sallameka yanzu In Allah ya yarda cikin zatin da ze kama nima zan shigo garin" ya qarasa yana laluba Aljihunsa ya zaro Rafar Yan goma na Takadda sababbi qal ya irgi dari biyar ya miqawa Hayatun.

Girgiza kai yayi cikin tsananin takaicin Audu ya miqe shima yace

"Banzo gurinka dan ka bani kudi ba kuma banyi maka abinda nayi shima saboda ka biyani ba nayi ne saboda Allah saboda kuma na daidaita rayuwarka tunda na fuskanci kai baka da alqibla ba kuma kasan ina kakw dosa ba. Abu daya da zance maka shine in har Allah yasa auranka da Bara'atu ya maidu kayi qoqari ka riqeta da kyau dan wlh muddin ka sake yarda Tuggu da makirci yacika ka rabu da ita se kayi nadamar hakan" yana gama fada masa ya fice daga Ofishinsa ya barshi nantsaye da kudi a hannu dan daman a sabon Kamfanin daya bude ya sameshi.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out  ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane  , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

Karo na farko da jikinsa yayi sanyi akan bacin ran daya gani qarara kan fuskar Abokinsa koma yace Amininsa. Ya mayar da kudin Aljihu yabi bayan Hayatun da har ya fita farfajiyar gurin ya kwala maaa kira. Dalilin ma'aikata dake kai kawo a gurin ya tsaya, da yawansu duk Yan uwane da qannen Abokanan nasa ya kwaso daga Bechi ya basu aiki se kuma manyan ma'aikata wanda masu kwalayen makaranta ne ya dauka aikin su suke riqe da manyan muqamai a gurin.

"Mu koma ciki muyi magana" ya fada sanda ya cimmasa.

"Tsayuwar da kaga nayi anan ma Albarkacin wadan nan yaran kaci bazanso su gane cewar kowa kana da Baraka dashi ba" Hayatu ya bashi amsa. Audu ya bata fuska yace

"Wai wane irin abu ne wannan? Ni wai a wane kalar mutum kuka daukeni da duk abinda nayi kuskurene kowa ganin baikena yakeyi?"

"Ni kuma tsanina da kai ai magana ta qare Alhaji Audu, kayi haquri ma da katsalandan din da na maka bakina da bashida linzami ne ya kasa yin shiru, bari naje kaga Rana da daga zan iya rasa motar komawa gida" Hayatu ya fada daga nan yasa kai ya tafi ya bar Audu a tsaye a gurin. Jiki babu kwari ya koma Ofis ya zauna

ya shiga Auna zamansa da Bara'atu da halayenta tareda na Bintan kamar yanda Hayatun ya shawarceshi.

Magana ta gaskiya ba tun yanzu ba yayi tunanin abubuwa da yawa da suka faru lokacin zaman Bintan da Bara'atu wanda ya fahimce su dalilin Auran Zubaida. Ya gasgata cewar A bayan idonsa Binta tana cusgunawa Bara'atu tayi amfani da yarintarta da wautarsa tayi wasa da hankalinsa abinda yasa ya fahimci hakan kuwa yanda ta kasa danne Kishinta akan Zubaida kuma har a gabansa bayyanawa takeyi shi kansa dalilin Auran Zubaidan ya fahimci halayenta da yawa da bata bayyana masa su ba a baya se yanzun kuma yaji rashin jin dadin yiwa Bara'atu uzuri a wancan lokacin har ya tsaya ya fahimci gaskiyar abinda yake faruwa ko ya bincika amma maganar mutuwar Zakariyya itace abinda ya gagara tsayar da matsaya akanta.

Magana ta Allah shida kansa ya zargi kansa daga baya da yanke danyan hukunci. Ya tuhumi kansa akan kasa bawa Bara'atun kariya koya shaideta saboda ai rainonsa ce, shine mutum na farko daya kamata ya gasgata duk abinda akace tayi ya san kuma tabbas bata da muguwar zuciyar da zata aikata kisan kai amma yanda Al'amura suka kasance a lokacin da yanayin zamansu hade da tasirin maganganun Binta ne suka juyar masa da hankali be kuma tashin gano hakan ba se bayan faruwar al'amarin daya wakana tsakaninsa da Zubaida inda qiri qiri Bintan tayi amfani da Duhun kansa ta ingizashi ruwa wannan ce tasa harya fara tunanin anya kuwa Lamarin Bara'atu ma babu lauje cikin Nadi kuwa?

To  amma kuma seya tuna Idan sharri Binta tayi mata Ya Za'ayi yan uwanta harda Yaya Sakina su goya mata baya?

Gaskiya baya tsammatar ace gaba dayansu sun hada baki akan al'amari irin wannan tilas da akwai qamshin gaskiya a cikin maganar koda ba duka ba. Wannan abin ne har yasa yayarda ze maido da Bara'atun a ganinsa hakan ze wanke laifinsa a gurinta sannan ya daidaita tsakaninsa da yan uwansa qarfin guiwar sa kuma daya samu hadin kan Binta.

Kai shi kansa ma ya sake qullewa kuma, Binta ta nuna tana son Bara'atu batayi kishi da ita ba ya auro Zubaida ta kusa haukace masa balahira babu kalar wadda be gani ba sannan yanzu kuma da kanta ta sake cewa ya maido da Bara'atu wai menene hakan ma tukunna?

Shine a birkice ko kuwa Binta ce bata da alqibla????

To duk yanda ake ciki madai ya himmatu ze maido Bara'atu, kuma kamar yanda aka saba inya nausa baya jin kira dan haka baya tsammatar akwai abinda zesa ya canza wannan qudurin.

Cikin satin ya shirya yaje Bechin, ya tara yan uwansa ya sanar dasu qudirinsa Yakubu da Baballiya ne kadai basa gurin se Hashimu da yace bashida lokacin saurar Soki burutsunsa ba kuma ze yarda dan da aka haifa a gabansa saboda yayi kudi ya zauna yana masa fadanci ba dan haka babu shi akayi zaman

Dukkaninsu sunyi matuqar farin ciki da Al'amarin kamar yanda ya tsammata ya san kuma Yakubu se yafi kowa jin dadin maganar har ya qagu yaga farin cikin da zeyi, ya bawa Yaya Baba kudaden daya ware matsayin na sadaki sannan ya sake ware wasu akan a bata tayi shirue shiryen da zatayi.

"Aa, wannan ai kai ya kamata ka bata hannu da hannu bamu ba" Yaya Baban ya fada masa amma ya dage akan su hada duka su kai saboda ya shiryawa ransa bazasu hadu ba harse an maida Auransu tukunna saboda gani yake zama ta rainashi idan yaje gurinta yanzu, amma idan yayi haka se abin yayi kamar yan uwansa ne ma suka tursasa dawowartata karma ta gane zumudinsa tazo tace zata rama abinda ya mata.

Dasu ka kai kudi kuwa ba'a tashi daga gun ba Mala Sadi yace a shafa fatiha kawai tunda ba sabon Aure bane, a karo na biyu Audu ya sake qullo Aure Binta bata sani ba se bayan daya koma ya fada mata maganar cikin Yaren da ya ke so ta fahimta a sannan cewar "Su Babangida zasu dawo nan da sati biyu".

Ta nuna jin dadi da murnarta a fili a zuciyarta kuwa dariyar mugunta takeyi tana shirya yanda zata kwarzabi rayuwarsu a ruwan sanyi kuma ba zata sake bari su koma Bechi ba balle Bara'atu taci Arziqinsa ta silarsu.

"Se a gyara musu dakin nan na tsakar gida ko, amma harda Abdullahi zasu dawo dukda dai ya nuna mun ni ba uwarsa bace tunda Bara'atu ta bar gidan nan ko hutu ne sake zuwar mana ba" Bintan ta fadi cikin kissa, Audu yayi murmushi yace

"Hardashi duk zasu dawo shi za'a gyara masa dakin tsakar gidan dai tunda yanzu ya zama saurayi su kuma su zauna dakin Mamarsu".

Bata kawo komai ba haka bata tambayeshi dawa zasu zauna ba to ina ruwanta?

Su zauna dakin su kadai ita bataqi ma wuta ta tashi cikin dare su qone ba kowa ya huta da lissafinsu.

Haka aka fara shirye shiryen gyaran tsohon dakin Bara'atu inda kuma Zubaida ta zauna, duk a salon kissa da kisisinar data qaro kwas yasa tayi shiru tana gani ana kankare kankare da liqe liqe har qofofi aka irin wanda aka canza na dakunanta da saman Audun babu jimawa sababbin shigowa na zamani se tayi tsammin ya canza ne saboda gidan duk yayi kala daya. Aka sake fente tsajar gida, ana ya saura kwana uku Bara'atu ta tare su Bilki da wasu yan uwan Bara'atu uku harda Hadiza qanwarta suka zo mata danki na neman magana.

Tarkacen kayan jere kadai suka taho dasu dan Audu ya fada musu ze saka mata Gado da Kujeru, Binta na daki tana baccin bayan Azahar suka iso Lantana da Mairo su na tsakar gida, Mairo na kai kawo tsakanin Kitchen da bakin famfo ita kuma Lantana tana daga jikin katanga inda Inuwa ta sauka tana zaro zance wanda duk gulma da tsegumin matan unguwa ne takeyiwa Mairon ita kuwa tafi ki mutu bata ce mata amma hakan be saka tayi shiru ba se zuba takeyi.

"Barka barka, baqi mukayi a gidan? Daga ina?" Lantana ta fada tana miqewa sanda su Bara'atu suka shigo da ubannin buhubhuna da suka lodo su kwalla da Samiru. Mairo ma tayi musu sannu da zuwa, ta gane Hadiza a zaman da tayi a gida dukda ta dan qara jiki amma kamanninta basu bace mata ba sannan kuma ga kamannin me gidan a fuskar Bilki hakan ya ankarar da ita cewar daga Bechi suke.

"Bismilla ku shiga tana ciki Hajiyar" ta fada musu bayan data gaidasu a mutunce, kafin suyi magana Lantana tayi tsugul tace

"Ban gane su shiga ba? Ke haka akeyi kawai daga ganin mutane kice su shigar mata daki kina ganinsu yarkace yarkace da wasu uban buhunhuna kamar yan

gudun Hijira qilama mabarata masu neman mafaka ko kinga sun miki kalar qawayen Hajiya balle kice su shiga daki kai tsaye?"

"Hayaniyar me akeyi ne haka? Lantana keda su waye?" Binta da subadadin lantana ya farkar da ita ta fada tana leqowa ta tagar uwar dakanta dake cikin tsakar gidan. Tayi sak ganin Bilki wadda suna hada ido ta tamke fuska tam.

"Kune tafe cikin ranar nan? Sannunku da zuwa aiko be sanar mun kuna tafe ba ku shigo" ta fada iyakar dauriyarta a qoqarinta na janyo su a jiki da kirki kamar yanda Turai ta bata shawara Bilki kadai ta sani cikinsu ko kuma ta gane tunda tasan Hadiza sedai sanin babu abinda ze kawota gidan yasa bata ma kawo a ranta ta santa ba. Dankwalinta ta shiga nema dan ta fito falo ta jiyo Bilki na cewa

"Da yake zuwan namu ba naki bane shi yasa be gaya miki ba, bari mu shiga can mun gode da tayi" daga haka suka ja kayansu zuwa dakin Bara'atun. Bi ta tabi bayansu da harara tareda sakin tsaki kafin ta daure kanta ta fito ranta na suya. Tsabar isa da samun guri ne yasa zasu kwaso jiki rabe rabe suzo mata gida kuma be gaya mata ba ko kuwa shima besan zasu zo ba sannan wadannan uban kwanukan da suke tafe dasu na menene ko daga Kasuwa suke? Take tambayar kanta harta fito tsakar gidan Lantana na tsaye guiwa tayi sanyi saboda yanda taji Hajiyar ta musu magana ya nuna mata sudin ba banza bane kamar yanda ta tsammata.

"Ashe baqinki ne Hajiya" ta fada tana sosa kai, Binta ta wuceta tana cewa

"Qannen megidan ne"

Seko ta dafe qirji ta zare ido, amma data tuna suda banza a gun Binta duk daya se ta dan saki ranta sedai mamaki ya kamata da har Binta tayi musu tayin shiga dakinta, to shiri suka fara haka ko kuwa duk cikin wasan kwaiwayon data fara ne?

Binta kitchen din tsakar gidan ta shiga ta tarar da Mairo na kwashe Shinkafar data gama dafawa Miyar na kan wuta tana idasa soyuwa.

"Idan kin gama akai musu abinci kafin nan a hada ruwa da lemo idan da Alkaki ki hada musu" ta bata unarni ita kuma ta amsa da

"Toh Hajiya".

Dakin da suka shigan ta wuce, sun shimfida tabarma cikin kayan da sukazo dasu Mata biyu na zaune Bilki na tsaye taba duban dakin daya qara kyau dalilin sabon fenti da qofofi harda Abun sak kwan lantarki duk aka canza se gurin ya qara haske da kyau.

Daga bakin qofar ta tsaya ta aika musu gaisuwa rai babu dadi kamar an mata dole suka amsa banda Bilki data shige daya daga cikin dakunan gurin, Binta tayi kyacci a ranta tana ayyana yanda zataci kan uwarta kafin ta kalli yar dattijuwar da ta fisu shekaru Qanwar Inna Hajara ce tace

"Bari a kawo musu ruwa, bamu san da zuwanku ba ai da an muku shiri me kyau"

"Ba komai yar nan hakan ma mungode" matar ta fada a ranta tana mamakin rashin kirkin Bintan da ake fada ita dai bata gani ba.

"Munafuka" Bilki ta fada bayan ta juya, matar da ake kira da Inna Habi tace

"Kai Bilkisu, niko banga abinda kuke fada akan matar nan ba. Yanzu wace macece zata tari dangin kishiya sunzo danki haka?"

Mairo ta aje Try data doro su ruwa da Lemo da kayan tabawa, seda ta zabura jin maganar Inna Habin ta kalli Bilki da tayi wata dariyar mugunta tace

"Karkiyi saurin yanke hukunci Inna ki dai jira kiga qarshen wasa dan in akayi wasa babu tabbacin ki fita da qafafunki daga cikin gidan nan muddin ta gano wacece ke".

Mairo ta hade yawu ta miqe tana gasgata zancen Bilkin tabbas Hajiya bata da wannan baqin Labarin, wato shi Alhaji baya gudun rigima ya ringa zuwa yana daura Aure matarsa bata sani ba dadi daya data ji da taga Alamar Bara'atu ce zata dawo dalilin ganin Hadiza.

A can daki kuwa Binta na zaune kan kujera ta harde qafa Lantana na daga qasa suna magana,

"Ku tabbatar da basu buqaci komai ba komai suke so a musu, so nakeyi idan sun koma dukda nasan waccen shegiyar ba zata taba fadar Alherina ba amma saura da yau suka fara zuwa dole dai suce na musu Kirki" Bintan ta fadawa Lantana ta miqe cikin rawar jiki tana cewa

"An gama Hajiya, kin san dama ni indai Ladabin Kule ne nan na fi kauri laka laka zanwa mutum kamar zan kwanta masa idan ina son abu".

Binta ta bita da kallo tana fassara maganarta a zuciyarta kafin taja tsaki a fili tace

"Kar nake kallonki ai karki dauka wawiyace ni kice zaki shammaceni".

Bajewa su Bilki sukayi suka kwashi Abinci abinsu, Hadiza ta tattaro kwanukan da suka gama dasu ta fito dasu waje gurin wanke wanke ta tarar da Lantana na wanke tukwanen da akayi abincin rana Mairo kuma na qoqarin dora na dare ta aje kwanukan hannunta tana musu sannu suka amsa Lantana ta qureta da ido tana si ta tuna inda ta santa bata tuno dinba Hadizan ta juya ciki. Haka taci gaba da wanke wanken tana ta qoqarin gano inda ta santa haka nan kuma ta tsaya mata a rai harta gama tana maida kwanuka ta kasa haqura ta cewa Mairo

"Nikam fuskar matar can batayi miki kalar sani ba?"

"Gaskiya Aa, ke kin santa ne?" Ta mayar mata da tambaya se ta tabe baki tace

"Oho nidai se na ga kamar nasan me kama da ita, qila kama ce to ko kuma a hidimar gidan nan muka taba haduwa da ita"

"Ta yuwu hakan" Mairo ta sake bata amaa tana cigaba da abinda yake gabanta.

Daga soro aka rafka sallama, muryar gardi ce Lantana da bata komai taja Gyalenta ta leqa taga Maza biyu da motar kayan katako a qofar gidan.

"Yauwa, kiyiwa Hajiyar magana kice ga kaya Alhaji yace a Kawo" wanda da alama shine Direba ya fada mata kafin ta bashi amsa Bilki da ta jiyo sallamar itama ta biyo sahu tana ganin kayan kuma ta gane nasu ne dan haka tace

"Ku sauke toh a shigo dasu, ga Almajirai nan su tayaku"

"Toh Hajiya" suka amsa mata kafin su fara kiciniyar kwance Belet din da suka zagaye kayan da ita.

Page 26

"Hajiya wasu Mazane da motar kayan katako, wannan me kama da Alhajin tace su shigo dasu gashi ana kaiwa wancan dakunan" Lantana ta sanarwa da Binta. Mamaki ya kama Bintan, kayan katako kuma na menene? Ta tambayi kanta, to kodai Bilkince zata dawo nan gidan da zama tunda ta samu Labarin a gida take auranta ya mutu? In ko haka ne da anyi tashin hankali da masifa kuwa, ita da gidanta bata san komai ba kawai taga ana shigo mata da kayan gado taqamar tana Qanwar Megida ko? To dashi da itan duk basu isa ba.

Fita tayi dan taji ba'asi, a tsakar gidan taci karo da Audu da batasan shigowarsa ba tana ganinsa tace

"Yawwa gara da kazo, ban fahimci zuwansu Bilki ba ga kuma wasu kaya da akw shigo dasu na menene?"

Fuska a sake ya dubeta bayan daya bawa Direban motar da suka kawo kaya kudi dan har sun gama saukewa yace

"Kayan su Babangida ne"

"Su Babangida? Su din ne aka siyawa kayan daki se kace na Amarya sababbin Gado da kujeru?" Ta tambayeshi fuskarta na nuna mamakin da take ciki.

Tafiya ya farayi zuwa dakin da su Bilkin keta kiciniyar hada kayan yana ce mata

"Amarya ce mana, ko bakya so a kwace miki kambunki?"

"Audu!" Ta kira sunansa a kausashe tana bin bayansa dan zuwa yanzu kanta ya fara qullewa bata fahimtar maganganunsa.

"Ina zuwa, bari mu gaisa dasu Goggo Ramma ki jirani a sama" ya bata amsa daga nan ya shige falon ya barta a tsaye tana saqa da warwara tana jiyoshi da Bilki yana ce mata

"Hajiya Bilki Tijjan Bechi"

"Kace na qulle jakata bana zan sauke farali" Bilkin ta mayar masa tana ajiye tsumman da take goge goge dashi, yayi murmushi yana tsugunnawa dan gaida Su Goggo Habi ya bata amsa da cewa

"Kusan haka, da dai layi za'abi se Yaya Mairo da Amina sunje sannanke amma yanzu kin san ance Albarkacin Kaza qadangare kansha ruwan kasko to kena Albarkacin qawarki bana zaku jera ku tafi tare in Allah ya yarda".

Bilki ta rangada gida wadda ta zama kamar saukar guduma a kwakwalwar Binta cikin karadi tace

"Nagode dan uwana Allah ya ida nufi, harna hangomu nida Bara'atu muna zagaye Ka'aba ya ubangiji ka nuna mun wannan rana" suka amsa matada Amin gaba daya.

A mutunce suka gaisa kafin ya fito ya ganta tsaye a gurin har sannan,

"To muje" ya fada mata se kuwa ta bishi kamar raqumi da akala zuwa saman nasa.

Zukudi tayi tana kallonsa tareda sauraron abinda yake cewa,

"Nasan ko a baya bakida matsala da ita, akasi aka samu akan abinda ya faru wanda da bakinki kika furta kin yafe har kika nemi dana dawo da ita kuma nayi matuqar jin dadin hakan, ina fatan zamanku ya canza salo a wannan karom dan zanja mata kunne sosai akan kar a kuma maimaita abinda ya faru a baya".

Murmushi yake yi irin rai fes din nan harya gama maganar, Binta data zama kamar wata hoto se idanu ke motsi suna yawo tsakanin fuskar Audun da bakinsa, so take ta lailayo Ashariya me maiqo sannan ta tambayeshi a gidan kut***r uban wa tace ya maido da Bara'atu sannan dawa yake zaton za'ayi zaman lafiya sedai bakinta ya mata nauyi, bata iya koda motsawa ba seda ya miqe yana mata sallama kan ze koma Kamfani, takun saukarsa daga matakala ne ya farkar da ita daga suman

zaunen da tayi ta zabura ta miqe sedai kafin ta kai ga sauka harya fice daga gidan dan tana kaiwa soro taji qarar Motarsa ya bar qofar gidan.

Zaman dabaro tayi ta dora hannu biyu a kai ta zunduma ihu kamar wadda aka aikowa da mutuwar Mahaifinta su Lantana da Mairo suka zaburo dan ganin menene, a dakin Bara'atu ma goggonninta biyu sun niyyaci fita banda Hadiza da Bilki da suka san za'a rina Bilkin ce ta dakatar dasu tana dariya ta cewa Goggo Habi

"Kinga abinda nake gaya miki ko? To yanzu aka fara, Hadiza rufi mana qofar nan dan ba hankali ne da ita ba se ta fado mana be kuma kamata mu biye mata ba dan ko gaban shari'a akaje mu za'a bawa laifi saboda gidanta muka zo"

"Hakane" Hadizan ta fada tana tura qofar ta rufe kamar kuwa sun san nan ta nufo dan zabura tayi kamar zakanya ta durfafi dakin tana kuka tana koro ruwan Ashariya tamkar zararriya ta shiga jijjiqa qofar da niyyar cirera sedai ko Gezau.

"Wallahi tallahi na rantse da girman Allah in baku bude qofar nan ba sena babbake ku a ciki, sena nuna muku ki qananan yan iska ne, ni za'ayiwa haka?" Ta fada cikin qaraji tana cigaba da bubbuga qofa. Dattijai biyun suka tsure, Goggo Habi fadi take

"Me gado a bude qofar nan karta qona mu kinji abinda take cewa"

"Kyaleta Goggo duk kurarin banza ne baki ne da ita babu abinda zata iya a aikace wanda zeyi abu ai baya fada" Hadiza ta bata amsa, Bilki dai bata tanka ba se jera samiru takeyi abinta tana yan waqoqi tamkar ma bata jiyo hauka da Tijarar da Binta takeyi a tsakar gida.

Iyakar masifa, bala'i da duk kalar Ashar wata ma a Bakin Bintan goggonnin Bara'atu suka fara jinta yau seda kamar yanda Hadiza ta fada kurarin banza take dan data gaji da buga qofar gefe ta zube tana kuka kamar me tana maganganu da cin Alwashi kala kala. Mairo data ga abin bana qare bane ta koma kan aikinta ranta duk babu dadi da wannan al'amari, ita kuwa Lantana tana nan tsugunne daga gefenta tun bayan data samu tsarabar hambari a qoqarinta na riqeta ta gwabje mata fuska daga nan ta matsa gefe amma taqi tashi daga gurin se fadi take

"Kiyi haquri Hajiya, ki tashi mu koma can daki kisha ruwan sanyi"

"Se naci "gi***n du***in uwarki Lantana idan kika sake cewa nayi haquri, Allah ya tsinewa haqurin kema Allah ya tsine miki" ta fada dole Lantana taja baki ta kame tana sosa fuska dan inda ta mangaretan har sannan be dena mata zafi ba tsabagen neman gurin zama da iya gulma yasa take zaune a gurin har sannan.

Binta na kuka wiwi kamar Jifa se ga Turai ta shigo gidan ita da wata mata, tun daga qofar gida ake jiyo ihu da kururuwar Bintan dan haka cikin sauri suka shigo dan ganin me yake faruwa.

"Na shiga uku ni Amina, me ya faru? Waya mutu Binta?" Turai ta fada tana nufar qawar tata da ta ke nan zaune kamar kayan wanke ta miqe qafafu kanta ya tuje dan tun fara Tijarar tata dankwali ya cire. Qoqarin kamata ta shigayi danta miqe amma ta kasa saboda yanda ta saki jiki ita aba ba kadab ba ganin Turan kuma yasa ta sake sakin wani kukan me ban takaici kamar wata yarinyar goye tana fadin

"Na shiga uku Turai Audu ya kasheni, wai Bara'atu ya mayar be gaya mun ba"

"Har naji sanyi a raina ashe ba mutuwa akayi ba, dan Allah kama jikinki ki miqe, Zainab zoki tayani mu dagata" Turai ta fada jin abinda Binta tace. Dakuar da sidin goshi bayan sun hadu su uku harda Lantana suka kai Binta daki se sannan ma suka tuna da Yaron da suka baro a daki ya fado daga Kujerar data kwantar dashi yana ta tsala kuka gwanin Tausayi.

"Dauke shi Dan Allah kuje waje ki rarrashe shi" Turai ta fadawa Lantana, ta dauke Nazirun tayi waje dukda ba haka taso ba, so tayi taji komai dukda ta tsinci kan zancen amma zata so ayi komai a gabanta yanda zata fi jin dadin bata labari idan ta fita.

"Yanzu saboda Allah me kikayi haka? Akan wata baquyiyar Bara'atu shine kika kwanta tsakar gida gaban masu aikin ki kina tumami kamar wadda ta kwace daga Turu wani irin abin kunya ne wannan Binta?" Turai ta fada cikin fushi. Binta dake kuka tace

"Ki qyaleni, saboda ba'a taba miki kishiyar nan bane shiyasa duk abinda nayi kike daukarsa shirme ke kinsan zafin abin ne balle ki gane yanda nake ji?"

"Koma menene, kome kikeji be kai ki zauna kina zubarwa da kanki mutunchi ba a samu abin fada akanki, wannan haukan da kikayi wlh Allah yasan inda ze tsaya dan wannan munafukar me aikin naki kina kallonta kinsan nadar rahoto takeyi. Allah na tuba ba Bara'atu ba ko mata uku Audu yace ya daura aure dasu ya kai ki kwanta kina kuka akai balle Bara'atun da ko kashin jikinki ya fita a gurinki, har meye abin tashin hankali a matar da kika san idan kinga dama ko ruwa ba zaki barta tasha da dadi a cikin gidan nan ba.

Kika kara da Zubaida ma kika koreta balle Bara'atu karan kada miya? Dan Allah karki bada ni mana, a gaban Audun kikayi wannan haukar ai kuwa kin kashe kanki kin ruguza duk wani shirinki na baya da wanda ya kamata muyi a gaba wlh murus kin kashe kanko a gurinsa".

A hankali ta fara rage kukan da take tana kallon Turai alamar sonjin qarin bayani, ta yaya ta kashe kanta a gurin Audu ta ruguza shirinta ma baya dana yanzu?"

"Wai ma tukunna, ta ya akayi har ya maida ta baki sani ba?" Turai ta jefa mata tambayar, taja Dankwalinta da aka tsinto mata a Soro ta face majina kafin ta shiga bawa Turai Labarin yanda sukayi kan zancen maido da yara sa dalilinta nayin hakan har zuwa kan zuwansu Bilki da maganar da sukayi dashi dazun.

"Tirqasa, au yanzu suna cikin gidan nan kikayi wannan abin kunyar gaskiya Binta baki haduba kwakwata kin bada ni wlh sauqinta daya be ga wannan qaramin haukan naki ba dan wlh da ace yana nan kikayi shikenan kin gama yawo babu wata fankama da zaki sake yi masa ya yarda" Turan ta sake fada kafin ta muskuta tayi qasa da murya taci gaba da magana.

Se bayan sallar Isha'i su Turai suka bar gidan bayan sun tattauna batutuwa da yawa da Bintan tareda matar da suka zo tare, jan kunne tayi mata sosai akan abinda suka tattauna ta fito ta rakosu zuwa sannan zuciyarta ta danyi sanyi kadan. Ta kalli dakin Bara'atun ta ciji yatsa, ta ci Alwashin seta gwammace mutuwarta da dawowa gidan Audu, zaman da sukayi a baya sharar fage ne yanzu ne zata nuna mata Asalin ita

din wacece ta shayar da ita ruwan azabar da ko kallon inda Audu yake aka ce ta yi ba zata yarda ba.

Tana tsaye tsajar gidan bayan ta rakosu Turai Bilki ta fito sukayi wa juna kallon tara saura ta wuce Abinta bakin famfo ta bar Binta da jan qwafa. Kaf setaci uwarsu wlh a sannu zatayi maganinsu. Se yanzu kam taga baiken kanta data kasa riqe kanta tayi shirmen dazu ai su Bilkin zasu qara rainata su tafi da ita a baki amma ta gode Allah da batayi a idon Audun ba. Tana hawa Barander yayi sallama, ji take kamar ta qunduma ashar a maimakon amsa masa amma ta dake iya dakiya ta amsa sedai bata iya ta tsaya ba balle ta juyi ta masa sannu da zuwa ta shige daki tana jiyo shi suna magana da Bilki kusan minti biyar kafin yabi bayanta.

"Uwargida ran gida ko Amarya zance?" Ya tsokaneta yana zama akan kujera tace

"Uhm" kawai tana cirewa Naziru Nafkin.

"Yau sarautar ta motsa kenan?" Ya sake sako mata wasa ta daure ba tareda ta kalleshi ba tace

"To kai ya ka gani?"

"Ras" ya fada kafin ya laluba Aljihunsa ya zaro wata Farar Embelop me dan girma ya miqa mata se sannan ta kalle shi ta saka hannu ta karba tana budewa, Awarwaro ne guda hudu a ciki na zinari, ta hadiye yawu Aljanunta na son abin duniya suka motsa.

"Tukuici ne, ko ince sadakin fadar kishiya ne" Audun ya fada.

Maganar Turai ta dazu ta fado mata da tace

"Ki kwantar da hankali kiyi masa laka laka irin yanda kikayi sanda kika shigo gidan, kina kallon dai wahalar da kikasha lokacin daya Auro Zubaida ta isheki ishara kisan tashin hankali ko masifa ba zata biyar da Audu ba sedai lallashi da kwantar da kai ta hakane zaki moreshi sannan ki samu biyan buqatarki to tabbas ta fara ganin gaskiyar hakan.

Dake taga abin duniya se gashi harda yi masa murmushi tace ta gode. Ta goye Naziru suka wuce dakinsa tare, ya shiga ciki ya watsa ruwa kafin ya fito ta shirya masa abinci a ranta tana lissafin abubuwan da zata nemi yayi mata yanzu da yake neman shiri da ita. Yana cin abinci yana mata zancen ai jibi Bara'atun zata tare

kuma su Bilki zasu zauna nan harse tazo kafin su koma Bechi haka ta ringa daurewa tana yaqe duk a qoqarin ta na amfani da hudubar Turai na karta bari ta canza masa tunani akan wanda yake mata game da Bara'atu ta hakan ne zata sake korata a ruwan sanyi ba tareda ya zargeta ba.

Kwanaki ukun da su Bilki sukayi a cikin gidan sun zamar mata kwanaki mafiya baqi da muni a rayuwarta. Idan ta tuna wai Bara'atu ce zata dawo mata gida se taji kamar ta shaqe kanta ta mutu kawai ta huta da takaici, ranar da zata tare din kuwa tun farar safiya yana fita itama ta fice gidan Turai dan bata da sama da ita a Kano wuni guda suna qulle qullen sharri na yanda za'ayi bata komo gida ba se bayan sallar Magriba lokacin ta tabbatar da su Bilki sun tafi idan ma Bara'atun tazo da yan rakiya duk suma sun koma inda suka fito.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

BARA'ATU

Gaba daya komai daya faru ya ringa mata tamkar fim, sanda ta samu labarin an mayar da auranta da Audu daga zuwa kai sadaki rasa tantance me zatayi tayi se kawai ta shiga daki ta kulle ta kwanta kan Katifa tayi shiru ta bar Inna Hajara da yan uwanta dake ta murna a tsakar gida.

Ita kadai take hangowa kanta makomar rayuwarta, su murna sukeyi amma ita tasan meta baro a gidan Audu wanda bata fatan ta koma ta tarar. Sannan abinda yake qara sanyaya mata jiki yanda har kawo lokacin bata saka Audu a ido ba dukda ta samu labarin yazo yana garin ta dauka kafin faruwar komai zeje su zanta yaji ra'ayinta taji nashi amma se kawai ta tsinci anmaida mata aure babu jin ta bakinta babu komai abinda ko sanda tana budurwa ba'ayi mata ba anya kuwa Audu ne yake son komen nan ko kuwa yan uwansa ne suka tursasashi maida ita? Tayiwa kanta tambayar.

Da yammacin ranar Kawunta ya kai musi kudin sadaki hade danashirue shirye da Audun yace a bata tayi, wannanya qara kassara mata jiki harta kasa daurewa ta fashe da kuka domin ta tabbatar da cewar ba ra'ayinsa bane na mayar da ita dole wani ne ya sakashi idan kuwa hakane ta tabbatar seta gwammace kida da Karatu gashi bakin Alqalami ya bushe ballantana tace a koma baya.

A sanyaye take komai ga sati biyun da aka saka na kwanakin tariyarta suna qaratowa har sannan kuma bata saka Audu a ido ba, da tayi maganar wa Yan uwanta Hadiza ce kadai ta fahimceta dan Inna Hajara fada take mata akan waita fiya saka damuwa a rai ai babu yanda za'ayi ace dole aka wa Audu ya mayar da ita tunda shi ba yaro bane ba rashin zuwan sa kuma bata san uzurinsa ba kuma dai duk tsiya gidansa za'a kaita idan taje can koma menene zasu tantance. A wannan gabar ita da kanta seda ta ga baiken Innar tata ta kuma fara yarda da abinda ake fadi a gari na cewar kwadayi ne yake Dawainiya da Innar tata.

Idanba kwadayin abin duniya ba kowacce uwa tana qoqarin siyawa yar tamutunci a gurin Miji amma ita wannan be dameta ba fatanta kawai ta koma gidansa duk irin rayuwar da zatayi bata sani ba. Cikin wannan zullumi da Taraddadi ta shiryi dawowa gidan Audu karo na biyu a matsayin matarsa. Tsirarun mutane suka rakota ciki harda yan gidansu Audun basu jima ba kuma saboda motar data kawosu yana tsaye ga kuma wadda zata maida su Bilki dan haka suka rankaya suka koma ana ta tsegumin Ina Binta ta tafi basu ganta ba.

Bayan sun tafi gidan ya mata shiru dan ita kadai ta taho yaran ance se ta kwana biyu a kawo su a cewar Hadiza tasha Amarci a tado da tsohuwar zuma tukunna, dariya ma maganar ta bata dan bata hango wannan Amarcin da suke fada muddin Binta na cikin gidan nan. Ta fita tsakar gidan ta tsaya tana qarewa ko Ina kallo, gidan na nan yanda ta barshi se yan canje canje na kwalliya da fenti da aka sakeyi masa yanda ko ina yake shiru cikin Aminci a ranta tayi fatan ina ma gurin ya dawwama a haka? Ina ma rayuwarsu ta baya sanda suke zaune a daki ciki daya a Bechi ta dawo?

Har akayi sallar Magriba babu Binta babu Audu, bayan tayi sallah ta gyara kwalliyarta, babu laifi ta qara jiki akan shekarun baya da take gidan dukda ba qiba tayi ta azo a gani ba amma ta murje, yanayin ta dai na Shiru shiru da sanyin jiki yana nan wanda halittace canzashi da kamar wuya, a bangaren wayo ko ace wayewar kai ma babu wani cigaban Azo a gani data samu domin shekaru kusan hudun a Bechi tayi su ta sake komawa duhun kan data baro, mutanen da taci gaba da mu'amala dasu sune dai wanda ta sani tun yarintarta babu wani sabon Ilimi ko wayo data qaro ita ba Makarantar Boko ta shiga ba balle Islamiyya kullum tana zaune a gida kwalliya kanta ba yi takeyi ba Hadiza ce tayi qoqarin ganin ta saitata tayi gyara ciki da waje a dan taqin kwanakin da aka saka na tariyar tata, ita da yake yanzu a cikin Kumbotso take aure babu laifi kanta ya waye fiye da Bara'atun dukda daman tun Asali ba zubinsu daya ba dan da ace Hadiza ce ta samu damarda Bara'atu ta samu ta auran Audu tabbas ba Binta ba kowacce Macece zata iya karawa da ita.

Seda aka fara kiraye kirayen sallar Isha'i taji motsin an shigo gidan, ta taga taga wucewar Bintan,gabanta ya yanke ya fadi har seda ta dafe ta shiga karanto Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un, fargaba da razanin da ta ke shiga duk sanda ta ganta a baya irinsa takeji a yanzu ta rigada ta tsorata da Bintan Allahya sani. Tana cikin wannan halin aka sake shigowa wannan karon Audu ne shida Musbahu. Faduwar gabanta ta ninku tana jiyoshi suna magana dan bata iya leqawa ma ta ganshi ba harya sallami Musbahun taji alamun tafiyarsa yayi can gurin Binta kafin ta iya sauke numfashi.

Tana cikin sallar isha ya shiga dakin, ganin tana sallar yasa ya fita bayan ya fada mata sallahun ta sameshi a falon Bi ta idan ta idar haka ta ringa taraddadin taje ko kar taje bayandata idar da dallar daga qarshe dole ta miqe, babu wani sauran magana ta rigada ta dawo cikin gidan nan abu biyu ne kodai ta tashi ta kwatarwa kanta yanci ko kuma rayuwarta ta qare cikin tsoro da firgicin Miji da kishiya.

Tana tafe sallaf salaf a ranta tana kewar Balaraba, qila basu san ma an mayar da Auran nasu ba tasan da tana nan data qara mata qarfin guiwa dan duk sanda sukaje Bechi idan taje gurinta maganar kenan take mata ta tashi ta kwatarwa kanta yanci wannan sanyin Jikin babu inda ze kaita.

Da sallama ta shiga falon kanta a qasa bata zauna ba har seda ya bata umarni ta dan dofana kan kujerar data fi kusa da ita.

Maganganu yayi musu dan ba za'ace Nasiha ba wanda kusan duka jan kunne ne ga ita Bara'atun akan abubuwan da suka faru a baya da baya so a sake maimaita irinsu ya kuma tabbatar mata da cewar Binta da kanta ta nemi daya maido da ita har yana fada mata a wannan karon itace qasa da Binta dan haka ta bata girmanta na kasancewarta Gaba da ita a aure da kuma shekaru.

Yanda ya ringa maganar gaba daya se taji ta muzanta ta kuma gasgata tunaninta na cewarba ra'ayin kansa bane wani ne ya sakashi ya maido da ita amma me yasa duk cikin mutanen se Binta? Meta shirya? Wace kitimurmurar take so ta sake hada mata data nemi a maido da ita iyakar Taskun data sakata a baya be isheta ba kenan?

Ya gama maganarsa ya basu damar me magana tayi, Binta da kanta ya gama fasuwa da yanda ya nunawa Bara'atun ita ba komai bace yanzu a gurinsa, taji ina ma haka ta kwantar da kai lokacin daya auro Zubaida tabbas da martaba da qimarta a gurinsa ta zarce ta yanzu amma hakan ma babu laifi zatayi duk iyawarta ta sake kafa kanta.

"Nidai babu wani abu daga gurina, Bara'atu daman tun asali yar uwa na dauketa ba kishiya ba ina fatan kuma itama wannan karon zata saki ranta ta zauna dani zuciya daya, sannan kafin a kai ga maganar rabon kwanaki akankwana uku da zakayi mata na qara muku sati kunga kwana Goma kenan saboda kuji dadin Amarci sosai a tuna baya" Bintan ta fada cikin kissa. Wata dariyar Bosawa Audun yayi, Ita dai Bara'atu kanta yana qasa, to me zata ce musu kuma? Tana jinsu suna ta soki burutsunsu shida matarsa kafin aka rufe taro yace taje yana zuwa.

Bata tsammaci zuwansa da wuri ba se gashi ko minti goma bata rufa da komawa ba ya shiga da ledar kayan Marmari da kaza.

Washe gari haka ta tashi mamaki na neman kasheta, wato Namiji ko, Namiji duk wadda taci laya akansa ta shigenge.

Irin yanda Audun ya ringa mata rawar jiki yana fada mata kalamai jinsa kawai ta ringayi, haka da safe be fita ba, Binta da ta kusa hadiye zuciya cikin dare ta mutu saboda baqinciki da kishi amma tun farar Asuba ta tashi ta hau aikin da babu lada domin ba dan Allah tayi shi ba. Lafiyayyen abin kari tayi musu ta kai qofar dakin Bara'atun ta kwankwasa kafin ta ajiye dan ba zata iya shiga ba zata iya manta shiri takeyi ta bazara komai gayyar ta watse. Haka ta ringa musu wannan kabakin arziqi harna kwana uku kafin ta kasa cigaba, yanda Audun ke rawar jiki akan Bara'atun ya tassama haukatata.

Ita dashi yake ce mata daya san ze samu wannan kwanciyar hankalin da nutsuwa a gidansa da Bara'atu ya maido a maimakon ya Auri Zubaida har yana tambayarta me yasa bata kishi da Bara'atu amma lokacin Zubaida taqi kwantar da hankalinta?

Ta rasa amsar da zata bashi, ba abin ta daddana masa Ashar ba se kawai tace saboda ita Bara'atu a gidan ta tararda kuma Zubaida ba wai kishi da ita takeyi ba kawai Asalinta ne be mata ba da ace itama a gaban Iyayenta ya aurota tamkar Bara'atun da lafiya lau zasu zauna.

Ango Audu dai ya ci karensa babu babbaka ya murji soyayya yanda ya kamata shi da kansa ya tabbatar da akwai banbanci tsakanin Abinda zuciyarka ce take sonsa da kuma wanda wani dalili yasa kake tare dashi. Bazeyi qarya ba yana son Bara'atu, haka Zubaida da kansa ya ganta yaji yana sonta har kuma yanzun da da dama ze maidata itama suci gaba da zama yanda yake jin su biyun a zuciyarsa Binta bata kama qafarsu ba amma kuma ya rasa yanda akayi ta fisu tasiri a ransa, yafi girmamawa da daukar maganarta fiye da tasu menene dalilin hakan?

Seda ya kwana uku cif yana hutun Angwanci kafinya koma fita aiki a ranar kuma Binta ta sauke hau din data dorawa kanta ta yi mush girki ta bar Mairo taci gaba. Baqin cikin data qunsa a kwanakin Allah yayi yawa dashi tana nan kuma tana jiran ranar ramuwa kwanaki goman nan cif su ta bawa Bara'atun matsayin kwanakin farin cikinta a gidan daga nan kuma wasan ze canza salo.

Kamar yanda ta qudurta kuwa haka ce ta kasance kwana goma Audu yayi a dakin Bara'atu wadda zata iya cewa kwanaki goman nan sun zarce shekaru goma na rayuwarta dadi dominbata taba sanin dadin Aure ba a zaman da tayi da Audu kamar na wannan kwanakin. Ya shayar da ita madarar qauna tarairaya da soyayya ba'a magana gaba daya ya goge mata hadda ya kuma goge duk wani shakku da take dashi akansa na cewar ya dena sonta ko yana da wata manufa akan maidota da yayi, walwalarta ta qaru har wani kyau da sheqi ta qara kana ganinta kasan hankalinta a kwance yake Yanda kuma Bintan take sabgogin gabanta bata shige mata irin na wancan karon yasa ta fara tunanin da gaske ta aje makaman yaqinta zasuyi zamane na babu ruwan kowa da kowa wanda zata so hakan.

Randa Audun ze bar dakinta zuwa na Binta har kuka ta masa ya ringa rarrashinta akan kwana biyu ne kacal ze dawo sannan a qarshen satin zasuje su dakko su Babangida ma su dawo gida a saka su a makaranta dan Zakariyya ma za'a dawo dashi duka za'a hadasu a kaisu makaranta me kyau wannan yasa ta dan rage damuwa. Lafiya lau yayi kwanaki biyunsa dakin Binta randa ya dawo matasuka tafi Legas wanda tafiyar tazo mata a bazata ce mata kawai yayi ta shirya zasuje wani guri ta dauki kaya kala biyu farko ma ta dauka Bechi zasuje seda ta ganta a filin jirgi ta shiga zare ido, yau gata zata hau jirgi itama bata sake tsinkewa ba seda suka sauka yace mata Legas sukazo ta ringa tsalle kamar yarinya kamar wasa se gasu a gidan su Yakubu.

Da murna tayi musu yawa ita da Balaraban se kawai suka fasa kuka, Yakubu ko bakinsa ya kasa rufuwa, Audun ya shammaceshi dan besan duk abinda ya faru ba wannan abun da yayi kuma ya saka ya wanke duk fushin sa da yake damfare a ransa yaji matuqar dadin ganinsu ko ba'a fada ba kuma yasan hankalin kowannensu a kwance yake.

Aka ringa hirar yaushe gamo, A gidan sukayi kwanaki biyunsu dukda Audu yaso su kama Hotel tunda gidan qarami ne dakuna biyu ne daga nasu Yakubun se na yaransu amma Yakubu yace dole su zauna haka baquntar kwana biyu dai haka suka dawo Kano cike da kewa dan kwanaki biyun ba qaramin dadi yayi musu ba sun fita yawo har bakin ruwa sukaje aka musu hotuna Audu be taho ba seda aka wanke musu hotunan suka taho da kwafi dinsu.

A kwanaki biyu ba qaramin Ilimi Balarana ta zazzagawa Bara'atu ba da kuma wanda ta gani da idonta ta koyo, sun dawo ta qudiri niyyar tabuka abin kirki a wannan karon itama, zatayi amfani da duk dabarun data koya mata na riqe Miji, zatayi iyakar yinta yanda ba fata takeyi ba koda ace wani abu ya sake faruwa badai a zargeta da sakarci ko rashin sanin ciwon kai ne ya janyo mata ba.

Tafiyarsu Legas ta qara rura wutar bala'i a zuciyar Binta, dukda ya gaya mata kafin su tafi abin ya zafeta matuqa harta kasa jurewa ranar da suka dawo a dakinta ya sauka bata iya shanyewa bata amayar masa da abin da yake cikinta tas akaci sa'a be kulata ba domin shima ya qaro karatun zama da mata, ya san da akwai abubuwan da mace zatayi wanda Kishine yake tunzurasu babu yanda kuma zakayi da ita dole kayi haquri.

Watanni uku da dawowar Bara'atu, a hankali kyakykyawan zaman daya fara ginuwa tsakanin Ma'auratan ya fara samun tazgado, salon da Binta tayi amfani dashi a zamansu na farko da Bara'atu shita sake maidowa na cusguna mata ta hanyar bautar da ita da kuma zaginta tareda muzantata sedai a wannan karon ta canza salo ta kuma biyo ta hanyar da a qaramin wayo da Dabarar Bara'atu ba zata iya kaucewa Kaidinta ba.

Da farko ta dakatar da Lantana da Mairo daga zuwa aikinsu wanda tayiwa Audu qaryar Lantana sata takeyi mata shiyasa ta koreta ita kuma Mairo ta dakatar da ita ne kawai su ringayin girkinsu da kansu be kyautu ace abincin me aiki ze ringa ci ba bayan yana da mata har biyu sauran Ayyukan gidan ma duk bazasu gagaresu,

"Da ze yuwu mu zauna da Maman su Baba mu tsara yanda zamu ringa ayyukanmu kawai ba se wani ya taimaka mana ba. A gidan Yaya Aminu naga irin tsarin ya burgeni kuma hakan ya qara shaquwa da fahimta a tsakanin matansa kana gani duk gidanku babu Kishiyoyi masu fahimtar Juna kamar matansa haka yayansa kansu a hade baka ma iya banbance wannan na waye to nima irin zaman da nake so mu gina a gidan nan kenan duk abubuwan da suka faru a baya su zama tarihi mu tun kari gaban mu" abinda Bintan ta tsarawa Audu kenan cikin salo na zallar kissa da iya hada tuggu.

Audun yayi na'am da shawararta kuma yaji dadi, tabbas Matan Aminun abin kwatance ne yanda suke zaune tamkar Dadansu da Goggo Fadi kafin rasuwar Malam Tijjani, haka suka tashi gidansu aiki da komai tare su Dadan su keyi kwana a Turakar megida ne kadai ze nuna maka wadda take da Girki a cikinsu shiyasa shawarar tayi masa dadi yasan kuma Bara'atu ma zatayi Na'am da hakan itama.

Sanda ya sanarda Bara'atu hukuncin da Bintan ta yanke na sallamar su Lanatana batace komai ba saboda daman ba ita suke yiwa aiki ba, sharar tsakar gida kadai abinda take mora a aikin nasu tunda ba Girki daya sukeyi ba kamar dai farkon zamansu ne me Miji tayi abinci dashi har gara Mairon tana kama mata wasu abubuwan idan tana girki a Kitchen din tsakar gidan Lantana kuwa kallon Arziqi ma baya hadasu balle aje a ga batun tayata aiki shiyasa sallamar masu aikin bata dameta ba.

Anyi kwana biyu da maganar ya tarasu falonsa domin tsara yanda zasu raba aikin gidan, Binta ce da girki ranar tana ta kai kawon hada musu abinci su duka gaba daya harda yaran dan sun dawo Abdullahi ma anyi hutun makaranta yana komawa gida ya samu labarin Innarsa ta koma Kano kwanansa biyu shima ya hado kayansa ya taho Audu da Binta suka ringa masa tsiya.

Seda aka qare cin abincin suka sallami yaran suka sauka qasa kafin suka nutsu cikin kujera dan yin maganar data tarasu din.

"Dan Allah ya kukaji abincin yau? Har wani dadi ya qara na daban saboda mun hadu Ahali gaba daya munci tare, gaskiya haka zamu ringayi daga yanzu saboda ni

daman a gidanmu mun saba tare muke cin abinci gaba daya kaima ai ka sani" ta yi maganar tana kallon Audu se shima ya murmusa ya mayar mata da cewa

"Kwarai kuwa, ina fatan kuma wannan hadin kan ya dore"

"Nikam daga gurina babu wata matsala ai kamar yanda na gaya maka komai daya faru a baya ya wuce itama ina fatan ya zama haka a gurinta dukda har yanzu dai naga ta kasa sakewa se ta ringa darare jikinta kana kallo fa tunda muka zauna yanzu bayan gaisuwa babu abinda ta qara cewa ta barmu muna ta zuba kamar lalatattun Radiyo" Bintan ta soko Bara'atu wadda kanta ke qasa tana kallon lallen da tayi kwanaki biyu da suka wuce sanda ta karbi girki maganar Bintan kuma bata saka ta dago kota amsata ba saboda ita har yanzun ranta yaqi Aminta da wannan takun na Binta ba kuma taso ta saki jiki da ita ta sake shammatarta irin na wancan karon.

"Nikam matsalata dake kenan Bara'atu kin fiya qauyanci kiyi abu wani salo salo kamar mara jini a jiki tsakanin nida Bintan waye baqonki da ba zaki sake a cikinmu kiyi sabgoginki ba?" Audu ya fada yana gyara zama.

Seta daga kai ta kalle shi, kalmansa sun mata zafi dan har kwalla ce ta tarun mata a ido, bata da dauriyar zuciyar da zata jure cin mutunchi ko tozarci yanzu zata karaya ta fara kuka banda tsabar wukaqanci ita ze kalla yacewa Baqauya to ya suke shida itan? ai babu me gorantawa wani Asali dan tushensu daya koda yake shi daman be iya maganaba.

"Haba kai kuwa ya daga magana kuma zaka fara ce mata yar qauye? Koda yake kunfi kusa ai, Qauyawa biyu, yan Qauyen Bechi" Bintan ta zage su duk su biyun a wasance garan kuwa se ya hau dariya yana cewa shi ba baqauye bane ai baqauye wanda bashida wayewa kenan shi kuwa da yake fes ko haihuwar Birnin ba zasu gwada masa wayewa ba ai ita kuwa Bara'atu abun ya sake qular da ita amma ta hadiye bata ce komai ba sedai ta quduri niyyar yi masa maganar muddin suka kebe, zata gaya masa bata so, karya sake wulaqantata a gaban Kishiya (as if zata iya).

"Yanzu dai muyi abinda ya taramu dare yanayi" Audun ya dakatar da wasan ganin Bintan na nema ta wuce gona da iri a wasan nata ta fara tabosu tana cewa wai kaf garinsu banda Yakubu waye yayi Karatun zamani dan shi kansa bata yarda yayi sakandiran ba

"Ke kuwa nasan dakyar ma idan kin taba shiga Aji" ta sake takalo Bara'atu wanna yasa ya dakatar da ita danshi basa shiri da raini.

Bintan ce dai tayi magana akan tsarin da take ganin zasuyi, Me girki ita zata dafa abinci wa gida gaba daya, zasu hade girkin kenan sabanin da da kowa takeyin nata sauran Ayyukan gida kuma shara da wanke wanke wadda bata da girki tayi harda sharar dakunan junansu sedai idan da wani uzuri ko lalura to dayar na iya daukewa dayar aikinta tsarin Binta kenan.

Maganar sharar dakunan Junan tayiwa  Bara'atu banbarakwai dukda take Baqauyiya mara Ilimin amma tasan ko a karkarar da suka fito Kishiya bata sharewa kishiya daki sedai idan da lalura ina laifin iya tsakar gida? Tana jira taji Audun yace wani abu akai amma shiru sema jaddada hakan yayi da yace sannan ya juya kanta wai yana tambayarta ya mata ko tana da magana? Taga to me zata ce musu? Ta ce be mata ba su samun abun magana daga shi har matar tasa kenan se kawai tayi shiru suka gama abinda zasuyi ta musu sallama ta wuce se bayan data koma dakinta kuma abin yayi ta damunta, Balaraba ta gaya mata karta ringa barin magana a ranta muddin akan abinda ze cutar da itane, koda za'a ce bata kyauta ba gara ta fada a gyara akan ta bar abin a cikinta ta cuci kanta da kanta to amma tana gudun tayi magana kuma su canza mata ma'ana saboda muddin bada zuciya daya Binta tayi wannan abin ba to tarko ta hada mata so take tace wani abu ta ruftata ciki, haka ta kwana tana saqe saqen me zatayi?

Ta yarda da wannnan tsarin ko kuwa dai ta gwada sa'arta gurinnusar dashi rashin dacewar hakan? Bata son fitina ba kuma tason abinda ze sake janyo mata matsala da Binta ko Audu, a baya shiga dakinta na qasa da Minti biyar ya janyo har aka laqa mata sharrin kisan kai inaga yanzu taje shara?

A bangaren su Audu kuwa Bara'atun Binta ta gyara zama tana tsiyaya masa Zobo a kofi tace

"Se naga kamar Bara'atu bataji dadin maganar da akayi ba"

"Kinsan ta ai ita ba'a fiya gane ina ta dosa ba tunda kikaji bata ce komai ba hakan ya mata itama kenan" ya bata amsa bayan daya kurbi zobo. Ba haka taso ji ba dan haka ta sake kalailayewa tana cewa

"Uhm haka dai kace amma ni yanayin fuskarta na karanci kwata kwata maganar man bata zauna mata ba, idan lura kuma ai tunda kuka dawo daga Legas din nan tsumewarta tafi tada, kafin ku tafi ai tana dan sakin fuska idan mun zauna irin haka amma yanzu fa sedai tayita sunkuyar da kai tana irga yatsunta kodai har yanzu ta riqe abinda ya faru a baya ne a ranta?"

"To idan maganar abinda ya faru a baya ne ai ke ya kamata ki qullaceta ba ita ba tunda ke akayiwa laifi ko?" Cewar Audu, se tayi narai narai da fuska tace

"Nima dai hala na gani, nida aka cuta na dubi Allahmace na yafe amma kuma tazo tana so tayi zaman gaba dani idan fa ba a gabanka ba ko gaisawa bama yi bana so ina kawo maka maganarta ne kaga kamar wani abun nake so na hada shiyasa amma wlh sam duk yanda nake so na jata mu zauna lafiya taqi sakin jiki kayi mata magana in dai akan abinda ya faru take tunani dataqi sakewa dani wlh na yafe kuma na manta komai ta saki ranta mu zauna lafiya abinmu mu kama ka ram yanda ba zaka sake hango wata ba balle wannan karon ma ka sake kwaso mana Kara da kiyashi".

"Allah sarki Zubaida, aiko kin tunamun gobe idan Allah ya kaimu zanje na dubo su Hassan dukda dai nayi musu aike cikin satin nan amma gara naje na ganosu da kaina" Audu ya fada dan maganarta ta qarshe yasan da Zubaidan takeyi aiko abinda ya fada ya doketa har seda ta kware da Zobon da take sha ta ringa tuttula tari yana mata sannu dakyar ya lafa mata ido yayi jajir ta ringa maida nufashi zuciya na tafarfasa.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh Iallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

"Sannu bari na shiga ciki nayi wanka kafin ki gama" ya fada mata bayan da tarin ya lafa mata ya shige daki tabi bayansa da harara tamkar idanunta zasu zazzago. Tashi tayi ta hau tattare kwanuka ta sauka dasu zuciyarta fal da tunani, Wannan shi ake kira goma da Ashirin abu na nema ya hade mata biyu bata gama da wannan yar qauyen ba ya maido mata da zancen Zubaida ashe har aike yake musu yana kuma zuwa ya gansu?

Koda yake itace sakarya data manta da ita gaba daya matsalar Bara'atu tasha mata kai ta manta da batun tsinannun Tagwayen can data haifa to yanzu ita ina zata kama? Bara'atun zata bari ta koma kan Zubaida? Ko kuwa bari zatayi seta fatattaki Bara'atu sannan ta dira kan Zubaidar?

Tana hada abubuwan da zatayi amfani dasu a dakinsa take wannan lissafin a ranta, ta gama ta dauki ledar data zuba kayan, Nazirun na saman har yayi bacci Zakariyya kuma dasu Babangida zasu fita ya bisu yanzu da bata gama yanke yanda zatayi da Bara'atun ba tana bar mata yaron ya kwana da yan uwansa ranakun girkinta dan haka ta rufe qofarta ta koma Saman Audun tana ayyana matsalar Bara'atu zata fara kaudawa, zata bar Zubaidan tukunna dan tata me sauqi ce take ganin.

"Wai ni watannin Yan biyun nawa nawane yanzu?" Ta daure ta tambayi Audun bayan sun kwanta, ya danyi lissafi akansa kafin ya kalleta yace

"Kamar Goma kenan ko? Ki lissafa tafiyarki Hajji yanzu watan sama kwanansa goma Azumi saura kwana Ashirin ko sha tara kinga a wata na Tara suke sun shiga na goma"

"Haka ne" ta fada daga nan ta maida kai ta kwanta tana ayyana dole ma ya karbosu sannan ya nemo me masa hidima dasu yawwa. Haka dai tayi baccin daren babu nutsuwar zuciya, tunanin yanda zata qulla can ta rushe can kawai takeyi, tana jinsa yana jan minshari hawaye ya silalo mata, kamar ta zabga masa mari taji, duk akansa take wannan fadi tashin.

BARA'ATU

Washe gari da Audu ya fito ze tafi Kamfani ya shiga yi mata sallama bayan sun sake gaisawa bayan wadda sukayi da Asuba, cikin risilama ta maido masa da maganar jiyan saboda tace tana da magana idan ya dawo yace ta fada sannan babu damuwa.

"Se naga kamar dakunanmu sirrinmu ne sannan gyaran daki akwai wanda zakaga yafi so yayi da kansa yafi ganin komai yayi masa daidai kamar dai ni, shiyasa zakaga ko dakinka duk sanda nake ciki se na sake gyarawa koda ace Maman Zakariyya tayi gyaran dan bana jin komai ya mun idan ba da kaina nayi ba" Bara'atun ta fada masa da yanayin da take ganin ze fahimta. Ya ringa jjjiga kai irin ya fahimce ta din nan sannan yace ze yiwa Bintan magana.

Seda da dare bayan ya dawo ya ya gama cin abinci ya sanarwa da Binta yanda sukayi da Bara'atun, daman tasha kwanan baqin ciki da yinin takaici dan zancen Zubaida da yayanta ya maqale mata a zuciya yaqi wucewa duk haka ta wuni babu walwala qyashi da hassada ya cikata ta ringa hasaso abinda Audun yake kai musu

waya sani ko itama gidan ya gina musu irin nasu Bara'atu tunda itama a gidan Laka suke ga Damuna kar yace ze rufto akan Yayansa.

Seda ta gama sauraron Audun tsaf kafin ta narke fuska ta samu mafaka abin kuma yazo a daidai yanda take so dan haka tace

"Ka ga magana ta ta fito ko? Jiya mena fada maka? Ai nace maganar batayi mata ba tayi shiru me yasa tuna gurin ba zata fadi nata ra'ayin ba se dai ta jaka gefe ta gaya maka, yanzu ai se aga kamar cutarta nakeyi shiyasa ba zata yi magana a gabana ba. Ni ina so muyi zaman lafiya da ita amma kaga abinda ta bullo dashi a taqaice dai tana nufin ni qazama ce banida tsaftar da zan iya yi mata gyaran daki ashe duk wanda nake maka ma in tazo seta sakeyi shikenan tunda haka ta zaba se mu zuba mu gani nida ita aga wanda ze sare in har tashin hankali take neman kai ka sani na iyashi wlh banda ma Allahya doramun qaunarta da son muyi zaman lafiya da ita meye ze hadani da wata Bara'atu ka bata labarin yanda muka gwabza da Gogaggiyar Karuwa ma balle ita karan kada miya" nan ta fara qoqarin tayar masa da Jidalinta.

Audu kuwa yaji dadin zaman lafiya baze so abinda ze tarwatsa masa kan gidan daya fara haduwa ba kuma se yaga zancen Binta gaskiya ne Bara'atu bata so ayi zaman lafiya shiyasa zata bullo da  wannan maganar inda taso ayi yanda Bintan tace in yaso duk abinda yayi mata badaidai ba ta gyara daga baya baki alaikum.

"Yanzu dai kiyi haquri, zanyi mata magana babu wani tashin hankali ko rigima daze bullo a gidan nan zaku cigaba da zamanku lafiya yanda kuka fara" Audun ya tausheta, se ta fara magana kafinta kai qarshe ta saki kuka tana cewa

"Ni idan zan fada maka wani abu daya shafeta ai a gabanta nakeyi bana munafunci me yasa ita se a gefe zakuyi magana ta da ita? Allah kadai yasan me take gaya maka akai na shiyasa naga kwanakin nan duk ka canza mun kuma ko rantsuwa nayi bazanyi kaffara ba waccen me kama da Zabiyar ta gidan Yakubu ce ta zugota zuwan da kukayi to nidai tunda naga alamun hade mun kai zakuyi tunda ita yar garinku ce ni kuma bare gara nasan nayi tunda sauran mutunchina kafin ka kunyatani ace qaramar Yarinya ta koreni daga gidan Miji"

"Wace irin magana kikeyi haka Binta? Daga zancen shara seki fara sako wani soki burutsu meye wannnan? bana son irin haka kin sani ko? Bari na kirata to tazo ayi

maganar a gabanki zan yanke hukunci kuma dole kowa yabi abinda nace" Audun ya fada yana miqewa se ta tareshi da cewa

"Hukuncin me zaka yanke? Bayanta zaka bi ko?"

"Se ki jira kiji tukunna" ya bata amsa fuuuu ya wuce kiran Bara'atu. Da gudu Binta ta shige bandaki ta wanko fuska tana qyalqyala dariya, ta gama tsanewa ta murza hoda da Gazal kafin ta ware dankwalinta ta gyara daurin tayi fes abinta kamar ba ita ta gama kuka yanzun ba.

Bara'atu na zaune da yara Abdullahi ne yace su kwaso Littattafansu a duba saboda an kusa komawa makaranta saura sati daya. Ba sanin abinda sukeyi tayi ba dan haka tana zaune kan Kujera kawai tana kallonsu tana kuma kwabar wanda taga ze bata littafinsa da zane musamman Zakariyya da ya fiya qiriniya se qoqarin batawa Yayyen littafi yakeyi da fensir Audu ya fada dakin sallama ciki ciki yana muzurai.

"Ina son magana dake" ya fada ya juya, tabi bayansa da kallo kafin ta miqe a sanyaya tana tunanin to meya faru kuma? Hijabi ta dora kan Baqar doguwar rigar jikinta ta bi bayansa, shi kadai ta tarar a falon se Naziru dake ta rarrafe a qasa ta daukeshi ganin ya nufi qofar da bata rufe dakyau ba ta zauna kan kujera tana masa wasa yana dariya, satar kallon Audun tayi taga ya tamke fuska yana muzurai zatayi magana kenan Binta ta fito daga daki tana masa magana ganinta yasa ta katse tace

"Au kece? Yau kinzo hira da kanki kenan ba tare da an kiraki ba"

"Uhm" kawai Bara'atu tace kafin ta gaisheta ta amsa tana zaunawa tana sake cewa Audu

"Kaga abin mamaki yau Bara'atu tazo hira damu"

"Ni na kirata" ya fada fuska a daure qasan ransa yana mamakin yanda tayi kamar bata san yaje kiran Bara'atun ba,

"Koda naji, nidai nasan badai Bara'atun dana sani ba" ta sake fada. Audu ya gyara zama yana kallonsu duka yace

"Na gayawa Binta saqonki sedai bataji dadin abinda kika fada ba kuma kamar yanda ta fada abinda kika bullo dashi so kikeyi ki ruguza mana zaman lafiyar da muka fara samu a gidan nan dan haka ni a matsayina na wanda ya ajiye ku duka

zan yanke hukunci, kamar yanda muka tattauna jiya magana tana nan zaku ringa ayyukanku kan yanda muka tsara babu wani ja inja ba kuma nason na sakejin wata magana daga kowanne bangare".

Abin be wani bawa Bara'atu mamaki ba domin tasan za'a rina wai an saci zanin Mahaukaciya wannan ba sabon abu bane a gurinta kuma yanzu ta tabbatar da zarginta na cewar Binta na nan kan halinta babu abinda ya canza kuma nemanta takeyi da sharri shiyasa ta kawo wannan tsari to amma ba zata zauna ta zama sakarya ba a wannan karon ma, dole ta fadi ra'ayinta koda kuwa Audun zeyi masifa bazata yarda taci gaba da zama yar amshin shata a gidan ba.

Ta kalli Binta dake murmushi tana lada qafa kafin ta fara magana ba tareda ta kalle shi ba tace

"A gaskiya kayi haquri nidai na yafe sharar dakina zan ringayin abata da kaina kuma ina roqar Alfarmar itama ka daukemun ta dakinta, na yarda ta canza mun da wani abun daban da zan ringayi mata amma banda sharar daki"

"Yanzu Bara'atu har kinyi kaurin wuyan da zan fadi magana ki musamun ni zan zartar da hukunci a gidana kice ba haka za'ayi ba?" Audu ya fada a fusace cikin tsawa yana kallonta, bata son fada sannan ya za'ayi a tauyeta kuma tayi magana ya nuna ta masa rashin kunya dan ta nemi haqqinta wannan ya karya mata zuciya Kwalla ta taran mata a ido amma ta kasa magana dan tana bufe baki tasan kuka zata saki, Binta da taji kamar ta taka rawar murna ce ta katseshi da cewa

"Haba Yallabai, haba ranka ya dade Allah ya huci zuciyarka ungo karbi ruwa kasha" ta miqa masa ruwa be karba se huci yake yana hura hanci ta sake marairaicewa tana cewa

"Haba mana Sadauki ni banga abin bacin rai a maganar nan ba kowaccen mu fa tana da damar da zata fadi ra'ayinta shiyasa tun jiya naso ta bude baki ta fadi abinda yake ranta take yanke da bamu zo yanzu ana bacin rai ba amma dukda haka daman maganar nan nina kawota tunda kuma a maimakon samun daidaito tana nema ta haddasa fitina na janye, zan saka a nemo mun wata me aikin kawai taci gaba da taimaka mun itama idan tana so a samo mata in kuma bata so taci gaba da aikinta yanda ta saba shi kenan magana ta wuce kowa yayi haquri".

"Bata isa ba wlh ita tayi kadan ta kawo mun tsarin da zanbi a cikin gidana yanda na tsara haka za'ayi" ya sake fada a zabure, Bara'atu ta kalleshi, yanda yake magana tamkar shiya kawo dokar tun Asali kamar ba Shirin Bintan bane ita ta kawo nata tsarin ya hau ya zauna ita kuma da bada sadaki ya aurota ba saboda ana so ayi mata rashin Adalci taqi shine yake wannan kumfar bakin.

"To bari na nemi alfarma, tunda tace abar mata sharar dakinta zatayi ni kuma nawa na canza mata da wani aikin ka barmu mu sasanta a tsakaninmu mana" Binta ta sake fada kamar da gaske sasancin take so ayi. Yayi shiru kamar baze tanka mata ba kafin kuma murya a dake kamar ta Boss yace

"Ina jinki".

"Yauwa Nawan, yau akwai tukuici na daban ladan wannan Alfarmar daka mun" seta juya kan Bara'atu tace

Bara'atu da taja Hijabi ta rufe fuska dan ta kasa riqe kukan daya zo mata qasa qasa takeyinsa tana share hawaye wato dai ranakun baqin cikinta basu qare a gidan Audu ba, maidota yayi ya qara sauke mata buhun hunan rashin mutunchin da be ida sauke mata a baya ba, da sauri ta dago kai jin abinda Bintan take cewa

"Kin ga ya dage dole mubi tsarin da aka kawo da farko amma tunda kin nemi a canza, idan kin yarda ni a bangarena a maimakon sharar dakina zaki ringa yimun Wankin kayan Yara ke ma seki fadi abinda zan ringayi miki a madadin taki sharar" ta qarasa tana doka murmushi kamar wawiya.

Kasa cewa komai tayi, ta kalli Bintan kafin ta kalli Audu tana jiran taji abinda zece se ji tayi yana cewa

"Babu maganan ta zabi abinda zaki mata, sharar dakinta ita tace ta yafe kar kiyi na dakinki kuma wannan da ba zatayi ba kika musanya mata" ya juya kan Bara'atu da tayi fakare tana sauraronsu yace

"Zaki ringayi mata wankin kayan yaran duk ranar da baki da girki, My decision is final" aka jefo turanci daga nan ya shige daki ya barsu zaune.

"Yanzu wasan ya fara yarinya" Binta ta fito mata a sak ta fada kafin ta miqe tana juya Mazaune tabi bayan Audu tana wata shaidaniyar dariya irin ta wanda ya nisa cikin lamarin duniya.

Page 28

Kwana tayi tana juyi duk motsi abinda ya faru daren jiyan seya fadomata zuciyarta tayi mata nauyi, idanunta banda radadi babu abinda sukeyi dalilin kukan data sha, Ta rasa a wanne matsayi zata ajiye Audu dan bata ta Binta kwata kwata ta gama sallama mata amma shi Audu fa?

Son zuciya ko kuwa qin gaskiya ne yake saka shi aikata abubuwan da yakeyi ko yaya? Me yasa duk hukuncinsa yake kasancewa na son zuciya kuma bisa goyon bayan rashin gaskiya?.

Rashin baccin da batayi ba cikin dare yasa ta makara, dakyar ta iya tashi tayi sallah kanta na bala'in sara mata ta koma ta sake kwanciya tana jin yaran na qu qunin Yunwa dan Zakariyya harya fara kuka gashi bata jiyo motsin Bintan ba alamarbata sakko ba balle ta dora abin kari, Audun m yau be leqa su da Asuba yaga ko sun tashi ba kamar yanda ya saba haka daya dawo wucewarsa daki yayi tunda fushi yake da ita kuma yau din Lahadi ce baya fita da wuri daman se qarfe sha biyun rana shiyasa Bintan ta qara samun damar tsula tsiyarta.

Abdullahi ta kira tace ya share tsakar gida ya wanke saboda hadari ya taso daren jiya ruwa be sauka ba se Iska ta taho da qura ita kuma ta daure ta hada ruwan wanka ta yiwa yaran kafin Hajiyar gidan ta gama qailularta ta basu abin kari. Tana cikin shiryasu ta jiyo hayagagar Binta ta san baze wuce da Abdullahi take ba. Cikin kayan Babannan ta samarwa Zakariyya wanda suka masa tace su zauna nan bari ta kawo musu abin karyawa ta zura Hijabinta tana qoqarinfita ta jiyo sallamar Bintan a qofar dakinta, tayi A'uziyya a zuciyarta domin Binta ta zarce shaidan kaidi, sanin Audu na gida kuma zata yuwu wani bala'in ta sake zuwa ta hada mata dan haka tayi saurin fita kafin ita ta shigo mata cikin dakin.

Faran faran tamkar babu wani mugun abu a ranta ta gaida Bara'atun ita dai daga lafiya ta gagara qara ce mata komai saboda zuciyarta gaba daya ma tsinkewa takeyi, ita dai kaf a karkararsu bata taba ji ko ganin Mace irin Binta ba, to ko daman wannan abin shine wayewar da ake fada? Idan kuwa hakane ta godewa Allah da ta kasance bagidajiya akan ta zamo daga cikin munafukai.

"Kuyi haquri na barku da yunwa ko? Bacci ne ya kwace mun yau, Bari in maza ko ruwan shayi ne a tafasa se a soya wainar qwai tunda muna da burodi" Binta ta fada tana murmushi. Cikin sanyi Bara'atu tace

"Babu komai ai" ta bata amsa a sanyaye daga nan Bintan ta juya tana murmushin da Allah kadai yasan ma'anarsa.

Kusan Minti goma tsakani Binta ta sake dawowa da qaton Fulas din ruwan zafi tun wanda Dada ta bata ne lokacin Amarcin da ake zuba musu ruwan zafi a ciki. Yana da girma ga riqe zafi shiyasa take jin dadinsa sosai.

"Sannu da aiki" ta fada sanda ta kabi Fulas din, Binta tayi murmushi ta koma kitchen ta sake kawo mata Farantin data Zubo faya fayen wainar qwai.

A babban Jug din da take hada musu shayi gaba daya ta zuba Madara da Milo da Sukari kadan kafinta tsiyaya Ruwan zafinta motsa, ta zubanata a kofi ta zubawa Abdullahi se ta qara ruwan sanyi akan sauran ta dan qara musu Madara da Milo sannan ta zubawa sauran Yaran.

Yanda suka rarumi Kofunan duk sunbata tausayi musamman Zakariyya da yake qaraminsu a ranta tace

"Wato muguntar harda dan cikinta takeyiwa" tana kallo ya kafa kai yana kurbar shayin a yunwace Babannan yace

"Umma Burodi da kwai"

"Yanzu zan baka ai uban gajen haquri" ta fada tana tura masa farantin data saka masa Burodinsa da kwan akai sauran ma duk ta miqa musu nasu. Abdullahi yakai kofi bakinsa ya kurbi shayi ba zato Bara'atu taji ya fesoshi da qarfi harya batata, a zafafe ta buga masa tsawa tana cewa

"Wane irin wulaqanci ne haka ai kasan shayin da zafi zaka kurba ya qonaka ji yanda ka batani duk ka tsalla mana yawu acikin abinci"

Abdullahim dake karkada harshe yawu na dilala dakyar yace mata

"Umma ba zafi bane, gishirine a ciki kamar ze tsinke mun harshe"

"Gishiri?" Ta fada cikin mamaki, Babangida daya matse fuska yace

"Nima da akwai a cikin nawa Umma".

Robar da sukari yake ciki ta janyo dan ta tantance ko kuskure tayi gurin daukowa sedau sukari ne a ciki, se kuma ta saka cokali ta dibi shayin gabanta dan kadan ta kai baki ai da sauri itama ta fesoshi jin wani azababben gishiri tamkar an jiqe kwano gida ciki ruwan fulas din to meya kawo gishiri ciki?

Kofunan hannun Babannan da Zakariyya wanda qiris ya rage ya shanye nasa ta kwace da alama shi be gane banbancin dandanon gishirin bama. Ta hade su a Jug kafinta miqe a sanyaye ta shige kitchen dinta na cikin daki. A Butar tafasa ruwa ta saka nan da nan yayi zafi bata ko Jira ya tafasa ba ta juyo ta sake hada musu wani zuciyarta ta aminta da cewar da gangan Binta ta zuba musu gishiri a ruwan shayi wai me wannan matar take nema da ita fisabillahi.

Bayan sun gama ta tattaro kwanuka ta fito dasu danta wanke sedata hado ma cikin kitchen ta zauna ta fara wanke wanke, Shayin dayaqi shayuwa ta tsiyayar a rariya Ta bude Fulas din zata zubar da sauran na ciki kenan ta ji muryar Binta a kanta tana cewa

"Aa, Maman Baba meya faru naga kin sheqar da shayi a rariya?"

"Shayi kuma?" Audu sa suka fito tareya tambaya yana kallon rariyar da shayin be gama wucewa ba,

"Gashi nan kuwa ka gani hadin kauri kuwa wlh, qila sun hada ya musu yawa ne maimakon ki barshi an jima ki dumamawa yara susha kuma se ki zubar ai Almubazzaranci ne wannan" Bintan ta sake fada. Bara'atu bata iya dagowa ba balle tace wani abu dan wannan Bom din kam tilas ya tashi da ita dan tafi kowa sanin Audu baya son wulaqanta abinci tun zamanin tana ita kadai a Bechi kafin su dawo Kano ko abu ya siyo ze gaya mata idanba zata iya amfani dashi duka ba ta fitar ta bayar kar abarshi ya lalace balle yanzu akan Idonsa ta zubar da shayi a rariya tasan ko Binta bata saka baki ba se yayi fada.

"Yanzu saboda wulaqanci abinci zaki wulaqanta haka? Da yayi muku yawa me yasa bazaki bawa Abdullahi ya fita ya bawa Almajiri ba?" Audun ya fada cikin fushi. Murya a sanyaye tace

"Kayi haquri ba yawa ya mana ba, kuskure aka samu gishiri ne a cikin ruwan da aka dafa se bayan dana hada mana sannan muka ankare kaga baze shawu ba shiyasa ma zubar"

"Gishiri a cikin shayin?" Ya tambayeta cikin sigar rainin wayo irin be kama abinda ta fada ba. Fulas din gabanta ta tura masa tana cewa

"Dama ba zaka yarda ba amma ga sauran ruwannan ka dandana kaji"

"Ikon Allah a garin yaya gishiri ya shiga ruwan shayi? bari muji" Binta ta fada tana dauke fulas din cikin mugunta datayi kama da kuskure ta sakeshi daga tsayen da take ji kake tush ya tarwashe a qasa ruwan ya watse duk ya tsallar musu a qafa harda Audun.

"Innalillahi na qone" Bintan daya fi zubar mata ta fada tana daqe qafafu, Audu ya zabga tsaki yana cewa

"Wane irin sakarci ne zaki yada fulas se kace bakya gani? Se ki dakko tsintsiya ki tattare gurin ai kafin yara su fito wani ya taka kwalba" yana fadar haka ya baza Babbar rigar da ta zame masa Kayan sawa yanzu ya fice daga gidan.

"Ke kin dauka zaki kwanta ki miqe qafa in daga miki abinci? To ba Gishiri ba idan bakiyi sannu ba wata ran shinkafar bera zan zuba miki" ta wuce ciki tana tsaki.

Sanadin zaman Bara'atu boyi boyi kenan a gidan, da ranar girkinta da ba nata ba muddin tana so yaranta suci abinci kan lokaci sedai ta tashi tayi, an koma makaranta Abdullahi ya koma makarantar kwana dan haka ita zatayi shara ta hada abin kari ta shirya yan makaranta su tafi sannan tayi wanke wanke ta hado wankin kayan Yaranta dana Bintan da wani sa'ilin harda nata kayan take tulo mata kuma bata isa taqiyi ko tayi magana ba ranar Audu ya ringa surfa mata bala'i akan ta fiya fitina bata qaunar a zauna lafiya.

Nana da nan kyan da tayi da cikar jiki suka zagwance Rama ta maye gurbinsu kulawar da take samu gurin Audun ta rasa domin ko sun shirya na dan lokaci Binta

zata sake kunna wata wutar da zata wargaza su, a haka Watan Azumi ya kama aiki ya ninkar mata dan bayan abincin gida harda na sadaka sukeyi wanda A baya Mairo da Lantana ke aikin yanzu da babu su itace komai haka zata wuni tsaye kan qafafunta idan dare yayi Iokacin da kowa yake Tsaye yana ibada ita kuma gabbanta sun gajiya sedai ta kwanta tayi ta muqusPusun ciwon jiki ga babu godiya balle kyautatawa daga Megidan a kullum gazawarta yake gani yan uwanta kuma sun gagara gane halin da take ciki idan ka cire Hadiza wadda tasan kan zaman da takeyi.

Sallah saura kwanaki Biyar su Yakubu suka zo Kano, a gidansu suka sauka da yake jirgi suka biyo se dab da shan ruwa suka tafi gidan Audu kamar yanda suka tsara da Yakubun sanda ya dakkosu daga Iyafot. Kasa magana Balaraba tayi sanda taga Bara'atu, Yakubu kansa kallo daya yayi mata sannan ya kalli Audu wani abu ya tokare masa maqoshi, farin cikin daya taho dashi ya dishashe nan take yanayinta ya nuna cewar an koma yar gidan jiya kenan Audu tuban muzuru yayi ba dagaske ya gane kuskurensa ba.

Shan ruwan haka sukayi shi babu karsashi Binta kadai ke subadadi ita kadai kamar kanta ya qone dan shi kansa Audun tunda yaga canjin fuskar Yayan nasa yasha jinin jikinsa domin yasan baze wuce dalilin ganin Bara'atu ba amma ta yaya zeyiwa Yakubu bayanin halin Bara'atu ya fahimat? Ita din Majicin sari ka noqe ce babu me fahimtar ainihin halinta se wanda ya zauna da ita. Suna gama tsakurar Abincin Yakubu yace ze tafi Balaraba ma ta miqe wannan ya qara tabbatarwa da Audu tabbas Yakubun ya fusata dashi ne.

A qofar gida Bara'atu data bi bayansu ta fashe da kuka, tuni Balaraba ta shige mota dan tace ba zata iya magana da Bara'atu ba zuciya tana iya dibanta ta watsa mata mari ko ta daddana mata Ashar haba wannan mutuwar zuciya har ina ta zauna Kishiya da Miji su nemi kasheta da ranta.

"Dan girman Allah Yaya Yakubu ka taimakeni kai kadai nake saka ran zaka fahimceni a yanzu, bazan iya yi maka bayanin halin da nake ciki ba amma ina roqonka da kayiwa Allah ka shiga lamarina ka nema mun yanci a gurin Dan uwanka wlh na gaji, ban zata cewar wahalar data fi ta bayace take kirana zuwa gidan nan ba, ban dauka ya maidoni bane saboda ya qara biyamun karatun da be kammala a baya ba, ni dai na haqura ina fatan wahalar dana sha ta zame mun kaffara a rayuwata" ta fada cikin matsanancin kuka daidai nan Audu ya qaraso Soron ya

kalleta ya kalli Yakubun daya daga kai sama yana kokawa da bacin ran dake taso masa.

"Me kikeyi a nan gurin Dallah wuce ciki" Audu ya fada yana zare mata ido ta juya cikin gidan bayan data sake kallon Yakubu irin kallon ka taimaka mun.

"Na zata anan zakuyi sallar Isha in aka idar da Tarawi se na maida ku gidan" Audu ya fada cikin inda inda, Yakubu ya juya ze fita yana cewa

"Babu damuwa zamu koma gida kasan muna tare da gajiyar hanya, idan ka samu lokaci kazo ina son magana dakai" daga nan ya sa kai ya fice daga gidan.

Masifa da Bala'i Audu ya ringa zazzaga mata bayan daya koma cikin gidan akan seta gaya masa abinda ta fadawa Yakubu dayace yana neman sa amma tayi shiru banda kuka babu abinda takeyi daya gaji ya fita gaba daya ya rikice dan be san me Bara'atun ta fadawa Yakubu ba, maganarta ta qarshe kadai yaji da tace wahalar datasha ta zame mata Kaffara wace wahala? Amma dai ba a gidansa take nufi ba? Ya ringa tambayar kansa. Sallar ranar dai yayita ne kawai ana idarwa kuma ya tafi gidan Yakubu.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number □08129249549*

*□07011401314*

Audu ya ringa Jijjiga kai yana buga qafafu haka nan zufa take keto masa kamar wanda yake zaune kan Kunama, bakinsa har kumfa yake saboda masifa Yakubu ya zuba masa ido yana kallonsa kawai, shi yanzu tantama yake anya Audu bashida wata matsala akansa kuwa kodai shaye shaye yakeyi be sani ba. Tambayarsa yayi akan me yake faruwa tsakaninsa da Bara'atu ya ringa zana masa maganganu marasa lissafi bare kan gado, a duk abinda ya fada masa babu guri daya dayaji laifin illa tsantsar Zalunci da Azabtarwa da ita suke mata, ya mayar da ita tamkar Baiwar daya siyo da kudi a cikin gidansa shin wai me Bara'atu tayiwa Audu ne a rayuwa dayake daukar fansa akanta yanzu?

"To Audu kasan dai Aure anayinsa ne bisa yarjejeniyar Mutum biyu Mace da Namiji, haka nan idan har ya zama da cutarwa kowanne bangare yana iya neman sauqi ta hanyar rabuwa idan har babu wata hanyar samun daidaito bayan wannan din, ni Ina ganin tunda dai zaman ku ya zamana da cutarwa ku rabu hakan ze fi Alkhairi akan kuci gaba da zama daya yana daukar Alhakin daya" cewar Yakubu.

Audu ya dago a fusace yace

"Wato ce maka tayi kasa na saketa kenan dazun?"

"Haka tace, ta gaya mun ta gaji da cutar da ita da kakeyi kaida matarka dan haka tana neman sauqi ka sawwaqe mata auranka taje tayi rayuwarta ta samu wani can ta Aura wanda ze sota tsakani da Allah ya san darajarta kaje kaci gaba da zama da matarka da kake ganin tafi maka kowa" Yakubun shima ya mayar masa cikin daga murya. Se Audu ya miqe yana cewa

"Bazan saketan ba, ka gaya mata idan tana da qarfi tazo ta kwaci sakin ko kuma ta saki kanta"

"Ai kuwa idan baka saketa ta Arziqi ba zaka saketa ta tsiya dan wallahi maka ka zanyi a kotu qaryar taurin kai kakeyi Audu zan nuna maka jini daya ne yake gudana a jikinmu yanda kake jin ka gado Taurin kai seda na fara gada kafin ka samu ragowa, karka kawo mun takardar sakinta kafin nan da gobe kaga yanda zamu kwashe dakai" daga haka ya shige ciki ya bar Audu a tsaye yana tsuma, Bara'atu tace ya saketa? Ita da kanta ko kuwa wannan matar Yakubun ce ta zugata?

Kwanaki uku aka kwashe cikin wani yanayi mara dadi, kwana biyu da Audu yaje gidan Yakubu bayan ya dawo ya samu Bara'atu yayi mata cin mutunchi da tijara ya kuma jaddada mata sedai ta mutu amma baze taba sakinta ba washe gari da safe yana kamfani se ga magatakarda daga Kotun Musulinci an aiko masa da sammaci, ya karba ya duba kiransa akeyi daga kotu matarsa ta shigar dashi qara ya wuto gida Afujajan sedai be tarar da Bara'atu ba tun safe yana fita itama ta fice ta tafi gidan Yakubu tare dashi sukaje Kotun da kanta ta shigar da qarar bayan Yakubu ya sake tambayarta ko zata yi haquri ta bada lokaci su sasanta ta rantse masa akan wallahi ta gama zama da Audu muddin baso suke wata rana a wayi gari zuciyarta ta buga ta mutu ba su qyaleta jin haka yasa yace su tafi Kotun take kuma aka rubuta takadda aka kaiwa Audu.

Ranar Jajiberin sallah Bara'atu ta karbi takardar sakin igiya daya data rage tsakaninta da Audu, a ranar ya kamata suyi zaman kotu, tun Asuba daya dawo ya kulle kansa a daki yaqi fitowa, besan yanayin da yake ciki ba wani irin qunci da zafi zuciyarsa takeyi masa. Binta da duk abinda akeyi a kunnenta da idonta amma tayi biris tamkar bata san wainar da suke toyawa ba tana tsakar gida tana aikace

aikacenta tana waqoqi Musbahu yazo, bayan sun gaisa yake ce mata gurin Baba yazo ta masa magana qarfe Goma ne zaman kotun nan gashi Tara da rabi tayi, dataje ta gaya masa beko waiwayo ba ya miqa mata farar takarda, duk yanda taso ta daure bayan ta karanta abinda yake ciki ta kasa seda ta rangada guda kamar wadda take saka Amarya a lalle. Tana bawa Musbahu takardar ta hau taka rawa a gabansa se ya rasa abinda zeyi kawai ya tsaya yana kallonta kafin jiki a sanyaye ya juya ya fice daga gidan ya kaiwa Yakubu saqon Audu.

Sanda takardar ta shiga hannun Bara'atu ji tayi kamar an mata bushara da gidan Aljanna, da Ajami ya rubuta dan haka ta gane komai abu daya daya dameta a ciki shine cewar da yayi karta tafi masa da Da ko daya, ta yaya zata barwa Binta yaranta? Matar data tsaneta kuma zata iyayin komai akanta da yaranta.

"Karki sakawa ranki damuwa akan yara babu abinda ze same su sannan kina nan a matsayinki na mahaifiyarsu babu abinda ze goge hakan komai daren dadewa kuma zasu nemeki. Ki fuskanci rayuwarki ta gaba, ki tashi kinemi ilimi ki tsaya da qafafunki in sha Allahu ubangiji zeyi miki sakayya a gaba da Mafi Alkhairi kinji" Yakubu ya tausheta.

A ranar suka tafi Bechi gaba daya dan dama can zasuyi sallah. Shiya kaita har gidansu ya kuma yiwa Inna Hajara bayanin komai, bayan tafiyarsa kuwa wuta ce kadai Inna Hajara bata hura ta jefa Bara'atu a ciki ba, ta kasa hango rayuwar da yarta take ciki da ta sa ta haqura da daular da ita hange, damuwarta kadai mutane zasuyi mata dariya, zasu rasa tallafin da suke samu a gurin Audun tunda ya kwace Yayansa, ita da take saka ran idan Bara'atun ta sauke farali Bana badi kuma a sakata a lissafi shine tayi mata baqin ciki shin Bara'atu wace irin yarinya ce ne? An gaya mata da akwai Auran da ake jin dadi dari bisa dari ne a ciki? Wace Macece zata samu Miji kamar Audu daula iya daula tayi wasa da damarta ai se sakarya irin Bara'atun gashi yanzu Auran ya mutu murus babu damar gyarawa.

An cinye watan Shawwal Mahajjata suka fara shirye shiryen tafiya qasa me tsarki, Audu ya rigada ya biyawa Bara'atu, Bilki da Aminu se Balaraba matar Yakubu, a hannun Aminun ya damqa duk wani abu daya kamata na Bara'atun, babu wanda beyi mamaki ba dukda sun san da ita cikin jerin matafiyan amma abinda ya faru yasa suka dauka za'a fasa tafiyar da ita sedai Audun ya basu mamaki. Lokacin tafiya yayi suka shirya sunyi bankwana da yan uwa da Abokanan Arziqi, dalilin su Bilki da Aminu ya saka Audu yi musu rakiya Iyafot dukda qasan ransa badansu yaje ba, haka nan zuciyarsa ta kasa nutsuwa a kwanakin, kullum ya kwanta se yayi mafarkin Bara'atun haka da rana wuni yake da tunaninta a ransa yana jin kamar ta cancanci ya nemi afuwarta koda har yanzun be yarda da cewar ya cutarda ita ba

kamar yanda mutane suke fada amma kuma haka nan zuciyarsa take ingizashi ga neman afuwar da besan ta mecece yake da buqata ba.

A iyafot Mahajjata sun hau layin karban tikitin shiga jirgi, yana daga tsaye can gefe dan ya sake zama baqo a cikin danginsa tun da ya rabu da Bara'atu ya sake rasa karsashin sakewa musamman a gaban Yakubu yanzun ma ganinsa tsaye suna sallama da matarsa yasa duk ya kasa sakewa gashi yana so yayi magana da Bara'atu amma shegiyar zuciyarsa me masa hudubar tsiya tana gaya masa girmansa ze zube idan aka ga ya mata magana a nan gurin.

"Be kamatu na tafi muna riqe da juna a zuciya ba, ina roqon da ka yafe mun idanna maka wani laifi a zaman da mukayi da kai, daga bangarena na yafe maka, iyakar wannan Alkhairin da kayi mun ka zama silar da zan ziyarci ma'aiki ya wanke duk wani laifi naka da yake cikin zuciyata sannan idan ka koma gida ka gayawa Matarka in har taji tsoron Allah ta gaya maka gaskiya ta wankeni daga zargin data saka mutane sukemun na kisan kai na yafe mata idan ba haka ba idan harna mutu ko ita ta rigani mutuwa tabbas shari'armu sedai a qarqareta a gaban Allah dan bazan yafe ba bayan raina a ringa aibata Yayana ana jifansu da abinda ban aikata ba" Bara'atu da be san sanda ta dawo gurin ba ta fada tana kuma gama maganar ta koma cikin Ayari tana daga masa hannu, kamar wanda aka matsawa Remote haka shima ya shiga daga mata hannun, zuciyarsa ta ringa tsinkewa wata faduwar gaba da besan dalilinta ba ta saukar masa haka ya tuqa motarsa ya koma gida yana maimaita zancenta na matarsa ta wanketa daga zargin data dora mata.

A karon farko ya tambayi Binta gaskiyar abinda ya faru? Ya akayi tasan Bara'atu ce ta kashe mata Da? Bintan dake cike fam da tafiyar Bara'atun tayi tsaki kawai ta tashi ta bashi guri. Bara'atun nema take ta zame mata qajaga, ta tunkudeta amma ba zata bar zuciyarta ta huta ba kenan? Abu daya ke sanyaya mata rai idan ta tuna aure ya qare tsakaninta da Audu duk Bala'i dole su haqura sannan ga Yayanta nan zube a tsakar gida suna watangaririya iya rabata dasu da tayi tasan zuciyarta ta quntata, jira takeyi Tagwayen Zubaida su shekara biyu suma tasa ya karbo su subi sahun yan uwansu domin tasha Alwashin babu wata mace da zata mori Audu bayan ita, yaya dai da suka haifa sun samu sedai su jira idan ya mutu su yafici abinda suka samu amma badai a yanzu da yake raye ba.

An kammala aikin Hajji lafiya Mahajjata nata lissafin kwanakin daya rage musu su dawo gida haka nan yan gida nata shirye shiryen tarbar yan uwansu, kwanaki biyu ya rage Jirgin su Bara'atu ya sauka, a daren ranar da zasu tafi Jidda inda daga can

za'a maido su Nigeria suna shirye shirye dan sun gama daure kayansu cikinta ya fara murdawa, kamar wasa tun tana jinsa kadan kadan har ta kai ga ta kasa zama cikin abinda be gaza Minti talatin ba da fara ciwon cikin rai yayi halinsa Bara'atu ta amsa kiran Mahaliccinta. Mutuwarta ta girgiza yan tawagarsu gaba daya bama su Bilki kadai ba.

Wata mata ce take fadin

"Dazu take cemun tun da muka hau jirgi tayi addu'a idan har ta kammala aikin Hajjinta lafiya kuma ibadarta ta karbu tana fatan ubangiji ya karbi ranta a binneta a qasar Ma'aiki tace tsoro takeji anya kuwa tayi Hajjinta daidai ashe lokaci yana tafe ubangiji ya karbi shahadarki Bara'atu Yarinyar kirki yarinyavme haquri Annabi yasan da zuwanki" haka akayi jana'izar Bara'atu da Asuba a masallacin Harami aka binneta a maqabartar da ba kowa yake samun wannan Alfarma ba se me tsananin rabo shikenan rayuwar ta qare ta tafi ta bar Binta a duniyar da take ganin ba zata qare ba.

Dawoqar Mahajjata a maimakon murna se Al'amari ya juye na koke koke da Jimami, duk wanda yaji mutuwar Bara'atu seya girgiza hatta da Binta da da take ganin idan aka bata wuqa zata iya dabawa Bara'atun se gashi sanda labarin mutuwarta ya rsketa zuciyarta seda ta tsinke ta kuma girgiza.

Munira qanwar Binta da tazo Kano tun Bayan qaramar sallah dalilin takurar da Mama take mata akan ta fitarda Miji bayan kamar wadda aka sakawa hannu Sauro be taba tsaida ita ba bare yaje gidansu da sunan zance shiyasa ta tattaro ta taho gurin Bintan saboda ta samu sauqi kuma qila ta samu Mijin a nan sanda taji zancen mutuwar Bara'atun kuka ta fasa ta dora hannu tana tumami

"Mun shiga uku Yaya Binta matar nan ta mutu bamu nemi yafiyarta ba wlh inaga haqqintane ya kamamu gashi naqi Auruwa Anty Sakina haka siddan aka koreta daga gurin aiki duk irin hanyar Dady da mutanen daya sani ta kasa samun wani aikin ga Mijinta ibtila'in daya fada masa daman da aikin nata suke lallabawa da tallafin da Dady yake bata to ta rasa aikin ita kanta Yaya Salima cikin garari take masifar yau daban ta gobe daban gashi yanzu ta mutu balle mu roqeta ta yafe mana qazafin da muka mata shikenan haka rayuwarmu zata qare a balbalce ni kenan bazan taba yin aure na na shiga uku na lalace wayyo ni Munira kaicona dana biyewa shedan muka laqabawa Baiwar Allah sharrin kisan rai bata ji ba bata gani ba" magana take cikin ihu da kururuwa wanda mutanen da suke tsakar gida Yan Bechi da sukazo tarar su Bilki duk sun Jita, Audu na kan Baranda dan jiri ne yake

neman kadashi tun sanda labarin mutuwar ya riskeshi shiyasa ya zauna a gurin ana masa fifita se ga wata sabuwa yana jiyowa daga dakin Binta.

Page 29

"Ke Munirah meye haka? Baki da hankaline kike daga murya baki san bamu kadai bane a gidan nan?" Binta ta fada a rikice tana qoqarin toshe mata baki Muniran ta fizge tana cigaba da cewa

"Ki barni Yaya Binta abin kukane ya sameni dole nayi, daman Yaya Ummu seda ta fada, tace akwai ranar da zamuyu kuka muyi Nadama, seda tace tun muna da sauran lokaci mu kwance qullin da muka daura a lokacin ban dauki maganarta da muhimmaci ba, haka kawai muna zaman zamanmu muka jazawa kanmu masifa ta hanyar shiga haqqin baiwar Allah da bataji ba bata gani ba muka bata mata suna kuma mukayi silar mutuwar Auranta gashi yanzu ta mututu ta bar mu a duniyarda nauyin haqqinta a kanmu nidai Allah ya isa tsakanina daku kun cuceni wlh" ta sake fada muryarta a sama tana rusa kuka.

"Alhamdulillahi! Dadina da gobe saurin zuwa, Allah nagode maka daka matsi bakin Azzaluman bayinka suka tonawa kansu Asuri, kaiconku wlh, kaicon Zuciya me cike da Mugunta da Zalunci irin taku. Yanzu ai ga duniyar nan gaba daya bama gidan Audu ba ta tafi ta bar muku se ku shinfida tabarma ku cigaba da zama kuna kasa abinda kukaga dama a cikin duniyar, amma ku sani wlh cutar da kukayiwa Bara'atu bazata barku ku zauna lafiya ba, yanda kuka saka rayuwarta cikin qunci da takura harta koma ga mahaliccinta da yardar ubangiji haka zaku qare taku" Bilki ta fada idanunta na tsiyayar da hawaye, ta waiwaya ta kalli Audu daya runtse ido kamar yayi bacci a inda yake zaunen tace

"Baka da banbanci kaidasu, yanda zasu qare rayuwarsu suna girbar sharrin da suka shuka kaima haka zaka qare taka kana Nadamar zamanka da Bara'atu"

"Ke Bilki menene haka? Da wanne kike so yaji dan Allah?" Aminu ya katseta. Bata kulashi ba taci gaba da kukanta. A cikin daki kuwa Munirah na gamsheqar kuka Binta na tsaye akanta ta harde hannye gaba daya kanta ya qulle ta rasa abin da zatayi a lokacin, ji take kamar ta rufeta da duka shegiyar yarinya ta kwance mata zani a Kasuwa yanzu da wace kalma take so ta gyara kwabar da tayi mata?

Tana jiyo sanda su Aminu suke fadawa Audu zasu wuce saboda kar suyi dare a hanya.

"Ka daure ka shiga daki ka kwanta, rayuwar kenan daman farkonta da qarshenta dan taqin kadan ita dai Bara'atu tata ta qare kuma In sha Allahu munayi mata kyakykyawan zaton tana Babban masauki addu'a kadai zamu cigaba da bibiyarta da ita kafin tamu tafiyar ta riskemu Allah yasa kuma abinda ya faru a baya ya zame mana darasi a rayuwarmu gaba daya" Aminu ya sake fada masa daga nan suka fara haramar wucewa Bechi.

Cikin yanayi me ban tausayi Audun ya miqe, dakyar ya iya ce musu Allah ya tsarw hanya ya daddafa ya haye samansa a falo yayi zango ya kwanta rigingine a qasa wani zafi da radadi yake ji daga can cikin zuciyarsa, numfashinsa ya ringa fita da sauri da sauri tamkar wanda yayi gudu a, a sannu ya baiwa Idanunsa damar fitarda abinda suke muradi, hawaye ya gangaro ta gefen idanunsa zuwa cikin kunnuwansa, tamkar me tsoron wani ya jishi ya saki kuka kamar mace, kuka me tafe da abubuwa da yawa a cikinsa. Cikin muryar da bata fita yake cewa

"Dana san mutuwa zakiyi Bara'atu da ban rabu dake ba, inama ina da damar maido da baya, dana canza zaman da mukayi zuwa mafarkinki, dana san rayuwarki ba zatayi tsaho ba da...da...." Ya kakare yama rasa abinda ze fada se kawai yaci gaba da kukansa a hankali kewar Bara'atun me nauyi tana dirar masa. Kalamanta na sallamar da tayi masa suka ringa dawo masa kamar sannan take maganar, tace ta yafe masa amma bashida tabbacin Allah baze kamashi da laifin cutar da ita ba wai meya shiga kansa shi? Meyasa ya kasa tantance gaskiya da qarya a zamansa da Bara'atu? Me yasa ya gagara yi mata uzuri ya ringa Muzguna mata yana tozartata? Yanzu gashi ta tafi ta bar masa duniyar dai, tayi masa nisan da baze taba taddota ba.

Seda yayi kuka me isarsa kafin ya tashi dalilin kiran sallar Azahar da ake tayi yana layi kamar wanda ya shawu ya dauro Alwala, baze iya sauka ba dan haka a nan yayi sallarsa addu'arsa gaba daya ta nemarwa Bara'atu Rahmar ubangiji ce, yana nan zaune yayi zuru zuru kamar wanda ya kwana zawo, motsin hawowa saman ya jiyo, ya waiwaya ya kalli qofa daidai nan Binta ta shigo da Try a hannunta ta doro kulolin abinci jikinta sanye da Zurmemen Hijabi har qasa fuskarta tayi jaa ta kumbura kamar wadda tasha kuka ta qoshi.

A gabansa ta ajiye Try din ta zauna se ji yayi ta fashe da kuka tana hailala da salati, yayi zukudi yana kallonta kawai.

"Mun shiga uku mun lalace Ashe Bara'atu mutuwa zatayi daman? Me yasa yarinyar nan bata haqura munyi zaman lafiya anyi rabuwar arziqi ba?" Yeeee ta sake rushewa da wani kukan.

"Binta" ya kirata cikin kaushin murya, tayi dif daga kukan munafurcin da takeyi ta kalleshi, cikin sautin daya fi na farko ya sake ce mata

"Zan sake tambayarki menene gaskiyar abinda ya faru ranar sunan Zakariyyah?"

"Wace gaskiya kuma wai kake buqatar sani bayan abinda nida yan uwana muka shaida maka tun a waccen ranar? Allah ya jiqan Bara'atu kawai ni daman tun tuni ai nace na yafe mata idanma wannan kake tunani" ta bashi amsa ba tareda ta kalli idonsa ba babu tsammani kuwa taji saukar yatsunsa a kuncinta irin marin nan na bazata seda ta wantsala gefe tana zare ido kafin ta taqarqare ta fasa qara tana kiran

"Ka mareni"

"Na marekin, kuma dukan tsiya zanyi miki yanzu muddin baki bani amsar abinda na tambayeki ba sa'innan na koraki gidanku" ya fada yana miqewa tsaye PPP ll ya razana Bintar bata taba ganin ya birkice haka ba, Bay's play llp ta fara ja ganin yana neme neme da alama abinda ze doketa dashi din yake nema hakan yasa tace

"Zan fada maka wlh, nidai na shiga bandaki ina fitowa kawai na tarar da ita ta zauna akan Jaririn"

"Har yanzu kina da bakin yimun qarya ko?" Ya fada yana nufota da wayar Radion daya zare, ta yunqura zata gudu Hijabin jikinta ya tadeta ji kake timm ta fadi a qasa be ko bata damar biqin radadin faduwar ba ya shiga zabga mata Bulaliya ta ko ina a jikinta. Dukanta yake kamar ya samu qato dan uwansa yana fadin "ba zaki fadamun gaskiya bako?"

Dadai ta tabbatar da gaskiyarta ce zata kwaceta a hannunsa dole ta fada,

"Wlh sune, basu fadamun daman ya mutu tuntuni ba se bayan da aka gama mana shari'a wlh ba laifi na bane kayi haquri ka kyaleni".

Be barta ba seda hannayensa suka gaji zuwa sannan ko motsin kirki bata iyayi ya mata lilis fatar jikinta duk ta fashe nan ya watsar da bulalar ya shige daki ya barta tana jan numfashin wahala dan kukan ma ta kasa cigaba da yinsa. Wanka yayi ya fito ya tsallajeta yayi waje abinsa, Munira na bakin qofar, tunda ta jiyo ihun yar uwar tata ta taho sedai tsoron karta shiga ya hada da ita yasa taci burki a gurin.

"Kar na dawo na tarar daku cikin gidana daga ke har itan" ya fada mata. Ta sauke ajiyar zuciya da be taba lafiyarta ba, seda ya sauka daga qasan kafin ta shiga, yanda taga Bintan ta tsorata ta kamata Binta ta fashe da kuka saboda Azaba ta ko ina jikinta radadi yakeyi mata.

Hudu ta gota sanda Munira ta hada musu yan abinda zasu buqata Binta ta coccogala suka fita daga gidan Audu saboda tsoron abinda ze iya biyo bayan zamansu Alhalin yace su tafi. Gidan Turai suka nufa dan babu halin Tafiya Kaduna a wannan lokacin, suka hadu suka ringa jimamin al'amarin.

"An auna arziqi dabe furta ya sake ki ba ai, lokaci kawai zaki bashi ya danyi fushinsa ya sakko komai ze daidaita" Turai ta fada.

Binta dake kwance magashiyyan Zazzabi na nuqurqusarta a haka ma wai taje Chemis an bata maganin rage radadi dana zazzabin shine taji dama dama.

"Yanzu ta mutuma amma tsinanniyar matar nan ba zata barni na zauna lafiya da Mijina ba Allah ya isa tsakanina da Bara'atu" ta fada tana sakin kuka. Munirah tace

"Yanzu ashe ba zaki saduda ba Yaya Binta? Wannan abun be isa ya zame miki ishara ba?"

"Zanci uwarki idan kika sake saka mun baki a magana" ta fadawa Muniran daga nan tayi shiru tana jinsu da Turai suna maganganu akan matakin daya kamata su dauka, ita dai Allah ya gani tayi nadama kuma tana fatan itama Bintan ta ganr gaskiya tun lokaci be qure mata ba sannan da sun je gida dole ta warwarewa Iyayensu komai daya faru saboda ayiwa tufkar hanci, muddin Binta bata rabu da wannan matar da alamu suka nuna ita take sake dorata a hanyar banza ba ba zata taba komawa ga Allah ba. Washr gari suka tattara suka wuce Kaduna, Binta bata tsammaci abinda ta gani bayan da Munirah ta fasa kwai ba, gigicewar da Salima da Sakina sukayi ba kadan bace Ummu ko fadi take

"Kun gani ko? Kunga abinda nake jiye muku ko? Yanzu wa gari ya waya? Gashi nan ta mutu ta bar muku duniyar kuji da dakon haqqinta".

Alhaji Zakariyya wanda yake fama da ciwon bugawar zuciya kusan shekara hudu kenan da ciwon ya ta'azzara masa abu kadan yake tayar masa dashi wannan tashin hankali daya riskeshi na abinda Yaran nasa suka aikata ya sake motsa masa ciwon sosai, ita kanta Maman Seda Hawan jininta ya tashi, Allah ya sani daga ita har Mijinta babu me muguwar zuciya da baqin rai irin wanda Yaransu suka gwada. Rashin lafiyar Alhajin tasa basu bi takan Binta ba qoqarin yanda zasu cetoshi kawai sukeyi a sannan.

AUDU

Tattara yaran yayi ya maidasu Bechi bayan da Binta ta bar gidan harda Zakariyya da bata tafi dashi ba, rayuwa ta masa quncin da be taba zaton ze tsince kansa a makamancinsa ba, komai ya sukurkuce masa, duk ya gigice ya fita a hayyacinsa shi kadai yake rayuwa a gidan abinci sedai ya siya ko yaje gidajen Abokanansa yaci. Be bi takan Binta ba balle yasan me take ciki dukda har yanzun be yanke hukunce dangane da cigaban zama da ita ba ko akasin haka cikin wannan yanayi ya share watanni biyu, Yakubu yazo Kano ya tarar dashi gashi nan shi ba me hankali ba shi ba zararre ba, dukda cewar yana da fushinsa a zuciya amma akace Jini ba wasa ba ya tausayawa Audun.

Shi ya ringa tausarsa ya nuna masa cewar kuskure dai ya rigada ya aikata a rayuwarsa yanzu abinda ya rage masa shine ya gyara sannan rabuwa sa Binta ba shine mafita ba a yanzu tunda dai ya fahimci wacece ita ya kuma san tuggu da makircin da take shirya masa a gida seya hankalta ya kuma san me yakeyi, sannan ya bashi shawara da ya hade kan gidansa, yaje ya maido da Zubaida ta raini Yayanta a gidan ubansu yasan kuma ita zata iya riqe Marayun Bara'atu ta hada da nata saboda zancen yace ze maidasu Bechi ma be taso ba ya kuma jaddada masa ya tashi ya koma makaranta ya nemi ilili na boko dana Muhammadiyya saboda Ilimi shine gishirin rayuwaz daga shi har Bintan Jahilci shine jigon abinda yake qara ingizasu ga shirmen da suke aikatawa a rayuwarsu.

Karo na farko da Yakubun ya dangantashi da Jahilci kuma ya amsa beji Haushi ba ya kuma tabbatar masa da ze bazama neman Ilimi ze kuma gyara mu'amalarsa, zancen Zubaida kuwa daman ya dade yana saqa hakan a zuciyarsa tun ma kafin Bara'atu ta sake fita daga gidansa dan haka ya roqr Yakubun dayayi masa Jagora suje dan yana kunyar Idon Mahaifinta ya sani be kyautawa Tsohon ba. Yakubu beqi ba suka shirya sukaje, ko a fuska Malam Hassan be nuna musu komai ba ya ringa Maraba dasu ga Yan Biyu sunyi girma sosai sunyi wayo idan ka gansu zaka dauka sun shekara uku ko sama kamanninsu daya sak sedai banbancin halayya inji Malam Hassan ya nuna Hussaini yana cewa

"Kaga wannan kaiya biyo sak, rigima a cikin Hussaini harda ta bayarwa sadaka shi kuwa takwarana yanda kasan wannan dan uwan naka salihin bawa babu ruwansa haka Tagwai din zeyita cin zalinsa yayi shiru na zakaji bakinsa ba". Audu ya sunkuyar da kai dan ji yayi kamar zaginsa Malam Hassan yake a fakaice Yakubu kuma yayi murmushi yana cewa

"Dama hakane ai duk tagwaye se an samu wannan banbancin dabi'ar daya me sanyi daya me zafi"

"Wannan gaskiya ne dan nima nawa Hussainin Allah ya jaddada rahma a gareshi haka muka sha fama tun quruciya har zuwa girma shekarun mu Arba'in da biyar Allah yayi masa rasuwa sedai shi be bar baya ba yaya hudu ya haifa duk kuma sun rigashi mutuwa" Inji Malam Hassan.

"Allah ya jaddada rahma a gareshi" Audu da Yakubu suka hada baki gurin fadi. Shiru sukayi nadan lokaci kafin Yakubu ya numfashi ya amayarwa da Malam Hassan abinda yake tafe dasu.

"Wai, ashe baka sani ba? Ai yau kwana Ashirin da tara kenan da Zubaida ta daura aure kwana goma sha biyu kuma da tarewarta, nan qasan mu babu nisa take Yaron Aminina Malam Bala ta Aura wannan da kuka taba gaisawa a nan har nake ce maka Daga qasar waje ya dawo yayo karatun Likitanci" Malam Hassan ya fada yana duban Audu Audun kuma ya kalli Yakubu kamar dashi ake maganar,

"Tooo ai babu labari Baba, da yake muma din an samu Rashi ne uwargidansa ce ta rasu a Makka sunje aikin Hajji ba'a dawo da ita ba wannan ya tayar masa da hankali har yasa ya dauki lokaci haka be leqo Yaran ba. Ashe kuma haka ubangiji ya qaddaro babu rabon komawarsu da itaz to masha Allahu munyi murna Allah ya sa hakan shine mafi Alkhairi a rayuwarsu baki daya" inji Yakubu.

*MAMAN MARYAM ONLINE BUSSINESS*

*Ina kuke Mata Yan kwalisa , Ina nufin isassun Mata ,Wai shin Kuna da labarin shahararren company nan namu na GHT wato good healthtreatments*

*Wanda yazo muku da fitattu Kuma* *ingantatattun suppliment ,na dukkan matsalolin ku*

*Ina maisan tayi kyau,irin na isassun Mata ya fitar Miki da shef dinki tayi Miki gyara in and out ,nemi royal jelly dinmu na company GHT*

*Wanda aka yishi da xuma ,kundai San amfanin Zuma basai na fada miku ba , hajiya ta kixo ki Yi gyara domin ki kerewa sa,a kije taro ko baki da ko sisi kiji Ana rangada Miki hajiya , saboda yanda Zaki Kara kwarjini ,kina walwali acikin mutane , magungunan ght anti agen ne suna maida tsohuwa* *yarinya ,yarinya Kuma ta koma jaririya*

*Muna da magunguna iri iri*

*NA GYARAN JIKI*

*NA GOGE NANKARWA*

*NA RAGE QIBA*

*NA CIRE TUMBI*

*NA QARIN HIPS*

*NA GIRMAN BREAST*

*NA QARA TSAHON GASHI*

*NA QARIN NI'IMA WANDA ZAI SAUKAR MIKI DA NI'IMA YA QARA MIKI DADI DA ZAQI A GURIN OGA*

*Muna da hadin bita zai zai ,indai kishiyar ki tana Shan magungunan GHT, tohh lallai sunan ki sorry domin kuwa tazarar dake tsakanin ku kamar tazarar sama ne da kasa*

*Muna da Wanda zai matseki ciki da waje Andai na yayin dinki uwargida*,

*Sannan company mu na GHTBai tsaya anan ba*

*Ya kawo muku maganin dukkan matsalolin ku*

*INA MASU HAWAN JINI?*

*INA MASU CIWON ZUCIYA?*

*INA MASU CIWON QODA?*

*INA MASU CIWON HANTA?*

*INA MASU SICKLER?*

*INA MASU HIV?*

*INA MASU CANCER?*

*INA MASU NEMAN HAIHUWA?*

*Tohh Ku matso GHT taxo muku da magungunan matsalolin ku*

*Kuma muna da testimonys da yawa ,na wadanda suka gwada suka da ce*

*Munanan a KANO KUNTAU*

*Kuma muna tura Kaya ko wanne gari cikin aminci da gaskiya , kuma kayan mu muna badashi ne cikin price Mai rahusa ga kyau ga inganci sannan ga Rahusa*

*Kutuntube mu ta wannan number 08129249549*

*07011401314*

Haka suka tattara suka tashi guiwoyi a sage, har sun shiga Mota Audu ya kalleshi yace

"Mu koma mu tafi da yaran"

"Idan ka dakko su ina zaka kaisu? Ko kuwa kai zaka haqura da fita nema ka zauna rainon Yara? Koda zaka karbe su ba yanzu ba ka fara bari ka nutsu kasan alqiblar daka kama sannan se kayi batun dakko Yara, yanzu dai gashi yayanka shida Audu Aure uku, ina fatan ya zama na qarshe saboda Aure Aure bashi da dadi, sau da yawa yana kawo rarrabuwar kawuna Ahali musamman a gida irin naka da Shugaban gidan be zama tsayayye ba, kaje ka zauna kayi shawara ka yankewa kanka hukuncin abinda ya kamata kayi a yanzu, kaga dai Bara'atu ta tafi inda babu dawowa, Zubaida Tayi Aure nasan kuma sedai wata qaddara ta ubangiji ce zata fiddota daga gidan auranta Binta kadai ta rage maka uwar Yaya da kake da damar cigaba da zama da ita dan haka ka maidota ta riqe Yayanta kana iya nemo wata Macen daka yarda da tarbiyyarta da zata mayewa wadannan Iyayen da basu tare dasu domin na tabbatar Bintan dana sani bazata riqa maka Yaro ko guda daya tsakani da Allah ba.

BAYAN WATANNI UKU

Watanni uku suka shude wata biyar kenan tun bayan rasuwar Bara'atu da kuma barin Binta gidan Audu, be waiwayeta ba be kuma je Kadunan ba kamar yanda Suma Iyayenta basu nemi da yaje ba. Mahaifinta yace duk hukuncin da Audun ya yanke akanta dai dai ne kuma shi baze shiga cikin maganar su balle Alfarmarsa tasa ya yanke hukuncin da bashi yaso a zuciyarsa ba. Wannan zama ya quntata Binta matuqa da gaske, babu walwala ko Yancin da take dashi a baya ta zama kamar wata mujiya kowa kyararta yakeyi tsakanin Iyayen abinda yake qara rura wutar Bala'i a zuciyarta kenan ta sake cin Alwashi kala kala akan komawarta gidan Audu.

Wulaqancin daya mata baze tafi a banza ba wlh seya gane kurensa.

A bangaren Audu kuwa bayan dogon tunani da shawarwari daga yan uwa da Abokanan Arziqi ya yanke shawarar sake Aure, duk wanda ya masa maganar Binta fa se yace yana sane lokaci ze nuna abinda ya kamata yayi da ita da yawa sun dauka ya saketa ne ma ganin an tasarma rabin shekara babu labarinta a gidab. Wannan karon mata biyu ya rakito a lokaci daya, Hadiza data kasance Bazawara auranta biyu na farko Mijin ya rasu sena biyun kuma rabuwa sukayi tana da yarinya daya dashi yar Ƙofar dawanau ce amma tana yawan zuwa Goron dutse gidan Yayarta a nan suka hadu da Audun kamar da wasa yayiwa Mijin Yayarta magana wanda suke gaisuwar mutunci dashi babu bata lokaci ya shige masa gaba magana taje gaban Manya.

Ta biyun kuma Aisha, yace ga Sarkin Ƙaraye Maimartaba Alhaji Ahmadu Isah na biyu. Ita din Ƙanwace ga Abokin kasuwancin sa Najibullahi Amadu wanda suka hadu

sanadin Noman Rani da Audu yakeyi a gonakinsa da suke Kusalla wani Ƙauye dake ƙarqashin Ƙaramar hukumar ta Ƙaraye Gonakin Audun sunyi iyaka dana Najibullahin wannan tasa suke haɗuwa idan sunje zagayen Gona daga haka kuma zumumci ya Ƙullu harta kai Audun yana zuwa gidan Najibu duk sanda ya shiga qaraye a nan kuma yaga Aisha kamar da wasa yacewa Najibun tayi masa dukda yarinya ce ƙarama shekarunta basu haura sha hudu ba tana cikin ta sha biyar sannan ganinta yana tuna masa da Bara'atu lokacin daya aureta banbancin ita Aisha tana da dan girman Jiki kadan tafi Bara'atu cika ido a lokacin da take da shekarunta.

Najibu ya tabbatar masa in har da gaske yake shi ze shige masa gaba akan maganar wannan tasa daya yanke shawarar Ƙarin Auran ya tuntubeshi, babu bata lokaci kuma ya gabatar dashi ga Maimartaba. Shaidar daya samu daga Najibu da sauran Mutanen garin da suke masa aiki tasa har Sarki ya Aminta dashi ya kuma ce yaje ya nemi yardar Aisha dan shi bayayiwa Yaransa Auran dole.

Aisha tasan Audu dukda Ƙarqarinsu gaisuwa duk sanda yaje gidan Yayan nata, tana bala'in girmamashi dan ganin babban mutum take masa kwatsam sega maganar Aure tana qoqarin shiga tsakaninsu, ita din yarinya ce me matuqar sanyin hali da biyya ga Manyanta wannan dalili ya saka sanda Yayanta ya sameta da maganar Abokinsa ya ganta yana sonta ya tambayeta ko tana da wani da take so tace masa Aa, shikenan magana ta Ƙullu har anje Tambaya.

Yakubu ne ya Tilasta masa cewar dole yaje gidansu Binta, babu yanda za'ayi yaci gaba da jingineta gaban iyayenta tsayin lokaci dan sun masa shiru bayana nufin basu son yarsu bane kawaici kawai sukayi masa kuma da son itama su koya mata darasi ta ganr kuskuren abinda ta aikata dan gaka baze saura sabon aure ba tareda Binta ta san Matsayarta ba. Dole ya shirya zuwa Kaduna, yanda Alhaji Zakariyya ya ringa bashi haƙuri yasa duk yaji wani iri, kamar ze durqusa masa yake roqonsa da yayi haƙuri akan abinda Ƴayansa suka aikata masa a madadinsu yana nema musu afuwa, ya Ƙara da cewa

"Bana so ka dubeni cikin yanke hukuncin makomarku kaida Mamana, karka cutar da kanka, idan har kana ganin bazaka iya cigaba da zama da ita ba ina goyon bayanka daka sauwaƙe mata domin tayi abinda ta cancanci hakan, amma idan kana ganin zaka iya yafe mata kayi mata uzuri to, ina da yaqinin abinda ya faru a baya baze maimaita kansa ba domin iyakar Fada, Nasiha da Tunatarwar daya kamata muyi mata a matsayin mu na Iyayenta munyi muma kuma fatan taji".

Se yaga kamar a fakaice Alhajin roƙonsa yakeyi akan ya mayar da Bintan, kuma bai kamatu ace mutum da yayi masa tarin Alkhairi a rayuwa kamar Akhaji Zakariyya ace shi ya gagara maida masa ba, darajar tasa shi Amincewa yayi bikon Binta, ya kuma sanarwa da Alhaji zancen auran da ze daura da Mata biyu sati biyu masu zuwa  Alhajin yayi masa murna da fatan Alkhairi haka ma Mama sannan ya kira Binta a gabansa ya shaida mata muddin ta koma ta sake aikata wani abu da ze tunzura Audun ya sake aikota gida to daga can ta nemi gurin zuwa badai gidansa ba, ya sake ja mata kunne sosai kanta na Ƴasa tana kukan munafunci tamkar taji abinda yake faɗi kuma zatayi amfani dashi.

Kwanan sa biyu da zuwa suka juyo tare, zaman dai babu yabo babu fallasa sabgoginsa yake yana ta shirye sgiryen bikinsa. Ta tarar da an sake Ƙalƙale gidan, banda dakinta da yake a kulle hatta da samansa an bare Asalin Tarazo da yake gurin an maida Na zamani kayansa ya sakko dasu dakin da Abdullahi yake ciki nan ya kafa Gadonsa yake kwana yanzun, tsakar gidan ma am Canza Tarazo, kitchen dinsu na waje an gyarashi sosai kamar dai na cikin dakunan su se aka yanki filin tsakar gidan aka sakeyin wani Kitchen din na Langa langa, babu fus bare ta tambayeshi wannan sabon shirin na menene haka a haka taci kwanaki goma da dawowa wanda kuma ya rage saura kwana biyu a daurawa Audu Aure ranar taga ana shigowa da sababbin kayan gado da Kujeru aka haura sama dasu.

Daya dawo da daddare ta dauka ranar zasu koma saman tunda an saka kaya harda katifa amma setaga ya bude sabon dakinsa ya shige abinsa se washe gari yake shaida mata gobe Daurin auransa, amma Amarya daya ce zata tare a goben dayar se wani satin.

Kamar sabuwar galahanga haka ta bude baki tana kallonsa jin wannan magana, wai Amarya daya, ita dayar se wani satin,

"Amaren har su nawane?" Ta jefa masa tambayar, ya wani kalleta sheqeqe kafin yace

"Su biyu ne kafin Allah ya kawo cikon ta hudun"

"A nan gidan zaka zubamu mu ukun?" Ta sake tambayarsa wannan karon kallonta kawai yayi be amsa mata ba ya juya ya fita.

Kuka ta fashe dashi, kishiya har biyu rana daya ita Binta ita za'ayiwa wannan tozarcin? Duk Bara'atu ce ta janyo mata wlhba zata saɓu ba dole ta nemi mafita. Har ta saɓi mayafinta zata fita ta tuno cikin sababbin sharuɗɗan daya gindaya mata harda fita babu izini, ta mayar dan yanzu neman yarda takeyi dole tayi biyayya akan duk abinda aka gindaya mata. Kuka wiwi ta ringayi, Turai take so taje ta gani su shawarta babu halin fita, tayi data sanin ƙin nemo Lantana tunda ta dawo da yanzu ita zata tasa kawai ta aiketa gidan Turan tunda ita ba zata iya zuwa ba. Yanzu haka zata zauna a kawo mata Kishiyar babu ko wanda ze tayata zama ya danne mata Ƙirji?

Washe gari kuwa kamar yanda yace tun farar Safiya yasha wanka ya bar gidan, fitarsa babu jimawa sega mota cike da Yan Bechi, su Bilki da wasu daga cikin faccalolinta. Tsohon falon Bara'atu suka baza tabarma suka aje kayayyakinsu. Gaisuwa kadai sukayi da Bintan suka hau haramar dora abincin dan sunzo da cefanensu rankatakaf kafin su shigo Audun ya fada musu inda zasu tsaya su karba danyan abinci kadai suka diba a store dinta suka hau girki.

Binta na daki kamar tsohuwar mayya ita da gidanta amma bata iya fitowa su kuwa hidima suke suna raha suna dariya, suka sauke abinci suka ware na Yan Daurin Aure idan dawo da kuma na karbar Amarya sukaci nasu kafin suka hau wanka da shiryawa.

Afujajan kamar an jehota Lantana ta diro gidan, taje sau babu Adadi sanda Binta bata nan seda Audu yace ze saka a kulleta idan ta sake zuwar masa gida neman wata Binta kafin ya samu salama ta dena zuwa. Binta na kwance ta dirar mata kamar jifa tana haki harta bata tsoro,

"Hajiya, ashe har bayan mutum ya mutu ma yana iya cigaba da kitsa tuggu da munafunci?" Lantanar ta tambayeta, Binta tana gyara zama ta galla mata harara tana cewa

"Wane kalar hauka da dabbanci yake damunki Lantana zaki faɗo mun daki haka se kace Asiri? Yaushe na fara sakar miki fuska da zakiyi mun wannan sakarcin?"

"Hajiya ki ƙyale wannan maganar tukunna muyi wadda ta kawoni, kinsan wacece Amaryar da Alhaji ya auro miki kuwa?" Lantana ta bagarar da maganar Bintan,

itama jin an soso mata inda yake mata Ƙaiƙayi yasa ta zabura tana tambayar wacece.

"Ƙanwar Sadiya ce Aminiyar Kishyarki Marigayiya Bara'atu, nidai nace ko a mafarki take zywarwa Sadiyar suka Ƙulla wannan Munafuncin? Ko kuwa daman tun Marigayiyar na raye ita Sadiyar tayi niyyar cin Amanarta ta aurawa Alhaji Ƙanwarta?"

"Allah mungode maka daka bamu lafiyar jiki data Ƙwaƙwalwa" Bilki datavshiga tambayar Binta ta bada abinda za'a saka mata abinci ta tsinci zancen nasu me kama dana zararru.

"Ban shiga sabgarku ba Bilki karki kuskura kishiga tawa" Binta ta gargadeta, se da tayi irin dariyar nan me cusa takaicin kafin tace

"Allah ya huci zuciyar Hajiya Binta uwargidan Dan Uwana Audu, daman kwano nazo ki bada a saka miki abinci, idan kuma kin Ƙoshi shikenan"

"Ku kuke yunqar Abinci nida kika ganni kinsan daga gidan wadata na fito abinci ya ishemu shiyasa har muka cida Dan uwan naki Butulu dayaci ya Ƙoshi yake gwada mana halin nas ana butulci, ita kuma annamimiyar da tana Ƙasa a kwance ma ba zata barni na huta ba wlh zamu gamu, Addu'a zan durfafiyi ubangiji ya shiga tsakanina da ita" Binta ta zaburoqa Bilki, seta juya tana dariya tace

"Tabbas jahilci yafi hauka ciwo, amma naji dadi da kikace zaki durfafi Addu'a, Allah ya dubeki ya kawo miki sauqi cikin lalular da take damunki Binta" daga nan ta fice Binta ta yunqura zata bita taji ba'asi wai tace mata Jahila kuma mahaukaciya Lantana ta tareta.

"Hajiya keda akuyarki tayi kura dan Allah ki nutsu ki Ƙyalesu yanzu matan unguwar nan zasu fara shigowa dan Sadiya babu wanda bata gayyata ba daman surutunki ya gama cika unguwa wasu ma cewa suke Asiri kikayiwa Bara'atu dukda ta fita daga gidan nan seda kika aikata lahira da yawa kinga ba fuskar da zasu shigo miki suka samu ba yanzu ko dalilin bikin nan kowa zata shigo kinayin abu a tafi dake a baki sharri se iya wanda kikaji wlh" da wannan ta tausheta suka zauna jigum jigum babu jimawa kuwa mata suka fara tururuwa a cikin gidan.

Ana sallame sallar isha'i aka kawo Amarya gida ya sake cika danƙam da mata, Lantana ce ta fita ta gano mata ina za'a saka Amaryar dan tana ta lissafa inda ze ajiye dayar tubda dai gidansu dakin mata biyu ne ko kuwa can ze gwamutsu kowa ta dauki daki daya su haɗa falo bata san musu ba.

Lantana tazo mata da labarin daya sake gigitata, wai sama aka dora Amarya, dama tana ta jiyo dudubniyar mutane ta dauka zazzabi da ciwon kan daya rufetane yasa take jiye jiye ashe da gaske ne, lallai wato da Gaske Audu ya tashi ci mata mutunchi a wannan karon.

Page 30

Se gurin sha biyu na dare suka samu sauqin Jamar da suka cika gidan maqil kamar wani sabon yinin biki akeyi,Binta na daki ita da Lantana da yau ta samu guri ga qugunta gana Binta akan Kujera tana bata shawarwari ita dai Binta jinta kawai take badanta fahimta ba, yanayin da take ciki yau din baze misaltu ba, Tashin hankali Kishiya biyu a rana daya. Bata iya runtsawa ba har gidan yayi shiru alamar kowa ya watse, maganganun habaici tasha su a waqe sedai wai yau ita Binta ta gagara yin gaba da gaba da mutanen da sukazo har gidanta suka takaleta da bala'i, yanda yan uwan Hadizan suka zo, dukda basu shigar mata ba waqe waqensu kadai ya sanar mata a shirye suke jira suke ta tanka musu su qaddamar mata dan haka ta kama kanta tana lissafin abinda zatawa Amaruar da zarar an watse domin ta rantse ba'ayi Macen da zata sha gabanta a gurin Audu ba, dole ta fita ta bar mata gida tun gabanin dayar da yake iqirari ta shigo.

Tana zaune tana gyangyadi Audu ya shigo, tayi firgigit ta miqe, Lantana dai tuni ta kwanta tana janna Rago taji Laushin Katifa ita ko tuna tana da Miji da yaya batayi ba ta baje a dakin Bintan.

"Bakuyi bacci ba ashe? Daman wasu kaya nazo dauka se gobe idan Allah ya kaimu zan shigo gidan" ya fada daga inda yake tsaye kafin kuma tace wani abu ya juya abinsa ya fice.

Washe gari ma haka gidan ya tashi da hayaniyar Ƙawayen Hadiza da suka kwana a gidan kamar wanda suka rako budurwa, tana jinsu suna cigaba da Habaice habaicen da suka fara jiya, gidanbe zama nasu ba se bayan la'asar zuwa sannan

Yan Bechi sun tafi Ƙawayen Hadizan ma duk sun tafi gida ya rage Binta da Amaryarta dake can sama abinta. Audu be shigo ba se bayan sallar Isha'i, Niƙi Niƙi da ledoji yana daga labulenta ƙamshin gasassun Kaji dana Tsire suka ziyarci hancinta dan ita din ba daga nan ba gurin iya tantance ƙamshi. A tsaitsaye suka gaisa yace mata seda safe ya fita, data rasa abinyi se kawai ta dora hannaye a kai ta rushe da kuka.

Washe gari bayan data gama lallashinkanta ta kuma tsara yanda zata ci uban Amarya domin ance ba'a bori da sanyin jiki, Ƙarfe tara tayi wanla tsaf ta sheƙa kwalliya irin wadda ta manta rabon da tayita, ta kashe ɗauri ta fesa Turaren da Mama ta bata sanda zasu taho, fuskarta fes amma da za'a tona ƙasan ranta yafi gawayi duhu. Ta fito saɓe da Naziru, tana fitowa tayi kyakykyawan gani, Amarya Hadiza cikin nata salon gayun ta fito daga tsohon kitchen ɗinsu na tsakar gida hannunta dauke da Fulas na ruwan zafi da kuma na Abinci.

Cikin taku me kama da rausaya ta kama matakalar bene ta haye abinta kamar bata lura da tsayuwar Bintan ba. Binta ta bita da idanu tana jin tamkar ta shaƙota amma ta cije, seda ta daidaici Hadizan ta isa saman har yaci ace ta zauna kafin ta yunƙura zata bi bayanta sallamar Lantana ta sake dakatar da ita.

"Yawwa, riqemun shi" ta fada tana miƙa mata Naziru ya lafe amma haka ta yakiceshi ta bawa Lantana ya kuwa tsanyara kuka amma bata dakata ba ta haye saman tana fadin

"Shegen Yaro me dafar tsiya".

Seda ta saisaita kanta ta gwada takun da zata shiga dashi kafin ta tura ƙofar ta shiga kanta tsaye ta durfafi dakin baccin Audu. Hadiza na tsugunne tsakiyar falon tana gyara zaman abin karin data ajiye musu tana kuma dakon fitowar megidan dake ƙarasa shiryawa a ciki tajo an buɗe ƙofa ta daga kai taga Binta ce bata kalli sashen da take ba ta wuce kai tsaye abinta zata shigar mata ɗaki babu shiri ta daka tsalle kafin Binta ta kai ga ƙofar tuni ta cimmata ta tare mata gaba cikin yanayina babu yabo babu fallasa take faɗin "baiwar Allah daga ina?"

Binta ta kalleta sheƙeƙe kafin tayi tsaki tace

"Ban gane daga ina ba? Kanki daya kike mun wannan tambayar ko kuwa baki san ni wacece ba sannan baki san cewar nan ɗin dakin Mijina bane?"

"Ɗakin Mijinki fa? da alamu kece kanki yake da motsi a ciki shiyasa har kika gaza tantance a inda kike, to idan ma ada nan din Ɗakin Mijinki ne a yanzu ba nashi bane mallakina ne, sannan ko ace har yanzu yana mazaunin Ɗakinnasa bakida damar ko shiga tunda ina ciki, kwana nane dole ki jira harse randa na gama uzurina na fita kafin ki shoga ki shimfida naki mulkin" Hadiza ta mayar mata da martani cikin lafazin dake nuna daidai nake dake. Binta ta lafta mata harara tareda da jan dogon tsaki ta kauce mata ta kama mabuɗin ƙofar tana cewa

"Idan na shiga se ki fiddo ni waje isashshiya me ɗaki" bata ko gama rife bakinta ba kuwa Hadizan ya fizgota ta maidota bayaz Binta tayi taga taga zata fadi ta kama bango, data tabbatar ta daidaita a ƙasa ta shammaci Hadizan ta wats amata mari.

"Bantan uba, kika mareni? Wlh kin jangwalowa kanki masifa da bala'i se kin san ni kika mara" Hadizan ta fada a haukace kafin tayi ƙasa, Binta na jira taga ko ramawa zatayi se ji tayi ta wawashi ƙafafunta kafin tayi wani yunƙuri ta kaita ƙasa. Dambe ne rikica ya sarƙe tsakaninsu, Binta nada garin jiki haka kuma tana da ƙarfi amma naci da dakiyar zuciyar Hadizan tasa take neman cin galaba akan Bintan dan tunda ta fahinci ƙafafunta nan ne Rauninta su take riƙewa ta watsar da ita a ƙasa ta hayeta ta kila idan ta mirgine ita ma ta sakata a Osi ta daka haka suke ta birgima a falon sun yi watsa watsa dashi labulen ƙofar dakin kansa yayo ƙasa sun rikito da ƙarfen.

Audu na bandaki ya ringa jiyo kamar hayaniya kamar kuma ana dukan Bango, ya bude ƙofa ya leƙo da kunnensa dan son tantance daga ina hayaniyar take tashi idan ba gizo ba se yaji kanar daga Falo ne, ƙarar fashewar abu dayaji Tusss ta sakashi rarumar Kwangorinsa ya ɗaura din daya  jikinsa duk kumfar da be gama ɗaurayewa ba ya fito yana goge ta fuskarsa, yana buɗe ƙofa ya tarar da dambaruwar da ake kwasa a falon, ƙarar dayaji kuma Talabijin dinsa suka rikito da ita ta fashe  basu ma lura dashi ba, seda ya buga musu tsawar da ta saka dole suka shiga taitayinsu sannan kowa taja gefe tana sauke numfashi kamar Zakaru.

"Wane irin hauka da dabbanci kuke mun a gida? nan ɗin sansanin dambe ne ko yaya? ke Binta me ma ya kawoki nan ma da farko?" Audu ya faɗa cikin tsananin fushi yana kallon Binta dataji jiki dan gar bakinta ya fashe yana zubarda jini. Cikin kuka tace

"Bakaga abinda wannn mahaukaciyar daka auro a matsayin mata tayi mun ba se tambayata kakeyi meya kawoni dakin Mijina?"

"Wane ɗakin Mijin naki? Ai kinsan banida wani ɗaki a cikin gidan nan yanzu. Banda fitina da son tayar da zaune tsaye meya kawoki? ki maza ki bar nan gurin kuma wannan ya zama kado na ƙarshe da zaki sake tako ƙafarki zuwa saman nan muddin bame dakince ta baki dama ba, fice Malama" Audun ya sake mayar mata da bacin ran dayafi na farko, Binta ta kalleshi ta kalli Hadiza dake sakin murmushin cin nasara wani kuka me tafe da zallar baƙin ciki da takaici ya zo mata seta wuce tana yinsa wiwi dan tasan a yanda ransa yake a ɓacen nan idan ta tsaya zubar da mutunchin seyafi haka Hadiza ta bita da kallo.

"Ke kuma akan me zaki kamata da dambe?" ya maida dubansa ga Hadiza se tayi ƙasa da kanta kawai ba tareda tace komai ba, yayi tsaki ya juya yaba ce mata

"Ki Gyara gurin kuma ki samarmun wani abun da zanci tunda kun lalata wannan"

"Yanzun kuwa in sha Allahu" ta fada tana duƙawa ta fara tattare barnar da sukayi ranta ƙal da beyi mata faɗa kamar yanda yayiwa Bintan ba.

Binta kuwa seda taji kanta na barazanar fashewa kafin ta haƙura ta dena kuka. Fuska tayi luhu luhu ga kuka ga Kutufon data sha a hannun Hadiza. Har mamaki takeyi yanda Hadizan da take gani tafi ƙarfi ta lallasata tilas ta canza salo tunda dai a doke ita zata ji jiki to ita ma ta ƙarƙashin ƙasa zata bi mata kamar sauran ta hanyar tuggu da munafunci dan ta rantse ba zata zauna ba ɗayar ba zata shigo ta tarar da ita ba. Ta tafasa ruwa ta gargasa jikinta ta kwanta tana cigaba da ƙulle ƙulle a ranta.

Audu kuwa fes suka karya da Amaryarsa suna raha da jin dadi ya mata sallama ya fice ba tareda yako leƙa ya gano halin da Binta take ciki ba. A haka yayiwa Hadiza kwana uku ya koma dakin Binta, a taƙin kwanakin nan kan Binta ta raina kanta domin duk wani tuggu da take jin ta iya Hadizan ta doketa ta shanye a kwana uku seda ta maodata abar tausayi a cikin gidan ta kankane komai ba ga me gidan ba hatta su Mairo se yanda tace dasu dukda daman Mairo bata da Matsala Lantana ce yar kwal uban kuma tun washe garin tarewar Hadizan ta saita mata zama data sakko da kwanuka Lantana na wanke wanake ta ajiye mata seta matsar dasu gefe bata wanke ba, bata kulata ba se da maigidan ya dawo har sannan kuma Lantana bata tafi ba taba daka dan yanzu ta zama ta hannun damar Binta da ita ake shawarta komai tunda basa haɗuwa da Turai suna zaune Audun ya shiga ya cewa

Lantana ta fice masa daga gida an sallameta. Binta tayi tsugul zatayi magana ya yarfata yace idan ta sa baki se tabi Lantanar tunda gidansa ne akan me Matarsa zata sakata abu taƙiyi Lantana ta ringa tumami tana roƙon ayi haƙuri dakyar ya barta bayan yaja mata gargaɗi shikenan ta shiga taitayinta.

Kamar yanda Audu ya faɗi kwanan Juma'a na zagayowa Iyalan Gidan Sarkin Ƙaraye wanda suka samu rakiyar Ahalin gidan sarkin Kano dan can aka ajiye Amarya masu yi mata danki ne sukayi gaba suka dirarwa gidan Audu. Unguwa tacika maƙil ana ta kallon su masu busa Algaitu natayi. A cikin gida kuwa yai din ba Binta dake neman haukacewa ba su Turai na danneta hatta da Hadiza tasha jinin jikinta ganin wadda ake shirin kawo musu a matsayin ta ukun ta tabbatar wannan duk abinda suke taƙama dashi ta damesu ta shanye, abun da ta sakawa ranta kuma suka shawarta da Yayarta shine ta zauna lafiya da Amaryar, babu ruwanta da shirginta muddin ba ita ta sanyota ciki ba domin fada da saraki babu riba.

Se bayan Isha'i Amarya ta iso bisa da rakiyar Gimbiyoyin Kano da Ƙaraye da suka kawota. Dattijai ne na ƙwarai, dukda kasancewarsu sarakai sun san mutunci da darajar Dan Adam, sda suka shiga dakinBinta da kuma na Hadizan suka kai musu Amarya kamar yanda Al'adar Bahaushe take, kafin su iso Kano seda suka kaita Bechi gurin Dangin Audu suka kwana sannan suka dakko hanya washe garin suka iso Kano dan haka babu wanda yazo daga can.

Amarya na lullube cikin Alkyabba yar ubansu Ƙwarjinin matan da suka rakota yasa su Turai suka kasa iya daga ido dakyau su kalle su bare su gano ya Amaryar take, Binta dai tana kwance dan ta gagara zama abin dai ba'a cewa komai aka gama musayar gaisuwa da Miƙa Amana suka wuce dakin Hadiza.

"Dukda ban ga Amaryar dakyau ba gani nake yarinya ce ma babu wani abu da ze firgitaki akanta Binta" Turai ta faɗa bayan fitarsu. Binta tace

"Hmmm" kawai dan baki ya mutu.

An bar Amarya da kuyanginta guda biyu ragowar suka musu sallama suka wuce. Turai taso su leƙa Amarya tunda yan rakiyar sun tafi amma Zainab tace Aa, su bari sa dawo takanas su ganta kawai hakan sukawa Binta sallama suka tafi. Ranar Ango be kwana dakin Amarya ba, nan dakin tsakar gidan dai ya shige abinsa ya kwana. Washe gari kafin sha biyu Kuyangin Amarya suka ƙarasa mata gyare gyare sukayi mata sallama kamar yanda ta basu umarni su koma gidan sarki saboda Ango yace ayi masa uzuri base sun zauna ba da akwai masu taimaka musu da ayyuka har biyu

anan gidan ya gayawa Yayanta Najibu kuma ya sanar da iyayensu suncr babu komai itama jiyan ya gaya mata shiyasa bayan sun kammala komai tace su wuce kawai.

Tun la'asar sakaliya Ango ya shige dakin Amarya wadda bata leƙo tsakar gida ba balle mutan gida su ganta. Hankalin Binta yayi ƙololuwar tashi da jin Al'amarin daya auku, kasa zama tayi ta tafi tagar dakin Amarya ta dasa kujera ason jin me zasu tattauna daya shiga daki tun yanzu tsabar zirgilli se gashi ta jiyo wa kanta abinda yafi ƙarfinta ta ringa kuka a tsakar gida jin Audu yana yiwa Amarya kyaututtuka cikin fitar hayyaci yace har gidan da suke ciki ya bata. Hadiza dake girki ta ringa wa Binta dariya kamar zata kife, faɗi take "Allah ya ƙara, a garin gulma da munafunci zaki jiyo abinda ze toshe miki dodon kunne ki dena ji gaba daya"

"Idan baki rufe mun baki ba senayi ƙasa ƙasa dake Hadiza" Bintan ta zaburo mata. Hadiza ta gyara tsayuwa ta dafe kwankwaso tace

"Idan baki fasa ba Binta, ai kin san karon mu dake wancan da nayi miki kadan ne wlh yau sace ki zanyi tas dan naga wannan luhu luhun jikin naki yasa kike neman masifar mutane"

"Zaki gane kurenki wlh dani kike magana" Binta ta maida mata tana shigewa daki dan ba hauka takeyi ba da zata sake gwabza dambe da Hadizan har yau bata gama jinyar ƙasusuwanta data tasamma karya mata ba.

Haka Ango ya yiwa Amarya sati guda, rawar kan da ya ringayi ba Binta ba Hadiza kanta ranta ya sosu amma da yake ita tana da kissar zaman duniya seta shanye bata ko nuna a fuska ba wannan tasa Audun yake ta tata ya kuma hadata da Amarya a cewarsa ta zama ƙanwarta ta ringa kula da ita Binta kuwa data tayar masa da hauka fita yayi a sabgarta ta nemi shiga sabgar yar Amaryarsa da banda gaisuwa da murmushi babu abinda ke hadata da mutanen gidan nan ya nuna mata ya fita hauka.

"Wlh ko bisa kuskure naji hannunki ya taba jikinta se kin gane baki da hankali" ya faɗawa Binta sanda tayi niyyar marin Aisha lokacin daya hadasu su ukun.

Haka aka ci gaba dagurgura rayuwa, watanni uku Bi ta ta tayarwa da Audu zancen ya kamata a ɗebo yaran Bara'atu da Tagwayen Zubaida su dawo gida kodan saboda makaranta dan a yanzun ta dan rage abubuwa a ƙoƙarinta na son maido da

darajarta data zube a idona Audun. Ya kuwa ji dadin maganar harya zanta da Hadiza da kuma Aisha. Hadiza tace zata riƙe su, zata karbe kayansu tunda daki daya ne da ita ba ze yuwu su ringa kwana can ba se su zauna nan dakin da Abdullahi yake amma Binta tayi tsallen Albarka tace ba'a isa ba. Ai ita ta tado da maganar a dakko su kuma ita ta zauna da uwarsu ita suka sani sannan itace babba a gidan dan haka ita zata riƙe Yaran. Daman ita Aisha yar kallo ce a tsakaninsu, idan ba an sako ta ba tafi ku mutu bata ce musu, seta wuni a daki in har ba ita take da girki ba shine zata fito Mairo tanayi tana kallo harta fara karban wasu abubuwan tana tayata dan a gida bata girki kusan yanzu ne ya kamata ace an fara sakata ire iren wadannan ayyukan se kuma Aure yayi mata sammako shi yasa koda suke rigimar waye ze riƙe yaran bata saka musu baki ba ƙarshe da Audun da kansa yace Binta ce zata riƙe yara haka kuwa akayi ya debo su suka dawo gidan, an musu nisa a makaranta wannan tasa aka sake maidasu baya Zakariyya ya wucesu se aka hadasu su biyar harda Naziru aka saka su.

Zama yaci gaba matayen uku suka samu ciki kusan lokaci daya, Binta bata lura da cewar sauran biyun duk sun samu ƙaruwa ba domin a duk sallar da zatayi se tayi addu'ar Allah yasa duk su kasance juya basa haihuwa ita kuma Allah yasa duk shekara tayita haihuwar Yara Maza ta cika gidan dasu tana ta kaɗifiri da iyayi wai ita me ciki bata san su biyun ma sun rigata samu ba se randa zataje Asibiti ta fito ta gansu duk su biyun kowa da shirin fita, bata ta Aisha domin tunda ta ganta tace wannan me sauƙi ce Hadiza ce a gabanta dan haka ita ta harara tana cewa

"Karma ki kuskura kice yau ma binmu zakiyi, ba zaki tashi fita ba se kinga zan fita da Mijina to se ki taka ƙafarki ko ki fita ki hau Bus"

"To ai yau ba ranar girkin ki bace balle ki nuna mun isa da iko, Miji kuma namu zakice dan bake kadai kike dashi ba" Hadiza ta maida mata. Aisha na gefe tana kallonsu bata ce uffan ba sema lafewa datayi jikin katanga tana kallonsu sega Audu ya fito

"Uhm Bismillahi zaku fara ba kudai se kace kajin hausa wlh baku da aiki se faɗa ce cacar baki Allah ya sawwaƙa muku" ya faɗa yana baza babbar riga. Binta ta tunzura dan ta tsani wannan wulaƙancin da yake mata a gabansu ya ringa nuna ita ba komai bace daidai suke da ita dan haka tace

"Idan ma fita zatayi ka gaya mata ko ta taka ƙafarta ko kuma ta nemi Bus dan ba zata bimu ba"

"Tunda motar takice?" Ya mayar mata ba tareda ya kalleta ba, ya juya kan Aisha ya dan saki fuska yace

"Bismillah, muje ko?"

"Kuje ina? Au itama fitar zatayi?"

"Kinga Binta idan baki zuwa ki koma ciki suma duk Asibitin zasuje". Tana cika tana batsewa suka fita wajen tayi wuf zata shige gaba Audu ya dakatar da ita da cewa

"Shiga baya, Aisha ce zata zauna gaba"

Hadiza ta kwashe da dariya Binta ta sake ƙuluwa ta lailayo Ashar ta watsa mata ita dai ta shige mota tana cigaba da dariyarta.

Bayan sun isa Asibiti tana tsammatar taga kowa ta kama gabanta dan a zatonta dubiya su biyun zasuje se gani tayi sun nufi bangare daya na yan Awo dan a waje ya ajiye su yace idan yaje kamfani Musbahu and juyo da motar ya jirasu ya mayar dasu gida.

Binta ta ringa binsu tana jira taga abinda ya kawo su gurin Awon ciki sedai daga yanda taga suna gaisawa da Ma'aikatan gurin tasan da sanayya a tsakani suka zauna gurin jira ana bin layi bayan an karbi Katunansu jikinta har rawa ya dauka sanda taga kowa ta zaro kati daga jaka ta miƙa kenan duk cikine dasu bata sani ba? Yaushe akayi? Tana zaman me?

Aka ringa kiran Binta Zakariyya ina bata ma jisu ba tayi nisa a duniyar tunani da zullumi karfa suma duk su haifi Maza dan taga kamar Audu bashi da ƙwan haifar ya mace. Matar da take musu awon ta kallera tace

"Baiwar Allah tunanin me kikeyi haka duk kin firgice kalli fa har jininki ya ɗaga?"

"Kedai kiyi aikinki ki sallameni ina da abinyi" Binta ta gwaɓa mata magana aiko matar ta harziƙo itama tace

"Se nice banida aikinyi ko ai bacci kika ga ina yi yanzu ko rawa"

"Kiyi haƙuri Sista" Hadiza ta tsoma musu baki aiko Binta tayi kanta da masifa ganin a waje suke yasa ta mata shiru se ma'aikatan ne suka haye itama Bintan kamar sa cinyeta Awon da ba'ayi mata ba kenan ta tattara ta fice ta haye Bus se unguwarsu Turai dan tana buƙatar su tattauna wannan matsala ta yaya za'ayi su biyu suyi ciki.

Audu kuwa isarsa kamfani ya tarar da wani mummuman Labari, motoci guda biyar da suka dakko masa Mai daga kudu haka nan wuta ta tashi sun ƙone ƙurmus harda direba guda daya dayayi ƙundunbala saboda motarsa ce ta ƙarsher sun tsaya zasuci abinci Abin ya faru tamkar Tsafi kawai wuta ta kama motar tsakiya kanka kace me sauran sun dauka an hanashi amma ya kafe ya tafi a zatonsa ze iya janye motar kafin wutar ta cimmata se gashi yana shiga ta kama gaba daya se tokarsa aka tattare.

Babban abin al'ajabi kamar yanda aka bashi labari ba iyakacin motocinsa bane a gurin mota tafi Ashirin da suka taho tare duk sukayi fakin suna cin abinci amma ibtila'in akan nasa suka sauka basu taba komai ba duk kuma iyakar ƙoƙarinsu na su kashe wutar abu ya gagara. Hankalin Audu ya tashi matuƙa domin ba ƙananan kudade ne suka narke ba sannan ga Rai da aka rasa. Gaba daya suka ɗunguma gidansu Direban daya rasu me suna Lawan sukayi musu Ta'aziyya, ya bawa Iyalansa kudade masu ɗan kauri da kayan abinci yace kafin su yanke abinda ya kamata suyi musu. Wannan damuwar tasa ya manta da matansa na Asibiti a can kuma bayan sun gama har bayan Azahar shiru Musbahun dayace ze zo ya maidasu beje ba Hadiza tace su tafi kawai ta yuwu aiki yasha kansa ya manta.

Hakan ko akayi suka kamo hanya suka dawo gida, sun sauka a bakin titi Hadiza tacewa Aisha

"Ko zamu ƙarasa gidan Yaya Yakubu dan naji Babansu Baba yace sunzo gari muje muyi Bikon Yaya Balaraba be kamatu ace bama zumunchi da ita ba gaskiya"

"Amma bazeyi faɗa ba?" Aisha ta faɗa cikin sanyinta. Hadiza tayi murmushi tace

"Haba dai gidan Yaya Yakubu ne fa babu faɗan da zeyi kuma tunda ba girki zamuyi ba kinga bamu da matsala da anyi la'asar se mu wuce gida idan ya dawo se mu sanar masa da munje".

Faran faran Balaraba ta tarbesu daman ta dan wayi Hadiza sukan hadu idan tazo gidan Yayarta lokacin da suke can unguwar suma Aisha ce bata sani ba dan bataje gidan ba Yakubun dai yaje yaga Amare da yace suje tace Aa ai bata da sauran

dalilin zuwa gidan Audu kuma. Se da sukayi sallar La'asar sannan sukayi haramar tafiya ta hada musu tsaraba cikin abubuwan data zo dasu, Dada da jininsu ya haɗu da Aisha tana ganin sun tashi tacezata bisu

"Ki bari muje da ita idan yaso se Baffansu ya maido ta anjima da daddare" inji Aisha suka tafi da ita.

Sun riga Binta komawa gida itace da girki kuma, sun tarar da yaran sun dawo daga makaranta Abdullahi ya tafasa musu taliya sunci da sauran miyar da yace ya gani a Kicin, shidin yana gida yanzu sun gama jarabawar fita daga sakandire da Audu yace ze fara zuwa kasuwa se kuma yace ya zauna ya huta dan ƙasar qaje yake da burin turashi idan takardar sa tayi kyau.

Binta bata dawo na se guraren biyar da rabi ta shiga gidan tareda Lantana da alama ko ta biya ta gidan tane ta kirata shigarsu babu jimawa Mairo ma tazo ta fara shirin dora abincin dare. Shiru shiru har akayi Isha'i Audu be dawo ba, Binta ta sake cika tayi dam saboda ita keda girki shiyasa yayi zamansa a waje da waccen yar shilarce ai da tuni a gidan ma zeyi Magriba jikinsa na rawa se kace nata Matancin na Gwal ne. Har tara ta buga shiru babu Audu, Hadiza ta leƙa falon Binta dake zaune tana kaɗa ƙafa tana kuma ayyana tijarar da zatayiwa Audu yau idan ya dawo taji muryar Hadizan na tambayarta ko ya shigo.

"Ke matarnan ki fita daga sabgata wallahi tallahi idan kika tiƙeni sena miki abinda bakiyi tsammata ba. Wato kunga gurin zama har kun bude mara kun ɗauki ciki to wlh ku kwana da sanin  zaku haifesu a gidajen ubanninku kuwa" Binta ta faɗa tana miƙewa tsaye. Hadiza da fuskarta ke cike da damuqa tace

"Ni ba tashin hankali ya kawoni gurinki ba, gani nayi ya zarta lokutan daya saba dawowa kuma idan ma zeyi dare irin haka yana sanar mana shiyasa hankalina ya tashi. Mijina na fari daga irin wannan fitar shiru shiru se bugamun ƙofa akayi na buɗe aka shigo da gawarsa"

"Keta shafa wannan ni tsakanina da tsohon mijin naki ai Allah ya isa ce da be mutu ba ai da Mijina be kwaso mun ke kinzo kin addabeni ba, ki barmun ƙofar daki kuma Audun ai ba Ji njiri bane da za'ace ya bata" Binta na rufe baki sujai dirar mota mintina kaɗan ya shiga fuskar nan kamar wanda aka aikowa da saƙon mutuwa be

kulasu ba ya durfafi sama harya fara hawa meya tuna kuma ya sakko ya wuto Ɗakin Binta.

"Au da hankalinka ya gushe can zakayi kenan an maka kiranye ka shigo kamar wanda aka jefo baka ko gani dakyau ai seka tafi can ɗin" Binta ta faɗa tana babbake ƙofarta. Hadiza tayi masa sannu da zuwa ya ɗaga mata hannu yana cewa Bintan

"Matsa na shige"

"Ai sedai ka koma inda da ka niyyaci zuwa" inji Binta. Tsaki me ƙarfi yaj ya juya ya haye saman Hadiza tabi bayansa Binta ta kwarma Ihu murya a sama tana kiran yau akwai tashin hankali a gidan ashe.

A saman kuwa harya fara cire kaya Hadiza ta isa, a tausashe take cewa

"Da alama gajiya tasa ka manta ba a nan kake na yau"

"Ina sane, sedai in kema korata zakiyi se in tafi" ya bata amsa.

"Ba haka bane, rigimar Maman Zakariyya ce bana so kana jiyowa gata can tana masifa bana son tashin hankali ko ƙo dazun a Asibiti seda aka ce mu guji yawan hayaniya" ta sake faɗa cikin taushin lafazi. Audu ya rafka tsaki, da matan nan sun san me yake ciki da sun ɗaga masa ƙafa. Rigarsa ya raruma ya sauka sukayi kiciɓus da Binta na hawowa ya raɓeta ya wuce ɗakin Aisha.

Ganinsa ba yanda ta sababa yasa ta masa sannu da zuwa ya shige ɗaki ta bishi da ruwa, tana jiyo hayaniyar Binta dukda bata jin me take faɗi sosai. Abincinta ta kai masa beci ba yana kishingiɗe ya harɗe hannaye ya zurawa guri daya ido, ta ajiye, tana so ta tambayeshi ko lafiya amma ta kasa se kawai ta fita ga Dada da tayiwa mamarta alƙawarin za'a maidota hartayi barci yanayinsa kuma ya nuna ba lafiya ba balle tayimasa maganar.

Tana zama Binta ta faɗo kamar jifa, ta mata kallo daya ta maida idonta kan Talabijin yanayin kallon Hadarin kajin da tayi matan ya saka Binta yin shiru dan kwarjini yarinyar ta mata, tabbas Sarauta ba Ƙarya ba. Ɗakin data san zata samu Audu ta tura ta shiga, Aisha bata san ya sukayi ba taga Binta ta fito sumi sumi ta wuce. Data sake leƙawa se taga kamar yayi barci dan haka ta shige dayan dakinta suka kwanta tareda Dada.

Seda aka kwashi sati daya cikin wani yanayi a gidan, Audu ba magana babu murmushi bare dariya duk kuma wadda tayi kuskuren shiga sabgarsa ta jawa kanta tijara. Basu san me yake faruwa ba se randa zugar Yan Bechi suka zo Bus biyu ranar befita ba kusan kwana biyu ma kenan be fita ba sedai yaransa dake ta zarya a gidan kuma sedai su fita can inda yake ajiye mota suyi magana ko Binta duk iya labenta bata tsinto abinda ake ciki ba har seda yan Bechi sukazo jaje.

Ashe bayan motar Mai kwanaki Babbar Gonarsa da yake noman shinkafa ruwa ya shanyeta. Gonata ba yar ƙarama ba. Shinkafar kuma tayi kyau dan har an saka ranar girbi Dam din dake kusa da inda yake Noman yayi ambaliya gana ɗaya ya shafe gonakin dake kan hanya abindai ya munana ba'a cewa komai.

Binta ta ringa kyarma jin Maƙudan kuɗaɗen da aka ce sun narke daga kan Mai zuwa shinkafar,

"Shikenan, a garin kwashe kwashenka ka kwaso mana me farar ƙafa" ta faɗa hannu biyu aka jiki na tsuma hawaye suna sakko mata. Duk akayi shiru aka zuba mata ido banda Audu dayaja tsaki dan maganar tata ɓacin rai ta ƙara masa ya tuna da wani lokaci can baya sanda suna Yara tun Malam nada rai Goggo Fadi na ce musu yayan me farar ƙafa, a lokacin abinda ya dauka saboda Dada Farace tar duk jikinta abinda take nufi kenan kalar fatar ƙafarta shiyasa be taɓa gayawa Dadan ba se bayan daya girma ya san ma'anar abin sannan ya fahimci zaginsu takeyi shiyasa duk inda yaji an faɗa se ransa ya baci.

Binta ta ringa kuka tana maimaita an Auro musu me farar Ƙafa shikenan zasu tagayyare su shiga wani hali yan jaje suka koma wasu na ganin salonta data saba laƙawa matan da yake aurowa sharrine wasu kuma sun yarda da abinda ta fada dan tun bayan Auran Audun abubuwa suka fara canzawa yanayin bunƙasar Arziƙin tayi ƙasa ba'a dai samu wani ibtila'i babba kamar wadannan ba.

A hankali rayuwar walwala da jin dadin da akeyi a gidan ta fara juyewa zuwa ƙunci da tashin hankali dan zuciyar megidan a kusa take kullum ƙiris yake jira a taɓashi yayi zazzaga ga mata uku kowacce da ciki haihuwa kusa hatta da yanayin cima ta sauya dan samun ƙasa yakeyi ba sama ba.  An kwashi watanni cikin wannan hali, Audu nada shirin mallakar rijiyar Mai tasa ta kasansa a kwankin baya domin har ya

fara harhaɗa kudade sun gama tsara yanda za'ayi da Alhaji Zakariyya wanda ze siyar masa da daya daga cikin rijiyoyinsa sedai matsalar daya shiga a yanzu da harta girgiza masa jari ta tilasta masa karbo kudaden daya bayar matsayin kafin Alƙalami ya sakasu cikin harkokinsa na Noma da kiwo wanda anan Ibtila'in yafi sauka, Amfanin gonar da ya noma a shekarar sama da kaso hamsin ƙwari sun lalatashi haka dabbobinsa na gidan gona Kaji sedai a shiga basu abinci a tarar da au fululu a ƙasa sun mutu ko a hangi Sa ya Tirƙeƙen Rago yana kakarin mutuwa sedai a danne a yanka.

Abu dai kamar wasa ana saka ran samu sauƙi se ya zamana kullum kamar Tiri ƙaruwa abubuwan sukeyi. Mutane da yawa sukace hannu aka saka masa, Asirine, jifansa akayi ya bazama shine waccen tsangaya ya kai sadaka shine waccen gidansa kuwa kullum cike yake da Gardawa anata saukar Karatun Alƙur'ani idan an gama ayi sadaka amma abin se godiyar Allah kawai.

Ana wannan yanayi Hadiza ta tashi da Naƙuda cikin dare, Audu da Aisha ne suka fita kaita Asibiti dan Bibta cewa tayi Allah ya kasheta babu inda zataje da Aishar ta shiga kiranta Audu kuma tace masa Yara, be kamatu a barsu su kadai a gida ba. Haka kawai sun hau Titi suna tafiya mota ta tsaya, ya fita yayi yaj dube dube ya sake kunnata yana ja inji yayi wata ƙara Baammm mota ta cake kuma ko ba'a fada musu ba sun san Injine ya buga, tamkar Audu ya fasa kuka, ya fita nemo taimako Hadiza dai nan cikin mota ta haihu ta santalo danta Namiji ƙato.

Wani mutum ne ya taimaka musu ya ƙarasa Asibitin dasu se safiya aka sallamosu bayan an tabbatar da ita da Jaririnta duk lafiyarsu ƙalau motar Audu kuma akaje da Janwe aka dauketa.

Binta da taga Hadiza ta dawo gida da Da Namiji ba'a cewa komai, baƙin ciki kamar ta mutu ko zuwa tayi mata barka batayi ba har akayi sunan Aminu Hadizan ta koma gida saboda jikinta dayaƙi mata dadi tun bayan haihuwar Binta faɗi take  ta tafi kenan ba zata dawo ba.

Haihuwar Hadiza ta sake zuwar musu da sabon sauyin dayafi na farko dan Asara ce take afkuwa kan Asara duk abinda Audun ya taba seya lalace Binta ta samu nayi ta ringa kwakwazo ai damab ta faɗa ya auro me Farar Ƙafa beji ba. Yakubu ya samu Audu yake tambayarsa

"Anya kuwa Audu kana fitar da zakka yanda take idan munyi lissafi?"

Cikin tsananin damuwa Audu yake ce masa

"Allah shine shaidata dukda bani da cikakken sani akan kasafin Zakka shiyasa ma bana fitarwa da kaina nake baka, kuma wlh Duk idan muka fitarda lissafin shekara yanda kace a fitar din nan haka nake cirewa da hannuna nake rabawa dan karma na bawa wani yayi ha'inci ya rage sannan ka san muna fitarda sadaka daban itama haka ake hadawa a rabar nidai na yarda wannan jarabawa ce kawai daga ubangiji ina kuma roƙon daya bani ikon cinyewa"

"Hakane, na godewa Allah daya sa ka yarda cewa duk wani tsanani daga shine haka kuma sauƙi ma daga gareshi ne. Kaci gaba da Addu'a muma muna tayaka karka kuskura ka bari wata maganar banza tayi tasiri a ranka ace maka wani ya maka Asiri ko wani abu, ka ƙaddara Allahn daya baka Arziƙin shine ya jarabceka akansa".

Kwanan Hadiza Ashirin da bakwai da haihuwa Aisha ma ta haihu ta samu Mace. A gida ta haihu daga ita se Bilki da kuma Unguwar zoman da aka kira dan Audu baya nan kuma babu mota balle a kaita Asibiti kuma Allah ya bata da sauƙi ta samu yarta Kyakykyawa me kama da ita. Binta na daki tana fama da kanta dan itama ta kusa Lantana ta kwaza mata zancen haihuwar, tayi wata dariya harda buga ƙafa tana cewa

"Ita kuma da ƙafar hagu ta shigo kowa na farawa da Magaji shine zata haifo mace? Koda yake na godewa Allah, Allah yasa in ma zata cigaba da haihuwar tayita jera irinta" Lantana ta tayata sukayita izgilanci akan Ikon Allah.

Da Audu ya dawo ya tarar da haihuwar, farin cikin jin Mace aka haifa ya wanke masa kaso hamsin na damuwar da yake kwana yana tashi a cikinta. Ya fita ya samo mota suka tafi Asibiti, su kadai yasa aka maido shi kuma ya tafi bakin Asibitin Nasarawa inda suke da zuwa Binta siyayyar Haihuwa dan rigar da aka sanyawa Jinjirar bashi ya siya ba be kuma san inda Aisha ta sameta ba halin daya shiga yasa duk ya manta da wai ana da buƙatar wasu abubuwan na haihuwa Hadiza ma se bayan data haihun ya basu kudi suka siyo abinda ya sawwaƙa tunda ta san yanda Al'amuran suke wannan kuwa cewa yayi a hada masa kayan barka na Alfarma, aka ware masa wanda ze tafi dasu lokacin ragowar yace a hade masa su ze turo wanda ze ɗauka ya wuce da sauran.

Binta data tsammaci Audu bazeyi murnar samun ƙaruwar Ɗiya mace ba se taga akasin haka, murna sosai ya ringayi, kwanan Aisha uku da haihuwa ta tafi wanka gida wanda daƙyar Audun ya bari gida ya rage Shida Binta se yara. Binta ta shiga zullumi, tunda Aisha ta haihu walwalar Audu ta ƙaru haka bashida wata hira seta yar jaririyar me suna Amina taci sunan Mahaifiyar Najibullahi yayiwa kara, basuyi sati biyu da tafiya ba ya kwashi yaran duka ya kaisu su gano Laila kamar yanda suke kiran yarinyar wannan ya ɗaga mata hankali ta kuma shiga zullumin to kodai itama ta haifi Mace ne saboda bata so ace wani Ɗa yafi nata shiga zuciyar Audu, amma da ta zauna tayi dogon Nazari seta watsar da waccen shawara, ita tana lissafine ne da abinda za'a mutu a bar mata, Yara Maza sune masu Gado duk wannan soyayyar da yakewa Lailan a banza tunda baze ɗauketa ya ɗora akan dukiyarsa ba da wannan ta watsar da tunanin haihuwar Mace taci gaba da lissafin zazzago Yara Maza.

Tsiranta da Aisha kwana goma sha tara ta haihu a Asibiti ta samu ya mace kyakykyawa da ita tamkar Laila dan yarinyar na fadowa Nurse din data karbeta ta dagata tana cewa

"Masha Allahu zankadi kin samu kyakykyawar yarinya da gani da Mahaifinta tayi kama dan ta fiki kyau" Nurse din ta gaya mata magana dan Binta ta gallabesu se dai idan bataje Awo ba amma tabbas se tayi faɗa da wata daga cikinsu.

Zabura Binta tayi ta fizgi ƙafar Yar kamar wadda ta fizgi leda ko wani abu mara rai, tawara ƙafafun tana so ta tabbatar dagaske Mace ta haifa ko kuwa tsokanarta sukeyi data tabbatar din kuwa seta saki yar Nurses da basu gama dawowa daga mamakin fincikar da tayiwa ƙafar yarinyar ba suka dulmiya cikin na sakinta da tayi ba taredadamuwar zata faɗi a ƙasa ba. Kuka ta fashe dashi bayan data koma ta kwanta. Nurse ɗin data cafe yar ta kalleta cikin ɓacin rai tace

"Amma kedai anyi yar ku*****ba, banda ke mahaukaciya ce dabba ki fizgi ƙafar Jinjira haka bakya ko tsoron ki ji mata ciwo sannan ki saketa a ƙasa? Wlh badan mu muka karɓi haihuwarki ba da nace sato yarinyar nan kikayi"

"To kice mana, idan ma kina sonta ki riƙe na baki kuma karki sake zagina wlh dan na fiki iya tashanci" Binta ta hayayyaƙo mata, matar zata sake magana sauran suka tareta sukace ta barta da alama tana da taɓi a ƙwaƙwalwarta.

"Sedai uwarku ce me taɓi a ƙwaƙwalwa bani ba" ta bisu da zagi sanda suka fita taci gaba da kukan ta.

Haka suka tattaro suka dawo gida abin dai babu daɗi yanda Binta ta ringayi kamar me taɓin hankali duk saboda ta haifi Mace wannan fincika da tayiwa ƙafar Nazira ita tayi sanadiyyar Nakasarta wanda ba'a gane ba har seda ta kai munzalin tafiya sannan bayan dogon bincike likitoci suka gano wasu ƙananan jijiyoyin dake riƙe Sangalalen ƙafa da tafin ƙafarta ne a tsinke shiya nakastata ya zama ƙafar bata ɗaguwa sedai ta jata a ƙasa.

Lokaci daya Hadiza da Aisha suka dawo, tafiyarsu lamuran Asare Asaren da Audu yakeyi ukayi sauƙi, suna dawowa tamkar an watsawa wuta fetur abu ya koma sabo farfaɗowar daya fara aka sake kwanciya rigijin harma abin yafi nada muni. Akace zuciya bata da ƙashi balle kuma irin ta Audu me cike da wasi wasi a hankali se famfon da Binta take masa akan ya auro masu fararen ƙafa ya fara tasiri a zuciyarsa. Ya fara tsangwamar Hadiza da Aisha domin a cikinsu ne yake ganin akwai silar taɓarɓarewar Arziƙinsa, kyara, hantara, wulaƙanci ya fara yawa, Hadiza bata shiru idan ya mata ramawa takeyi daman Binta bata isheta kallo ba dan tasan gamonsu Aisha ce take masa shiru dan haka diban Albarkar tasa yaso yafi yawa akanta musamman da Binta ke yawan cewa daman an fi samun masu farar ƙafar cikin mata masu shiru shiru kuma ai data tafi wankan gida abubuwa sun farfaɗo amma tana dawowa ta dawo da tsiyarta.

Abu dai gaba yakeyi kullum ba baya ba, idan yayi kamar yabi ta Binta yaje ayi masa istahara a fayyace masa wwacece silar rugujewar Arziƙinsa se kuma ya tuna nasihar Yakubu dayace jarabawa ce saga Allah idan yayi haƙuri a sannu komai ze zama tarihi seya kanne yaci gaba da Addu'ar neman ɗauki daga ubangiji. Cikin wannan yanayi aka cinye shekara guda wanda a kullum ta Allah abin zama yake jiya tafi yau, Audu da harya fara mance lissafin abubuwan daya mallaka se gashi a hankali ya fara ɗaga kadarorinsa yana siyarwa a ƙoƙarinsa nason farfaɗo da harkar Mansa dake neman durƙushewa baki daya ya saki komai ya mayar da hankali akanta domin itace ƙarfin tattalin Arziƙinsa.

Binta ce takai wa mahaifinta rahoton abinda yake faruwa da Audun, shiri tayi ta kwashi kayanta domin tafiyar da tayi bata saka ran zata dawo ba, to ta dawo tayi me? Arziƙin da take zaman gadi yana shirin bin rariya wahala na doko musu sallama ita kam bada ita za'ayi wannan zaman ba. Alhaji Zakariyya ya tashi ɗan aike takanas aka kira masa Audu, sun tattauna amma a duk maganar da sukayi ya kasa gano musabbabin wannan Asara dake hawan Audu kamar wanda akayiwa Baki haka nan be bi takan shirmen Binta ba ya sake daukar Kudade masu kaurin gaske ya bashi yace kuma duk in wata matsala ta tashi karya jinkirta ya je gareshi, wannan karamci na Alhaji Zakariyya ya ƙara samarwa da Binta gurin zama a zuciyarsa domin ya sani Allah ne ya haɗa shi da Alhajin amma Auran Binta na daga abinda ya

ƙara dankon zumunta a tsakaninsu kuma duk abinda zeyi masa zeyi dan Allah kuma saboda yana auran yarsa, wannan tasa ya ƙara kulla aniyar riƙe Binta dakyau domin bashida wata hanya da ze sakawa da Alhajin sama da hakan tunda duk sanda zwje gurinsa se yayi masa tanbihin ya kula masa da Binta karya dubi halinta.

Wannan kudi da Alhaji Zakariyya ya bawa Audu basuje ko ina ba yana dawowa Kano wani Abokinsa yayi masa tallar Farin wake, a shekarar an samu ƙarancinsa acan wani ƙauye suka samoshi yace su siya da yawa su ajiye zuwa A kwana biyu idan farashi ya hau su fitar su siyar dashi su samu riba. Audu be taɓa yin irin wannan kasuwancin ba dan ko wani yaji ze siyi kaya ya ɓoye zuwa yayi tsada sannan ya siyar se yayi magana ya nuna masa rashin dacewar hakan amma a halin da yake ciki yanzu ta yanda ze farfado da jarinsa kawai yakeyi shiyasa ba tareda dogon tunani ba ya siyo wake aka jibge a suto, ba'a rufe watanni uku ba wake yayi muguwar tsada ya ninka kudinsa sau biyu akan abinda suka siyeshi lafiya lau Alhaji Mala Abokin Audu ya kwashe wakensa ya kai Kasuwa ana bude store din da kayan Audu suke aka tarar da wake dai babu na moro Ƙwari sun masa kaca kaca dayawa har ya fara yin gari tsabar yanda ya lalace kamar wanda ya shekara biyar a ajiye.

Hankalin Audu yayi ƙololuwar tashi da wannan Al'amari, Alhaji Mala da Bashir suka sake jaddada masa tabbas idan ba Asiri ba to cikin matansa akwai me Baƙar ƙafa a tasu falsafar. Mala yace ya shirya ze kaishi gurin Malaminsa duk abinda ake ciki ze fayyace masa, yace Malamin yayi tafiya nan da sati ze dawo shima daman zeje dan akwai tafiya da zeyi yana so a bashi sa'a.

"Ai Ba'a zama haka Alhaji Audu yanda mutane suka ɓaci da jefw jefe wani ido kawai ze saka maka kaga komai naka ya tasamma lalacewa idan kayi sake magauta se sun kaika ƙas wlh kana kallon dai yanda abubuwa suke tafiyar maka kai base an ce maka da wani abu a ƙasa ba, idan ka biye ta wannan Yayan naka kana ji kana gani sedai ka koma jiran wa wani shago ana sammaka na cefane sunanka ya tashi daga sahun matasan masu kudi ka koma layin yan karayar Arziƙi" Inji Mala.

Yana komawa gida ranar Binta ce take da girki, damuwa ta masa yawa yanzun shiyasa abu da yawa ba s an tambayeshi ba yana zaune zeyita rattabo zance kamar wanda kansa ya kwance.

"Ina za'a jira har nan da sati ai ka tashi kawai kaje nan gurin Malam Salisu Mijin Lantana, ba tuntuni nake gaya maka ba amma kaƙi jin ta tawa ai yanzu da aka faɗa maka a waje ka yarda. Bari kaga inje in gano maka idan yana nan ai ba'a bori da sanyin jiki wlh gara asan abinda ake ciki" Binta ta faɗa tana saɓar Hijabi.

Audu bashida zaɓi a wannan gaɓar ruwan kashe gobara kawai yake buƙata shiyasa be hanata ba, Hadiza na zaune tsakar gida kan tabarma tana cin Abinci garin da dan zafi zafi ga tsohon cikin da take dashi ya ƙara mata jin zafin Binta ta wuceta tana cewa

"Maza kici gobe sedai kici a gidan me dattin hula".

Can ta samu Lantana suka gama ƙulla yanda za'ayi Lantana ta shiga ta zayyanewa Malam Salisu yace babu damuwa duk yanda tace hakan za'ayi. Seda sawu ya fara daukewa Sha daya saura kafin Audu ya tafi gidan Malam kamar wani munafuki, Malam Salisu ya tambayeshi sunan sa dana Matayen nasa gaba ɗaya ya gama zana ƙasarsa yana jan wani kwandalelen carbi se muzurai yake da ido yana motsa baki yayi zane ya share yafi sau biyar kafin ya kalli Audu yace

"Gaskiya Alhaji akwai gagarumar matsala, wai ma ya akayi haka wannan Aure babu bincike?"

"Kamar yaya? Anyi bincike mana" Audun ya bashi amsa yana kallonsa a wani ɗage, Malam Salisu ya murmusa yana cigaba da zanen sa yace

"Ba binciken halayya ko Asali nake nufi ba, Aa burujin ƙasa. Ya kamata ace in za'ayi Auran Alhaji a ringa bincikawa aga taurari matar ya suke zasuyi daidai da naka ko kuwa? Kamar dai yanzu kaga ita ta farin Fatsuma Binta kace sunanta ko? Wannan mahadin Arziƙi ce.

Kaga kai Tauraronka wuta ne, ita kuma Iska ce, ya kaga wuta a lokacin bazara yanda iska take fifitata inta ringaci balbal ai Allah kadai ke iya kasheta to haka ne hadin naku taurarinta suna ingiza Arziƙinka zeyita hauhawa ne to kuma se akayi rashin dace ita Aishatul Humaira taurarinta na Ƙasa ne, wuta kuwa da an yafa mata ƙasa ai mutiwa takeyi to me kankat kuma Hadizatul kubura ita taurarin ruwa ne shiyasa da suka hadu su biyu se ƙarfinsu ya danne na fatsuma suke neman nakastaka kuma in har ba'a dauki mataki ba gaskiya Alhaji abin bazeyi kyau ba dan abinda ƙasar nan take nunamun idan ba'ayi da gaske ba har rigar sawa ka fita seka wayi gari baka da me kyau abinci kuwa wata rana se an kwana ba'a ci ba sannan yawan haihuwarsu yanwan Talaucin da zasu cigaba da saukar maka a gida".

Ranar kwana zaune Audu yayi yana ƙullawa da kwancewa, Binta bata tambayeshi yanda sukayi ba domin ita ta tsara komai se dariya take a cikin bargo dan ta

saddaƙar gobe daga Hadiza har Aisha kwanan gidajen tsoffinsu zasuyi. Washe gari da duku duku ya mata sallama yace ya tafi Bechi, be ko bi takan sauran matan ba, yara da suke gaidashi ma be iya amsawa ba ya fita burinsa ya isa Bechi ya samu Hashimu domin wannan sabgarsa ce shine yasan takan Malamai. Ya isa Bechi be zarce ko ina ba se gidan Hashimun yayi rashin sa'a baya nan amma inji Jamila ba dadewa zeyi ba dan yace a aje masa abincin rana. A tsakar gidan ya zauna kan Turmi tsabar halin da yake ciki ya gagara shiga turakar Hashimun da tace ta masa shimfiɗa ta aje masa ruwa da fura.

Seda akayi Azahar Hashimu ya shigo, an gaya masa anga wucewar Audu amma be yarda ba dan har can gida ya ratsa be ganshi ba se gashi ya tarar dashi a tsakar gida kan Turmi fuskarsa ta gama bayyanar da tashin hankalin da yake ciki. A taƙaice ya masa bayani babu bata lokaci ya goyeshi a mashin suka tafi wani dan ƙauye dake gabansu kadan. Bayanan Malam Salisu sunyi kamanceceniya da juna sedai an saɓa lamba a wasu guraren kamar Taurarin Aisha da Binta dashi bafulatanin yace masa taurarinsu iri daya ne da nasa dan haka babu matsala a hadinsu Hadizan dai itace me matsalar kuma akasin da aka samu Taurarinta nada matuƙar haske shiyasa ta tasiranci duka su ukun suke karbar gashi.

Bala'un da Dan fulani ya jere masa je afka idan ne rabu da ita ba sun zarce na Malam Salisu, Hashimu yace

"Dama a garin aure aure tun mutum na kwaso Arziƙi harse ya ɗebo tsiya gashi dai ka gani ai se ka san abinyi tunda wuri dan duk abinda Malam Sallau ya faɗa da wuya kaga be faru ba, seda ya hanani Auran Saude naƙi gashi ko ina karbar sakamakona"

"Aishi ba Allah bane bare kace duk abinda ya faɗa seya tabbata" Audun ya bashi amsa. Hashimu yayi dariyar rainin hankali yace

"Na fika sanin haka, amma tunda muka yarda dashi har muka zo tambaya gabansa ai magana ta ƙare, ya rahe naka ka ɗauki matakin daya dace" a gurin sukayi sallama Audu ya juyo Kano zuciyarsa fal wasi wasi. Ya daukarwa Yakubu Alƙawarin baze sake sakin wata mace ba gashi kuma yanzu dole ta saka zeyi sakin kuma ya san duk ta yanda zeyiwa Yakubu bayani baze taba fahimtarsa ba. Maganar gaskiya kuma baze zauna yanaji yana gani ya rasa komai nasa dalilin wata mace ba.

Bayan daya dawo a ɗakin Hadizan ya sauka ta karbi girki, ya ringa kallonta ga Aminu dake da shekara daya da watanni biyu ga ciki da ko yau ko gobe zata iya haifeshi. Tausayinta ya kamashi duk da halin da take ciki amma tana ta kaida kawowa tana hada masa abinci. A zamantakewa Hadiza bata da laifi, mace ce ta gaske dan ze iya cewa a duk matan da ya aura babu tsayayya kamarta. Ta iya kula dashi haka tsakaninta da sauran Matansa tana mu'amalantar kowacce da sigar data zo mata. Duk bala'in Binta ta sarara mata sedai tayi a bayan idonta amma ya zeyi? Shidai baze cigaba da zama da ita ba domin ko ita idan zata masa Adalci inta san itace matsalarsa yaci ta nemi rabuwa dashi da kanta kawai su haƙura da juna ze saketa badan baya sonta ba sedai dan hakan shine maslaharsu baki daya ze kuma cigaba da daukar nauyinta har iyakar rai ze cigaba dayi mata duk abinda ya kamata tamkar tana gidansa.

Da daddare harsun kwanta ya tashi zaune, cikin nutsuwar dashi kansa besan yana da ita ba ua shiga yiwa Hadiza bayanin halin da ake ciki.

"Kuma ka yarda? Tamkar fa kayi shirka ne Audu ka tara sani da Allah. Ya za'ayi ace maka nice silar Karayar Arziƙinka kuma ka yarda shin Allah baya jarabtar mutum haka nan dole se wani abu ya zama sila?" faɗa hawaye ma zubo mata.

Audu ya murtuke fuska, yasan gaskiya ta fada to amma magana ta ƙare tunda har aka gaya masa kuma ya yarda dan haka yace

"Kinga muyi haƙuri kawai nidai na rigada na yanke hukunci na sakeki saki biyu, kina da zaɓi na kici gaba da zama a gidan nan ba se lallai mutane sun san na sake ki bama".

Kallon kayi hauka tayi masa kafin ta miƙe tana kuka ta shiga haɗa kaya, se yayi fakare kuma yana kallonta duk yaji babu dadi, da ace da wata hanyar da ze magance matsalar sa ba lallai seta rabuqa da Hadiza ba daya bi amma babu yanda ya iya. Washe gari ta bar gidan, Binta ta ringa rawa tana shewa, satin Hadiza ɗaya da tafiya ta haifi Aliyu, tayi maza biyu kenan sunyi kankan kan da Binta wadda keda cikin da na biyar Aisha nada na biyu a sannan. Tun Binta na saka ran Aisha zata bi bayan Hadiza har suka haihu wannan karon ma kusan tare tsiran kwana goma tsakaninsu Binta ta fara haihuwa ta samu Yakubu takwaran Alƙali, seda Babanta ya shiga maganar kafin ta haƙura da wannan takwara da aka mata da babban maƙiyinta Aisha kuma Abdullahi suna kiransa Sarki Al'amuran Audu kuma suka fara daidaita sannu a hankali Arziƙi yaci gaba da bunƙasa harya fi nada.

Aisha da Binta sukaci gaba da jera haihuwa, bayan su Yakubu Binta ta haifi Aisha wadda Audu yayiwa ƙanwarsa takwara ta rasu wata daya kafin haihuqar Bintan itama yarinyar watanta hudu ta koma a lokacin kuma Aisha ta haifi Ahmad shekararsa daya cif Binta ta haifi Jafar se suka sake jera haihuwa Binta ce ta fara ta haifi Faisal Aisha kuma Salim, shekara biyu suka sake yin mata duk su biyun Binta ta samu Hafsa suna kiranta Hajiya Ƙarama ita kuma Aisha Khadija. Daga nan Binta haihuwar ta dan tsayawa Binta har seda Aisha ta haifi Maimuna da Aslamiyya sanan Binta ta sake haifar Bashir da Lawal, burinta ya cika, ta tara yaya maza zarata har guda shida tafi kowa Kaso cikin dukiyar Audu.

Tsakanin Binta da Aisha zaman dai ba'a cewa komai, Binta bata fasa halinta ba ita kuma Aishar seta zame mata ƙarfen ƙafa domin dukta inda ta buga babu riba tayi tuggun tayi munafurcin amma abun yaƙi yaci. Audun da take taƙamar data san Lagonsa se Aishar ta fita bin yanda yake so domin zama tayi tamkar ruwa a cikinsu, hannu idan an saka mata ba zata ciza ba, duk abinda Binta zatace tayi idan ta titsiyeta ba zata musa ba koda batayin ba zata bashi haƙuri ta kuma baiwa Bintan ta yanda in Binta ta sake tada maganar daga baya a maimakon yaga laifin Aisha se faɗan ya juya kanta yace ta fiya son tada zaune tsaye.

Halin Aisha kuma ba Munafurci bane ko Kissa irin ta Binta Aa haka Allah yayita da sanyi, sedai nata sanyi ya zame mata Alkhairi ba irin na Bara'atu na haka ita bata ɗauki wargi ko rainin da har Binta zata bautar da ita ba kallo da ido idan bata ga dama ba zata mata ba idan kuwa zata kwana tana magana setaga dama zata ɗaga kai ta kalleta, da Binta ta buga ta buga taga babu riba seta saki lamarin Aisha ta koma kan Yayan gida wanda ruƙonsu gaba daya ya koma hannunta harda na Hadiza guda biyun ta saka an karbo su tun data yaye Aliyu an watsasu cikin yan uwansu.

Riƙo take musu irin na jeka ka mutu, iya babu kwaba, abinci me kyau idan sunci a gidan to ranar girkin Aisha ne wadda iyakarta dasu kenan in ta dafa abinci ta basu. Sanda aka maido dasu Aminu tacewa Audu zata ɗauke su har ta kai kayan yaran ɗakinta Allah kaɗai yasan me suka tattauna da Binta washe gari yace ta mayar dasu cikin yan uwansu saboda baya so kansu ya rabu sannan duk abinda ya shafi wani yaro a gidan muddin ba ɗanta ba babu ruwanta a ciki ƙarƙashin kulawar Binta suke.

Ita ɗin bata zurfafawa akan abubuwa dan haka bata tsananta ba ta maidasu kamar yanda yace ayi ba kuma ta shiga sabgar Yaransa muddin ba su suka kai kansu

gurinta ba wannan zata musu duk abinda ya kamata sedai idan taga wani abun cutarwa ne take tsoma baki wani sa'ilin yaji ya sa a gyara wani lokacin kuma ya gwasaleta yace ai Yayansa ne ba kuma ta fishi sonsu ba, wannan halin sanyin nata da nuna ko in kula akan wasu abubuwan shiya janyo matsalar gidan bata tsaya iyakar kan Yayan tsakar gida ba ta shafi harda nata.

Da Binta taga ta kasa cin galaba akan Aisha seta haƙura ta mayar da hankali gurin ganin ta sake kama Audu a hannu da gidan gaba ɗaya, kamar yanda Turai tace mata ta bar batun Aisha domin ba wata tsiya bace ba kuma wani ji da ita Audun yakeyi sama da ita ba ta mayar da hankali gurin gina gobenta data Yayanta. Abinda yake a gabanta yanzu shine tasan duk ta yanda zatayi ta cusa yayanta a zuciyar Audu ya zamana bashida wani tunani idan bana su ba sannan tayi duk me yuwuwa ta dakusar da ragowar a gurinsa, karta barshi ya shaƙu dasu ta hakane kawai Yaranta zasu zama sune kan gaba a kamai nasa hakan kuwa akayi babu Boka babu Malam seda ta san yanda tayi ta raba tsakaninsa da Yaran dukda daman shiɗinma ba wai yana ta tasu bane sosai domin tunda harkokin Arziƙi suka sake buɗe masa ya zamana bashida isashshen lokacim zama a gida ma balle yayi hira da yaran yasan matsalarsu.

Duk wani abu na gidan a hannun Binta yake kama daga abinci, sutura harkar karatu da duk wata buƙata kome ya tashi ita zece a tambaya, Riƙo take musu na mugunta ga Azabtarwa, a gabansa takan nuna ta damu da yaran ta ringa kai masa sukar duk yanda take ƙoƙarin jansu amma basa sakewa da ita irin dai yanda ta ringayiwa iyayensu, yaran Zubaida dana Hadiza da suka tasa se suka fara gudu suna tafiya gurin iyayensu dan itama Hadizar tayi Aure tuni, akan wannan Bintan ta haɗasu da Audu ya musu mugun duka dan tace iyayensu na zugosu duk zuwan da zasuyi se sun dawo da sabuwar ɗabi'a ya kuma kafa musu dokar hanasu zuwan daga ƙarshe ma tasa aka kaisu makarantar kwana banda Nata Yayanso se na Aisha data cw bata yarda ba sunyi ƙanƙanta, idan zasu tafi a Arziƙi irin na ubansu Garin kwaki ne da suga se ƙuli ƙuli provision dinsu idan ya bada kudi yace ayi musu siyayya seta soke ba kuma su isa su faɗa masa ba domin izayar da zasu sha se sun gwammace basu faɗa ba shima ɗin kuma be zama lallai ya yarda ba.

Yanayin matsatsi da damuwa da suke a ciki tasa cikin su shidan Hassan ne kaɗai se Aminu suke mayar da kai a karatu daman duk aji daya aka sakasu harda su Babannan da yaci ace sunkammala sakandire a sannan amma aka mayar dasu Aji daya na ƙaramar sakandire gaba daya. Banbancin da ake nuna musu ƙarara a fili tsakaninsu da sauran da iyayensu suke a gidan dukda Yayan Aisha ma ba wai sun tsira bane banbancinsu dasu uwarsu tana a gidan kuma ita bata jiran Audu ko Binta da komai na gida yake hannunta a yanzu duk abinda ya tashi na yaranta zatayi

musu wanda sauran basa fahintar hakan gani sukeyi su aka tsana aka ware wannan tasa suka washshi uban da matan uban da sauran yan uwansu gaba daya kowanne ya ƙudire wani abu daban a zuciyarsa.

Haka rayuwa taci gaba da wullawa shekaru sun shude a kullum kuma rayuwar gidan Audu lalacewa takeyi a maimakon ta gyaru, ya saki komai a hannun Binta ya fantsama duniyar neman kudi kuma Alhamdulillahi rayuwar tana gara masa. Yanda ya faro tushen Arziƙinsa tareda Yan uwa da yayan yan uwansa wanda ba wani karatu me zurfi sukayi a wancan lokacin ba a sannu zamani yana canzawa sauye sauye suna zuwa a duniyar kasuwanci da akwai buƙatuwa ta mutane masu wata kwarewa ta musamman akan wasu al'amiran dole ya fara shigo da bare yana daukar Ma'aikata masu kwarewa ta musamman. Wannan ya zaburar da Binta, ta watsa yaranta zuwa ga fannonin da take da yaƙinin sune zasu riƙe manyan muƙamai a cikin Empire da Audu yake ginawa ta kuma cigaba da cusa masa su, ya zamana duk abinda zeyi ko kuma duk inda zashi tare dasu ne su su ukun nan Manyan su duniya ta sani a matsayin Magadan AUDU BECHI domin tun kafin Zakariyya ya gama makaranta Audu yake turashi ya wakilceshi a tarurrukan kuma a duk inda yaje ya kan gabatar da kansa ne a  matsayin Babban Ɗan Audu Bechi, Yakubu yayi iyakar yinsa gurin ganin Audu ya daidaita amma abin yaci tura dole ya saki ya kuma zubawa sarautar Allah idanu domin a yanzun karan Audun ya aki tsaiko, ya isa, sunansa ya fantsama ya zaga ko ina Burinsa na zamowa ɗaya daga cikin mutanen da duk idan aka ambaci sunansu a faɗin Najeriya babbba da Yaro Mace da Namiji ya sanshi Allah ya cika masa wannan buri nasa.

Ga dai zuri'a ta taru amma babu hadin kai, babu shaƙuwa babu jan juna a jiki balle jinƙai a tsakani kowa ya tashi ta kansa kawai yakeyi a gidan. Wadanda babu iyayensu sun girma cikin wani yanayi sannnan sun samu labarurruka na gaskiya dana ƙarya akan yanda zamantakewar Audun da kasancw da iyayensu, ita kanta Aisha da yanzu akw kira da Momy ba dadin zaman takeji ba.

Itama ta tafka kuskuren da se a yanzu ta gano qautar da tayi, tayi saken da yaranta suka tashi akan tarbiyyar sauran yaran gidan, babu jitiwa a tsakaninsu kowa sabgar gabansa kawai yakeyi wata irin bahaguwar rayuwa tamkar a garin gwarawa haka ake a gidan Audu babu babba babu ƙarami kowa Tantirin kansa ne, tsakaninta da Binta har yau dai se a hankali dukda dai shekaru sunja kuma Bintan ta watsar da harkar kishi domin ta harba musu makamin da yayi musu illah sama da Hayaniyar zaman kishi, ta tarwatsa musu gida ta cusa muguqar Aƙidar yan ubanci a zuciyoyin Yaran gidan koda yake baza'a kira abinda sukeyi da yan ubanci ba domin ciki dayan ma kowa tasa ta fishsheshi akeyi sedai idan sabga ta haɗo tsakanin ɗan wani ɗaki da wani ba sannan ne sukan nuna haɗin kai kowa ya goyi bayan ɗan uwansa har

kuwa Yayan Bintan dan abin yafi muni ma a tsakaninsu son kai da kyashi yayi tasiri a zukatansu.

Ahmad da Jafar su kadai suka fita daban. Su biyun sun zama tamkar zakka a cikin Ahalin Audu, halaye da ɗabi'unsu sun fita daban dana sauran. Allah ya haɗa jininsu suna bala'in ƙaunar junanau yanda suke mu'amala ba zaka taɓa ɗauka ba uwa daya ta haifesu ba, Binta tayi masifar tayi Bala'in har Malamai ta shiga akan ta raba Jafar da Ahmad amma abu yaci tura, Jafar din duk cikin yaranta tafi jinsa a cikin zuciyarta, tana da burika masu yawa akansa sedai tun fara tasowarsa ta fuskanci kwata kwata Alƙiblarsa daban da tata yanda kasan an canza mata shi a Asibiti idan badan kamanni da yakeyi da ita ba tsaf zata ce ba ɗanta bane.

Duk abinda Jafar zeyi seya shawarci Ahamd haka shima Ahmad ɗin, makwancinsu daya, a makaranta ajinsu daya hatta da kayan sawarsu basu banbantawa guri daya suke ajiyesu. Data rasa yanda zatayi domin tana so taja Jafar ta fara kitsa masa abubuwan da take so ya cimma tun da shekarun ƙuruciya amma abu yaci tura, Turai ce ta bata shawarar ta tura Jafar Makarantar kwana tunda Aisha bata ao bata taɓa tura Yaranta ba tasan bazata bar Ahmad yaje ba a haka zata janye Jafar sedai a banza domin tana tayar da maganar bata ma san anyi ba seda ranar tafiya tazo taga Ahmad ya shirya shima babu yanda ta iya ta barsu suka tafi akan zata sake shiri.

Daga sama Allah ya aiko mata da mafita, Jafar yana son kwallo tamkar ransa wanda ita kuma bata so domin tana gabin Kwallon na ɗauke masa hankali ta hanashi karatu Rana tsaka Babban Yayansu ya kirata akam ya samarwa Jafar gurbin karatu a Acadami ta Ƙungiyar Manchester dake Ƙasar Ingila ta sanarwa da Audu idan ya yarda a fara shiri. Da fari taƙi, tana gani za'a cuceta a cutar mata Ɗa ita da take da buri akansa acw ya tafi wata makarantar Ball, amma da Yayanta ya kwatanta mata irin Kuɗin da yan kwallo suke samu take ta amince ta kumayi murna ko banza ta samu hanyar raba Jafar da Ahmad.

Wannan tafiya ita ta raba Ahmad da Jafar, Ahmad baya bal  Jafar kuma baze iya barin burinsa ba dukda a farko yaso yayi tirjiya akan baze tafi na se sun kammala sakandire idan Yaso Yaya Ahmad kamar yanda yake kiransa ya nemi Jami'a a can su tafi tare amma Ahmad ɗin ya ƙarfafa masa guiwa akan ya tafi basu rabu ba suna tare, hakan ko akayi shekarunsu goma sha uku a lokacin Jafar ya koma Ingila tareda kawunsa ya zama se Ahmad kadai a Najeriya, burin Binta ya cika na rabasu saura kuma na aiwatar da shirinta akan Jafar din domin ba wai kwallon ta kwanta mata

bane har a rai Madarar kudin da Yayanta yace mata ana samu ne yasa harta yarda ta barshi ya tafin.

Rayuwa taci gaba da gurgurawa abubuwa da yawa sun faru na dadi da akasin haka, anyi rashe rashe yan uwan Audu gaba daya sun kwanta dama ya rage dashi da Yakubu se Bilki data dade da dawowa gidansa da zama tunda suka bar Goron Dutse suka koma Hotoro GRA inda ya tamfatsa gida Gari guda me sassa babu Adadi lokacin ne kuma ya ƙara aure ya auri Rabi'atu yar Malam Haladu Shugaban Maroƙa na wannan shiyya. Malam Haladun shiya tallatawa Ausu auran yarsa a lokacin Audun nada niyyar neman Aure domin yana ganin yaci ace ya ƙara mata dukda ya auri wata Fa'iza a can yawon Ƙasashen duniya suka haɗu da ita amma bata kai ga tarewa ba auran ya watse dalili yace sedai tazo gidansa ta zauna ita kuma tana ganin da uwar kuɗinta da gidanta sedai ya bita har an daura da taƙi tarewa ya sallameta iyalansa basu sani bama se bayan da auran ya mutu wannan tasa ganin Rabi'a tayi daidai da tsarinsa kuma yayi tambaya gun Malaminsa domin tuni shima ya zama dan hannu a sabgar Malamai baya abu da ka kamar yanda suke faɗi aka tabbatar masa Rabi'ar hadinsu yayi daidai shikenan ya Angwance abinsa.

Shekararta goma sha biyar kenan, da ace tana da zuciya koda yake ace iyayenta nada zuciya da tuni sun kashe Auran sun huta da gorin Binta. Bala'inta daya kwanta dama ta tattaro ta maido gaba daya ta ɗorawa Rabi'a, gorin safe daban na rana daban na dare daban yar matsiyata yar Maroƙa, tun ba data fara zuba Yaya tayi Namiji na fari daga nan hankalin Binta ya sake tashi, da tayi na biyu tagwaye mata se ta ɗan samu sassauci ana uku ma ta sakeyin Mace sannan ta dakata da haihuwar wannan yasa Binta data koma Hajiya a yanzu ta ɗan ɗaga mata ƙafa kadan daga kwarzabar da take mata ta sake mayar da hankali ga Audu da dukiyarsa da kuma yanda zasu gaje komai ita da Yaranta.

Babangida da Aminu su kadai suke aiki a ƙarƙashin Audu wanda suma sun shiga gurin ne bisa tursasawar Yakubu da ya zamewa Binta ciwon ido. Duk sanda wani ya mutu a gidansu Ausu se tace inama Yakubu ne ya mutu, ita dai ya tsare mata abubuwa da dama shi yake rage mata Tasiri yana kuma hanata rawar gaban hantsi. Sanda taso ta watsa duk wani Ahalin yan Bechi da yake aiki a ƙarƙashin Audu ta gama shirya yanda zatayi ta saka ya sallamesu Yakubun ne ya watsa mata shiri. Dukda haka bata saraya ba kuma a ƙalla taci riba domin tayi nasarar ɗora Yaranta a manyan kujeru na jan ragamar kamfanunuwan Audun.

Zakariyya shine Manaja na baki ɗayam BECHI GROUP OF COMPANIES, Naziru kuma shine Shugaban sashin Manfetur da sauran Albarkatunsa ɓangaren daya fi kowanne samar da kuɗin shiga, Aminu shi aka dora a matsayin Akanta kujerar data so ace Yakubunta ne akai amma hakan bata samu ba se a yanzu suke saka ran faruwar hakan.

A sauran Yaran gidan kuwa, Hassan ya zama Likita harta kai ga bude Asibiti na kansa wanda babu ƙwandakar Audu a ciki, be tambayeshi ba shima kuma beyi yakanar ya taimaka masa da wani abu ba yanda besan ya akayi yayi karatunsa harya kai wannan matsayin ba haka nan besan yanda yayi ginin Asibitinsa ba.

Babannan harkar Noma ya kama domin shi dakyar yayi dipiloma ya ajiye boko ya koma Bechi ya cigana da Noma gonar da suka Gada gurin Bara'atu kuma Allah ya saka masa Albarka abun musammanda Babangida shima bangaren Harkar Noman ya karanta shiyasa ma Yakubu ya dage seda aka naɗashi shugaban sashin harkar Noma shi yake taimakawa Babannan ɗin da dabarun Noman zamani da Iri masu kyau dan haka sosai yake samun Alkhairi a sabgar ya siyi gonaki da yawa yana ta Noma abinsa acan Bechi Yayi Aure yake zaune da Iyalansa.

Hussani shugaban masu taurin kai da kunne na gidan kenan, da fari yaso ya bi wata hanya ta daban, damuwa tasa yaƙi karatu ya fara bin Abokana banza yana shaye shaye, da Addu'a da Nasiha Zubaida data janye Yayanta da dabara ta samu kansa, be cigaba da Makarantar ba ya kama kasuwanci kuma yana da Nasibi kamar Audun sega harka ta buɗe masa dukda girma ya fara zuwa amma dai ba'a bar Yan bushe bushen duka ba shiyasa idan buyaginsa ta tashi babu me shiga sabgarsa a gidan dan ko Alhajin daidai yake dashi.

Aliyu ma dai Injiniyarin ya karanta yana kuma aiki a wani babban Kamfani a Legas shigarsa Kano ma shi se sa'i da lokaci, cigaban da suka samu ya zama duk cikinsu babu wanda ya lalace ko yake aikata wani abu na Ashsha ba ƙaramin cin zuciyar Binta yakeyi ba, taso ace nata ne kadai suka ci gaba a gidan, taso rayuwar sauran ta tagayya ta yanda zasu zamana babu mamora se abinda suka yaga suka basu amma hakan ma babu laifi yanzu rayuwar ta fara.

Yakubu ya zama Alƙali har seda ya kai ga zama Mataimakin Shugaban Alƙalan Najeriya kafin yayi Ritaya, rayuwar gidansa kishiyar rayuwar gidan Audu ce, Matarsa Ɗaya tilo har wayau Balaraba suna zaune cikin Amince da Yara Biyar data

haifa masa Mata uku duk sunyi Aure se Maza biyu suka rage,Audu ya fishi, kudi, yawan zuri'a da kuma suna a duniya domin sunan Audun ba iyakar Najeria kadai ya tsaya ba a yanzu yana cikin jerin manyan masu Kuɗi a Africa duk wanda ya kwana ya tashi ya san da zaman Mamallakin BECHI GROUP OF COMPANIES wato ALHAJI AUDU BECHI sedai shi kuma yayiwa Audun zarra a gurin samun NUTSUWA DA KWANCIYAR HANKALI TAREDA AHALI ME CIKE DA QAUNA DA KUMA SOYAYYA.

END OF BOOK 1